[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 WA ZAI FURTA??🤐
0️⃣1️⃣

*Gaba daya labarin tukuici ne ga Hajiya Rabi badawi ( maman Ibrahim ) Allah ya shirya Miki zuri'a ya Kara arziki Aunty Rabi tawa*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD MARUBUCIYAR ALJAZEERA DA DR. JUNAID.*

*FARKO*

*Federal University dutsinma*

Gudu-gudu, sauri-sauri take tafiya Babu abinda kirjinta keyi sai dukan tara-tara, dodazon mutanen dake chunkushe bakin gate wadanda security suka dakatar don bincike saboda Babu dalibin dake wucewa wurin sai ya gwada I D card, takaici da karuwar faduwar gaban suka Hana ta sukuni, sakamakon yaune ranar farko da zata Fara shiga aji a makarantar.

Tana cikiniyar wucewa taji an janyo hijabinta alamar an mayar da ita baya Shi Kuma ya wuce da sauri Yana faman daga ID card din nasa, ta bishi da kallo saurayi ne matashi dogo..... *Anwar! Anwar !!* Wani ya bi bayansa da gudu, dai dai ta nuna nata ID card din ta wuce Shi Kuma ya juyo don ganin Mai kiransa har lokacin bai tsaya daga saurin da yake faman yi ba.

Ta kalleshi sosai tare da samun tabbacin fuskar bazata taba guje mata ba, tayi guntun tsaki tabi wata hanya.

Da tambaya ta gano ajin, da Shi ta Fara tozali lokacin da ta kunno Kai, ta hade fuska gabas da yamma ya bita da kallo har ta zauna ....kallon ta yakeyi Yana karanta karancin shekarun ta yanda har ta shigo jami'a wannan yar ficiciyar diyar...... Ya Dan tabe baki, may be giyar kudi taja iyayenta mata jumping.....shigowar lecturer din yasa Shi watsar da zancen.

Sakamakon sune Yan alfarma list din karshe na admission yasa lectures duk sunyi nisa har wasu sun kusa karewa, da alama ajin ita kadaice musulma domin duk matan ajin arnaku ne babu Mai alamar ko gyale ko wace ka gani gashi hirtsi-hirtsi.

Yawancin su ko *zo in kashe ka* basa ji da hausa, a gurguje malamin ya raba script na test din da yayi, yace class rep. Ya raba ma kowa, layi-layi yake bi. Zuwa can malamin idon sa yakai gareta, ya tako zuwa inda take tare da Fara jefo mata tambayoyi.

Gaba daya hankalin Yan ajin ya dawo kanta ana jiran aji idan zata iya bada amsa da turancin kamar yanda yake magana wasu nata sumke dariya cikin su harda Anwar saboda kowa yasan yaran hausawa da kwabar turanci.

Ta Sha *mur* kawai yayi maganar duniya taki bashi amsa. Kowa mamaki yakeyi *Anwar* ya Kara binta da kallo duk miskilancin sa yau ga kakar sa ya samu. Hankalinta a kwance ko motsi takiyi haka malamin ya gaji ya kyaleta tare da Shan alwashin idan tasan wata ai Bata San wata ba. Dai dai lokacin da class rep ya gama raba takardun. Lecturer din ya ce Wanda baiga nashi ba ya fito, mutum biyu suka fita duk Mata sunfi mintuna shidda a tsaye kafin yace su kadai ne? Duk akayi shiru yayi ta maimaitawa Amma ba Wanda yayi magana, ya fiddo takardu uku yace *Hamza Yusuf* ya Kira sunan yafi sau goma Amma da alama baya ajin yace shine highest he scored 9/10 ya kalli biyun yace kune second highest kunci 8/10 ya Mika wa kowace takardar ta

da one thousand naira, yace class rep ya turo mishi *Hamza yusuf* office domin ya amshi kyautar sa da Kuma script din nasa.

Har ya kai bakin kofa ya juyo what is your name? Kanta a kasa sai da ta kusa da ita ta zungurota sannan ta dago har lokacin fuskarta a murtuk, da kyar ta iya bude baki tace *Bilkisu Abdullahi gada* ya kada Kai *Discuss the macro objectives of ERGP In Nigeria* you'll present it next week in front of everybody as your make up of this test.....ya na gama fadar haka ya fi ce abunsa, ta sunkuyar da Kai kawai tana rubuta question din a bayan littafin ta .......kowa ajin ita yake kallo ganin ba wani alamun damuwa a gareta .....Anwar ya kalli abokin sa yace waccen yarinyar gadararriya ce yayi murmushi ta kaika?.

Ganin an Fara mikewa yasa tayi zumbur ta Mike Babu inda tayi ma tsinke sai sit din Anwar Yana ta kokarin tattara takardu zai Mike ta tsaya kansa, agidan ku ba'a koya maka tarbiyyar daratta mace ba? Ta fada Kai tsaye gaba daya shock ya Kama Yan ajin masu niyyar fita duk suka dakata, da sauri ya kalleta..... Ta jefe Shi da wani mugun kallo na wulakanci kafin ta ce kawai don ka dauki mutane banzaye Ina tafiya zaka Kama mun hijab ka mayar dani baya .......ke! Ya daka mata tsawa tare da mikewa tsaye .....itama ta daka mishi tsawa, zaka dakenine marar tarbiyya? Tare da zaro mishi ido idan hannunka ya Kara gigin taba mun hijab wallahi duk Wanda ya tsaya maka a school din nan sai na ganshi mtseww....ta buga tsoki sannan ta nuna Shi do yatsa, ka kiyaye ni banzo Nan don inyi wasa ba kasa hakan a ranka ta watsar da takardun kasa ta koma ta zauna, wani uban tsalle yayi wallahi sai ya daketa aka rike Shi yana ta faman ihu kamar mahaukaci , ko ajikin Bilkisu taci gaba da rubutun ta kawai da kyar aka fitar dashi ajin.

Mutane sunfi ashirin bisa kansa suna bashi hakuri hada Yan aji uku da hudu akan kada ya biye Mata yarinya ce. Da kyar aka shawo kansa.

Ya fakaici idon kowa ya tafi amsar script dinsa domin baya so a gane Yana da kokari cewarshi Shi baizo don nuna shidin wani ne ba, yayi wa malamin karyar baya aji ne kawai.

Yana komawa hostel ya Fara karatun presentation din Bilkisu domin yi mata tambayoyi, ita kuwa da yake wani gida take na haya dakuna shidda ne a gidan kowa ne daki sai mutum hudu ko biyar su Kama Amma ita nata Bata Kama da kowa ba iyayenta ita kadai suka Kama wa daki daya sakamakon dakunan suna da tsada ko wane da kitchen da toilet akan dubu dari da ashirin 120k. Notes din da aka wuce ta tabi wadannan Yan matan biyu dasuka ci gift ta karbi nasu tayi photo copy ganin sune masu kokarin ajin. Karfe biyu suka koma wata lecture din Bata yarda ta makara ba, taki sakar ma kowa fuska saboda tana son sanin halin kowa don tasan dawa zatayi abota.

Karatun hauka Anwar keyi saboda Bilkisu ya gama tsanar yarinyar kamar yanda itama Bata kaunarsa, kullum tunanin sa yanda zai rama wulakancin da tayi mishi yayin da ita Sam ta shafe babin sa  ta manta da al'amarain shi daga masallaci sai daki tayi kwanciyar ta tana duba litattafai abinda ya shige mata Kuma sai tayi goggling.

Ranar presentation ta zagayo kasancewar ajin sunfi dari yasa malamin zuwa da microphone tana cikin tashin hankali da firgici Amma miskilancin Bilkisu yasa ba Wanda ke gane hakan. Abinda kawai ya kawo malamin shine don tayi presentation din kusan Shi da Anwar Abu daya suke sakawa a zuciya watan sai sun kunyatata.

Fuskar ta tamau ta Mike ta isa gaban Allon yayin da ya Miko mata abun maganar jikinta ya tsinke da kyarma anan ya fahimci hakan wurin amsar abin maganar yanda hannun ta ke

kakkarwa. Idanun ta suka kawo ruwa tayi saurin cewa *innalillahi wa'inna ilaihi raji'un. Ta tsaye tare da sunkuyar da Kai kasa ta Fara magana a hankali cikin taushin murya wacce ke cike da tashin hankali.......

My name is Bilkisu Abdullahi gada and I'm here to present the macro Economic objectives of Economic recovery and growth.......yanayin fitar turancin nata yasa ajin natsuwa tare da Kara zura mata ido lecturer din ya Goya hannuwa biyu kawai Yana kallonta Shima .....
Bayani take karantowa cikin natsuwa tana Kara lankwasa turancin nata cikin kalmomin kwarewa da birgewa hakan ya Kara tarwatsa zukatan kowa ciki harda Anwar ta share kusan mintuna hamsin tana magana har sai da malamin ya dakatar da ita Shi kansa jikinsa yayi sanyi.

Ta saki ajiyar zuciya a hankali har lokacin kansa na sunkuye ....ya kalli Yan class din *Any question*? Duk akayi tsit! Amma wasu idanun su Yana ga Anwar kallonta kawai yakeyi ya rasa ma mezai fassara tunanin sa. Malamin ya watsa hannu tunda ba tambaya ni ina da ita, ya jefa mata daya.....tayi jimmmmm kamar bazata iya amsawa ba kafin ta Dan motsa kadan ta Fara zakulo bayani, gaban ta yazo ya tsaya Yana kallonta har ta Gama, sannan tayi shiru.

Yafi mintuna shidda baiyi magana ba kafin ya kalli Yan class yace please will you help me give her a roundplus? Duka ajin yadau tafi.......raf raf raf abun mamaki ciki hada Anwar.....ya fiddo five thousand ya Mika mata congratulations you score 10/10 wallahi......ajin ya dauki ihu da sowa.... Ta danyi murmushi kadan kafin ta karba ta wuce abinta har lokacin jikinta na karkarawa.

Duk ajin ya rikice da hayaniya kowa na fadin albarkacin bakinsa, haka malamin ya fita kamar jira Anwar keyi ya Mike ya Isa wurin ta, congratulations sai a bamu ladar ganin ido......Ibrahim da sauran Yan aji kowa ya zaro ido domin kowa yasan Anwar da gadara, rainin saying da Kuma girman Kai.

Kowa na jiran abinda zatayi sai kawai ta dago tana Yar dariya ( domin Bilkisu Bata da riko ko kadan da anyi mata zata rama Kuma ya wuce har abada wurinta).
Ta tura mishi kudin to gashi ai ba nisa sukayi ba ta fada tana Kara Yar dariya, tadanji kunya matuka domin neman fada yazo, ya danyi murmushi kya turan kudi? Kiban kaso na kawai ko rabawa zamuyi? Ta Dan kalleshi kadan.......gabansa ya Fadi kwarai a karo na farko. To mu raba Mana ta fada tana maida kanta bisa littafi.... Okay ya Mika hannu bani nawa toh, ta nuna kudin da baki gasu nan ka dauki naka kabar mun nawa..

Yayi Yar dariya kafin yasa hannu ya dauki 2500 yabar mata 2500.

Amma Kuma ya kasa tafiya sai juya kudin yake da hannu Yana murmushi. Ta dago Kai ta juya mishi ido alamar tsayuwar ta mecece tunda ta sallameshi? Sai kawai ya bushe da dariya yace okay thanks. Ya fice class din abikansa da wasu Yan ajin suka bi bayansa, ta kwashi Yan takardunta tayi daki domin sai 2 zasu dawo wata. Yana tsaye duk an rufeshi ana mishi surutai sai dariya kawai yakeyi tazo ta raba ta wuce ya ringa satar kallon ta har ta kule.....

*****************

*KADUNA RIGASA*

Amira kiyi hakuri wannan auren da zanyi ki daukeshi amatsayin kaddara wallahi wallahi bazan taba wulakanta ki ba don girman Allah kiyi hakuri ki daina wannan kukan......baban Ahmad Dan Allah ka fita ka bani wuri wallahi ko ganin ka bana sonyi na tsaneka da dukkan wannan rayuwar.....ya zukunna na tuba na rantse Miki da Allah ba zanyi auren nan don in wulakanta ki

ba mu daukeshi matsayin kaddara Amira kiyi hakuri nasan ban kyauta Miki ba, ta Mike tsaye yaudarar maza wacece ban sani ba? Haka kuke cewa Amma wallahi ka zalunceni ka cuceni kaci amanar kauna.....kada kice haka na rantse da Allah har gobe Ina kaunar ki.....karya kakeyi baka kaunata da baka ga wata har ta birgeka kake kokarin kawo ta gidan nan ba. Shima mikewar yayi bacin Rai zaisa ki Fadi haka Amma Ni nasan wallahi ba haka bane Amira kiyi hakuri laifi ne na riga nayi na tuba Dan Allah kiyi hakuri.....mtsew ta wuce nabar maka dakin tunda Kai bazaka tafi ba. Tabar Shi Nan tsaye.

Ya dafe Kai kwalla suka zubo mishi Shi kansa yasan Yana kaunar Amira Kuma baida niyyar Kara aure, matsalar kanwar abokin sa ce yasan kaunar da yarinyar keyi mishi tun Yana saurayi da farko Yana ba yarinyar fuska ba tare da Yana tunanin zata iya like mishi haka ba, kowa yasan suna tare Yanzu idan yace bazai aure ta ba kamar yanda abokin nasa ya bukata lallai zasu Bata.

Ya zauna bisa gefen gado ya dafe Kai dole in lallaba Amira har ta sauko tabbas bazan yi auren Nan ba matukar Bata cikin kwanciyar hankali.

Ya kwashe kusan kwana biyar Yana faman lallashi kafin ya shawo kanta hakan yasa Shima ya Sami sukuni da kwanciyar hankali. Nan da Nan suka Fara hidimar aure shida ita . Ya dauketa suka tafi Kano hado lefe, ya zauna gefe yace to ki Fara zabar lesuka , tayi jimmmmm kamar zata ce dauko mun Yan dubu uku da dari biyar sai Kuma wata zuciyar ta kwabe ta da cewar kisa tsoron Allah ga wannan lamarin bazaki taba tozarta da wulakanta ba.

Ta Fara ma lesussukan kallo tana tambayar farashi har aka kawo na karshen masu kudin daga dari suka Fara, ta ce nawa za a Sanya ne? Yace yanda duk kike ganin ya Isa ni Dan kallo ne, ta dunga darzo manya manyan lesussuka tana warewa idan ta dauki red Shi sai ya dauki pink ko maroon, haka sukayi tayi har aka Gama da suturu aka koma kayan shafa da kalmomi.

Sun kashe kudi yafi miliyan uku sannan suka je gurun jakun Kuna da akwattai nan ma aka darje kusan set takwas ta daukar ma Amarya pink shi Kuma ya dauki sky blue.

Bata kawo komai cikin ranta ba, tana ta addu'o'i na Kara karfin guiywa kamar yanda mahaifiyarta ta Bata shawara.

Ita dashi aka Kai lefe, gidansu yayi wa Amarya sabon gini kusa da nata, sai dai yafi nata kyau nesa ba kusa ba saboda tsarin yabanbanta.

Sati daya saura bikin ta dawo gidansu da maraice ta tarar an fitar da kayanta duka anata fenti tayi tsaye turus, sai gashi ya fito daga gidan amaryar yace shigo kiga anyi wa Amarya jere Amira. Gabanta ya bada Ras! Da karfi ta daure tana yake tabi bayansa, na mutu.....kawai na mutu...abinda take nanatawa kenan cikin Rai ganin dukiyar da aka lafta gidan. Sai dai kwalla su cika idanunta tayi saurin mayarwa ganin yanda yake ta zakwadin nuna mata ko'ina. Jikinta yayi mugun sanyi ya kamota suka zauna babban falon Wanda suka Fara wucewa, Amira ya naga jikinki kamar yayi sanyi? Ta Dan kakaro murmushi ba komi tana faman sunkuyar da kai, yayi kasa da murya ki aminta Dani Amira tunda Kika kwantar da hankalinki tare da kwantar mun da nawa wallahi na Miki alkawarin bazan taba watsa Miki kasa a ido ba, yanda mutane suka zuba Ido suga wata baraka Basu gani ba Yanzu daga wurin ki ba wallahi bazan taba bari su gani ba. *Wannan gidan naki ne bana amarya ba* ita gashi can ana mata fenti kayanki gasu can ana sakawa mota za a Kai wa su *Umma* ( mamar ta ).

Tayi saurin dago Kai Amma suna hada Ido sai ta rushe da kuka.....ya rungumota kiyi hakuri na Miki laifi I knew!

Ita kanta Bata San ya sunan kukan da takeyi ba Yanzu. Amma Tasha almwashin zata Kara daurewa taba maradda kunya har sai taga iya gudun ruwansa though har yau ta kasa aminta da kalaman sa tana ganin kamar yaudara ce irin da mazan yau.

Ya sungumeta zuwa dakin da Basu shiga ba Nan taga ikon Allah duk yafi dakunan kyau da girma yafi ko'ina Jin kayan alatu sannan taga akwatunan da ya saya jere sky blue yace kema ga lefenki can. Kece shaida Babu abinda na banbanta sai kala.

Ahmad da Almustapha ma nasu na tafe gobe anmun waya sun zama ready.

Ta kankame Shi ta saki wani irin kukan Dadi.....kayi hakuri abinda na maka wallahi bazan taba watsa maka kasa a ido ba.....ya Kara rike ta nasan haka Amira kiyi hakuri.

Tuni labari yakai gidan su Amarya Nan da nan maganganu suka tashi wasu na cewa ta Gama dashi wasu na cewa tsoronta yakeyi surutai kala kala har Amarya takai ga ta harzuka.........😄😄 Turkashi a tsumayi diyar Aunty Rabi (mamn ibrahim) kada a manta a ringa Sanya mun ita cikin addu'a Allah ya Kara mata yawancin kwana ya shirya Mata zuri'a da rufin asiri.

Har Yanzu babana ma Yana bukatar addu'a Allah ya bashi lafiya yaba maman mu ladar jinya.

💞 Ni din dai ce Zainab Dahiru wowo maman Abdullah 😄😄💞

[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 WA ZAI FURTA??🤐

0️⃣2️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( maman Ibrahim) Allah ya shirya Miki zuri'a ya Kara arziki*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD KO DA YAUSHE*

*DOMIN KU AUREN FARI FANS ANA MUGUN TARE*

*Federal University dutsinma*

Semester tayi nisa komai yayi zafi har Yanzu Bilkisu bata Sami sakewa ba, karatun Yana mata mugun wahala, ahankali take bin su chinyere suna nuna mata abubuwa duk Wanda ta fahimci Yana da kokari zataje don Kara fahimtar abinda ya shige mata.

Su Anwar sune Yan baya ga komai, ya biye wa mashiririta yaki nuna ma kowa Shi din Mai kokari ne, masu karyar suna da kokari sai ya kwantar da kanshi Yana Jin yanda suke kwabar bayani musamman idan akazo gun lissafi.

Hankalin sa a kwance duk C.A din da akayi shine overall, Yana amsa sunan Anwar a zahiri ba Wanda yasan Shi da Hamza Yusuf a badini.

Fahimtar halin Bilkisu na rashin girman Kai yasa Shi suke gaisawa da ita sama-sama Yana son kulla mu'amula da ita Amma Yana ganin hakan a gareshi zai zubda mishi aji. Ita kuwa a gareta Sam bai ma gabanta ko kadan idan an hadu a gaisa idan ba a hadu ba Bata ko tunanin sa. Shine ma sau da yawa take Dan takura tunanin sa kadan kadan.

Ta Dan Fara sakewa da su chinyere saboda ta lura sune masu kokarin ajin, takan zauna tayi tunanin akwai department din da yakai Economics barin wuta duk makarantar? Sau da yawa tana tunanin Anya ba hausa ko Islamic zata koma ba?

Ta gama tsorata da makarantar musamman yanda taji ana bada carry over, probation da Kuma withdraw. Takan yi tunanin ai ita abun kunya ne gareta ta sami Koda carry over din ne ma

hakan yasa ta Kara dagewa tana Kara naci cikin karatun ta musamman da jarabawa ta karato kullum tana library ko Kuma tare da su chinyere tana Kara koyon karatu.

Saura kwana hudu su Fara jarabawa misalin karfe hudu na marece tana zaune wani class tana faman karatu yazo wucewa kunnensa like da air piece har ya gitta said yaga kamar ita, yayi jimmm Yana tunanin ita ce ko gizo idanun sa keyi Masa kamar kullum?

Kamar kada ya dawo sai Kuma dai ya koma don tabbatarwa .....ita din daice tana ta faman Mimi da baki ya kyalkyace da dariya lokacin daya kunna Kai ajin hankalinta naga littafi har yazo ya zauna kusa da ita....tayi firgigi cike da tsoro ko da taga shine bata San lokacin da ta balla mishi harara ba.....yayi murmushi afuwan matsoraciya duk wadannan mutanen meye zai kamaki da rana gatse gatse haka? Ya karasa maganar Yana janyo littafin ta gaban sa, meye kike karantawa ayi mun bayani.

Haushi ya turnuketa domin karatun ya Fara shigar ta sosai gashi yazo zai rikita ta, Tasha mur tare da janyo littafin Dan Allah karatu nake zaka rikitani ka tashi ka bani wuri.....bazaki koya mun ba?

Nima Yanzu ai nake karantawa ta fada cikin fada fada, yayi murmushi it's alright go ahead and read ya sunkuyar dakai kawai bisa desk din. Ta ci gaba da karatun ta ba tare da ta Kara bi ta kansa ba.

Idan ta karanta sai that bude can karshen littafin ta rubuta haka haka Yana ta lura da ita duk ta dage bakin Rai bakin fama Nan da nan ya gane hadda ce takeyi. Yana so ya mata bayani Amma ya rasa ta inda zai Fara......

Tana son kamshin turaren sa ainun Anwar Dan gayu ne matuka Yana daukar wanka gashi kyakkyawa. Kamar ta karanci zuciyar say ta Dan karkato Dan Alalh wannan kalmar me take nufi? Ta sungo mishi littafin a gaban sa. Daman tun zaman sa kusa da ita ya kashe music din hakanan wayar ke jikin kunnen sa.........yayi kamar baiji me tace ba har sai da ta kalleshi sannan ya Dan zare wayar daga kunne Shi ala dole baiji me tace ba ya dan kalleta Shima kina magana ne?

Cewa nayi me wannan kalmar ke nufi? Ta nuna mishi da yatsa ....yabi hannun nata da kallo Yana kallon Zara zaran yatsun ta ya ce bari muji sentence din, Ya fada mata ma'anar kafin yace kin gane course din nan ne? Ta Dan bata rai to gashi dai Ina karantawa...... Ya Kara janyo littafin gaban sa ya budo shafin farko...... Kin San fa abun duk labari ne Kinga.......ya Fara mata bayani a hankali ahankali Nan da nan ta Fara fahimta sosai saboda bayanin nasa duk da hausa yake mata. Haka haka har ya gama mata littafin. Taji dadi sosai da sosai ta fadada fara'ar ta ohhhhh Ashe ka Gama covering komai ko???.......a'a fa nima kawai na gane darasin ne lokacin da yake bayani a class.....Amma wallahi ka iya bayani saboda har kafi malamin ma iyawa....ya danyi dariya tinda na Miki bayani da hausa ko? Ta kyalkyace da dariya yabi fuskar ta ta Yana Kara kallo ta bude jakar ta to Dan Allah ka gane wannan math din? Ta fiddo littafin. Dariya kawai yake cikin Rai Amma a zahiri yadan basar.......ya kalli littafin, gaskiya ban iya Shi ba Amma ki bari yau sanje dakin wani dan aji hudu ya koya mun gobe sai mu hadu in nuna Miki......da karfe nawa? Ta katse shi, Yayi murmushi duk lokacin da kike so goben....... 8:00am Zan jiraka anan.

Ya zaro ido 8? Gaskiya sai dai 4 saboda barci bazai barni na fito da wuri ba.

Kamar zatayi magana sai Kuma ta fasa ta ce Allah ya kaimu lafiya tare da janye littafin yabi Dan karamin bakin ta da kallo har ta sunkuya.

Ta Mike tana kokarin sagala jaka ta kalleshi tana murmushi Dan Allah ka koya da kyau Zan jiraka anan din goben in shaa Allah.
Yace ba damuwa.....see you then. Ta wuce.
Yabi ta da kallo kamar ya rufa mata baya amma Shi kansa yasan bazai iya hakan ba ( saboda gadara ).
Zuciyarta Fara fes! Ta isa daki taji dadin bayanin Anwar matuka.
Washe gari tana fitowa masallaci ta wuce class din kamar yanda sukayi alkawari, ta fiddo wani course theory ta Fara karantawa kafin ya iso. Ta nayi tana Dan kallon taga tare da duba agogon wayarta har kusan hudu da arba'in.
*Anwar* kuwa Yana can Yana shakar barci abinsa sammm ya manta da maganar su.
Allah ya taimaketa kawai sai ga su chinyere sun shigo karatu Suma Kuma cikin sa'a statistics din zasuyi solving sai kawai tayi joining suka Fara.
Tana yi tana tunanin watakila Anwar bai iya bane Yana Jin kunyar zuwa....ta tabe baki to meye na karyar zaije ya koya bayan yasan bashi da wani kokari....mtsew taja guntun tsoki.
Bai farka ba sai shidda saura ya tashi a hargitse ga takaicin lokacin sallah ya shige ga Kuma tunanin sabawa Bilkisu alkawari da yayi.
A gurguje ya watsa ruwa yayi sallah ya fito da sauri.
Ya shawo kwana ita Kuma ta fito ajin zata tafi. Tana hango Shi tayi sauri bi ta dayan side din tabayan azuzuwa tayi hanyar fita gate sauri sauri.....tana tunanin watakila Yana can Yana faman koyo don yazo ya birgeta..tayi tsoki to karya tame ne?
A hargitse ya shiga ajin sai wurge wurgen ido yakeyi girman Kai da nuna Isa sun Hana ya tambayi su chinyere ko sun ganta. Rai bace ya fita Nan ya Fara bin azuzuwa neman ta.
Helen ta tabe baki I don't like this Anwar honestly.... Mtsew don't mind idiot abeg inji chinyere Nan gulma ta tashi.
Ya cika girman Kai da nuna Shi wani ne, baya yi ma kowa magana sai abokansa uku. Surutai kala kala saboda Shi din Daman baida farin jini a class din tun zuwansu Wai ya cika fadin Rai da gadara.
Tunda ga ranar bai Kara Sanya Bilkisu a ido ba yayi neman har ya gaji gashi baida no. Ta bai Kuma San Wanda zai tambaya ya bashi ba haka Kuma baisan accommodation dinta ba hostel take ko off campus. Wasa wasa abun ya Dan dameshi.
Ranar da zasu Fara jarabawa da yake ta karfe uku ce tun biyu saura yake hall din Yana so ya ganta, ita kuwa tun 8 tana library sai biyu da Rabi ta fito bayan tayo sallah. Kansa sunkuye baiga shigowar taba har ta zauna bayansa.
Lallai Anwar ka kyauta shine ka shanya ni rannan ko? To kayi dai dai ta fada tana faman hararar sa .
Da sauri ya dago Kai zaiyi magana kenan invigilators suka shigo tare da fadin everybody out..ta rigashi fita, ko da aka Fara shiga ma tayi saurin fadawa don Zama gaba gaba.
Alhamdulillah jarabawar ta mata dadi ainun domin duk abinda ta karanta suka fito.
Ita ce ta biyar din bayarwa ( submitting ) bata jira kowa ba tayi masallaci don gabatar da la'asar saboda lokacin biyar da kusan ashirin.
G
Haka semester din ta kare ba tare da sun Kara haduwa da Anwar ba, ko kadan Bata yarda su hadu tasan karya zai shirga mata don kare kansa.

Shi Dan garin Kano ne ita Kuma Abuja mahaifinta ke aiki Amma asalin su Yan katsina ne.

Washegarin da suka Gama jarabawa tabar garin Anwar kuwa karfe biyar na ranar yabar dutsinma.

Hutun baida tsawo sati biyu akayi aka dawo. Sun dawo da sati daya aka saki result a *portal* Murna tsalle ga Bilkisu saboda ta cinye ko wane Bata da carry over ko daya ga point dinta 4.33

Hakan ba karamin dadi yayiwa Yan gidan su da iyayenta ba.

Anwar kuwa 5:00 dai dai ya samu saboda duka courses din da sukayi goma Sha daya ko wane *A* yaci. Yaja bakin sa ya tsuke.

A cikin ajin kowa nata fadin result din sa daga Mai 4 point sai masu 3 point da abubuwa. Duk Wanda ya tambayi Bilkisu sai ta ce lafiya Lau ne ni Daman carry over ke bani so to ban samu ba. Bata yarda ta fada ma kowa result dinta ba. Tana zaune an gama lecture din wani mugun malami ta kura ma dan rubutun da tayi ido tana nazarin ya zata ci jarabawa da Dan wannan rubutun? Suleiman ya mata sallama.

Suleiman matashi ne Shima a cikin ajin Mai natsuwa da son addini babancin say da Anwar yafi Anwar saukin Kai da yarinta. Ya zauna kusa da ita bayan ta amsa sallamar Dan Allah Hajiya Bilkisu na kasa bude portal dina ya akeyi ne?

Tayi murmushi Ina wayar taka in nuna maka?

Wallahi daki na barta ki nuna mun da taki.......hankalin Anwar na kansu haka kawai sai yaji ya tsani Suleiman karon farko a rayuwar sa.

Ta fiddo wayar tare da tambayar sa password da matric number.

Portal din na budewa ta Mika mishi wayar kaga inda zaka Danna..... Ya danyi dariya to bude Mana ai ba komai don kin gani. Ta kalleshi tana mamaki saboda tasan Portal sirrin dalibi ne ba kowa kake yarda ka nuna mawa ba. Ya Kara Yar dariya ki bude ba komi. Ki gane mun Ina da carry over?

Ta ce to a sanyaye tana mamakin irin warda da yayi mata farat daya zuciyar ta cike da Jin dadi tare da ganin kimar say da mutunci.

Kaiiii....ta fada tare da zaro ido ka Fadi accounting. Sai kawai yayi murmushi nasan za'a rina sai wane? Ka  Fadi GST English  Shikenan. Nawa ne point dina? Ta duba can kasa tana warware ido..... Okay gashi Nan 2.65. Ta kalleshi, amma Suleiman me yasa ka yarda dani haka?......Au kin San sunana kenan? Ya fada Yana kallonta cike da mamaki, tayi murmushi eh Mana nasan sunan ka Suleiman.

Ina fatan ke dai lafiya lau ko? Sai kawai ta budo mishi portal din ta tace kaga nawa.

Ya zaro ido kaiiiiiii...... Ta danyi murmushi Amma bana son Dan Allah ka fadawa kowa result dina.

Ya Jin jina Kai in shaa Allah Zaki sameni Mai rike sirrin ki, amma Bilkisu kinyi wuta da yawa fa!

Ta yi Yar dariya kawai.

Allah yasa albarka. Kiban no. Ki dan Allah ko da wani Abu Yana tasowa Kuma idan bazaki damu ba Zan ringa matsowa kina tasar Dani inda ban ganewa.

Ba matsala ga number rubuta........

A harzuke Anwar yabar class din tunda ga ranar sai kawai yayi baya da ita ko gaisuwa baya son suyi  cikin kankanin lokaci ta Saba da Suleiman ta fahimci Yana da saukin Kai bashi da girman Kai sannan Yana da addini tare da daratta mutane.

Ko da ya gane Bilkisu nada kokari sai ya like mata ko C.A zasuyi Yana manne kusa da ita

baya yarda tayi mishi nisa.
Ko kadan Bata da mugunta duk amsar da ta kakare mishi zata bashi ya kwashe tsaf!.
Akwai wani course Mai matukar wahala gashi three credit unit ne Kuma calculation Mai rikitarwa kowa Yana Jin course din. Anwar yayi burus da ita Yana Jin kowa na kokawa Amma ya ki nuna ya iya. Kwana takeyi karatu da salloli, Ranar jarabawar course din ana ta jera layi kawai malamin yace ta zauna can, hankalin ta ya tashi ganin ya cillata gaba don yau baya take son Zama saboda ta Sami taimakon wani.
Tana Zama sai taga Anwar ne a gaban ta, ita dai kawai sai addu'a takeyi tasan yau sai Allah da malaman gari. Tambayoyi bakwai be a amsa biyar tambaya ta farko dole ce gata da 'ya'ya har goma.
Saura kadan ta kurma ihu saboda duka tambayoyin guda daya ne kawai ta sani itama theory ne ba calculation ba.
Idanun ta suka kawo ruwa, taga tunda Anwar ya duke bai dago ba, hall din yayi tsit! Ta yi zugummm, zuwa can kawai ta Fara amsa wacce ta sani.
Mafi yawancin malaman dake tsaron nasu duk sun maida hankali wurin Yan baya. Haka ta dunga rubutu Dan Allah yasa ta Sami Koda *E* ne a course din ta wuce wurin.
Tana gamawa tayi zugummm kawai tana  fargaba.
Yadan waigo kadan ganin malaman basa kusa yace kin iya question one naga tana da wahala fa.
Tayi kasa da murya wallahi question 4 kadai na iya cikin bakwai din nan ga Shi ta farkon naga 30marks ne.
Ya dan gyara zaman sa kadan tare da kango mata booklet din sa yace kiyi sauri ki kwasa.
Habaaaaa.....ga bilkiyda saurin rubutu gata very smart. Duba daya sai ta kwaso layi biyu. Cikin sauri ta gama shafin tace juya....Shi kansa yayi mamaki yace ke duba da kyaufa kada kiyi shirme. Wallahi na gama ka juya kawai.
Haka ya bata dukan sauran question hudun da bata iya ba.
Sai da ya tabbatar ta Gama tsaf sannan yaci gaba da amsa Shima question 4 din da tace tayi.
Ta Dan waiga ta hango Suleiman can baya an cillashi sai zare ido yakeyi.
Duk Wanda ka kallo zakaga ko Yana zufa ko Yana ta raba ido.
Kije kiyi submitting...ya fada kasa kasa ta ce toh.
Kowa sai kallonta yakeyi Yana mamakin yanda zata bayar da wuri haka, Wasu na tunanin kawai ta gaji ne da zama kamar yanda Suma suke zaune, tafi mintuna talatin kafin wasu tsirara suka Fara fitowa duk Wanda ya fito idanu jawur ana tsinar malamin kusan kowa ya sadakas da kawai faduwa zaiyi course din saboda rashin iya amsawa. Suleiman kawai take jira ya fito sai kuwa gashi Yana ganinta yace, Bilkisuuu..... Yau naji wuta wallahi Allah dai ya kyauta Amma question biyu kawai nake da tabbaci cikin sauran.
Tabbb....wallahi ni Allah ya taimakeni Anwar ya bani duka Wanda ban sani ba....hada question one?
Eh Mana.
Wai da gaske kike?
Wallahi kuwa.
To Ina Jin keda shine kawai kuka amsa ta don ko su chinyere gasu can suna cewa Basu gane ba.......Allah dai ya kyauta ta fada tare da cewa sai gobe ta ruga hango Anwar yayi hanyar

*Gate* Yana ta faman sauri.
Anwar.. ta kwada mishi Kira, yasan za a rina Shi yasa yaso ma kada su hadu.
Ya Dan tsaya Yana murmushi , ya jarabawar Bilkisu ya fada Yana latsa waya.
Hmmm jarabawa yau Allah ya rufa man asiri bacin Kai ai Dana shiga uku. Na gode na gode Allah ya Kara ilimi......Daman ka iya course din sosai haka? Naga yanda ake ta kuka dashi Kai komai ka amsa.....hatta jamilu ma naga naka yake kwafa ( copying ).
Murmushi kawai yayi yace ba damuwa.
Ya wuce kawai. Ta bishi da ido. Anwar...ta Kara kwada mishi Kira.....ya juyo wallahi na gode kaji?
Sai kawai ya kyalkyace da dariya ya juya abinsa.
Taji dadi sosai da sosai a Ranar domin course din kadai kowa ke kuka dashi wannan semester din.
Hutun ya kasance dogo akalle ankwashe watanni biyu a gida kafin a dawo aji biyu.( Su Bilkisu an Fara manyanta ) wannan karon suna gida result ya fita inda take da 4.22 ta Dan sauko kadan saboda ansha wahala matuka Shi Kuma Suleiman Yana da 2.72 Amma ya Sami carry over daya.
Sun koma da makaranta da sati biyu akayi *convocation* tare da bayar da kyaututta ga first class da over all.
Bata halarci wurin ba. Saboda ba kowa ya maida hankali ga taron ba. Hakan yasa Anwar zuwa tare da karbar five pointer award da Kuma overall student na aji daya da suka gama.
Kamar munafuki ya karba sim sim sim yayi saurin barin hall din ganin babu alamun Yan ajin su ko wani Wanda ya sanshi. Ashe Suleiman yana wurin.
Ba karamin mamaki yayi ba watan Anwar shine *Hamza Yusuf* din da ake nema cikin class Amma wallahi sai ya fadawa Bilkisu.................
*************
*KADUNA RIGASA*
Yana ta mamakin yanda ummi ta mishi text tana son ganin sa alhalin bata taba hakan ba.
Yana zaune babban falon gidan nasu an cika gaban sa da kayan ciye ciye da lemuka kamar kullum ta shigo tana ta faman Bata rai .
Ya kalleta tana ta faman karairaye karairaye......Amarya bakya laifi ko kin kashe Ahmad ( Babban yaron sa ) ya fada cikin zolaya Yana Yar dariya hannun sa rike da samosa mutumen shi Yana ci.
Banga alama ba, ta fada tana taunar cingam.
Ya kalleta jin maganar ta fito gatsal....
Kamar Yaya?, Ya bukata.
Kamar yanda kaji.
Kamar yanda naji?
Ya maimaita cike da mamaki kafin ya ajiye guntun samosan bisa plate ya tattara hankalin sa duka wurin ta.....me ke faruwa ne ummi?
Tayi shiru!
Dake nake magana...me ya faru?
Ta gyara Zama, Ina ce apartment din da kayi sabo Ni ka gina mawa Amma labari yazo cewa Aunty Amira ta koma....... Ke ya daka mata tsawa.

Nan da nan ya harzuka, Ni na fada Miki Ina Miki gini?
Gabanta ya fadi tayi tsuru tsuru, kinji? Munyi dake Ina Miki gini?
Okay ita da Zaki aure Mata miji Bata kawo mun matsala ba sai kece Zaki fara kawo mun tsirfa? Saurara da kyau ya Mike tsaye Yana nuna ta yatsa wallahi matukar kina son Zama dani tare da Jin dadi sai kin daratta Amira kin mun biyayya kin Mata bazan dauki sakarci ko kadan ba.
Dukkan ku Ina sonku to dole kowace tabi ra'ayi na, idan Kika saki na gane kina da matsala to wallahi zakiji ba dadi.
Mtsew ya buga tsaki ya wuce.......ta yi zuruuuuu tana zare ido lallai ta gwada Bata ji dadi ba.
Kwallah suka zubo Mata. Ta buga ma babbar yayar su waya domin ita ce abokiyar shawarar ta .....salati ta kamayi ubanwa ya aike ki? Ai kinyi sauri bari zakiyi sai kinje gidan yasan dadin ki lokacin yazo hannu tukun Amma Yanzu ai lallaba matar sa yakeyi tunda ya Mata laifi.
Ki bari Zan baki ahawarwari idan na shigo gobe.
Tun daga ranar Bata Kara Sanya Shi a ido ba. Tuni a Mata hudubar kada ta saki ta dauki raini ga matar sa Kuma idan ta a gidan ta Sami damar juya Shi yanda zata amshe ragamar komai.
Babu yanda ba a yi dashi ba ko kamu ayi yace bai son bidi'a ba Dan komai ba kada ma akirkiri partyn Amira taji ba dadi.
Ranar walima akayi mashi Sha Tara ta arziki hada mota.
Yana falon sa zaune yaji marokiya na sanarwa. Shima ya Mike ya kirawo marokiyar ya bada makullin mota kirar  *GLK* baka 2019 model ta kusan miliyan Tara yace yaba Amira ayi sanarwa.
Nan dangin Amarya kuwa suka Fara surutai............
Ko ajikin sa. Dangin ango dana Amirai kuwa suka Fara rangada guda suna tayata Murna.
Hakan ba karamin harzuka Amarya da danginta yayi ba. Nan suka Kara hure Mata kunnen wallahi sai ta tashi tsaye Dan kwato ma kanta yanci.
Kuka takeyi wuiwui.
Kafin karfe shida gida ba kowa duk an tafi.
Ana gama sallar isha'i ya ja Amarya zuwa sashen Amira don yi masu huduba.......

*Ayi hakuri da typing error please yanayin typing din ne saboda kawai ta WhatsApp nake yi Kuma gaskiya bana bi idan na Gama kawai nake turawa.
*Daga zainab wowo*💞💕💗😄✍🏼🤐 WA ZAI FURTA??🤐
02

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( maman Ibrahim) Allah ya shirya Miki zuri'a ya Kara arziki*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD KO DA YAUSHE*

*DOMIN KU AUREN FARI FANS ANA MUGUN TARE*

*Federal University dutsinma*
Semester tayi nisa komai yayi zafi har Yanzu Bilkisu bata Sami sakewa ba, karatun Yana mata mugun wahala, ahankali take bin su chinyere suna nuna mata abubuwa duk Wanda ta fahimci Yana da kokari zataje don Kara fahimtar abinda ya shige mata.

Su Anwar sune Yan baya ga komai, ya biye wa mashiririta yaki nuna ma kowa Shi din Mai kokari ne, masu karyar suna da kokari sai ya kwantar da kanshi Yana Jin yanda suke kwabar bayani musamman idan akazo gun lissafi.

Hankalin sa a kwance duk C.A din da akayi shine overall, Yana amsa sunan Anwar a zahiri ba Wanda yasan Shi da Hamza Yusuf a badini.

Fahimtar halin Bilkisu na rashin girman Kai yasa Shi suke gaisawa da ita sama-sama Yana son kulla mu'amula da ita Amma Yana ganin hakan a gareshi zai zubda mishi aji. Ita kuwa a gareta Sam bai ma gabanta ko kadan idan an hadu a gaisa idan ba a hadu ba Bata ko tunanin sa. Shine ma sau da yawa take Dan takura tunanin sa kadan kadan.

Ta Dan Fara sakewa da su chinyere saboda ta lura sune masu kokarin ajin, takan zauna tayi tunanin akwai department din da yakai Economics barin wuta duk makarantar? Sau da yawa tana tunanin Anya ba hausa ko Islamic zata koma ba?

Ta gama tsorata da makarantar musamman yanda taji ana bada carry over, probation da Kuma withdraw. Takan yi tunanin ai ita abun kunya ne gareta ta sami Koda carry over din ne ma hakan yasa ta Kara dagewa tana Kara naci cikin karatun ta musamman da jarabawa ta karato kullum tana library ko Kuma tare da su chinyere tana Kara koyon karatu.

Saura kwana hudu su Fara jarabawa misalin karfe hudu na marece tana zaune wani class tana faman karatu yazo wucewa kunnensa like da air piece har ya gitta said yaga kamar ita, yayi jimmm Yana tunanin ita ce ko gizo idanun sa keyi Masa kamar kullum?

Kamar kada ya dawo sai Kuma dai ya koma don tabbatarwa .....ita din daice tana ta faman Mimi da baki ya kyalkyace da dariya lokacin daya kunna Kai ajin hankalinta naga littafi har yazo ya zauna kusa da ita....tayi firgigi cike da tsoro ko da taga shine bata San lokacin da ta balla mishi harara ba.....yayi murmushi afuwan matsoraciya duk wadannan mutanen meye zai kamaki da rana gatse gatse haka? Ya karasa maganar Yana janyo littafin ta gaban sa, meye kike karantawa ayi mun bayani.

Haushi ya turnuketa domin karatun ya Fara shigar ta sosai gashi yazo zai rikita ta, Tasha mur tare da janyo littafin Dan Allah karatu nake zaka rikitani ka tashi ka bani wuri.....bazaki koya mun ba?

Nima Yanzu ai nake karantawa ta fada cikin fada fada, yayi murmushi it's alright go ahead and read ya sunkuyar dakai kawai bisa desk din. Ta ci gaba da karatun ta ba tare da ta Kara bi ta kansa ba.

Idan ta karanta sai that bude can karshen littafin ta rubuta haka haka Yana ta lura da ita duk ta dage bakin Rai bakin fama Nan da nan ya gane hadda ce takeyi. Yana so ya mata bayani Amma ya rasa ta inda zai Fara......

Tana son kamshin turaren sa ainun Anwar Dan gayu ne matuka Yana daukar wanka gashi kyakkyawa. Kamar ta karanci zuciyar say ta Dan karkato Dan Alalh wannan kalmar me take nufi? Ta sungo mishi littafin a gaban sa. Daman tun zaman sa kusa da ita ya kashe music din hakanan wayar ke jikin kunnen sa.........yayi kamar baiji me tace ba har sai da ta kalleshi sannan ya Dan zare wayar daga kunne Shi ala dole baiji me tace ba ya dan kalleta Shima kina magana ne?

Cewa nayi me wannan kalmar ke nufi? Ta nuna mishi da yatsa ....yabi hannun nata da kallo Yana kallon Zara zaran yatsun ta ya ce bari muji sentence din, Ya fada mata ma'anar kafin yace kin gane course din nan ne? Ta Dan bata rai to gashi dai Ina karantawa...... Ya Kara janyo

littafin gaban sa ya budo shafin farko...... Kin San fa abun duk labari ne Kinga.......ya Fara mata bayani a hankali ahankali Nan da nan ta Fara fahimta sosai saboda bayanin nasa duk da hausa yake mata. Haka haka har ya gama mata littafin. Taji dadi sosai da sosai ta fadada fara'ar ta ohhhhh Ashe ka Gama covering komai ko???.......a'a fa nima kawai na gane darasin ne lokacin da yake bayani a class.....Amma wallahi ka iya bayani saboda har kafi malamin ma iyawa....ya danyi dariya tinda na Miki bayani da hausa ko? Ta kyalkyace da dariya yabi fuskar ta ta Yana Kara kallo ta bude jakar ta to Dan Allah ka gane wannan math din? Ta fiddo littafin. Dariya kawai yake cikin Rai Amma a zahiri yadan basar.......ya kalli littafin, gaskiya ban iya Shi ba Amma ki bari yau sanje dakin wani dan aji hudu ya koya mun gobe sai mu hadu in nuna Miki......da karfe nawa? Ta katse shi, Yayi murmushi duk lokacin da kike so goben....... 8:00am Zan jiraka anan.

Ya zaro ido 8? Gaskiya sai dai 4 saboda barci bazai barni na fito da wuri ba.

Kamar zatayi magana sai Kuma ta fasa ta ce Allah ya kaimu lafiya tare da janye littafin yabi Dan karamin bakin ta da kallo har ta sunkuya.

Ta Mike tana kokarin sagala jaka ta kalleshi tana murmushi Dan Allah ka koya da kyau Zan jiraka anan din goben in shaa Allah.

Yace ba damuwa.....see you then. Ta wuce.

Yabi ta da kallo kamar ya rufa mata baya amma Shi kansa yasan bazai iya hakan ba ( saboda gadara ).

Zuciyarta Fara fes! Ta isa daki taji dadin bayanin Anwar matuka.

Washe gari tana fitowa masallaci ta wuce class din kamar yanda sukayi alkawari,  ta fiddo wani course theory ta Fara karantawa kafin ya iso. Ta nayi tana Dan kallon taga tare da duba agogon wayarta har kusan hudu da arba'in.

*Anwar* kuwa Yana can Yana shakar barci abinsa sammm ya manta da maganar su.

Allah ya taimaketa kawai sai ga su chinyere sun shigo karatu Suma Kuma cikin sa'a statistics din zasuyi solving sai kawai tayi joining suka Fara.

Tana yi tana tunanin watakila Anwar bai iya bane Yana Jin kunyar zuwa....ta tabe baki to meye na karyar zaije ya koya bayan yasan bashi da wani kokari....mtsew taja guntun tsoki.

Bai farka ba sai shidda saura ya tashi a hargitse ga takaicin lokacin sallah ya shige ga Kuma tunanin sabawa Bilkisu alkawari da yayi.

A gurguje ya watsa ruwa yayi sallah ya fito da sauri.

Ya shawo kwana ita Kuma ta fito ajin zata tafi. Tana hango Shi tayi sauri bi ta dayan side din tabayan azuzuwa tayi hanyar fita gate sauri sauri.....tana tunanin watakila Yana can Yana faman koyo don yazo ya birgeta..tayi tsoki to karya tame ne?

A hargitse ya shiga ajin sai wurge wurgen ido yakeyi girman Kai da nuna Isa sun Hana ya tambayi su chinyere ko sun ganta. Rai bace ya fita Nan ya Fara bin azuzuwa neman ta.

Helen ta tabe baki I don't like this Anwar honestly.... Mtsew don't mind idiot abeg inji chinyere Nan gulma ta tashi.

Ya cika girman Kai da nuna Shi wani ne, baya yi ma kowa magana sai abokansa uku. Surutai kala kala saboda Shi din Daman baida farin jini a class din tun zuwansu Wai ya cika fadin Rai da gadara.

Tunda ga ranar bai Kara Sanya Bilkisu a ido ba yayi neman har ya gaji gashi baida no. Ta bai Kuma San Wanda zai tambaya ya bashi ba haka Kuma baisan accommodation dinta ba hostel

take ko off campus. Wasa wasa abun ya Dan dameshi.

Ranar da zasu Fara jarabawa da yake ta karfe uku ce tun biyu saura yake hall din Yana so ya ganta, ita kuwa tun 8 tana library sai biyu da Rabi ta fito bayan tayo sallah. Kansa sunkuye baiga shigowar taba har ta zauna bayansa.

Lallai Anwar ka kyauta shine ka shanya ni rannan ko? To kayi dai dai ta fada tana faman hararar sa .

Da sauri ya dago Kai zaiyi magana kenan invigilators suka shigo tare da fadin everybody out..ta rigashi fita, ko da aka Fara shiga ma tayi saurin fadawa don Zama gaba gaba.

Alhamdulillah jarabawar ta mata dadi ainun domin duk abinda ta karanta suka fito.

Ita ce ta biyar din bayarwa ( submitting ) bata jira kowa ba tayi masallaci don gabatar da la'asar saboda lokacin biyar da kusan ashirin.

G

Haka semester din ta kare ba tare da sun Kara haduwa da Anwar ba, ko kadan Bata yarda su hadu tasan karya zai shirga mata don kare kansa.

Shi Dan garin Kano ne ita Kuma Abuja mahaifinta ke aiki Amma asalin su Yan katsina ne.

Washegarin da suka Gama jarabawa tabar garin Anwar kuwa karfe biyar na ranar yabar dutsinma.

Hutun baida tsawo sati biyu akayi aka dawo. Sun dawo da sati daya aka saki result a *portal* Murna tsalle ga Bilkisu saboda ta cinye ko wane Bata da carry over ko daya ga point dinta 4.33

Hakan ba karamin dadi yayiwa Yan gidan su da iyayenta ba.

Anwar kuwa 5:00 dai dai ya samu saboda duka courses din da sukayi goma Sha daya ko wane *A* yaci. Yaja bakin sa ya tsuke.

A cikin ajin kowa nata fadin result din sa daga Mai 4 point sai masu 3 point da abubuwa. Duk Wanda ya tambayi Bilkisu sai ta ce lafiya Lau ne ni Daman carry over ke bani so to ban samu ba. Bata yarda ta fada ma kowa result dinta ba. Tana zaune an gama lecture din wani mugun malami ta kura ma dan rubutun da tayi ido tana nazarin ya zata ci jarabawa da Dan wannan rubutun? Suleiman ya mata sallama.

Suleiman matashi ne Shima a cikin ajin Mai natsuwa da son addini babancin say da Anwar yafi Anwar saukin Kai da yarinta. Ya zauna kusa da ita bayan ta amsa sallamar Dan Allah Hajiya Bilkisu na kasa bude portal dina ya akeyi ne?

Tayi murmushi Ina wayar taka in nuna maka?

Wallahi daki na barta ki nuna mun da taki.......hankalin Anwar na kansu haka kawai sai yaji ya tsani Suleiman karon farko a rayuwar sa.

Ta fiddo wayar tare da tambayar sa password da matric number.

Portal din na budewa ta Mika mishi wayar kaga inda zaka Danna..... Ya danyi dariya to bude Mana ai ba komai don kin gani. Ta kalleshi tana mamaki saboda tasan Portal sirrin dalibi ne ba kowa kake yarda ka nuna mawa ba. Ya Kara Yar dariya ki bude ba komi. Ki gane mun Ina da carry over?

Ta ce to a sanyaye tana mamakin irin warda da yayi mata farat daya zuciyar ta cike da Jin dadi tare da ganin kimar say da mutunci.

Kaiiii....ta fada tare da zaro ido ka Fadi accounting. Sai kawai yayi murmushi nasan za'a rina sai wane? Ka Fadi GST English Shikenan. Nawa ne point dina? Ta duba can kasa tana warware ido..... Okay gashi Nan 2.65. Ta kalleshi, amma Suleiman me yasa ka yarda dani

haka?......Au kin San sunana kenan? Ya fada Yana kallonta cike da mamaki, tayi murmushi eh Mana nasan sunan ka Suleiman.

Ina fatan ke dai lafiya lau ko? Sai kawai ta budo mishi portal din ta tace kaga nawa.

Ya zaro ido kaiiiiiii...... Ta danyi murmushi Amma bana son Dan Allah ka fadawa kowa result dina.

Ya Jin jina Kai in shaa Allah Zaki sameni Mai rike sirrin ki, amma Bilkisu kinyi wuta da yawa fa!

Ta yi Yar dariya kawai.

Allah yasa albarka. Kiban no. Ki dan Allah ko da wani Abu Yana tasowa Kuma idan bazaki damu ba Zan ringa matsowa kina tasar Dani inda ban ganewa.

Ba matsala ga number rubuta........

A harzuke Anwar yabar class din tunda ga ranar sai kawai yayi baya da ita ko gaisuwa baya son suyi cikin kankanin lokaci ta Saba da Suleiman ta fahimci Yana da saukin Kai bashi da girman Kai sannan Yana da addini tare da daratta mutane.

Ko da ya gane Bilkisu nada kokari sai ya like mata ko C.A zasuyi Yana manne kusa da ita baya yarda tayi mishi nisa.

Ko kadan Bata da mugunta duk amsar da ta kakare mishi zata bashi ya kwashe tsaf!.

Akwai wani course Mai matukar wahala gashi three credit unit ne Kuma calculation Mai rikitarwa kowa Yana Jin course din. Anwar yayi burus da ita Yana Jin kowa na kokawa Amma ya ki nuna ya iya. Kwana takeyi karatu da salloli, Ranar jarabawar course din ana ta jera layi kawai malamin yace ta zauna can, hankalin ta ya tashi ganin ya cillata gaba don yau baya take son Zama saboda ta Sami taimakon wani.

Tana Zama sai taga Anwar ne a gaban ta, ita dai kawai sai addu'a takeyi tasan yau sai Allah da malaman gari. Tambayoyi bakwai be a amsa biyar tambaya ta farko dole ce gata da 'ya'ya har goma.

Saura kadan ta kurma ihu saboda duka tambayoyin guda daya ne kawai ta sani itama theory ne ba calculation ba.

Idanun ta suka kawo ruwa, taga tunda Anwar ya duke bai dago ba, hall din yayi tsit! Ta yi zugummm, zuwa can kawai ta Fara amsa wacce ta sani.

Mafi yawancin malaman dake tsaron nasu duk sun maida hankali wurin Yan baya. Haka ta dunga rubutu Dan Allah yasa ta Sami Koda *E* ne a course din ta wuce wurin.

Tana gamawa tayi zugummm kawai tana fargaba.

Yadan waigo kadan ganin malaman basa kusa yace kin iya question one naga tana da wahala fa.

Tayi kasa da murya wallahi question 4 kadai na iya cikin bakwai din nan ga Shi ta farkon naga 30marks ne.

Ya dan gyara zaman sa kadan tare da kango mata booklet din sa yace kiyi sauri ki kwasa.

Habaaaaa.....ga bilkiyda saurin rubutu gata very smart. Duba daya sai ta kwaso layi biyu. Cikin sauri ta gama shafin tace juya....Shi kansa yayi mamaki yace ke duba da kyaufa kada kiyi shirme. Wallahi na gama ka juya kawai.

Haka ya bata dukan sauran question hudun da bata iya ba.

Sai da ya tabbatar ta Gama tsaf sannan yaci gaba da amsa Shima question 4 din da tace tayi.

Ta Dan waiga ta hango Suleiman can baya an cillashi sai zare ido yakeyi.

Duk Wanda ka kallo zakaga ko Yana zufa ko Yana ta raba ido.

Kije kiyi submitting...ya fada kasa kasa ta ce toh.

Kowa sai kallonta yakeyi Yana mamakin yanda zata bayar da wuri haka, Wasu na tunanin kawai ta gaji ne da zama kamar yanda Suma suke zaune, tafi mintuna talatin kafin wasu tsirara suka Fara fitowa duk Wanda ya fito idanu jawur ana tsinar malamin kusan kowa ya sadakas da kawai faduwa zaiyi course din saboda rashin iya amsawa. Suleiman kawai take jira ya fito sai kuwa gashi Yana ganinta yace, Bilkisuuu..... Yau naji wuta wallahi Allah dai ya kyauta Amma question biyu kawai nake da tabbaci cikin sauran.

Tabbb....wallahi ni Allah ya taimakeni Anwar ya bani duka Wanda ban sani ba....hada question one?

Eh Mana.

Wai da gaske kike?

Wallahi kuwa.

To Ina Jin keda shine kawai kuka amsa ta don ko su chinyere gasu can suna cewa Basu gane ba.......Allah dai ya kyauta ta fada tare da cewa sai gobe ta ruga hango Anwar yayi hanyar *Gate* Yana ta faman sauri.

Anwar.. ta kwada mishi Kira, yasan za a rina Shi yasa yaso ma kada su hadu.

Ya Dan tsaya Yana murmushi , ya jarabawar Bilkisu ya fada Yana latsa waya.

Hmmm jarabawa yau Allah ya rufa man asiri bacin Kai ai Dana shiga uku. Na gode na gode Allah ya Kara ilimi......Daman ka iya course din sosai haka? Naga yanda ake ta kuka dashi Kai komai ka amsa.....hatta jamilu ma naga naka yake kwafa ( copying ).

Murmushi kawai yayi yace ba damuwa.

Ya wuce kawai. Ta bishi da ido. Anwar...ta Kara kwada mishi Kira.....ya juyo wallahi na gode kaji?

Sai kawai ya kyalkyace da dariya ya juya abinsa.

Taji dadi sosai da sosai a  Ranar domin course din kadai kowa ke kuka dashi wannan semester din.

Hutun ya kasance dogo akalle ankwashe watanni biyu a gida kafin a dawo aji biyu.( Su Bilkisu an Fara manyanta ) wannan karon suna gida result ya fita inda take da 4.22 ta Dan sauko kadan saboda ansha wahala matuka Shi Kuma Suleiman Yana da 2.72 Amma ya Sami carry over daya.

Sun koma da makaranta da sati biyu akayi *convocation* tare da bayar da kyaututta ga first class da over all.

Bata halarci wurin ba. Saboda ba kowa ya maida hankali ga  taron ba. Hakan yasa Anwar zuwa tare da karbar five pointer award da Kuma overall student na aji daya da suka gama.

Kamar munafuki ya karba sim sim sim yayi saurin barin hall din  ganin babu alamun Yan ajin su ko wani Wanda ya sanshi. Ashe Suleiman yana wurin.

Ba karamin mamaki yayi ba watan Anwar shine *Hamza Yusuf* din da ake nema cikin class Amma wallahi sai ya fadawa Bilkisu.................

*************

*KADUNA RIGASA*

Yana ta mamakin yanda ummi ta mishi text tana son ganin sa alhalin bata taba hakan ba.

Yana zaune babban falon gidan nasu an cika gaban sa da kayan ciye ciye da lemuka kamar kullum ta shigo tana ta faman Bata rai .

Ya kalleta tana ta faman karairaye karairaye......Amarya bakya laifi ko kin kashe Ahmad ( Babban yaron sa ) ya fada cikin zolaya Yana Yar dariya hannun sa rike da samosa mutumen shi Yana ci.
Banga alama ba, ta fada tana taunar cingam.
Ya kalleta jin maganar ta fito gatsal....
Kamar Yaya?, Ya bukata.
Kamar yanda kaji.
Kamar yanda naji?
Ya maimaita cike da mamaki kafin ya ajiye guntun samosan bisa plate ya tattara hankalin sa duka wurin ta.....me ke faruwa ne ummi?
Tayi shiru!
Dake nake magana...me ya faru?
Ta gyara Zama, Ina ce apartment din da kayi sabo Ni ka gina mawa Amma labari yazo cewa Aunty Amira ta koma....... Ke ya daka mata tsawa.
Nan da nan ya harzuka, Ni na fada Miki Ina Miki gini?
Gabanta ya fadi tayi tsuru tsuru, kinji? Munyi dake Ina Miki gini?
Okay ita da Zaki aure Mata miji Bata kawo mun matsala ba sai kece Zaki fara kawo mun tsirfa? Saurara da kyau ya Mike tsaye Yana nuna ta yatsa wallahi matukar kina son Zama dani tare da Jin dadi sai kin daratta Amira kin mun biyayya kin Mata bazan dauki sakarci ko kadan ba.
Dukkan ku Ina sonku to dole kowace tabi ra'ayi na, idan Kika saki na gane kina da matsala to wallahi zakiji ba dadi.
Mtsew ya buga tsaki ya wuce.......ta yi zuruuuuu tana zare ido lallai ta gwada Bata ji dadi ba.
Kwallah suka zubo Mata. Ta buga ma babbar yayar su waya domin ita ce abokiyar shawarar ta .....salati ta kamayi ubanwa ya aike ki? Ai kinyi sauri bari zakiyi sai kinje gidan yasan dadin ki lokacin yazo hannu tukun Amma Yanzu ai lallaba matar sa yakeyi tunda ya Mata laifi.
Ki bari Zan baki ahawarwari idan na shigo gobe.
Tun daga ranar Bata Kara Sanya Shi a ido ba. Tuni a Mata hudubar kada ta saki ta dauki raini ga matar sa Kuma idan ta a gidan ta Sami damar juya Shi yanda zata amshe ragamar komai.
Babu yanda ba a yi dashi ba ko kamu ayi yace bai son bidi'a ba Dan komai ba kada ma akirkiri partyn Amira taji ba dadi.
Ranar walima akayi mashi Sha Tara ta arziki hada mota.
Yana falon sa zaune yaji marokiya na sanarwa. Shima ya Mike ya kirawo marokiyar ya bada makullin mota kirar *GLK* baka 2019 model ta kusan miliyan Tara yace yaba Amira ayi sanarwa.
Nan dangin Amarya kuwa suka Fara surutai............
Ko ajikin sa. Dangin ango dana Amirai kuwa suka Fara rangadaguda suna tayata Murna.
Hakan ba karamin harzuka Amarya da danginta yayi ba. Nan suka Kara hure Mata kunnen wallahi sai ta tashi tsaye Dan kwato ma kanta yanci.
Kuka takeyi wuiwui.
Kafin karfe shida gida ba kowa duk an tafi.
Ana gama sallar isha'i ya ja Amarya zuwa sashen Amira don yi masu huduba.......

*Ayi hakuri da typing error please yanayin typing din ne saboda kawai ta WhatsApp nake yi

Kuma gaskiya bana bi idan na Gama kawai nake turawa.
*Daga zainab wowo*💞💕💗😄✍🏼
[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?* 🤐
0️⃣3️⃣

*TUKUICI NE GA AUNTY RABI ALLAH YA KARA ARZIKI DA RUFIN ASIRI*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki.... blood sister khadija Dahiru wowo miji na gari I pray my besty*

*DAYA TAMKAR DUBU AL'AMEEN ZUBAIRU* TANNY ALLAH YA RAYA MIKI YARON NAN YA KARA MISHI KYAU DA KWARJINI💖

*Federal University dutsinma*

Tunda aka dawo bai yarda sun hadu da Bilkisu ba har suyi wata magana. Tana ta kokarin su hadu Amma yaki yarda.

Suna tsaye ita da su favour bakin ajin da zasuyi darasi ta hango Suleiman na taho wa, tun daga nesa suke ma juna dariya saboda Yanzu sun Zama tamkar *Wa da kanwa*, Anwar har yazo ya wuce ta gaban ta bata ganshi ba amma Shi Suleiman man din ya hango shi.

Yana karasowa malamin Shima ya iso haka suka rankaya zuwa aji.

Ko Zama Yanzu kusan tare sukeyi.

Har Yan class din sun Fara lura da shakuwar su.

Ya fakaici idon malamin ya Fara mata magana kasa kasa.

Wai Bilkisu kinsan Hamza Yusuf din say ake nema ajin nan Anwar ne?

Ta zaro ido *Anwar*?

Eh wallahi. Jiya gaba na ya amshi award din first class da Kuma overall award ina kallon sa yayi saurin boyewa ya bar hall din da sauri.

Ta rike baki. Innalillahi, wallahi sai na mishi magana naga wannan semester din ma tunda muka dawo sai wani shareni yakeyi.

Hmmm, ai da yake kece, Amma  Anwar inba ke ba waye ke mishi shigar kawara duk makarantar Nan. Kinsan girman kansa, jiji da Kai da kuwa maida kowa banza yasa aka tsane Shi wallahi ya cika gadara....... Duk yaji dashi nikam daga yau wallahi ya shiga uku dani.

Ba abinda nake nema wurin sa inba karatun ba.....ta katse shi.

Hmmm Hana wallahi nayi mamakin *Business finance* din last semester, bana fada maka cikin mintuna da Basu wuce talatin ba ya gama kusan questions 4 kowa na kuka da question one amma Shi duka yayi. *B* fa gareni course din Kuma wallahi C A da 22 na shiga......ohh ni *Balky* ai wallahi ya shiga uku dani.

Suleiman man dai sai dariya yakeyi yace idan kin kwaso wurin sa Kya ringa koya mun....tabbbb tare zamu je kyaleshi ai wallahi sai na fitine Shi ga wannan semester din kurar ta tafi ta aji daya.

Daya ke Anwar din Yana ta gefenta sai kawai ta yi ta kallon sa.

Tun bai lura har ya fahimci tana kallon sa. Ya Dan juyo suka hada ido ta balla mishi harara Shi Kuma sai ya kawar da Kai Yana murmushi kawai. Haka sukayi tayi da sun hada ido sai yayi murmushi ita Kuma ta harareshi.

Yana ta sake sake cikin Rai *Kuma yau me nayi Ni Hamza* bana iyawa rigima da fitinar Yarinyar can. Ya kawar da Kai bai yarda sun Kara hada ido ba har aka gama.

Hankalin ta na kansa yana mikewa itama ta Mike.

Abinka ga namiji kafin ta sunkuya ta dauki jaka har yabar ajin. Da gudu tabi ta kofar baya kawai sai dai ya ganta gaban sa.

Gaban sa yayi mummunan faduwa Amma miskilancin Anwar bai yarda ta gane hakan ko a fuska ba hasali ma sai yayi Yar dariya *Hajia Bilkisu an tashi lafiy?*

Ta rike kugu To yau Allah ya Kama ka, Ashe Kai ne *Hamza Yusuf*........ Har ga Allah ya Dan razana. Amma a zahiri sai kawai yayi dariya duka kumatunsa suka lo6a ....inji wane makaryacin? Ya fada Yana dan waige waige kada sauran Yan aji masu fitowa suji,

Wallahi Kaine *Hamza Yusuf*.... Ta fada tana hararar sa. Tana matukar bashi dariya saboda ko gida bai taba samun Wanda ke mishi magana Kai tsaye Babu shakka ba irin Bilkisu.

Yadan Sha mur Yana Dan zare mata ido ke ni bani bane ya gitta zai wuce .....Tasha gaban sa da sauri tare da ware hannuwa ba inda zakaje sai ka fada mun wanene jiya aka bashi kyauta ya boye ya gudu?......tuni hankalin mutane ya dawo kansu an Fara fahimtar meke faruwa.

Ya zaro ido..... Ke ni bani bane..... Wallahi Kaine.

Naji nine yanzu meye kike so? Ya fada Yana Yan waige waige kamar marar gaskiya. Zaka ringa koya mun karatu wallahi don bazan kyaleka ba....shine damuwar? Ya fada cikin kosawa, shikenan duk lokacin da kika shirya Zan nuna Miki. Ya wuce da sauri ya barta tsaye.

Suleiman ya karaso kin dai gani ko?

Kyaleshi ai wallahi na daina wahala daga yau addabar sa zanyi.

Nan wuri ya rikice da surutai kowa na mamaki.

Tun daga lokacin kimar Anwar ta Kara karuwa duk masu Jin haushin sa suka daina. Matsala daya ce Babu Mai iya tunkarar sa da maganar koyo duk ana Jin tsoro da shakkar sa.

Tun daga lokacin Bilkisu ta dami Anwar ya rasa yanda zaiyi da ita ba abinda takeyi mishi sai terere kowa Yanzu yasan wanene Shi , ya rasa dalilin da baya son mata wulakanci kamar yanda yake ma kowa.

Ko lecture za ayi Mafi yawan lokuta sai ta zauna kusa da Shi sai dai yayi ta dariya.
Na kusa dashi mamaki kawai sukeyi yanda baya hantarar Bilkisu ko kadan don ko su din lallabashi sukeyi.

Satin da ya kasance daga Shi sai na yin first C.A sun fito lecture seven to nine ( 7-9 ), Yana tsaye ta fito da sauri don kada ya gudu sakamakon daya ce kawai garesu a Ranar.

Anwar muje ka koya mun *Math for Economic* din nan ban gane komai ba gashi jibi yace Shi zaiyi nashi test din.

Duk Wanda ke wurin sai da ya kalli Bilkisu cike da mamaki yanda take mishi magana Kai tsaye haka, Sam bashi ma take kallo ba ko lokacin da takeyin maganar hankalin ta naga jakarta tana saka littafin da suka gama, yayi Dan murmushi ba dai Yanzu ba ko? Saboda ko break banyi ba yunwa...... Ta dago Kai da sauri Nima banyi ba ai idan mun gama duk ma tafi muje muyi.

Ta nuna mishi hanya wuce muje wallahi yau ba inda zaka je......bai San lokacin da ya kwashe

da dariya ba Yana ganin karfin halin yarinyar nan sosai, zai Kara magana ta rike kugu tare da tafa hannu kasan Allah ba inda zakaje...... Wuce kawai.
Naji muje yayi gaba ita Kuma tabi Shi a baya. Duk illahirin wurin binsa akayi da kallo ana wani irin mamaki.
Shi ya Fara Zama kafin ta zauna.
Yawwa ko Kai fa....ai ka gama shiga uku dani watan Kaine Mai kokarin aji shine ka mayar damu samnoni ko?
Dariya kawai yakeyi, tana surutai tana fiddo littafi da calculator. Ta Mika mishi biro da doguwar takarda ..ungo Fara daga farko.....
Dariya yakeyi sosai .....daga farko Kuma? Ki dai fadi abinda baki gane ba.
Ni ban gane komai ba.
Ban yarda ba Allah nasan kina son wahalar Dani ne kawai gashi yunwa nake ji walhi.
Ko me kakeji yau muna Nan sai ka koya mun kawai Fara.
Ya bude littafin to bari mu gani ko na iya.
Ta bishi da harara
Yayi murmushi yace seriously.
A hankali ya Fara mata solving dalla dalla. Dayake Bilkisu na da kokari da saurin fahimta hakan yasa bai wahala ba nan da Nan ya fahimci lallai tana da basira saboda da yawa idan Yana koya ma wasu sai su kusan awa hudu bisa example biyu. Akasarin Bilkisu da Mafi yawan formulas din ma ta haddace su idan yanayi da ka take kawo mishi su.
Ya kalleta hajiyar dai ashe guruwa ce ko? Ya ajiye biro gaskiya na gaji wallahi duk kin iya kina son bani wahala ne kawai ko Bilkisu?
Ta Dan sunkuyar da Kai haka kawai taji Yar kunya ....wallahi a'a ban iya ba.
Yabi fuskar ta da kallo Yana Kara kallon yarintar da ke cike da kyakkyawar fuskar tata.
Ke ni yunwa nake ji gaskiya ya fada Yana rufe littafi.
Dan Allah ka taimaka saura fa biyu da mun gama sai mu tafi Zan siya maka break idan mun fita waje.
Au Zaki biyani ne?
Ta zaro ido wallahi a'a naga hostel zaka koma gashi har Sha daya ta kusa, Kuma yaushe kaje ka nemi abinci?
Ke Kuma fa?
Ni indomie zanci dana koma daki.
To Nima ita zanci. Ya fada Yana ci gaba da rubutu,
Ba damuwa Zan siya maka wurin Abdul Mai shayi na Nan waje ai nasan mutumun ka ne.......da sauri ya kalleta waye ya fada Miki?
Tayi Yar dariya ai Ina wuce ku ta wurin Mafi yawan lokuta.
Ya Dan harareta ke kin samun ido ko?
Ta kyalkyace da dariya Wai ma.....
Eh Mana.
Rabi labari haka suka gama duk idanun sa sunyi ja....Nan da Nan ta fahimci lallai baya da jimirin yunwa yanda har ya Fara galabaita.
Tare suka jera suna tafiya, baka da jimirin yunwa ta fada tana Yar dariya.
Ya danyi murmushi yunwa nada sabo ne?

Eh Mana Amma ga jaruman maza.
Dariya yayi sosai kafin yace naji ni ba jarumi bane ba.
Eh, ta fada tana murmushi
Ke ni sai anjima ya fada tare da yafito Dan mashin.
Ta zaro ido Ina zakaje?
Hostel.....
Indomie din fa?
Na gode....
Wallahi baka Isa ba , Dan mashin din na zuwa tace malam tafi.....ta kalleshi Allah sai na siya maka break kafin ka tafi ko muyi rigima.
Yau ni naga ta kaina....ya fada cikin zuciya.
Ya kalleta, kiyi hakuri da wasa nakeyi na gode,
Ni ban gode ba kawai muje ta nuna mishi hanya.
Dariya ma ya kamayi.
Haka suka je indomie din akwai layi tace kaga kada mu jira zo muje.... Yace to.
Bin ta kawai yakeyi yana kallon ikon Allah sai sauri takeyi suka zagaya babban restaurant din wurin duk yafi ko Ina kyau da tsada, tayi mishi take-away na chips and eggs aka Sanya mishi salad da sos din hanta sannan ta siya mishi gasasshiyar kaza daya da maltina biyu da Madara. Yana tsaye bakin kofar Daman ita kadai ta shiga. Ta fito da sauri tana ta wurga ido kafin ta hango shi can jikin bango.......barkan ka wallahi na dauka tafiya kayi yau da kaga tsiya.
Kallonta kawai yakeyi Yana Yar dariya.
Muje ka hau mashin din zaka shigo anjima school da karfe 4? Ina son ka koya mun *Human resources* ya danyi jimmm..... To bani tunani Amma Ina ga Zan shigo.
Ta fiddo waya samun no. Ka in kiraka kada ka shanya ni kamar last time. Yayi murmushi duk jikin sa yayi sanyi ya ce okay rubuta..... Yana fada mata Yana kallon fuskarta.
Yana Gama fada yace Shi Suleiman bazai koya Miki ba?
Eh bazai koya ba idan ya iya zance Kaine?
Ta hayayyako mishi. Ya kyalkyace da dariya Allah ya bada hakuri. Daidai lokacin da ya tare Dan mashin. Sai da ya hau sannan ta Mika mishi ledojin sannan ta Mika wa Dan mashin din naira dari tace hostel zaka kaishi. Duk meye kika ciko mun anan?
Malam ku tafi kaji...ta kalleshi tana Yar dariya na gode kwarai Allah ya Kara basira sai mun hadu anjima.......kirjinshi ya halba da karfi Shima ya bita da murmushi kawai. Sai kawai ta daga mishi hannu. Hakan Shima ya mayar mata Yana Jin wani masoki na sukar sa...........shi kadai yasan yanda yakeji a zuciyar sa, tana tafiya tana tunani da surutai a zuciya, a gaskiya yau ta Kara tabbatar wa da kanta Anwar na ganin mutuncin ta da kima saboda cikin karfin hali tayi attacking din sa tayi tunanin zai ki yarda kamar yanda yake ma kowa wulakanci.
Shi kuwa Yana zuwa hostel ya baje abincin dakin a cike Yan zaman jiransa kowa ya bude baki Yana mamaki lokacin da yake fada musu Bilkisu ta siya mishi. Bashir ya ce Wai Kai oga anya tsoron yarinyar nan kakeyi ne naga ba Wanda ke maka shigar kawara irin ta kana mata biyayya, dariya yayi kafin yace *ya na iya da Bilkisu*? Wallahi bana iya wa rigimarta ko baku lura ita Sam Bata tsoro na ba?
To ka dai bi a hankali domin Dr Dan Musa da alama Yana ciki wallahi ya gane kana kusa da ita haka zaka. ......mtsew bai iya mun komai wallahi. Ina ga Suleiman ya kamata ku ja ma kunne ba

nima ba domin Shi ke binta Ni Kuma tana Bina .....ya lunkuma nama baki ya kallesu ..hope Kun gane karatun..

( Shin Wai wanene Anwar wacece Bilkisu? )
  ********************

*KADUNA RIGASA*

Yaran duk sunyi barci.
Tayi ma falon kallon ta natsu .....lallai akwai aiki haka ya hada mata aljannah duniya?
Ya kalli ko wace kafin ya tsaida ido ga Amira ya Fara magana a hankali.
Alhamdulillah dukkan godiya ta tabbata ga Allah Wanda ya kawo mu wannan lokaci, kasancewa dare ya Fara yi Zan muku bayani Kai tsaye abinda ya tara mu a Nan.
Amira kece babba dake Zan Fara ga Ummi, kiji tsoron Allah ga dukkan al'amuran ki akanta ki dauketa tamkar kanwarki Salma, ki sani cewa kema Ummi Amana ce a wurinki kamar yanda dukanku kuke Amana a gareni. Babu wacce tafi wata a wurina sai wacce ta fi mun biyayya da tsare dokokina, tabbas ko wacece cikin ku zata fi Power ban baku a boye ba, Zan yi kokarin adalci a gareku Ina rokon dukkan ku duk wacce taga za a tauye mata hakki ko nayi kuskure ko akasin haka na baku damar nuna mun hanya domin ko wane Dan Adam ajizi kuma wasu a wurin da sukeyin kokarin yin dai dai suke ba dai daiba.
Bana son gulma , bana son Jaye Jaye abokai da yawan fita yawo marar amfani.
Ke Kuma Ummi ga Amira Nan, ki bata girma kamar sailuba bana son raini, rashin kunya da tsageranci. Tabbas na zauna da Amira nasan halinta don haka ki bita a sannu ku zauna lafiya. Duk abinda ya shige Miki na gidan nan ita Zaki tambaya tunda ni ba mazauni bane.
Da ita Zaki zauna kiji dadi ba ni ba saboda tafiya Zan ringa yi ina barin ku.
Ina da Yara, ko da wasa kada ki zagesu domin ba a zagi a gidan nan, idan sun Miki laifi kiyi musu duk hukunci amma banda zagi.
Amira dai tunda ta sunkuyar da Kai bata dago ba tana ta karanta addu'o'i a zuciya, Ummi din ma ce ke ta Yan wurge wurge.
Sai maganar kwana, a musulunce zanyi kwanakin da aka halatta a dakin Ummi a matsayin ta na budurwa daga Nan ko wace Zan ringa kwana biyu biyu hakan ya muku ?
Duk sukayi shiru.......Amira ya muku?
Ta dago Kai umm hakan yayi ko Ummi?
Ta Dan yatsina fuska ..um.
Da kyau!
Maganar abinci Kuma duk Mai aiki ita zatayi abinci, Ummi tsarina a gidan Nan ko Ina Nan ko bana Nan karfe Sha biyun Rana ya zamanto kin Gama abinci saboda Yara da masu gadi da Kuma sauran mutanen gidan.
Bana son kwauron abinci a ringa dafawa a wadace, tun daga safe har dare.
Amira zata Miki bayanin quantity din idan Kun zauna.
Ba wacce zanbi dakin ta lokacin kwananta duk ranar aikinki Zaki sameni sashena ban yarda da raba kwana ba Koda munyi fadan soke soken wuka.....
Ya kalli Ummi wannan shine tsarina. Duk wacce nayi ma laifi kafin ta tsiri yin fushi dani ta Fara sanar Dani idan har nayi bisa kuskure Zan bata hakuri, idan Kuma akasin haka Zan Fadi

dalilina.
 Duk Mai bukatar abu ta tambayeni Kai tsaye domin nine mijinku, idan anzo muku da magana akaina ku Fara sanar dani da Kuma Wanda ya kawo maganar ku fadan wanene.
 Idan cikin ku wata keson haddasa fitina ta kawo muku gulmar daya to ku tsaidata ku kirawo wacce ake maganar kusanya ta maimaita a gabanta zakuyi maganin munafukai.
 Ina fatan duk kun gane?
Wacce keda magana tayi.....duk sukayi shiru.
 Ya Mike Ummi jeki Ina zuwa......kamar jira takeyi ta Mike.
 Ya Mika wa Amira leda uwargida ga taki kazar.......wayar say tayi Kara ya ganka a kunne hello........na'am hajiya.....Nan ta fahimci mahaifiyarsa ce. Ya yahuto ta da hannu alamar tazo ta rufe kofa zai fita Yana ci gaba da tafiya.
 Yana fita ya Sha kwana ya latse wayar daman fakaitar idon ta yayi ya latso wakar saboda Shi baisan yanda zai mata bankwana ba. ( Namiji?.....)
Tana rufe kofar ta duke a wurin tafara kuka na ban tausayi....( Kishi kumallon mata.....)

Ina bada hakuri Dan Allah.......

*zainab wowo ku muku fatan alkhairi*......✍🏼💖😄
[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
 0️⃣4️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

*Kinfi Alawiyya farin jini unex ta hannun damata ( Hussaina Nasir )* Allah yabar kauna. *Alawiyya*👉🏼😝

*Federal University dutsinma*

Tun lokacin da Bilkisu ta siya ma Anwar break abun ya mishi tsaye cikin Rai saboda karon farko daya taba karbar kyauta daga hannun wani ko wata bayan iyayen sa.
 Wasu mutanen basa raina alheri ko kadan hakan yasa Anwar yaji Bilkisu ta shiga ransa farat daya ba don Yana sonta ba ko makamancin hakan sai dai lura da yanayin takun yarinyar, Bata da Jaye Jaye kuma baya tunanin zatayi yawan surutu.
 Ita kuwa tuni ta fitar da abun a ranta saboda bata dauki hakan da tayi da wani girma ba, kawai she feel like making him happy kamar yanda ita ma ta kasance cikin Jin dadin bayar da lokacin sa gareta ya koya mata karatu .
 Ya kasa sukuni ganin lokacin yakeyi baya gudu duk wadanda keson Karin bayani ya Basu

hakuri sai zuwa dare, yanayi Yana duba agogo da Kuma wayar sa Koda zata Kira, me yasa ni ban karbi wayar tata ba? Mtsew yaja guntun tsaki, uku na bugawa ya kasa hakura kawai yayi wanka ya shirya cikin kananan Kaya gayu yayi sosai, uku da ashirin ya Isa makaranta, anata Kiran sallar la'asar hakan yasa Shi wucewa masallaci. Lokacin da aka fito sallah uku da hamsin, ya kura ma wayar sa ido kamar ya rotsata da kasa, shin Wai bazata kirani ba?

Bummmmm......ta fada daga bayansa alamar tana son bashi tsoro.

Ya tuntsure da dariya lokaci guda Kuma zuciyar sa ta mishi sanyi, Ni Zaki ba tsoro? Ko kin dauka kowa irin ki ne matsoraciya?

Tayi murmushi kawai, Yanzu na fito masallaci Ina Shirin kiranka na hango ka........ Ba wani baki da niyyar kirana tun yaushe Kika karbi wayar ba sai ki yi mun ko flashing bane don Nima nayi saving taki?

Suka jera suna tafiya,

No need....kawai na barta ne sai lokacin da Zan Kira.

Bana daukar wayar da bansan no. Ba so better call me to save yeye.

Ta kyalkyace da dariya yabi fararen hakoranta da kallo.......Ni ce yeye?

Ya mata banza kawai.

Karo sukayi da Dr Dan Musa akan hanya, ta gaida Shi Anwar kuwa ko kallo ya wuce abinsa, ya bishi da kallo cikin bacin Rai laifi biyu gashi suna tare da Bilkisu sannan Kuma gashi baya gaida Shi kusan sau hudu kenan suna haduwa Anwar din na watsin kasa kasa dashi, don akwai lokacin ma da suka hasu banki Anwar din ya kalleshi ya watsar ba tare da ya gaida Shi ba. Ya kuta cikin Rai zaka ci ubanka, ya kalli Bilkisu sai Ina Kuma haka kuna da evening lecture ne?

A'a zamuje karatu ne Anwar zai mun bayani. Wanene Anwar?

Ya bukata, Hamza Yusuf wancen ta nuna Shi da yatsa Yana tsaye gaba kadan Yana ta faman latsa waya da alama ita yake jira, Au wancen Dan iskan yaron Mai girman Kai Wanda ya Raina mutane?

Ta zaro ido......raini Kuma sir?

Ya harareta kawai ya wuce abinsa yabarta tsaye. Ta bishi da kallo tana mamakin me ya hada Shi da Anwar din domin tasan Shi mugu ne ana kuka dashi a department.

Me ya hada ka da Dr Dan Musa? Ta karasa inda yake tsaye da sauri.

Ya kalleta cike da mamaki. What the hell are you talking about. Meye zai hadani dashi kuwa inba Yanzu da ya ganmu tare ba.......kada ka mishi fassara, yace ka Raina mutane and this is the second time I hard about something like this a bakin lecturer.

Me yasa baka gaida Shi ba Yanzu Kuma kaji na gaida......saboda baya gaba na.

Malama stop interrogating me about those idiots...... idiot? Anwar kanka lafiya kuwa?

Bai tanka mata ba har suka zauna wani class.

Ki fiddo littafin da zamuyi.

Bazan fiddo ba ....me yasa malamai ke cewa ka Raina mutane Kai kowa ma daukar ka yakeyi ka Raina kowa......Amma ai ke kinsan ban Raina ki ba ko? Hasali ma tsoron ki nakeyi to meye zai dameki? Ya karasa maganar Yana Yar dariya .

Ba wani... ai su malaman ka.....

Bilkisu me yasa kike kirkiro unnecessary problem ki dorawa kanki?

Meye abin dagewa anan Wai? Sun Dade basu kirani da Dan rainin hankali ba so what?.......sai suyi maka mugunta a result,

Basa iyawa ki daina damuwa......
An Gaya ma na damu ne?
Kai ba a Isa a fada ma kana kuskure ba ka gyara.? Ta dunga balbala mishi masifa.
Hannunsa duka biyu ya goya a kirji tare da tsareta da ido Yana mamakin.
Meye abin hakikancewa anan? Ita meye nata aciki? Wai me yasa take kokarin shiga harkarsa ne ma?
Ya sha mur Yanzu kin kirani anan ne don ki nemi rigima ko kuwa karatu zamuyi? Cos I'm tired of it already.
Ya janyo littafin dake gabanta bari mu Fara ...........
Gab da magariba suka gama, tare suka taho yana ta binta, har suka karaso kwanar gidan ta, lokacin ne ta kalleshi zaka bini ne?
Ashe kin gane , ya fada Yana murmushi....
Tabbb da ka ci na jaki kuwa muyi maka ihu Kato.
Wannan karon dariya yakeyi sosai nine katon?
Eh Mana namiji a gidan mata.
Kin San ma'anar katoa hausa kuwa? Ta kalleshi eh Mana gashi na fada kato namiji kamar Kai......barawo ake ce ma Kato fa ni barawo ne?
Kai Ni dai bance ba kada kamun fassara.
Test din gobe ina bayanka please.
Da gaske kike?
Allah kuwa......
Okay ba damuwa.
Kiyi man flashing nayi saving no. Ki Mana.
Zan kiraka anjima kada ka damu ai na ce Zan karanta abinda mukayi inda na manta Zan maka waya ka tuna?
Ke ban yarda ba kirani Yanzu.
Allah Zan kiraka kaji na rantse.
Sai da safe gashi can an Fara Kiran sallah.
Kina korata ne? Me yasa like zaune a off campus bakya son hostel? Hakanan Ina da kyankyamin toilet maganar gaskiya Kuma Ina son privacy in ma life.
Kai me yasa kake son zaman hostel?
Kar na Zama Dan iska Shi yasa a off campus mata zasu dameni Yanzu ma Yana iya......harara ta balla mishi sannan ta buga tsoki kaji dasu can, sai da safe.............. Bilkisu.... Bilkisu... Bilkisu..... Amma inaaaa tayi shigewar ta gida ta kyalesa.
Yayi murmushi yarinyar rigimammiya ce wallahi. Kut!
Wai ni Anwar yau mace tayi wa tsoki banji haushi ba shin Wai wanna yarinyar wacece ita?
**************

*KADUNA RIGASA*

Tunda suka Fara raba kwana matsaloli suka Fara kunno Kai daga bangaren Ummi, duk ranar girkin ta sai ta Mila tasha iska take data abinci wani lokacin sai dai Amirar ta dafa ma Yara indomie ko su Sha oat ko wani simple food, tun abun baya damun Amira har ta Fara Jin Yan aikin gidan kansu sun Fara korafi.

Gashi baya nan yayi tafiya.
Ranar da ya dawo kuwa akayi sa'a dakin amaryar yake.
Bayan sallar isha'i Yara sunyi barci ta sameshi acan. Yana kishingide bisa kujera ita Kuma tana saman kafet tana chatting......dukkan su ta kalla sannan ta watsar.
Ya Dan zabura Amira yau kece anan? Lafiya dai ko?
Domin bai taba ganin ta sashen ba idan Yana nan wata kila ko tana zuwa sai idan baya nan ne.
Zuwa nayi in tambayeshi ka, Kaine ka Sanya matar ka ta ringa yin abinda taga dama gidan nan?
Ya zaro ido Ni? Me tayi?
Ta zaburo Au karata.....ya daka mata tsawa idan Kika Kara magana bakin auren ki wallahi kada ki dauki mutane Yan iska ke gidan ku ba manya ne?
Abinda kikeyin mun daga ni sai ke Ina shanyewa idan Kika ce zakiyi gaban jama'a kece Masha wuya.
Amira me ya faru? Zo ki zauna..... Ba Zama ya kawo ni ba.
Ina so in sani cewa Kaine ka ce matar ka ta ringa Mana horon yunwa a gidan nan? Daman ka sanya doka ne na Mai miji tayi girki don ka fifita daya?
Tun zuwan Ummi gidannan a duk lokacin da aka ce kasa kafa kayi tafiya to mu da abinci sai taga dama Yara har sai sun Fara kuka sai dai a nema masu wani abun.
Bata ganin kowa da mutunci ban Isa in nuna mata kuskure ko shawara ba shine na ke son gani a gabanta ka fada mun idan Kaine ka daure mata...... Wallahi bani da masaniya.
Kuma me yasa tun farko Baki fada min ba ......saboda Ina tunanin ko hada bakunta ne Shi yasa Amma na lura galari ne da daurin gindi....wurin wa? Na rantse da Allah ban sani ba.
Ke Ummi kinji abinda ta ce haka ne?
Ta yatsina fuska, eh saboda Ni ko a gidan mu ba saba dafa abincin gandu da......what?
Nan gidan ku ne?
Da sauri ta kalleshi.
Ya zaburo na ce Nan gidan ku ne?
To bari kiji in fada Miki Nan gidana ne matukar kina son Zama Dani wallahi sai kinbi abinda nake so da abinda na tsara.
Waye zakiyi ma gadara kice gidan ku? Idan gidan naku kike so sai a maida ki kije kiyi abinda kike so Amma anan matukar kina son Zama to ya Zama wajibi kibi abinda nake so. Bazan taba daukar raini da wulakanci ba ai nasan halinki na ga take taken ki na rashin tarbiyya da tsageranci idan nayi la'akari da yanda kike datsa mun magana many times.
Ya nuna ta da yatsa wallahi ki taka a sannu......Amira dai juyawa tayi abinta.
Ya kirata Amira tana juyowa tace abinda ya kawo ni kenan idan itama tana da nata korafin Ina jiranta.....tayi ficewarta.
Amma ke wallahi Baki da wayau Ummi. Da kin San Hali irin na Amira da kin lallabata Kun zauna lafiya. Kin Aure mata miji Kuma kin dawo kina wani hauka...... Gori zaka mun? Ai ba ni na kawo kaina ba....... An Miki gorin.
Wallahi matukar kina son Zama Dani cikin Jin dadi sai kinbi Amira Kun zauna lafiya.....fuuuuu ya tashi ya shige daki ji kake gammmmm.
Kwalla suka zubo mata, zuciyarta tayi mata kunci wanna masifa dame tayi Kama?

******************

*Federal University dutsinma*

Sun fito lecture 9-11 kenan aka aiko registration officer dinsu na kiranta.
Babban mutum ne ana yawan Kira mishi kirki da mutunci.
Tana ta faman tunani ko lafiya?
Bayan sun gaisa ya mata fatan alkhairi sannan yace yaji dadin gajin result dinta da Kuma yanda ta Sami shaida a department na tare mutunci amatsayin ta na budurwa Kuma ita kadai mace musulma a ajin.
Sannan idan har tana da wata matsala kada tayi kasa da guiwa ta je ta sanar dashi in shaa Allah zai taimaka.
Tayi godiya sosai, ta koma aji dayake suna da wata lecture ta 11-1 sannan suyi test 2-4.
Sadeeq babban abokin Anwar, Wanda kowa yasansu tare tun aji daya, ya hangota yace mutumen ga fa bilky can .
Yayi kamar baiji Shi ba miskilin........

*Zainab wowo*..💖✍🏼ayi hakuri da kadan pls
[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
06

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

*Masoyana ku sani cewa Ina alfahari da ku 100% a ko'ina kuke. Na gode da kauna*👏🏼

****************

*Federal University dutsinma*
Duk dube dubenta bata hango ta inda zai bullo ba, juyawa tayi don tafiyar ta..... Saura kadan suyi karo.
Ta razana ainun, hazbunallah! Ta fada da sauri tare da yin baya kadan ........harara ta banka mishi kafin tace. Wallahi ka tsoratani.
Ya danyi murmushi matsoraciya kawai meye zai kamaki Yanzu da rana gatsal cikin wannan bainar jama'ar?
Mtseww...... Ta gittashi zata wuce.
Ina zakije Kuma Ina ce nemana kikeyi.
Barshi kawai , ta fada tana Kara yin gaba.
Ikon Allah, ya fada tare da rufa mata baya..... Wai ke me yasa kin cika nemana da rigima?

Ta Dan harareshi, ni nake nemanka da rigima ko kuwa Kaine ke nemana da rigima?
Me nayi?
Saboda me yau kayi wa Suleiman wulakanci ni kuma ka kunyata ni?
Kunya ta ki Kuma?
Eh, ai kasan tare muke dashi sannan ka tabbatar idan na copy naka zai Sami damar yi shine ka rufe kayi biyu Kuma don mugunta baka tashi bani ba sai da aka ce submit.
Shine laifin da nayi?
Ban sani ba.
Allah ya Baki hakuri what next?
Kaje kaba Suleiman din hakuri......you are not well wallahi nine Zan ba Shi hakuri? Da na mishi me?
Shi ko kunya baya ji zai zauna mace na goya Shi Kuma......ai baya ganewa.
Please Bilkisu come to your senses Mana. Me yasa kike kawo fada marar amfani tsakanin mu.
Ya ja ya tsaya Bari kiji na fada Miki, tunda Kika ajiye girman Kai Kika nuna kina son ki karu dani toba abinda bazan miki ba don naga kinyi passing no matter how, Amma duk masu zagi na suna mun shaidar banza a class kallonsa kawai nakeyi.
A gabanki ake cewa Ina da girman Kai, bani da kirki....this and that..Amma Ina so in tambayeki lokacin da Kika nuna Zan koya Miki karatu Kinga negative response a wurina?
Akwai Wanda Kika taba Jin yazo wurina da sunan Zan koya mishi karatu na koreshi ko Kuma nace  bazanyi ba?
Ko kuwa saboda kawai Ina son a yaba mun sai nayi ta yake baki Ina shelar ku taho kutaho Zan muku karatu imagine for God sake.
Eh na fahimceka amma ai baka sakin fuskar ma da za a tambayeka.....ke me yasa Kika tambayeni?
Tayi murmushi ai ni kace.
Ke Bilkisu ko?
Ashe ka gane ....ta fada tana Yar dariya.
Mtseww......ya kamata ki daina mun wannan rigimar gaskiya bana so........ Sai kayi kokari ka canza Hali?
Nayi meye?
Na farko, Idan ka shigo class ka danyi wa mutane magana, na biyu, ka ringa yarda ana hada ido da Kai sai kayi Dan murmushi.......wata muguwar dariya ya saki har Yana buga kafa kasa.
Yarinyar nan wallahi kin rainani da yawa. Watan kaman wani karamin yaro ko?
Suka ci gaba da tafiya.
Nidai na fada maka.
To naji, sai Kuma me?
............. Shegen gora, wallahi daman sai da Anas yace tare da Bilkisu kake wannan ihun.
Dukkan su suka juya, sadeeq ne da Anas.
Yawwa sadeeq Allah ya kawoka zo ka taya ni yi mishi fada.......duk suka zaro ido fada Kuma? Ai wannan mugun dan daba ne wallahi yafi karfin mu.
Au baku fada mishi gaskiya kenan?
Kedai jaraba....suka ce tare da wucewa suna Yar dariya.
Shi kuwa sai hararar su yakeyi.

Ta rike baki....ohh, watan Kai kowa tsoron ka yakeyi......Banda ke,
Hmmm,ai wallahi koni ma ta Kara sauri sai anjima kaga tafiyata.
Shima ya Kara sauri Ina zakije Ina Jin yunwa muje ki siya mun abinci tunda kin Fara dandana mun.....eh lallai yi kokari ka cinye Yan pocket money din ta fada tana hararar sa.
Ba Shi kenan ba mun koma 1/1 kenan..... Amma muje Zan jira ki dafo mun indomie....ta zaro ido, Kai rufan asiri koma kada ma ka janyo mun surutai ace .......kin Fara yawo da Dan iska?
Ko kin Fara zuwa da Dan iska kofar gida......na tuba, ba haka nake nufi ba, inba haka kike nufi ba sai ki zabi daya, ko ki dafon indomie ko muje ki siya mun suya ko kaza ko chips......ta kyalkyace da dariya watan sai ma ka zaba,
Ka jira anan naje na fito da kudin nan Babu a jaka, muje na ranta miki gobe ki fito mun da kudi.
Ikon Allah kamar cin rabo?
Eh, ai nasan karamin aikin ki ne idan kin shiga inji shiru kinki fitowa.
Mtseww......au abinda kasa ma ranka kenan.....ke mufa juya wallahi bazaki shiga gida ba.
Haka ta juya badon ranta yaso ba suka je shagon Alhaji Hari, ta kalleshi zabi abinda kakeso toh.
Ya koma gefe zabo mun dai ni wace gareni tunda kawoni akayi?
Kamar ta nutse kasa don kunya shagon cike mutane an musu ratai da ido. Kowa yasan Anwar Kuma Mai shagon yasan wanene Shi mamaki kawai yakeyi yau shine tare da mace?
Ta Sha mur Alhaji bani meat pie hudu, Pepsi biyu, shortbread biscuit din can manya biyu.....gaban Anwar ya Fadi Jin kayan tsadar da take lafto mishi Amma da ya tuna Shi zai biya kudin sai ya kyaleta.
Leda bammm aka cika. Ya mata totalling dubu hudu da dari shidda....... Ta bude jaka ta fiddo ATM Daman Yana da *POS* tace fidda kudin pls.
Ba karamin faduwa gaban Anwar yayi ba.
Ya rasa yanda zaiyi duk yaji wani iri.
Ta fito niki niki da leda oya muje ta fada tana hararar sa.
Ya sunne Yana Yar dariya.
Dan mashin ta tsaida mishi sannan ta kalleshi Yanzu ka shafan lafiya ka tafi ko?
Ya kyalkyace da dariya korata kikeyi?
Eh, ka isheni...go!
Wannan karon dariya sosai yayi, shikenan ba damuwa.
Zaki Kuma nemane ai.
Ta Mika mishi ledar bayan ya zauna kaci yau kaci gobe acici.
Wannan lokacin tare sukayi dariya.
Ta wuce tabarsu anan.
Tana niyyar tsallakawa titi ne suka suka zo zasu wuce yace: *A ringa duba titi*
Ta mishi murmushi kawai tare da daga hannu.
Haka kawai ta tsinci kanta cikin wani irin matsanan cin farin ciki,
Shi kuwa Anwar gaba daya ya kasa fassara yanayin da yake ciki haka kawai fuskar sa ta kasa daina guntuwar dariyar da yakeyi lokacin da suka daga ma juna hannu.
Anas ya rabka salati......Wai da gaske Bilkisu ta maka shopping yau ma?
Murmushi kawai yayi,
Sadeeq ya Kai mishi duka, munafuki kwa gama sumke sunken ku bayyana kanku, Daman na

Iura ka Fara tsanar Suleiman simply don Yana tare da ita, Kiri kiri dazun ka hanashi amsa wallahi baka kyauta ba Anwar........suka dunga mishi surutai ya musu banza miskilin bai dai ce kunyi gaskiya ba bai Kuma karyata su ba.

Duk abinda Bilkisu Bata so Yanzu kafa biyu Anwar gudun sa yakeyi.

Ba Wai ajin nasu kadai ba har takai aji daya ma nemansa sukeyi don ya koya musu.

Maimakon hakan yayi wa Bilkisun dadi sai ya kasance kullum cikin fada da rigima sukeyi musamman idan ta ganshi tsundum cikin mata sun saka Shi tsakiya kamar tayi hauka sai su kwana biyu uku Bata mishi magana ba Shi Kuma ya rasa dalili.

Idan kuwa ya kuskure ya dauki hoto da wasu to sai sun kusa sati bai sanyata ido ba, ko lecture sai dai tasa a mata attendance.

Ya rasa inda zai saka kansa.

Taki yarda suyi magana daya nemeta sai ta zille,

Yan mata sunyo mishi chaaaaaa har Yan wasu department ashe daman ko wace ta ciki na ciki rashin bada fuska ne.

Hakan ya Kara harzuka Bilkisu Jin kowa Anwar .... Anwar.

Gashi ta riga ta Saba da bayanin sa, duk Wanda zai mata sai dai ya Gama babatunsa Amma Sam Bata fahimta.

Shi kansa yana bala'in son koya mata.

Ranar Alhamis ana fitowa lecture tana kokarin fita ya tare kofa ya maida ya kulle.......gaba daya ajin akayo masu chaaaaaa da ido.

Kamar ta bude kasa ta shige don kunya.....ke me na Miki kike fushi Dani?, Na gaji da fadan hakanan wallahi mu shirya.......Dan Allah bani wuri in wuce ji yanda kasa ake kallona.

Duk wannan mazuran naki yau bazasuyi tasiri ba sai kin fada mun Yanzu Kuma laifin me nayi naga abun naki Dada hauhawa yakeyi.

Ta kalleshi sama da kasa , sai naji zafin makara tukun ta ja kofar da karfi ta fice ya bita a fusace saboda yaji haushin abinda tayi...

Wai Bilkisu me na Miki haka? Ko kin gaji dani ne kina son in Baki wuri in kyaleki?

Yau kusan kwana uku Ina kokarin kizo muyi karatu kina zillewa.......ta dallo mishi manyan idanun ta, yaushe kake da wannan lokacin?

Ai Yanzu mutane sun Fara maka yawa batani kake ba......Nan da Nan ya sauko zuciyarsa tayi sanyi kalau sauran kadan dariya ma ta kubce mishi Wai yarinyar nan badai kishi ke damunta ba?

Ya tari gabanta.....jira muyi magana daina tafiya.

Wallahi tallahi Ina da lokacin ki, basune suke zuwa na koya musu ba?

Ke kuwa nemanki nakeyi ko ranar Monday nace ki jira Ina son ganin ki kawai Kika gudu Kuma kece kemun fadan Ina sharesu da farko Yanzu kulawar ce zata haddasa Mana matsala?

Gabanta ya Fadi kada fa ya mata fassara.

Ta Fara in..in..in.

Bude Baki kiyi magana. Idan har Baki son in koya ma kowa wallahi daga yau na daina.

Ni Yanzu Kika ce Babu ruwan ki Dani Bilkisu ai na shiga uku waye zai ringa siya mun kayan dadi?

Bata San lokacin da ta yi dariya ba.

Shima dariyar yayi...kiyi hakuri na tuba bazan Kara ba. Daga Yanzu matukar kina son time dina

ko wane lokaci ne Zan baki Ina ce Daman shine damuwar ko?
Ta Dan zumburo Baki eh.
Yayi murmushi, Zan kiyaye. Yanzu Ina zakije?
Daki.
Karatun fa?
Tayi shiru,
Kinji?
Ko har Yanzu Baki huce ba?.....
Kai Dan Allah. Ta fada tana Yar dariya.
To muje muyi ko sai anjima?
Eh,
Da karfe nawa?
Hudu.
Yanzu meye zakiyi idan kinje dakin?
Girki.
To zanci. Kizo mun dashi 4 din.
Okay.
In rakaki ko in kyaleki?
Kyaleni kada ka janyo mun duka gun Yan......maganar ta makale.
Ya zaro ido gun wa? Karasa Mana.
Tayi Yar dariya kawai, ya kuwa bita da kallo har tayi nisa........ Kyaleta hakanan tunda tayi nisa maye. Sadeeq ya gani gabansa.
Ya dunkule hannu zai Kai mishi duka ya goje.
Zanci ubanka ne, na gaji da wannan sa idon naka Kuma da alama kaman Bilkisu kawai kake man wannan shisshigin.
Kai mugu ai na lura kwana biyu baka da sukuni saboda ta Fara daina kulaka.
Mtsew you are not well, ya fada tare da barinshi wurin tsaye .
**************
*KADUNA RIGASA*
Ya Fara dukan kofar kamar mahaukaci, Amira Ni Zaki rufewa kofa?
Naje na rufe, Daman baka shirya ma irin wannan ranar ba da mace zata hanaka barci ka karo auren?
Idan laifi kayi mata sai ka koma ka Bata hakuri ku sasanta da matar ka...idan kuma ita ce ke da laifi sai ka koyi yanda ake hukunta mace dai dai laifinta ba ka kaurace mata ba.
Kaine ka kawo dokar Banda raba kwana Koda za'ayi soke soken wuka...au fadan na maganganu ka kasa dauka har Kaine yau zaka karya dokar ka da kanka?.......Amira ki dubi girman Allah ki buden kofa zuciyata na iya bugawa......
Wallahi bazan bude ba saboda hakan haramun ne a wurin ka dani.
Ka koma can dakin matar ka.....watan idan ana dadi zanji shiru sai ta baci .......kada kishi ya janyo kiyi mun butulci.
Butulci ai Kai ne kayi mun tunda har ka iya hango wata bayan ni.......kasa daurewa yayi yabar gidan a fusace.........Ya duba agogo karfe Sha daya saura, ya kuwa Danna Kira......
Bugu biyu ya dauka.

Hello Abokina ya?
Kazo gidana Yanzu Ina nemanka, Ummi na bani matsala mukhtar.
Gabansa ya Fadi yasan a rina, ko a gida Ummi bata da kunya ta Raina kowa.
Cikin mintuna Sha shidda ya karaso.
A waje ya tareshi saboda tun fitar sa zuwa gidan Amira itama ta garkame side din nasa.
Tare da mukhtar din sukayi ta dukan kofa Amma taking budewa su duka suka hasala.
Cikin fushi ya kalleshi Abokina gobe kawai ka maido Yar iska gida idan ta dandana zaman gidan a matsayin zawarci ......bani sakinta wallahi. Ya katseshi.
To ka mayar da ita duk da haka ka Bata hutu kamar na wata guda taji taji. Kuma kada kaje ka Bari Ni Zan ma su hajiya bayani babu ruwanka.
Yayi shiruuuuuuuuu......ya ka sa magana Yana dai nazari.

Ayi ta hakuri kaman yarda na ce Ina da hidindimu Shi yasa

*Zainab wowo ce*...✍🏼💖[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
0️⃣5️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

*Kinfi Alawiyya farin jini unex ta hannun damata ( Hussaina Nasir )* Allah yaba kauna.
*Alawiyya*👉🏼😝
*********************
*Federal University dutsinma*
Tana isowa ya tashi yabar gurin.
Haushi ya kamata ganin zai dizga ta bayan Kuma yasan cewa wurin Shi tazo.
Sai Shan kamshi yakeyi yau ta rasa dalili.
Ta kalli sadeeq yau me akayi wa abokin ka ko Yan wulakancin ne bisa Kai.?
Yayi murmushi to wa ya sani.?
Sadeeq Yana da kokari Shima sosai musamman bangaren calculation ya iya Math sosai da sosai.
Tayi murmushi kyaleshi don nace zamu zauna test tare ne yake faman hade rai.
Murmushi kawai sadeeq yayi.
Suleiman na zaune gefen ta, tace sadeeq kara nuna mun nan please ta bude littafi ( Bilkisu kenan ba girman Kai indai maganar karatu ne ), ya danyi Yar dariya bari in Kira Miki mutumen ki kada.......bana so kyaleshi kawai nunan.
Tare da Suleiman ya nuna musu sai ma ta ga cewa yafi Anwar iya koya lissafi Shi Kuma yafi iya

theory ( labaran banza ).
Yana shigowa ajin ya gansu tare da sadeeq ya Kara hade rai, wani haushi ya turnukeshi ji yakeyi kamar ya rufesu da duka su biyun.
Zai gitta sadeeq ya rikoshi malam zo ka koya mata.....kyaleshi banso ta fada a hasale.
Baka ga sai wani Shan mur yakeyi ba simply don nace Zan zauna test kusa dashi? Mtsew ta balla mishi harara.
Duk kunya ta kamashi,  saboda Shima fa bai San dalilin fushin nasa ba,
Gaban sa ya fadi kaddai fa kishin yarinyar nan yakeyi. Yayi saurin kawar da tunanin yadanyi tsaki a hankali.....
Ke bana son Sheri, yaushe ma na ganki da har Zaki mun wannan shaidar.
Eh Mana, Ina ma ka ganni ai baka so ko ido mu hada kana ta wani muzurai......mtseew ya finciko sadeeq tashi munafuki. Ya zauna kusa da ita kamar ya ingije Suleiman yakeji , kawai baya son raini ya shiga tsakanin su.
 Zaka karya nine?
Ya mishi banza..., Ita ma bai Kara mata magana ba.
Suleiman dai na gefe ta juya tana mishi magana......idan na wanko ga Anwar ka wanka kada kayi kasa da guiywa....ya kyalkyace da dariya ita ma dariyar tayi.
Ya Kara hade Rai....yarinyar nan ma ta daukeni Dan iska Amma ba laifin ta bane Suleiman zanci ma uwa......akan me? Wata zuciyar ta bukata. Yayi saurin kawar da zancen ya maida Air piece dinsa a kunne. Ya ajiye littafin sa ya fita waje.
Kowa nata karatu Amma Shi ba yanda zaka ganshi da littafi.
Handsome and intelligence guy amma girman Kai da wulakanci sun bata Shi. Vivion dake zaune gaba na ta fada tare da kallon uchechi.
Ai ya Raina kowa don Yana da kokari.
Ga kyau Kuma ko?
Eh, Amma baya birgeni saboda gadarar sa, jiya munyi ta kiransa yaki daukar waya nida su faith.
Hmmm mu samun sa mukayi dazun after lecture muna son ya koya Mana Amma kowa ya kasa Masa magana........ Maganar ta makale ganin Yana dawowa.
Ashe malamin nee gani ya taho.
Ko Zama baiyi ba ta nuna su uchechi gasu Nan suna son ka koya musu amma sun kasa tambayar ka......sai ke Mai Baki Zaki tambayeni?
Idan abun ya damesu ki bari su fada Mana.
Zata Kuma magana ya nuna mata hannu alamar ta duba ga malamin nan ya shigo.
Sadeeq na bayansa.
Ta fiddo paper zata rubuta suna yayi saurin daukewa ya rattaba nasa sunan ya wani hade Rai.
Ta kura mishi ido Baki bude.....gashi Bata da wata.
Ko wa ya dauke jakar sa....malamin ya fada.
Ya dauko jakar ta ya saka littafinsa Suleiman ya Miko nasa a saka mishi da wayar sa kawai ya Mike ya saka tashi wayar yakai jakar can gaban malamin.
Ita Bata San me yayi ba, Amma Shi Suleiman din yaji haushi sai dai Yana uchechi ta saka mishi a tata jakar.
Sadeeq kuwa dukewa yayi Yana sumke dariya.

Bilkisu tayi zugum tana zare ido Anwar ya kwace takarda.
Tana tsoron tayi magana ya canza mata wurin Zama.
Ko ajikin Anwar tuni ya Fara rattaba number sa bayan ya rubuta suna da course code.
Suleiman ya Ankara Ashe biyu gareshi. Ya Miko mata.
Wani sanyi taji ta balla ma Anwar harara sosai sannan ta Fara rubuta suna.
Gaba daya ajin yayi tsit!
Tana rubuta suna taga Anwar ya fiddo wata takardar ashe daman Yana da ita.
Haushi ya Kara kamata shin me take nufi da akoreta sit din ko meye? Nan da nan ta Kara kulewa.
Har malamin ya gama raba question paper Bata gama duminiyar Jan layi da rubuta suna ba.
Lokacin da ya bada umarnin a Fara kowa ya bude takardar Amma sai wutar kowa ta dauke saboda yanda ya mako muguwar tambaya Mai sarkakkiya.
Sadeeq taji na magana a hankali, Anwar wannan 35 din zamuyi amfani da ita kuwa?
Ya kada Kai alamar a'a.
Yawwa na gode.
Bilkisu tayi zugum, Suleiman ya zungurota alamar ta iya?
Ta girgiza Kai ya ce to kawai tayi ta kwafo musu na Anwar.
Ganin ya Fara rubutun tayi saurin maida hankali don samun abinda zata tsira.
Kamar injin haka yake rubutun zu..zu..zuu kafin tayi layi hudu har ya juya , haushi ya turnuketa bai jira ta gama? Wannan wace irin mugunta ce?
Nan da Nan ta zuciya kawai sai ta ci gaba da rubuta shirme.
Gara naci zero da in yi naka ....ta fada cikin zuciya.
Kafin kace kwabo har ya gama ya janyo wata sabuwar takardar, ya canza biro black ya ci gaba da rubutu, sakamakon ta farkon da ya Fara da blue biro.
Tana kallon sa ta wutsiyar ido ko ya Turo mata wacce ya Gama da ita ta rubuta sai ma ya sanyata kasan tashi , idanun ta har ruwa ruwa sukeyi saboda fushi .
Wallahi Ni da Anwar har abada au Ni zai ma rashin mutunci?
Duk inda ka waiga kowa sai mazurai yakeyi an kasa rubuta abin kirki.
Tana kallon sa ya gama kawai yasa hannu biyu a kirji.
Kamar tayi ta tsunkulinsa takeji don takaici.
*stop writing*, ya Fara karbar wadanda ke gaba layi layi........ai kamar jira akeyi ajin yau dauki gungunai.
Jin haka kawai taga ya dauro mata takarda bisa tata.
Sunanta, number, course code.....da komai da komai.
Ta zaro ido Wai Daman biyu yayi tawa da tasa?
Tayi saurin kallon sa, ki soke wannan shirmen da kikayi kisa mistake. Ta kalli takardar ita ce ya Fara solving da blue biro.
Suleiman ya Fara kunno Kai zai Fara kwafa , malamin har ya zo wurin su, duk suka Mika.
Shiru Suleiman din yayi yama rasa meye zaiyi don takaici, Tabbas yasan don Shi Anwar yayi haka.
Ta kalli Suleiman din cike da damuwa ka gama kuwa?
Wallahi banyi komai ba ya fada Yana kakaro murmushi,
Innalillahi..... Ta juya zata ma Anwar magana Ashe har ya bar class din.

Ta waiga ta Kara waigawa Amma Ina tuni yabar shiyyar class din ma.
Kayi hakuri , ta juya tana ma Suleiman magana.
Nima wallahi har na sadakas, ashe rubuta mun yayi. Kai Anwar karshe ne wallahi.
Murmushi kawai yayi.
Ai kaga da ya barni na kwafa har kaima kayi.....kayi hakuri Suleiman.
Haba ba komai wallahi. Ya fada Yana Yar dariya.
Haka suka fito duk jikinta wani iri.
Kai Anwar case ne. Watan Shi dole inba wulakanci yayi ba baya taba Jin dadi.
A bakin kofa sadeeq ya karaso Bilkisu ya test din....yawwa sadeeq zo kaji Dan Allah. Ta yi gaba Yana binta.
Sun danyi nisa kadan inda ba mutane sosai ta tsaya.
Ka ringa yi ma Anwar fada Dan Allah Shi me ya dauki rayuwa?
Me yayi ba dai tashi yayi ba ya bada ba tare da ya baku ba?
Hmmm , kusan haka.
Kaga yasan tare nake da Suleiman na Kuma fada mishi Amma sai ya hana in copying Yana ta sauri sauri Ashe so yakeyi yaci lokaci yayi nawa yayi nashi Kuma don mugunta bai bani ba har sai da za'ayi submitting saboda Allah ya kyauta?
Tun tsirewa yayi da dariya, Dan iska, abinda yayi kenan?
Wallahi kuwa, kaga ai Babu dadi.
Gaskiya ba dadi.
Kiyi hakuri Dan Allah Yana Ina yanzu?
Kasan halinsa ai, har ya gudu ya tafi.
Kiyi hakuri Zan mishi magana.
Ka kyaleshi Daman idan ka lura bai niyyar Zama Dani ba yau tun safe yake ta wani Shan kunu..... Baki tunanin ko kin Masa laifi? ...Laifin meye?
Jiya ne mukayi Zan kirashi a waya na manta inaga kilan shine ......shine ma kawai.
Mtseww.....to kyaleshi .
Anwar na Bilkisu.... Bilkisu ta Anwar ai in ba keba Shi.
Kai ai kyaleshi zanyi don ban iya hakurin wannan mugun halin nasa.
Dariya sadeeq keyi sosai.
Ta wuce fuuuu.
Waya ta dauka, ta kirashi.
Yana tsaye zai siyi *Pepsi* yaga Kira.
True caller ta bayyana sunanta a screen din wayar sa *Balky gada*
Kawai sai yaji gabansa ya Fadi ras!
Ya danyi murmushi....... Hello
Kana Ina?, Ta fada?
Cikin dakewa kamar bai San wake magana ba yace Ina Ina?
Eh kana Ina?
Wake magana ne?
Bilkisu.....kana Ina Wai?
Wace Bilkisu ? Ya Kara bukata.... Dariya ta kusa kubuce mishi Jin har ta Fara hasala.
Bilkisu Gada ....... Oh ya fada tare da yin shiru.

Au shine kayi shiru mtseww.....ta katse waya.
Yabi fuskar wayar da kallo Yana kyalkyatar dariya ohh ni Hamza tawa ta sameni.
Wai yarinyar nan idan Sona takeyi haka zata shigar da kanta da tsiya ba da ARZIKI ba?
Ni wallahi na Fara tsarguwa da tambayoyin da nake faman amasawa kullum akanta .
Ya kirawo ta......kamar bazata dauka ba har ta fito cikin makarantar sun rabu da Suleiman tun a bakin gate.
Ai naji kana ta wani rainan wayo saboda nice na kiraka ba credit Dinka ba. .......Allah ya bada hakuri. Kina Ina ne?
Ni na Fara maka wannan tambayar baka bani amsa ba don haka........ohhhhh na ma hangoki.
Kawai ya kashe wayar.
Ta Fara waige waige....
**************
*KADUNA RIGASA*

Kutumar bala'i .....Kai Wai me aka daukeni gidan nan?
To bafa Zan Dauka ba.
Daman some somen hauka zubda miyau, Ni fa ko lallashin da akeyi ma Amarya ban samu ba, bani da wata kima sai ta bisa gado ya iya lallaba da lallashi bisa gado....yau za ayi ta takare.
Ta tashi Yana kwance rubda ciki, ta banka kofar da karfi har ya Dan razana....kace nan ba gidan mu bane daman na ce Nan din gidan mu ne?
Ya dago Kai da sauri ....kada ki kawo man hauka....an kawo ma hauka kayi maganina Mana mijin tace?
Nine mijin tace?
Kaine......kana da wani sunan da yafi wannan shanyayye?
To Bari kaji in fada maka idan an shanye ka ni ba'a shanye Ni ba, ba malam ba boka amma dole ka maidani gidan ubana bani wannan wahalallen auren naka marar fa'ida..... Ke ba a Isa a Gaya miki gaskiya ba ko? Duk lokacin da kikayi kuskure aka nemi a Miki gyara......haka ake gyara a wulakance da cin fuska?
Ai Daman kallon ka nakeyi tun kafin in zo gidannan kake nuna mun bani da wani matsayi sai matarka..... Shut up.....ya daka mata tsawa......bazanyi Shurin ba......ita ma ta daka mishi tsawa....ka sake Ni a yau Mana idan kana ganin Kai ke iko da kanka ba wat ke juya ka ba. Idan Kuma baka iyawa .....ta bude kofa kazo ka wuce ka tambayo ta idan ta amince yau ka bani takarda ta ita wacce ke auren naka.
Kai Bari kaji in fada ma Bashir.....wallahi wallahi baka cikin tsarin mazan da nake so in aura saboda Ni duk Mai mata baya gabana musamman Wanda bai da gabata irinka sai abinda aka gindaya mishi.....Ummi Ashe Baki da kunya?.... Yau ne kasan haka?
Kai baka iya maganin rashin kunya ba?
Ka je ka tambayo ta ya ake maganin marar kunya sai kazo kayi hakan Dani mijin tace....fuuuuu ya tashi yabar dakin ta bishi tana balbala bala'i ta inda take shiga Bata Nan take fita ba....idan hankalinsa tayi dubu yau a tashi yake, yayi hanyar dakin Amirar....ta daga murya....Arrrrrr Ni nasan baka da idea din kanka sai wacce aka saka maka.......nesa nesa yake Jin maganar.
Da karfi yake buga mata kofa.....a rude tazo cikin tsoro take magana...wanene?
....ke bude nine....da sauri ta bude....lafiya baban Ahmed?

Waccen yarinyar Bata da tarbiyya Amira wallahi wallahi ban tunanin Zan iya Zama da ita.....Nan da Nan tamu ta mata ta motsa ( kishi )....to Yanzu me kake nufi?
Zan kwanta anan ne saboda........saboda ita tafi karfin ka?
To ba anan ba wallahi.
Ta barshi tsaye ta shige dakinta kawai tasa key........
Ya zaro ido😳😳😳😳

Nima na zaro nawa😳........✍🏼

Ayi hakuri da kadan.......✍🏼 *ZAINAB WOWO*
*Maman Abdallah*💖
[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
09

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*
*Wallahi tallahi inajin dadin masu kirana da mun text WhatsApp musamman don jinjinawa Aunty Rabi dayi Mata addu'a da masu yiwa mahaifina addu'a na gode Allah yabar kauna my fans my pride ana mugun tare irin sosai dinnan*💖🤝🏼.
*Arziki irin na Aunty Rabi kowa ke fata Wanda zaka ba kowa ba arziki irin nasu o'e ba daga mu sai 'ya'yanmu🙄 Wanda ya tsargu dashi nake*😏🤣🤣🤣🏃🏻‍♀️

_Wayata na bani matsala wallahi Shi yasa bana update da wuri_

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

*Ke ta tabance UMMI MAMAN KHAIRAT DA ZARAH, makwabciyar Alawiyya Ina godiya*

👉🏼 *Unex*💖( Babu kamar ki ).

*Alawiyya Ina Kara godiya fa Allah yabar tare Allah yabarki da malam ya tsone idon munafukai*😄

👉🏼 *AUREN FARI FANS*💕💕💕💕one love well.

*INA CIGIYAR MZ*🗣🗣🗣😄

***************

*KADUNA RIGASA*
Tabbas Ummi Taji uwar bari,

Ta zabga uban tagumi, competition zanyi da Amira wallahi dole in ajiye wannan jahilcin in kwatar ma kaina yanci. Mutane dake cewar duk namijin da yayi sabuwar Amarya uwargida ta Zama banza yau na karyata hakan, naga inda year gida ke fin Amarya daraja da kima.

Tun kafin inzo gidan Nan yakeyi man gargadi akan matarsa, ban Kara tabbatar da hakan ba sai da nazo, Bata laifi, bata gundurar sa. Ya Zama wajibi Nima nabi hanyar da tabi don mallakarsa.

Ranar ya koma aiki, tunda ya tafi tana bangaren Amira suna fira, abin ya bata mamaki ganin ba wani alamun sauyi daga fuskarta, ta sakar Mata jiki suna ta fira Mai dadi ( ba abinda yafi Zama lafiya dadi, abinda mutane suka kasa ganewa kenan ).

Ta Dan muskuta Aunty wata alfarma nake nema wurin ki.

Ta kalleta cikin natsuwa sosai kafin tace Ina jinki ummi.

Wallahi Aunty na rasa gane Kan Abban Ahmad ko wane lokaci duk abinda nayi Ni Kam ban iya ba.

Kinga ko abinci na dafa mishi idan na kawo mafi yawa fushi yakeyi yabarshi a wurin Koda kuwa nayi abinda yake so. Idan Kuma na sameshi daki...........ohhhhh na fahimci zancen ki. Ta katseta tana Yar dariya.

Baya Miki korafin Baki da kula?

Wallahi yanayi Aunty.

Yawwa, kin gane, Shi mutum ne Mai son kula gaskiya.

Misali: wurin abincin da kike korafi, Shi yafi so idan Kika kawo mishi abinci ko ki zauna kuci tare, ko Kuma ki zauna kusa dashi yanaci Koda kuwa kin koshi, ya tsani ki bashi abinci kibar wurin.....ke abinda ma yafi so Bari in fada Miki shine ki na bashi da kansa.

Ya tsani lokacin da yake zaune dake ki maida hankali akan waya ko kallo ko wani abu saboda Shi mutum ne Mai tsananin son kula.

Ko a kwanciya ya tsani mace tayi mishi tababababaaa Nan da Nan sai ya harzuka.......gabanta ya Fadi...tohhh wannan dalilin ke sawa kullum sai sunyi rigima?

Ikon Allah.

Ta yi shiru dai, taji Amira ta shiga ranta sosai ganin ba bakin ciki ba Jin zafi ta zauna tana Mata irin wannan bayani Mai tsada Wanda ta tabbatar idan ita ce bazatayi hakan ba.

Kunya ta kamata sai kawai ta sauko bisa kujera.....Dan Allah Aunty Amira kiyi hakuri abubuwan da nayi a baya wallahi hada zuga irin ta mutane Amma Yanzu na gane........Dan Allah tashi ki zauna ba komai. Shawarar da Zan baki shine ki kuji fitar da sirrin auren ki ga ko wanene wasu ba shawarar kwarai zasu Baki ba, ko meye kiyi keda mijinki ba Wanda yaji ya gani ko wace Kika gani gidan aurenta wallahi hakuri takeyi. Shi Aure 90% hakuri ke raya Shi sauran 10%din ne ilimi da soyayya. Saboda haka Dan Allah ki zauna mu fahimci juna tunda kaddara ta hada mu ba kanmu aka Fara ba iyayenmu da kakanni duk haka muka gansu Kuma zamansu lafiya ba don Babu kishi ba sai don hakuri da hangen nesa.

In shaa Allah Aunty Zan kiyaye Allah yayi Mana jagora..........

Tirkashi, competition zai tashi muje zuwa muga cikin Amarya da uwar gida wacece zata amshi first position????????

**************

*Federal University dutsinma*

Yana son buga tsalle ya kasa , kanshi ya kumbura jinshi yake Babu kamar sa, ya gyara kwalar rigarsa sannan ya kalleta sama da kasa I warned you several times but u refused to listen to me, idan takamar ki *Hauka* ki sani Nan school din akwai *iyayenki*.........Shima yasa Kai yabi bayan Bilkisu. Wuri ya dauki ihu.......mufeeda tayi tsaye ta kasa motsi tana sonyin kuka Amma ta daure kada ta Kara zubda ma kanta abin magana......
Yasan wata sabuwar rigimar ce, tana niyyar Zama Aisha tace me Kuma ya faru naji ana ihu?
Ni da waccen sakaran fa, ta tareni jiya suna mun wani kuri na banza akan Anwar shine na kaita gabansa nayi Mata nawa gargadin ta gane cewa ni ba tashi nake ba........wa?
Aisha ta bukata tana zaro ido.....dai dai lokacin da ya karaso tayi kamar Bata ganshi ba tace *Anwar* Mana.
Me nayi? Ya bukata tare da tsareta da ido,
Wai ke me yasa bakya Sona da kwanciyar hankali?
Ta kalli Aisha tana Yar dariya kinji fa?
Sannan ta kalleshi, Da sunyi mun tsinannen duka jiya ai Ni Dana shiga tashin hankali ko? Ya zaro ido, duka?
Ta balla mishi harara wallahi tallahi duk ranar da ka janyo mun duka wajen ajabon Yan matanka a school dinnan har Kai sai sunja maka bala'i don security office zanje nayi reporting......ya kyalkyace da dariya Yan matan nawa ne ajebo?
Ke meye naki da zasu dake ki?
Ban sani ba kaje su baka amsa........ya Kara dariya matsa in zauna.....da sauri ta matsa ganin Yana kokarin Haye Mata kafa.......kana da hankali Anwar?
Wani lokacin Ina taba hauka,, ya fada Yana dariya.
Aisha Mike Kai wallahi bazan biye muku ba Bari in koma baya inyi karatu.
Ita da yunkura zata tashi yayi saurin rike habar hijab dinta ya mayar da ita ta zauna....... Ba inda zakije wallahi.
Wai ke me yasa kin rainani?
Idan kina son abu gardama banayi sai nine Zaki ..........zaniyi me?
Mutane fa na kallon mu ya sunan abinda kayi?
Aisha ta girgiza Kai ta wuce tana murmushi.
Tasha mur, karatu zanyi ko ka tashi ko Kuma Ni na tashi.......babu daya ciki. Kiyi abinki bazan dameki ba.
Gobe ne birthday dina me Zaki bani gift?
Tayi murmushi kai dai ka cika roko wlhi. Zan siyi ledojin pure water na ba Yan class suyi maka wanka,
Tabbb, ai bazan zo class ba gobe saboda hakan.
Wasa kakeyi ......
Allah kuwa.
To shikenan ka huta.
To meye Zaki bani?
Ta kalleshi cike da kosawa to meye Zan baka ne?
Gift!, Yace Yana Yar dariya.
Ta Sha mur, ka Fadi abinda kakeso Zan baka.
Zakiyi mun special girki, sannan ki kaini shopping.......... Ta kyalkyace da dariya.

Yabi kumatun ta da kallo Yana son dimple dinta ainun.
Shikenan Zan maka what next?
Karfe nawa zanzo?
Da safe kafin na tafi class kaga gobe har 6 Ina school.....no is too early. Bayan magrib dai......... Bana fitar dare sai dai kazo 2 kafin muyi lecture 4........ Hmmm shikenan ya fada ba don ransa yaso ba sai don gudun kada tace duka ta fasa.
Tare suka shiga test din ka kujerarta ga tashi. Ta kanga mishi fuskar computer din Yana tashi yanayin nata.
Sai gashi suna gamawa taci 20/20 Shi Kuma Yana da 18/20.
Tayi ta tsalle tana Murna.
Sun jero sai dariya takeyi tana Jin dadi, ta kalleshi yau wace rana naci CBT 20 last session wallahi naci da yawa 11 ko 12.
Murmushi kawai yayi.
Ta hango su Aisha shikenan bye bye wanna go thank you till tomorrow.
Ya juyo zai magana tuni ta tsallaka tana sauri so takeyi kawai ta Basu labari.
Ya danyi tsoki kawai ya wuce.
Nawa kuka samu?
Aisha ta yatsine fuska 13, khausar tayi tsoki Ni 10....... Wallahi saura kadan na shiga cikin department dinku Kinga ruwan Yan 7,8 da 9?
Ta zaro ido wallahi Anwar yayi mun duka na cinye........duk suka zaburo 20?.
Cike da Murna tace wallahi kuwa.
Ohhh Allah ya kashe ya Baki inji Aisha.
Ai yau nayi sa'a Kuma wallahi ba layi daya muka hau ba.
Yana tsaye shagon Abdul ya hangosu.
Kamar ya kwada musu Kira kwatsam sai ga Dr Dan Musa ya tari gabansu.
Bilkisu see me by 2 in ma office........okay sir. Ta ce kawai suka wuce.
Wahalalle naga ubanda zai gani.
Baki zuwa? Inji khausar,
Eh, kullum aikin kenan kuma ba wat maganar arziki ba kame kame.
Anwar ya bishi da harara lokacin da yazo zai gitta.
Bayan sallar la'asar ta tafi dakin su Jennifer sukayi mata kwatancen gidan zainab wowo wacce keyi wa Yan makarantar cake. Ta iya cake sosai na biki da birthday ga sauki.
Aisha ta rakata. Mata Mai fara'a ta amshe su hannu biyu biyu.
Sannan suka ce cake sukeso na birthday Amma na maza.
Tace ba matsala.
Ko na nawa kike so Zaki samu. Kuma karfe nawa? Akwai Wanda Zaki ba yakai man goben wajen 1:30 haka?
In shaa Allah bani number da za a nemeki da ita.
Sukayi musayar number ta biya kudin babban cake na gani na fada.
Bayan sun fito ta kalli Aisha Zan surprising din sa ne.
Suka biya super market ta siyo manya manyan lemuka carton daya *na grapes*
Hmm kawai Aisha ta ce tana murmushi.
Ta harareta, Fadi ta cikinki Mana, *there's nothing ooo just wanna surprise him and show my

gratitude on what he has done for me Sha*
I knew, inji Aisha tana Yar dariya.
Karfe shidda na safe ta tura mishi text ```Happy birthday Anwar wishing you more dollars in your account, you are an amazing person stay blessed```
KO minti daya ba'ayi ba yayi reply
``` Thank you my personal person```
Murmushi kawai tayi.
Shi kuwa ya karanta text din yafi sau dari.
Ko wa ka gani a class da ledar pure water saboda Shima haka yakeyi wa mutane Amma ba Anwar ba alamar sa, ko su sadeeq Basu San cewar baya zuwa class ba.
Bilkisu kadai tasan haka.
Sadeeq ya karaso kusa da ita hajia Kira Mana Anwar please...
Tayi murmushi yace yau bazai shigo school ba.
Aji ya dau surutu suka ce ko hostel ne yau sai sun bishi.
Kamar yanda sukayi alkawari da zainab sai ga cake...... Cake abinda ka cake sky blue yayi kyau karshe an nado Shi a leda cikin kwali. Sai kamshi ke tashi. Flowers din sunyi kyau Mai Rose ne da wasu design cake din ya tsaru.
Tana kwance daki ya kirata.
Yana jiranta bakin hanya.
Ta ce toh, sanye yake da round neck shirt orange Mai ratsin fari a jikinta an rubuta *You are mine only* a gaban rigar. Dark blue jeans ne wandon da facing cap Fara anyi rubutu orange *Mine for ever* daga sama.
Kunnensa like da ear piece. Kanta a kasa tana tafiya a hankali.
Ya saki ajiyar zuciya kadan idonsa na kanta har ta karaso.....
Murmushi ta sakar mishi kafin tace happy birthday once again.
Godiya! Ya fada Yana latsa waya Shi adole ba kallonta yake ba.
Ta harareshi dai dai ya Dan dago.
Yayi murmushi ko amsar Bata Miki ba?
Yayi kyau karshe....ta fada a zuci a zahiri Kuma tayi shiru kawai.
Muje.......tace tare da yin gaba kadan.
Ki jira muyi hoto Mana..... Da wa? Tabb
Ya Dan Sha mur, dake ko bazakiyi ba?
Eh, tace tana Kara ci gaba da tafiya.
Yaji haushi sosai.
Are you serious? Ya biyota.
Ta Dan waigo *did I look like a joker?*
Dan Allah kizo muyi pic Bilkisu........ Ta zaro ido Wai da gaske kakeyi?
Sai ta danyi dariya kawai ta sunne Kai....
Ya ja tsoki, don ya karanci kunya takeji.
Suna Isa shagon ta ce me kake so?
Ya Sha mur Yana fushi duk abinda ya Miki.
Tayi kamar Bata lura ba ta amso meat pie da soya milk drink na cikin kwalba Mai tsadar guda goma.
```

Ta fito, gashi sai me?
Ya karba da hannu daya dayan Kuma Yana latsa waya. Yace shikenan thanks.
Duk taji ba dadi kamar tace suje to suyi hoton Amma gaskiya Bata iyawa.
Suka jera zuwa bakin hanya sai fushi yakeyi.
Zaka koma hostel ne?
Akwai abinda Zan Miki ne idan na tsaya?
Zan baka sako ne muje da mashin din a bakin gidan mu ka karba....... Ki je ki kawon Ina Nan.
Har lokacin fuskarsa ba fara'a.
Ta langabe Kai Wai Anwar fushin na menene?
Mtsew kawai yaja guntun tsoki.
Kaji?
Oh my God , me kike so Yanzu Wai?
Muje ka karbi sakon.
Jeki gani Nan zuwa.
Har zata Kara magana sai Kuma ta fasa ta wuce don itama ta Fara kulewa.
Tana niyyar shiga gida taji tsayuwar mashin, da sauri ta waiga sai kawai tayi murmushi ganin shine ya Dan harareta.
Tayi ciki tana dariya.
Kwalin lemun ta Fara fitowa dashi tasa agaban mashin din sannan tace Ina zuwa ku jira.
Ta dawo da cake din ta Mika mishi ga cake kaci sosai........ Da sauri ya kalleta.
Tayi murmushi.
Kamar zaiyi magana sai Kuma ya fasa yace da Dan mashin din muje.........
Kamar tace dawo muyi hoton Amma bakinta yayi nauyi.
Haka ta shiga gida sukuku............
A hostel party sosai akayi yaji dadi abinda tayi mishi Yana son Allah ya kawo ranar da Shima zai Bata mamaki. Amma rashin yin hoton nan ya Bata Masa rai matuka, ya Fara gajiya da halin ko'inkula da ta keyi mishi, yanda Yan Mata ke rokonsa akan suyi hoton dashi Amma shi yau yabroki mace suyi taki amincewa *dame Bilkisu ke takama?*
Wajen Sha biyu ya tura Mata text *Thanks for the cake* sai da safe ta gani.
Bata Sami halin reply ba.
Yana zaune ta shiga class din Koda suka hada ido tayi murmushi Shi Kuma ya daure fuska ya kawar da Kai.
Gabanta ya fadi, ranta ya Fara baci menene abin Jin haushi daga tace bazatayi hoto dashi ba?
Ya taba ganin tayi hoto da wani ko wata?
Ta ajiye books dinta ta Isa wurin sa.
Ina kwana?
Ya dago Kai tare da cire ear piece. Ya kalleta Yaya? Fuskar sa ba yabo ba fallasa,
Zamuyi macro after this lecture please if you are free........ It's alright. Ya fada a takaice.
Ta juya ranta ba dadi.
Yan aji sai zolayar sukeyi jiya yaji tsoro baizo class ba kada a mishi wanka yana ta dariya da yazo zasu hada ido sai ya kawar.
Duk taji babu dadi.
Ana Gama lecture wasu suka shigo alamar venue din su ne.

Fitowa sukayi, ajin dake hade dashi ba mutane sosai Yana tsaye bakin taga tace Anwar muje Nan naga ba kowa......... Anwar let's snap please Helen ta karaso tare da dafa kafadarsa....... Wani dadi ya ziyarce Shi yace anzo wurin.
Ya kalli Bilkisu okay jirani Ina zuwa.
Kawai suka Fara hotuna. Kamar jira akeyi sai ko wace ta taso wasu ma wucewa zasuyi ga Anwar da farin jini
Nan da Nan hankalin Bilkisu ya tashi ta kasa daurewa ganin yanda suke faman rikeshi wasu na kwanciya kafadar sa.
Ta shiga ajin idanun ta duk sunyi ja.....
Yafi mintuna talatin tana zaune ta ma kasa tashi suk tana hangensu ta taga.
Sadeeq ya karaso maigadon ya naga kinyi zaune baku Fara ba?
Eh, hotuna yakeyi yabar Ni Nan kamar sakarai, ta fada a wahale kamar zata kurma ihu.
Malami ya shigo yace ku fita zamuyi darasi......
Haka suka fito tare da jingina jikin icce ita da sadeeq har lokacin hotuna sukeyi ko kallon inda take baiyi ba.
Sadeeq ko zamu je ka nuna mun Dan Allah? Ta fada Rai bace........ A 'a ki jira ya Gama kinsan halin mutumin....wallahi yau Kam bana so ko da kuwa yazo.
Tohhhh..... sadeeq yace kafin ya Kara magana sai ga Anwar din.
Bilkisu muje.
Ta kalleshi kallon da ya gwammace bugu dashi sannan tace bana so kaje kawai.......
Duk akayo musu ratai da ido.
Nan da Nan ya hasala don yasan a rina iyakar rainin wayo yarinyar nan ta daukeshi sakarai, Saboda me Baki so? Ya bukata a hasale....
Ina ce hoto ne a gabanka, ko? Ina jiranka mintuna kusan talatin.....Kai ma abokina meye haka. Zanci ubanka sadeeq...ya daka mishi tsawa.
Kada Allah yasa taso waya rasa?
Don kinga Ina lallabaki naje nayi hoton me ya hana kizo ayi dake?
Ko Zaki hanani ne?
Sadeeq zai Kara magana ya nuna Shi da yatsa a hostel zamu hadu zanga ubanda ya tsaya maka kaima......duk suka zaro ido lallai fa da gaske yake. Sannan ya kalleta kada Allah yasa kiso ke Kika rasa........ Ya wuce fuuuuu ya fada wani class ya zauna Rai bace kamar zaiyi hauka idanun sa sunyi jawur.
Bilkisu ta rasa inda zata Sanya kanta, kuka zatayi ihu zatayi, itama nata idanun sukayi ja tare da kawo ruwa kamar zatayi kuka abin yazo kaina?
Hakan take ta nanatawa cikin zuciya.
Sadeeq ya kalleta hankali tashi, wallahi fada zamuyi dashi tunda Kika ji ya rantse....... Ta zaro ido fada?
Hmmmmm Baki San halin Anwar ba..... Sai akwai tabar Shi nan ta wuce class din da taga ya shiga....
Yana zaune ya hade Kai da table. Ta zauna kujerar gabansa, ta Kira sunan sa,
Anwar!..
Ya dago da sauri sai da gabanta ya Fadi ganin yanayinsa.
Ta daure ta Kura mishi ido zuciyarta kamar zata fito amma ta daure kada tayi sanadin raba

abokai . Ta Fara magana a hankali.....
Ba ruwan sadeeq cikin maganar nan, kada laifina ya shafeshi duk abinda zakayi mishi kayi mun Amma kada ka Sanya Shi ciki kayi hakuri ka kyaleshi .......bazanyi hakurin ba. Ya fada kamar zai mareta.
Duk ajin akayi shiru ana kallonsu,
Ya daga murya, ke har Zaki ce na Bata lokaci Baki so na koya miki? Ni idan naje wurin malamai su koya mun korata sukeyi wani lokacin sai na kwashe fiye da awa daya sannan suce in tafi in Basu wuri, bana zuciya gobe sai na koma sai ke daga Yan mintoci Zaki nemi kiyi mun wulakanci cikin jama'a?...... Naji kayi hakuri,......
Bazanyi ba nace ki tashi ki bani wuri.....gabanta ya Fadi.
Ta daure ta hadiye kwallan dake son taruwa a idonta tace sadeeq nake nufi kayi....... Bazanyi hakurin ba ya Mike, idan ke bazaki tashi ba ni na tafi.....kawai yabarta wurin.
Na shiga uku ni Bilkisu ta fada.
Tashi tayi tabar class din don kwallar sun kasa tsaiduwa.
Ni Anwar zaiyi ma wannan wulakancin? Ni Anwar zai dizga?
Ni Anwar zaiyi ma gorin karatu?
Me yasa tun farko na bashi fuska?
Idan sai Anwar ya koya mun karatu zanci jarabawa billahil azim na hakura da degree har abada. Biji biji take ganin hanya....ba abinda kanta keyi sai sarawa, kaicho na ni Bilkisu na kyale Anwar har abada tallahi ko kallonsa bazan karayi ba.....ta bude daki ta fada bisa katifa sai kuka.........
Hankalin sa yafi nata tashi, kamar mahaukaci ya Isa daki Anas ne kwance ya fada bisa katifa Anas na shiga uku nayiwa Bilkisu wulakanci.
Ya zaro ido me ya faru.?
Yarinyar nan kureni tayi yau, na rasa ta inda Zan bullo mata.....naji me ya faru.
Ya Mike kamar mahaukaci.......laifinta ne nasan gobe zata Kara bani hakuri. Zamu shirya .....ya fice dakin.
Duk duniya Yanzu Babu Wanda takejin tsanar say ranta irin Anwar ko sunan sa Bata so a fada ta fita batunsa Amma kullum cikin kuka take.
Kwananta biyu daki kwance ta kasa zuwa lecture saboda Bata kaunar Kara ganin sa.
Shi Kuma jira kawai yakeyi tazo ta Kara bashi hakuri su dai dai gashi Yana ganin ya zubda ma kanshi class matukar ya kirata a waya, abinda bai sani ba har ta goge no. Sa cikin wayarta.
Abu kamar wasa kusan sati Bata zo school ba, sai dai kullum tabi dakuna ta karbi note tayi. Ranar laraba ta Kama kwananta tara rabonta da school Shima tazo ne dole saboda za'ayi C.A Kuma course din da tafi tsoro.
Dadi ya kamashi yasan dole yau ta nemeshi.
Yana zaune Yana koya masu Helen ta shigo gabansa ya Fadi ganin irin ramar da tayi though Shima ya Dan fada.
Layin da yake Bata kalla ba ta Isa can baya, Damian please help me here ta fada a hankali..... Ashe bai iya uwar komai ba nan da Nan hankalin Anwar ya tashi ganin ana koya Mata wrong. Helen ta zungureshi ga fa Bilkisu..... Eh na ganta, tana fushi dani ne Kinga taje Damian na koya Mata hauka. Mtsew ya buga tsoki.
Ya kasa ci gaba da koya ma Helen din.

Damian na gamawa tabar class din sai lokacin test ta dawo.
Tana shigowa ta hango sadeeq ta Isa wurin Shi....... Alhamdulillah dama Ina ta addu'ar kada a riga ni.
Yayi murmushi kawai, tare suka zauna ya Bata ta kwashe hankalin Anwar na kansu kamar zai haukace.
Tana gamawa taje tayi submitting tayi tafiyarta daki Koda Anwar din ya fito bai ganta ba ya Kara hasala....... Sadeeq na fitowa ya Fara surma mishi Zaki har Yana yunkurin dukansa Wai ya zauna tare da Bilkisu test.......🤣🤣🤣🤣🤣🤣 Tirkashi.

Ayi hakuri da kadan...✍🏼. Zainab wowo ce💖😄
Juma@ mubarak don't forget to receive suratul kahfi👏🏼
[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
0️⃣7️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

*Ina alfahari daku kawayen yarinta:*
*Rakiya Amadu m/bread da badiyya Amadu m/bread*

***************

*Federal University dutsinma*
Aisha, sumayya da khausar sune kawayen Bilkisu na kut da kut!, Tare suka zo makarantar secondary school daya sukayi watan federal Bakori dake shiyyar funtua ta jihar katsina.
Aisha da sumayya political science sukeyi, khausar na micro biology sai ita Bilkisu dake Economics.
Su ukun dakin su daya, Bilkisu kadai ke nata dakin.
Mafi yawa su ne suka fi zuwa dakinta ko a secondary ana tare Amma ita komai nata daban ne.
Tana yawan yin girki baka raba ta da ko miya ce Shi yasa Mafi yawa sune ke zuwa wurinta neman abincin musamman irin lokacin da semester ta raba tsakiya komai yayi zafi.
Khausar na bala'in son Anwar Amma tun lokacin da ya dizga ta daga magana taji ya fita ranta.
Aisha ce ta shigo dakin tana ta kokarin yanka carrot da zata Sanya cikin farar hinkafar Daman tun safe kafin ta fita tayi miyar kifinta.
Ke yunwa fa nakeji har bana gani.
Tayi murmushi to gashi Bata karasa tsanewa ba ko zakiyi tsame yau ma?
Mtsew tayi guntun tsoki, tare da kwanciya bisa lumtsetsiyar katifarta, wannan uwar shinkafar Kuma fa ko yau kin tabbatar zamu zo kwaraka ne?

Ta dan tabe baki Anwar ne Mana da rigimar sa nace zanyi girki Wai zaici na tafin mishi dashi class 4 idan zamuyi tutorial.
Hmmm, kawai tace.
Ta Dan waigo Fadi kada ta kasheki.
Ta kyalkyace da dariya keji Kama Kai ai bandai *furta* ba ko?
Murmushi tayi kawai,
Daga Nan Bata kara mata magana ba.
Yar madaidaiciyar cooler ta samu ta zuba mishi miyar Kuma tayi amfani da Yar roba Mai marfi.
Saboda kurewar lokaci a daki tayi sallah tun kafin ta sallame yayi mata missed call biyu.
A gurguje ta shirya ta fito.
A bakin gate ta kirawo shi, bugu daya ya dauka.
Malama kinfa shanyani,
Ya hankuri gani na shigo school kana Ina?
Lecture room 2, ya fada.
Okay I'm coming......ta kashe wayar.
Sanye take da doguwar riga ta lace coffee brown, hijqbinta kalar flowers lace din maroon.
Tana saka kafa wayar ta na Kara *Daddy ne ke mata video call* ta karasa da sauri tana murmushi.
Ya hangota Amma sai yayi kaman bai ganta ba har ta zauna kusa dashi dai dai kuma lokacin da ta ajiye mishi ledar abincin sannan ta latsa wayar.....Hello daddy. Ta fada tare da fadada murmushinta zuwa Yar dariya.
Yabi fuskar ta ta da kallo Yana masifar son tayi dariya Shi kadai yake ganin abinda yake gani.
Bilkisu ya kike?
Kina class ne?
Eh daddy kaga nazo karatu ne wurin Anwar ta kanga fuskar wayar saitin Anwar din.
Yayi saurin sunkuyar da Kai...... yarinyar nan nada hankali kuwa?
Anwar?.......ya dago ido da sauri....barka da wuni Daddy ya fada da sauri tare da rusunawa Yana Dan murmushi.
Dariya yayi ......Kaine Anwar? Yau ba'ayi fadan ba kenan?
Ya zaro ido kadan kunya ta baibayeshi yayi saurin kallon Bilkisu atuhumce.
Ta janye wayar.....mun shirya daddy yaban hakuri ta fada tana dariya.
To yayi kyau. Allah ya taimaka a kula dai kada amanta Allah Yana tare da kowa a zahiri ko badini.
Na sani daddy.
Ta zaro ido Wai daddy kana sokoto ne???
Eh mun zo nida mommy bikin saifullahi ko?
Ta zumburo Baki daddy......ke sai anjima kuyi karatu kada lokaci ya shige......
Daddy zakuzo din ko?
Eh in shaa Allah zamu shigo jibi......yeeeeeee ta fasa Kara yayi saurin latse wayar Yana dariya.
Ta kalli Anwar su daddy zasu zo jibi......ya dalla mata harara. Ya akayi yasan muna fada?
Ta danyi guntun tsoki.... Ai sun Sanka Ina Basu labarinka sosai.....kina cewa me?
Tayi murmushi.

Kinji?
Hmmm kawai tace.
Magana zakiyi meye kike fada ne?
Ka gane sun San wajen ka nake daukar karatu to ya kirane yace yau bamuje karatu ba nace munyi fada dakai shine........yaushe mukayi fada?
Me yasa zakiyi karya? Sai kice fushi nakeyi dashi ba kice muna fada ba.......naji sorry oya muje ta bude littafin.
Ko sai kaci abincin zamuyi?
No, Zan tafi dashi hostel ne.
Okay.
Lafiya lau sukeyi tana ganewa sosai, yana magana tana satar kallonsa idan taga ya maida hankali ga littafin sai ta daddage kuwa ta Kura mishi ido.
Yana da kyau, natsuwa da Kuma kamala problem dinsa kawai miskilanci.....da yazo zai kalleta sai tayi saurin kawar da ido....haka..haka....sunyi nisa sosai sai taji an kwada mishi Kira ```ANWAR```.....
Dukkansu suka kalli wajen... Mufeeda ce.
Gaban Bilkisu yayi mummunan faduwa.
Saboda, mufeeda ana raderadin budurwar Anwar ce physics department take yarinyar ta hadu karshe saboda iya daukar wanka, Bata fi Bilkisu kyau ba Amma saboda iya gayun ta yasa idan tana wajen baza'a taba ganin kyan Bilkisu ba da kullum cikin hijabi.
Sanye take da wani material dinkin Riga da skirt, tayi kyau matuka fuskarta sanye da kwamemen glass ya mata kyau sosai.
......... Ta tsaya daga jikin taga alamar ganinsa take sonyi.
Kawayen ta Kuma na gefe suna jiranta.
Ya kalli Bilkisu please Ina zuwa, ya mike.
Wani abu ya taso mata ya tokare a makogoro tunda ta yi kasa da Kai bata dago ba.
Tana ta latsa waya ta ma kasa gane inane take shiga tana fita.
Agogo kawai take dubawa.
Mufeeda nada daukar hankali, kafin kace me.....Anwar ya fara shafa'a.
Ai nayi tunanin bazaka taso ba tunda ance tsoron ta kake ji.
Yayi murmushi sai kuma na taso Kika gane hakan ba gaskiya bane ko?
Wai meye tsakanin ka da yarinyar can da kullum baka tashi koya mata sai da marece Kuma ku biyu kawai?.
Yanzu dai gani. Ya fada Yana murmushi.....
Ta dalla mishi harara minti nawa ta baka ne?
Ni kamar baka cikin natsuwa ma wallahi. Baka daukar waya baka amsa gayyata idan ma an iske ka..... Ikon Allah mufeeda ki Bari zamuyi waya anjima Kinga Babu dadi......babu dadi ka barota kazo wurina?
Bai San lokacin da ya kyalkyace da dariya ba ......dai dai lokacin da Bilkisu ta dago Kai, kutumar bala'i....
Yana mamakin yanda yanmata ke tuhumar Shi akan Bilkisu.
Mikewa tayi ta hada litattafan sannan ta dauki ledar abincin kawai ta fito......
Ba karamin razana yayi ba don yasan kwanan zancen..... *Bilkisu*.......... *Bilkisu*....

*Bilkisu*!!!....... Amma Ina! Ko waige....
Duka yaushe ya samu suka daidaita, mtseww.
Please zamuyi waya ya fada tare da Dan rugawa *Bilkisu*.......
Sauri takeyi sosai, ya cimmata da kyar...Dan Allah kiyi hakuri.
KO kallonsa batayi ba.
Wallahi ban manta dake ba Ina cikin kwatanta mata naga kin fito......... Nace ka manta Dani ne? Ko kaji nace nayi fushi ne? Kaje ka gama da ita ni lokacin da kake free Zan dawo tunda nice nake nema a wurinka......kiyi hakuri Dan Allah.
Ta tsaya cak tare da kallonsa..... Banyi fushi ba, kamar yanda ba haushi naji ba, ai kana da damar ka ko?
Wannan bin da kakeyi mun Shi zai hasalani don haka ka koma ka kyaleni.......ya daga hannuwa sama, naji Amma kiban abincin Mana......wallahi bazaka ci Shi ba. Ta fada tare da wurga mishi kallon da yafi komai tsana sannan ta tafi tabar Shi tsaye.
Wai me yasa bazai kyale yarinyar nan ba?
Duk Yan mata na shakkar sa me yasa ita bata tsoron yi mishi gadara?
Ko ya ayyana zaiyi fushi da ita Shima me yasa baya iyawa?
Yaja wani dogon tsoki....... Ya wuce a fusace.

*******************

*KADUNA RIGASA*
Wannan ba shawara bace, kasan su mata shaidanin su babba ne, Basu da hankali ko kadan. Idan nayi haka mun Zama daya dasu kenan.
Abinda nake gani ka dawo gobe da safe kawai Bari na shiga masallaci na kwanta.
Amma yarinyar nan akwai Yar iska..... Ya dafa kafadar idanun sa kamar garwashi kada ka damu, mu zauna da safen...... shikenan Zan taho dasu hajia......noooo kada ka Kira kowa please.
Dole ya hakura ya tafi ba don ya so hakan ba ..... Abin Babu dadi hakan yake ta nanatawa a cikin Rai domin yasan kawaici ne yakeyi mishi saboda kada abotar su tayi rauni.
Ya girgiza Kai......zata ci ubanta goben.
Ina Kai Yara school 7:30 gidan Zan yi ma tsinke.
Hakan kuwa akayi,
Kamar kullum karfe bakwai Yara suka fito Yana hangosu ya fito masallacin saboda Babu Wanda ya gane a can ya kwana daga cikin masu aikin gidan sai Mai gadi.
Ya ce Ahmad je ka karbo mun mukullin motar mamar ka.
Da gudu ya juya, tana kitchen tana gyaggyara inda tayi aikin kayan break din yaran domin ( Amira tana da masifar tsafta Sam da yawa Bata jiran masu aiki musamman bangaren da ya shafi dahuwar abinci).....Kai lafiya ko jakar ce ka manta?
Abba yace ki bashi makullin mota.
Ta kalleshi sosai Ina Abban?
Gashi can ya fito daga masallaci....gabanta ya Fadi. Kamar zata Kuma tambayar Shi sai ta fasa ta tafi daki don dauko mishi.
Ya kura ma kofar ido ya kalli agogon wayar sa har da kwata tayi Yana mamakin dadewar da Ahmad din yayi sai gashi ya fito da gudu.

Ya Dan saki ajiyar zuciya har Almustapha ya Dan kalleshi abinka ga yaro bai hasaso komai ba saboda Babu kwalwar tunanin.
Duk abin nan tana tsaye jikin taga tana kallon su, Yana fita da motar ko layin bai shanye ba ta fito da sauri don komawa bangarenta, maimakon tabi ta hanyar baya kamar kullum sai ta fito ta kofar gaba, abinka ga babban gida kuwa tana mikewa zata Sha kwana Yana shigowa da mota. Gabanta yayi mummunan faduwa ta tsorata ainun sim...sim ...sim ...zata wuce ya fito. Wurinki nazo daman.
Ta yi zuru zuru da ido alamar rashin gaskiya Yaya Ina kwana ta Dan rusuna, ya wuce gaba muje daga ciki.......
Mai aikinta har tazo tana ta goge goge, saboda tana da nata makullin.
Yana shiga yace ke fita ki jira a waje..... Tayi saurin ajiye mop kuwa.
Tana bayan sa zugum tayi tsuru tsuru tsaye....waigowar nan da zaiyi kuwa sai kauuuuu ya wanka mata Mari ta gigice kafin ta saka hannu ya Kara wanka mata......sai kawai ta zukunne don girman Allah Yaya na tuba......ta fada cikin karaji tana kuka....
Dan ubanki kina tunanin kin wuce duka har Yanzu? Ke har Zaki rufe ma miji kofa Kuma nazo nayi magana kinji muryata saboda ki nuna bamu Baki tarbiyya ba shine Kika yi shiru. Ya daga hannu zai Kara Kai mata bugu yaji an rike hannun........Kana da hankali zaka Dakar mun Mata?....... Ya fincike hannun cikin bacin Rai....Dan ubanta ta wuce a dake ta ne?
Ya janye Shi, malam ba haka ake sasanci ba....Ni kiranka nayi ka sasanta ni da matata ba ka rikita man ita ba........ Sasanci? Kishin nata na hauka shine zaisa a sasanta ku? Sai dai in Mata rauni in karairayata Dan ubanta...kizo ki iske Shi da matar Shi da yaranshi ki nuna Baki kaunar su don Kina mahaukaciya har kiyi tunanin zakiyi daraja da kima?
Duk suka zauna lokaci guda...... Saurara malam.
Matsalar Ummi daya tsageranchi da wannan mugun kishin na kwatanta Mata Amira Bata da matsala......ko tana da matsala ba dole tayi hakuri ba tunda ta Aure Mata miji don ubanta.....
Dan Allah ka daina hargitsa lamarin nan.
Ummi koma can ki zauna.....ya nuna Mata kujera...ba gardama ta tashi fuskar har tayi fushi.
Wallahi tallahi ban auri Ummi don in mayar da ita zawara ba. Amma Ina Mai tabbatar maka da cewa muddin ta Kara kuskuren da tayi jiya na rantse da Allah sai na rabu da ita Koda zata kawo karshen alakar mu......saboda tun farko ita ce ta hada mu?
Noooo....
Then, what do you mean, wannan idiot din ta Isa ta rabamu ne? Daga alfarmar Dan ubanta?......Dan Allah ya Isa.
Ummi .....Ummi...ummi.
Ya Kira sunanta sau uku.
Ga Dan uwanki zan maki magana ta karshe daga yau.
Kina son Zama Dani?
Tayi shiruuuuuuuuu,
Ki bude Baki kiyi magana yau zanyi wa tubkar hanci.
Kin shirya Zama Dani?
Da kyar ta daga Kai alamar eh.
Good, to saurara.
Muddin kina son Zama dani sai kinbi wadannan dokokin wallahi tallahi inba haka ba Zan

sawwake Miki Yanzu matukar kikaji sunyi Miki tsauri.
Idan kuwa Zaki iya to ki sani Koda wasa Kika kuskure Nan gaba daga gone har shekara dari Nan gaba kada ki taba tunanin ban iya rabuwa da mace don na haihu da ita ba wallahi ko duniyar Kika safke mun sai na sallameki.
Na farko Amira wacce ta zame Miki damuwa tun kafin ki shigo gidan Nan. Matukar kina son Zama Dani sai kin Mata biyayya da kyautatawa, na biyu maganar abinci ya Zama wajibi kiba kowa hakkin sa lokacin da kike da dama. Na karshe Yan aikin gidan nan ki sani ba bauta suka zo ba neman abinci suka zo yi to ya Zama wajibi a kyautata ma nemansa ta ko wace hanya. Cin fuska ,izza da gadara bazan Kara dauka ba.
Allah ya gani naso in biki ta ruwan sanyi to maganar gaskiya yau na kafa shaida da yayanki akan kadan daga cikin wautar da kikeyi gidan Nan. Maganar iyaye na Kuma ko na Amira kice ma Baki sansu ba wannan kanki kikayi mawa domin duk Wanda ya kashe uwarshi to Shima baza 'a mishi kani ba.....
Wannan kenan shawara Kuma Yanzu ta rage daga wurin ki............

*************

*Federal University dutsinma*

Idanun sa jawur kamar garwashi ....dakin a cike Amma ana ganin yanayin sa kowa ya Fara zarewa one by one. Ko takalmi bai cire ba ya fada bisa katifa ruf da ciki.
Anas ma fita yayi sadeeq kadai ya rage.
Anwar......ya Kira sunan sa.
Bai amsa ba Amma ya dago Kai.
Lafiya dai ko?
Kamar jira yakeyi...... sadeeq bana tsoron yarinyar nan wannan Zan biye Mata fa.
Bilkisu?
Ya buga tsoki who else?
Me Kuma ya hada ku?
Simply useless girl din nan mufeeda tazo muna karatu she couldn't even understand abinda nake undergoing a wurin yarinyar nan ta fito a fusace, nayi Kiran duniya tayi burus Dani na bita Ina Bata hakuri shine ta barni a wurin ta wuce abinta, Kuma tana fada mun Bata ji haushi ba idan bataji haushi ba zata ce in daina binta?
In don Bilkisu zuwa safe za'a ga tana ma magana....... A da ko? Yanzu fa ko itace tamun laifi sai nine Zan Bata hakuri I called her on ma way here for more than seven times she refused to pick up the call.
Nawaoooo....sadeeq ya fada Yana murmushi.
To Wai meye ke kawo yawan fadan Nan naku? Ya kamata ku zauna ku gano Shi ......itace keda problem din buh I'll soon leave her and rest.
Are you sure?
Mtsew abeg leave me alone. Ya juya abinsa.
Waje sadeeq ya fita Yana kyalkyatar dariya. Zai so yaga ranar da ko wane zai ajiye girman Kai ya bayyana zuciyar sa, sun tsaya sai ba juna wahala sukeyi.
Bilkisu kuwa harda Yan kwallanta. Ko da mommy ta kirata ma bayan isha'i maganar batayi tsayi ba karyar kanta ke Mata ciwo.

Washe gari sai 11 suke da lecture.
Ta riga Shi zuwa, tasan cewa ya tsani Zama gaba sai Sami gefe kusa da Ruth ta zauna.
Lokacin da ya shigo har an Fara lecture.
Idanunsa na kanta har aka gama, malamin na juyawa zai fita ya Mike don yau lecture daya garesu gobe ma free ce idan ta fita shida ita sai jibi.
Can karshe take jikin bango Yana zuwa yace masu Ruth duk su fito zai zauna yasha bakin glass Yana sanye da shirt Fara Mai ratsin light blue haka da blue jeans.
Ta Kara tsuke fuska ta Mike itama zata fita kawai ya hawo bisa table din ya tsallaka ya zauna.
Dole ta koma ta zauna. Sadeeq na can baya Yana kallon drama.
Ina zakije bayan kin San don in zauna nace su tashi?
Ina da aikin yi ne.
Yayi murmushi na sani. Har Yanzu fushi akeyi dani?
Fushi ta kalleshi up and down ta watsar kallon da ya gwammace duka dashi kafin tace fushi akan meye? Kamun laifi ne?
A'a ya girgiza Kai.
To bani wuri in wuce ta mike tsaye, ya daga Kai me yasa kike son mun wulakanci gaban jama'a?
Kamar ta kurma ihu don takaici, ta dalla mishi idanu wulakanci? Simply don nace kabani wuri in wuce shine na maka wulakanci?
To jiya fa da........ Anwar na tsani tariyo duk abinda ya wuce a rayuwata kullum Ina hangen abinda gaba zatayi. Ban wuri in wuce jiya Kuma Kai ta shafa bani ba.
Amma ai na Baki hakuri ko?
Ikon Allah nace ban hakura bane? To idan kin hakura ki zauna mu Kara abinda muka Fara jiyan.....tayi murmushi Mai Kama da kuka Allah ya albarkaci abinda mukayi din ya wadatar wallahi bana so na yafe.
Ya kife Kai bisa table....shikai yasan yanda zuciyar sa ke mishi.
Kai nake jira.
Ya dago Kai har Yanzu taki yarda su hada ido, me kike so Yanzu in Miki?
Ka bani wuri in wuce. Ta fada fuska chunkushe.
 Anya yarinyar ba zafin kishi ke addabar ta ba? Me yasa bazata fito tace tana sonsa ba kamar yanda sauran Yan Mata keyi Masa?.
Zan Baki wuri ki wuce Amma sai kin mun alkawari Zaki dauki wayata anjima.....banyi ba Kuma bazanyi ba ka bani wuri in wuce Wai Ina dalili?.
Ya Mike tare da say hannu duka biyu aljihu Yana gaba tana bite kamar zata tureshi Yana fita sit din tayi hanyar waje da sauri ya bita da ido har ta yi nisa ta taga.
Sadeeq na can baya kansa bisa littafi kamar Mai karatun gaskiya. Ya ce su tafi library din.
Ita kuwa daki ta koma.
 Tana sallar azahar barci yayi awon gaba da ita, sai biyar ma ta wuce ta tashi. Ga wayarta silent missed calls kusan goma shaa biyu. Khausar biyu, mommy biyu, hudu sabuwar lamba sauran Anwar.
Sai da ta Dan watsa ruwa tayi sallah sannan ta bi Kiran, khausar abinci zata Mata tayi, mommy Kuma zata fada Mata gobe zasu shigo Murna tsalle.
Alamar shigowar sako ta gani tana budewa taga wata number.

```i'm guilty I knew, please accept my apologies it will never happen again I promised```
Hmmm, tace kafin ta ci gaba da magana a fili.
Bana iyawa Yan matanka nesa nesan zaifi gaskiya don haka ka gaji ka kyaleni.
Washe gari karfe biyu su daddy sunka iso. Cikin wata Hummer Jeep bullet proof. Duk inda motar ta gitta binta akeyi da kallo. A bakin hanya ta taro su tunda sukayi waya ita da khausar, su Aisha sunje test. Murna, tsalle, da ihu kawai takeyi.
Hankalin Yan compound din ya dawo kansu *lallai Bilkisu ba diyar kananan mutane bace* Nan da Nan kallo ya dawo gunsu musamman lokacin da sukaga irin kayan da ake shiga dasu ciki. Har dakinta Shima daddy.
Ta rasa inda zata sa kanta tana makale jikin kafar mommy ana shagwaba. Kayan ciye ciye baje na gani na fada. Daman sunce ko ruwan zafi kada ta dafa.
Kawaye aka Fara shigowa da makwabta ana gaisuwa abin ya birge kowa......
Daddy ya kalleta Ina *Anwar* ki kirashi mu gaisa da abokin fadan naki......mutanen dake cikin dakin duk aka Kama dariya.
Gabanta ya Fadi.
Wannan karon fa fadan na gaskene ......mommy tayi karaf, ai dole mu ga Anwar yau Kam maza kirashi a waya kice gamu munzo...........

Ayi hakuri da kadan. Wallahi nayi typing 7 dinnan kawai mistakenly na gogeshi Shi yasa na rasa ta inda Kuma Zan Fara .
Afuwan😄😄👏🏼👏🏼👏🏼 zainab wowo ce💖✍🏼
[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
0️⃣8️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*
```wallahi tallahi ban taba ganin maiyi don Allah ba irin ki ya Allah ya Kara Miki lafiya da tsawancin kwana kina Raina Koda yaushe Kuma addu'ar mu in shaa Allah muna rokon Allah ya karba alfarmar fiyayyen halitta SAW```🤲🏼
*Abinda mutane suka kasa ganewa shine, ba daukar kudi ko wata kaddara kaba mutum kadai ne kyautatawa ba, a'a..... Mutuntawa, girmamawa, magana Mai dadi da sakin fuska na daya daga cikin abinda ke saka soyayya, shakuwa da Kuma girmamawa, Amma sai kaga wasu jakkan sun maida mutane banzaye basa daratta kowa kuma suna tunanin dole ayi musu biyayya saboda suna da hannu da shuni....sammmm ba haka abin yake ba, ga Wanda ya San ciwon kansa ka Zama bola daga ranar.* Ya Allah ka wanke Mana zuciyar mu irin ta *Aunty Rabi* ya hana mu kyama da wulakanta Wanda bashi dashi amin.

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

*Ke ce uwar gida Kuma Amarya in shaa Allah Alawiyya Nasir, matar Daddy uwar maamah da sofy, aminyar gaje Abu kawar Yar hareez Ina godiya ga namjij kokarin Samar mini Yar aiki na gode my disturber 🙄. Gaje Abu ga taki 👉🏼👍🏼👍🏼💖 na gode Allah yabar tare*

*****************

*KADUNA RIGASA*
```Wuya makarantar kare``` sunan wani littafin ```ZeeDee```
Ummi ta bala'in shiga hankalinta.
Ranar yabar gidanta, tun la'asar ya mata sallama kagare yake magariba tayi don Yana son Zama da Amira itama.
Gidan ya dauki kamshi tana ta soye soye da gashe/gashe,
Sai dai taga mutum bayan ta. Zabura tayi cikin tsoro.
Ta turbune fuska wallahi ka bani tsoro.
Ai gara haka, Ni jiya ba korata kikayi ba na kwana masallaci......Kai kajiyo. Ta katseshi.
Eh nasan cewa kishi ne yasa kikayi mun haka ....Ni na jiyo tunda na Kara Aure ko?........
Bana son irin wadannan maganganun ya kamata zuwa yanzu ka fahimceni.......naji...naji, shikenan.
Yanzu dai kawon abinda ya samu yunwa nake ji ....ya juya zuwa falo.
Dambun naman kaji, meat pie, doughnuts, da lemun kwakwa ta Fara kawo mishi. Yana Gama ci ya tafi isha'i, lokacin da ya dawo ya tarar da farfesun hanta, hunhu, Koda da tunbi.
Yana son sa sosai, saboda yanayin yanda takeyin sa:
*Farfesun hanta,hunhu,Koda da tumbi*
Bayan ta wanke su da kyau ta zuba a tukunya sai ta kawo albasa Mai yawa (musamman Mai lawashi), tafarnuwa,da citta sannan ta Dan zuba Maggi onga na sachet ( gari ) Shi kadai. Bata zuba ruwa sai ta dora Kan wuta low Yana heating a hankali kamshin kayan zai dakesu sosai ya danyi dry sannan sai ta zuba jajjagen tarugu da albasa again ta tsaida ruwa ta rufe.
Lokacin da ya dauko dahuwa ne ta zuba sauran Maggi da Dan gishiri to taste tare da curry kadan. Idan ya hade sai maganar ci.
Tana zaune gefen sa, suna ci tare, Ahmad ne ya shigo da gudu anyo mishi wanka,
Kai lafiya?
Abba gobe Aunty tace kowa yaci gayu zamuyi class picture.....
Shine zaka fado haka ba sallama daga Kai sai boxers? Ta fada tare da balla mishi harara....sim sim sim ya juya zai koma.
Ya kalleshi naji Ahmad in shaa Allah gobe gayu zakuci je hassu ta baku abinci kaji ko?
Yace toh ya juya.
Kin cika zafi yaran nan yanda suke tsoron ki koni basa tsoro haka meye abin fada ga shekaru irin nasa ma abinda yafi haka yi zaiyi.
Hmmm, kawai tace.
Ya finciko ta......zo in koya Miki yanda ake ba miji amsa idan yayi magana ba hmmm ake cewa ba.........dai dai ita Kuma ta turo kofa ashe bude yabarta lokacin da ya shigo.
Yana kokarin Kai bakinsa ga nata sukaji an turo kofa itace tayi saurin zamewa tunanin ta ma ko Yan aiki ne.
Tuni idanun ta sun gane Mata.....me ya kawo ni?
```

Wace kaddara ta aikeni?
Na gano ma kaina Ni Ummi........gabanta ya dinga halbawa da karfi da karfi.
Ita Bata karaso ba, Bata Kuma juya ta koma ba.
Gashi ya rike Amirar gammmm yaki saki, sai kichiniya takeyi amma ya riketa tamau . Dole ta hakura ta kalleta, ki karaso daga ciki Mana Kika yi tsaye bakin kofa.
Bai dago Kai ba Yana ta wasa da hannun Amirar yace idan wani abu kike bukata me zai hana ki Kira waya?
Shiru dai tayi har ta zauna bisa kujera tana facing dinsu amma ta kasa Kara maida idanu ta kalli takaici.
 Tayi shiruuuuuuuuu, sai Kuma kwallah sharrrr, duk motsin da takeyi idon Amira na kanta saboda tana ta mamakin zuwan nata.
Ganin zubowar kwallah yasa ta zunguro shi,
Ya maida Kai gefe Ummi lafiya dai ko?
Ita kanta tasan kukan da biyu takeyin sa, kasa ta sauko ta Fara magana a hankali,
Aunty Amira kiyi hakuri Dan Allah Akan abubuwan da suka faru sharrin shaidan ne, in shaa Allah hakan bazai Kuma faruwa ba......Ayya Ummi ba komai ya wuce.
Ta fizge hannun ta bari in zubo Miki abinci......um um na gode ta mike.
Ina zakije toh? Ki zauna muyi fira.......ya Kara hade fuska ya tsuke.
Ta Dan tabe baki , a'a barci nakeji da wuri sai ko zuwa gobe haka.
Har kofa ta taraka, kafin taja kofar.
......... Gaskiya abinda kakeyi ko kayi Abban Ahmad wallahi baka kyauta ba, Shi ido ba mudu ba yasan kima.
Ka rikeni gaban Ummi ai wannan cin fuska ne.
Ya kalleta sosai.......makaho idan Yana Kashi in har ba'a zungureshi ba to bazai gane ana kallonsa ba.
Yarinyar can abinda take nuna mun tun kafin in aureta dole in bita in Mata yanda takeso ita bazata bi ra'ayi na ba.
To Ni da ita wake auren wani?......duk da haka Yanzu kaga.....kiranta mukayi?.
Inba kilibibi da tsugudidi ba me ya kawota Yanzu?
Ba a haka......ke naji.
Tayi murmushi.... Ita Amarya ai Bata laifi.
To wannan dai tanayi.
Naji dadin zuwan ta yau din wata kilan ta Dan Sami darasin kula da miji idan ita din Mai hankali ce.
Ya Mike idan kin Gama sallamar Yara Ina jiranki.

*Ummi* taci kuka kamar ranta zai fita, tabbas ya kamata tayiwa kanta karatun ta natsu. Ashe ita sunan tana Aure Amma har Yanzu Bata San meye Jin dadin Aure ba, ta goge hawayen da ke shatatowa, dole in kwantar da kaina inci arziki in barshi inda yake saboda tabbas idan naki abinda yake so nice Masha wuya.............

*****************

*Federal University dutsinma*

Shigowar su Aisha ya bata damar neman mafita.
Ita kanta ma tana son ya zo su gaisa amma bazata iya kiransa ba.
Text ta tura mishi.
_Kaxo ku gaisa da su daddy yanzu_.
Wayar na hannun sa Yana kallon film.
Zaune ya tashi zumbur.
Sadeeq ya kalleshi lafiya?
Ya jefa mishi wayar.
Anzo wurin Dan ubanka sai kaje ka gabatar da kanka.
Munafukan banza Kun tsaya sai ba juna wahala kukeyi.....mtsew malam ban wayata.
Ya jefa mishi.
Wani text din ya Kara shigowa ... _zasu tafi in d next 30 minutes so hurry up and come_
Kara jefa ma sadeeq wayar yayi.
Kai seriously fa ...ya fada Yana zaro ido.
Ya tuntsire da dariya sai ka tashi ka tafi.
Ku dai tashi mu tafi wallahi bazanje Ni kadai ba. Kasan dai rashin zuwan Nan kuma wani problem din ne.
Anas ya Mike zumbur Tabb ku tashi mu tafi rigima dame ta cimma kurege.
........ Ya kallesu sai faman canza Kaya sukeyi, yayi murmushi wallahi Yan iska ne ku.
Kaman zakuje biki?
Sadeeq ya jefo mishi wani farin boyal malam saka mu tafi...
Ya Mike idan Kun Gama mu je banson shirme.
Duk sukayo mishi chaaaaaa wallahi sai ka canza Kaya Dan ubanka da wannan hug din zaka je?
To meye aciki?
Kana hauka ne?
Ku daine mahaukata, Kun zauna Kuna ta faman wata kwalliya kamar zakuje daurin Aure.
Yayi hanyar waje.
Anas ya finciko Shi, kasa manyan kayan nan kada muci ubanka.....kici kici suka Fara kokawar cire mishi riga. Ba arziki ya cire su.
Sukayi juyin duniya yasa hula kube yakiya dole suka hakura sai dariya yakeyi masu duk sun Sha huluna.
Daddy ya Fara mikewa Zan jiraku waje ku karasa kada muyi dare....... Tuni su Aisha sun rufo mishi baya don barin Bilkisu ta gana da mommy.
Mashin din muhseen roba roba suka amso.
Sadeeq ne driver, Anas tsakiya Anwar karshe.
Suna shawo kwana sadeeq ya kurma zagi ashar, wancen muguwar motar fa?
Dai dai su daddy na kunno Kai sai dai ji sukayi Anwar ya dire da yake ba gudu sukeyi ba.
Ga Anwar nan kuwa inji Aisha.
Murmushi daddy yayi, nesa kadan sukayi parking.
Tare suka jero su uku.
Wata irin faduwar gaba yakeji wacce bai taba Jin irinta ba, duk suna durkushe lokacin da suka karaso.....Barka da rana.

Idanu su Aisha suka bude duk girman Kan su?
Ya fadada fara'ar sa ya Mika musu hannu, Assalamu alaikum duk Wanda suka gaisa sai ya dago hannun alamar ya Mike tsaye har yakai ga Anwar,
Wani shocking yaji duk illahirin jikinsa ya dauka dai dai lokacin ne Kuma Bilkisu da mommy suka fito.
Ta danyi dariya to mommy ga Anwar can .
Da sauri ta Fara waige waige Yana Ina?
Gashi can daddy ya rike hannun sa.
Tunda ya dago daddy bai saki hannun sa ba, ya rikeshi gamm suna Yar tafiya hakan yasan su sadeeq da Aisha stepping back kadan suna bin bayan su.
Sai murmushi yakeyi Yana sunsunne Kai.
Daddy ya kula dashi tsaf!, ( Abinda bai sani ba yasa an kishi bincike kaf akansa tun lokacin da Bilkisu tace wurin Shi take daukar karatu ).
Ya karatu?
Alhamdulillah! Ya fada,
Kana fama da rigimar Bilkisu ko?
Yar dariya kawai yayi, har lokacin yaki yarda su hada ido dashi.
Ai kullum labarinta Anwar, ko an Kara wani fadan ne?
A'a ya fada Yana murmushi.
Ta ce Kai Dan Kano ne ko?
Eh, ya ce har lokacin fuskarsa ta kasa daina murmushi.
Me yasa baka jituwa da malamai?
Lokacin ne ya Dan saci kallon daddyn ta gefen fuska....
Ya kasa amsa tambayar.
Ganin haka yasa yaci gaba da cewa, mutunta malamai akeyi ana gaishesu, wasu akasin hakan duk kokarin ka sai sunyi maka mugunta.
Haka ne!, Anwar din ya fada a hankali.
Sai a kiyaye kaji ko?
In shaa Allah. Yace.
A bakin mota suka tsaya.
..........ga Anwar ga Anwar , tun daga nesa mommy ke fada tana dariya.
( Na shiga uku ni Hamza ). Ya fada cikin zuciya.
Duk su sadeeq suka gaisheta Bilkisu na gabatar dasu.
Ya yunkura zai zukunna don gaisheta daddy ya rikeshi, ku gaisa a tsaye kamar yanda sunna ta koyar.
......ya akayi Kika gane shine Anwar? Daddy ya tambayeta Yana murmushi.
Balky ta nuno min Shi lokacin da mun fitto.
Idanun ta na kansa Shima Yana son kallonta Amma ya kasa.
Su Aisha sukayi bankwana suka juya, Shima ya saci kallon su Anas alamarr su ware lokacin dasu daddyn kema su Aishar bankwana da nasiha.
Sai dariya sukeyi mishi daga nesa. Daman tun da suka taho da daddy din suke mishi dariya ganin duk yanda ya dabarbarce.
Anas yace munafuki kaga duk rashin kunyarsa yaki sakewa Kuma don sun dauki mutane Yan

iska Basu so a gane suna son juna.
Anas ne ya matso ya Dan rusuna zamu koma hostel Allah ya tsare hanya...... Amin Amin ya zaro envelope ya Mika musu. Har lokacin hannun daddy na cikin na Anwar.
Ya kalli Anwar tafiyar ku daban ko?
Ya Dan sunkuyar da Kai tare muka zo.
Ohhh, to su tafi sai mu ajiyeka...... Ba Anwar din ba ita kanta Bilkisu tayi mamakin hakan.
Ya kalli Bilkisu ba abinda kike bukata Kuma?
Tace eh. Okay muje kada dare yayi suka bude mota.
Lokacin ne ya Sami hada ido da ita.
Ya sakar mata murmushi sai kawai ta harareshi ta juya.
Gaba ya shiga Yana nuna hanya.
Allah dai ya baku sa'ar karatu ya kareku daga dukkan sharri.
Yace Amin
Dan Allah kusa tsoron Allah ga dukkan al'amuran ku Anwar kada kuci amanar iyayenku, kaji ko ?
In shaa Allah mommy. Ya fada.
Yayi matukar godiya lokacin da suka ajiye Shi daddy ya umurci driver ya sauke mishi sauran kayan dake boot , sannan ya Mika mishi envelope Mai kauri.
Yayi godiya sosai. Aka Fara sauke Kaya, cartons din lemuka , ruwan roba, carton din indomie, oat,Madara family size 3, corn flakes, biscuits kala kala,Dan kalin turawa cikin buhu, plaintain, kwai Crete hudu,fresh milki,   gasassun kaji, kilishi, soyayyar miyar naman rago, dambun Daman kaji,  fanka Mai chargy ( Daman Yana da ita ), sabon carpet kato Mai laushi da turaruka. Cikin kwalaye aka jero kayan.
Yabi kayan da kallo kafin ya Kara komawa bakin tagar motar yadan rusuna, Angode Allah ya Kara arziki Mai albarka ya bada lafiya da tsawancin kwana. Duk suka amsa Amin Amin.
Ya daga musu hannu Allah ya kiyaye lokacin da driver yaja mota, gaban hostel din cike da mutane Shi kawai ake kallo saboda motar da ta janyo hankalin kowa.
Da gudu su sadeeq suka karaso.
Ya kallesu ku shiga da kayan Nan zanje in ga Bilkisu......kawai ya tsaida mashin ya koma..............Tana ta faman shirya kayan Jennifer ta shigo, Bilkisu Anwar want you......ta kalleta da sauri Anwar?
Yah, he's out side...... Tana fadar haka ta fice abinta.
Ikon Allah, lallai ni ta bance , duk FUDMA kuwa akwai macen dake juya Anwar kamar Ni?. Wallahi Bata taba tunanin zaizo ba lokacin da tayi mishi text despite fushi da rashin daukar wayarsa, Wai me yasa Baya mata fushi da gadara da Kuma wulakanci kamar yanda ya Raina kowa?.
Hijabi ta saka ta janyo dakin.
Yana tsaye ya harde hannu duka biyu a kirji.
Manyan Kaya na mishi kyau matuka, ya Kura Mata ido kamar zai cinyeta.
Ta karaso kanta kasa, Ina wuni.....ban amsawa.
Wai Bilkisu me kike nufi ne?
Me Kika fadawa su daddy akaina?
Ta dago Kai me fa, wani abu ya faru?

Komai ma ya faru gashi kince dole nazo mu gaisa ya Mika Mata kudi Kinga bayan Wanda aka ba su sadeeq ga nawa Kaya Kuma nacan an ajiye mun kamar.....to meye ne ba kyauta bace?
Ya kalleta, Kuma only me?
Ta daure fuska Ni ban gane abinda kake nufi ba...... Meye Kika fada ma iyayenki a kaina? Simple question.
Ta gyara tsayuwa, sun San cewa Kaine kake koya mun karatu Kuma Koda yaushe Ina Basu labarin karatun da mukayi.....ya akayi daddy yasan bana shiri da malamai?
Ta zaro ido wallahi bamuyi wannan maganar ba.
Kin tabbatar?
Ta balla mishi harara na maka ta kudin ka.
Ya kyalkyace da dariya, to ai abun ne ya bani tsoro,
Mtsew ....tayi tsoki.
Mun shirya ko? Tunda na amsa Kira na Kuma bada hakuri Nima ayi hakuri na gaji da fadan Nan wallahi.
Mun shirya ko? Ya Kara maimaitawa Yana murmushi,
Ta yi Yar dariya eh,
Good, Dan Allah kiyi mun godiya sosai na gode.
Ba komai. Sai gobe.
Korata kikeyi?
A'a bana son dai a Kira magriba kana Nan ko?
Hmmm, kawai kin koreni sai anjima ya Dan juya kamar yayi fushi.
Allah ya baka hakuri ka dawo ban koreka ba.....ya juyo Yana murmushi tunda kin bada hakuri kin tsira.
Zan kiraki please.
Ta juya.
Kinji?
Na ce toh.
Tuni magana ta Game ko'ina akan zuwan iyayen Bilkisu Kuma anga Anwar a wurin.
Hankalin mufeeda yayi mugun tashi ta dunga bala'i a daki. Tare da Shan alwashin dole ta gyarawa Bilkisu Zama ta Kuma ja mata kunne akan Anwar.
Sha daya da kwata na dare ya kirata. Labarin kayan da aka kawo mishi da makudan kudin da aka bashi yake lissafa Mata sanannan yadanyi Mata bayanin course din da zasuyi gobe.
Sha biyu ta wuce suka ajiye.
Su sadeeq sunyi sunyi yayi confessing akan Bilkisu Amma amsar kamar kullum itace, *baku da hankali*
Kowa yayi mamakin ganin su rumi rumi.
Sai karfe hudu suka gama lecture.
Duk ta gaji tana tafiya da kyar kawai taji anfinciko hijabin ta.......jira karamar Yar iska.
Kafin ta Ankara sun Mata zobe.
Ta kallesu daya bayan daya tace *Anzo wurin* cikin zuciya.
Lafiya?
Ta bukata tana musu kallon up and down.
Ko zamuji na jaki ne tukun?

Ko Kuma Ni ko?
Wallahi tallahi duk Yar iskar da ta Kara ja mun jiba sai naci kutumar........ke banza...mufeeda ta katseta.
Wani kallo ta wurga Mata nice banza?
Eh kece banza ko Zaki Rama ne?
Akan meye Zaki kirani banza?
Saboda Anwar..!
Wallahi idan Baki fita harkar sa ba Zaki......Zaki fiddani karatu FUDMA?
Ta bukata.
Amma ke a matan ma rakiya kikayo, ai mace idan ta cika mace namiji binta yakeyi ba itace ke bin sa ba. Kije ki tambaya Dani da Anwar waye ke bin wani?
Ko an fada Miki dashi da Babu suna da banbanci a wurina?
Karatu ma da mukeyi Shi ke rokona da inzo ba Ni ce ke makalewa ba. Ta fiddo waya ta latso missed calls.....ta nuna Mata fuskar wayar kalla ki gani.....don haka wallahi tallahi sai kinyi Dana sanin kirana banza......ta ingijeta ta wuce , gigin yasa jamcy ta Kai hannu zata rikota ji kake faaass.... Ta wanka Mata Mari , Marin da ya janyo duk illahirin masu wucewa da wadanda ke zaune sannan ta daga murya....duk wacce Kuma take ganin ita Yar Tasha ce tazo ta yi gigin kwatanta abinda tayi ko a nemi wata ta Rama Mata...... Bilkisu lafiya meke faruwa?
Suleiman ta gani.
Tayi murmushi cike da takaici duka na suka zo yi saboda inji tsoro in daina karatu da kula Anwar .
Duka?
To bisimillah kuzo ku dake ta wallahi summa tallahi da na karya hannun yarinya ko waye ubanta....duk suka juya suna gunguni, yace:, Yan iskan karya.
Muje kyalesu. Suka jera.....
Haushi ya kamata lokacin da ya Kira taki daukar wayar.
Tasan akan maganar test din *GST* ne. Yasan cewa ta tsani CBT,
Ya buga tsoki, duk duniya Babu Mai Sanya mishi ciwon Kai irin Bilkisu.

Bakin Auditorium din cike da dalibai abinka ga general course. Tana can gefe ta makure sai faman karatun past question takeyi, Shi kuwa sai wurge wurgen ido yake ta inda zai hangota, Mufeeda na can jikin bedi sun Kura mishi ido.
.......Wai Daman kina Nan? Yanzu naga Anwar Yana nemanki nace bamu hadu ba, Aisha ce ta karaso rike da past Q din itama.
Yana Ina?
Gashi can....
Ta Mike , okay jirani Ina zuwa.
Yana hangota ya nufo ta.
Tayi kamar Bata ganshi ba ta nufi inda su mufeeda.
Ya biyota.......ke nake nema fa tun dazun kin Kuma hangoni kina neman sharewa........ Da karfi ta finciko mufeeda tare da bankada ta kusa dashi har yayi saurin ja da baya ganin zata fado jikinsa.
Ya zaro ido.....ita Kuma ta juyo a hasale ta Kara maida keyar ta tare da nuna ta da yatsa.......Ni agabansa Zan Miki *warning*

Ko a Yanzu wakika ga yabi wani cikin mu?
Tuni an musu zobe ana kallon ikon Allah,
Ta daka Mata tsawa nace ubanwa Kika ga yabi wani cikin mu?
Na tabbatar tun dazun ya ganki anan Amma bai nemeki ba saboda haka kece *BANZA* Gashi nan nabar Miki Shi duniya da lahira idan kina bukata Ni karatu ya kawoni ba shashanci da bin maza ba don haka idan kina son sanin wacece Bilkisu please try and confront me again wallahi you'll regret it for the rest of your life useless fool.........
Kawai ta bi cikin mutane ta wuce abinta.😝

Zainab wowo ce dai😄✍🏼💖
[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
🔟

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

************
*KADUNA RIGASA*

Tun daga bakin gate yake jiyo kamshi, mamaki ya cika Shi, shin ko yayi batan lissafi ne gidan Amira yake ba Ummi ba?
Tana tsaye cikin Riga da skirt na leshi tasha ado ya shigo.
Da gudu ta rungumeshi yaji wani tsammmmmmm...... Anya Ummi ce?
Nan danan ta Fara sabon salo. Shigowa yayi kawai ya ajiye jaka ya wuce wurin Amira sannan ya dawo Amma inaaaa tuni hankalin ya karkata........ Bayan yayi wanka, ta zauna tana bashi abinci kamar yaron goye tun a daki da ya motsa sai ta bashi hakuri yanzun ma tana bashi abincin tana Kara lallashi duk ya sukukunce ya rikice.
Ya kalleta wallahi Ummi Ina sonki, kawai halayenki ne suka Sanya mun ko kwanto a zuciya Shi.......ta rufe bakin da chokaci ta debo peppé soup, sorry my love zaka ga changi I promise...... Ai na ga changi wallahi please keep it up.......
Amira Bata Sanya Shi ido ba sai bayan isha'i ta gama kulewa ta Kai karshe.........

**************
*Federal University dutsinma*
Kowa yasan sadeeq baida fitina, murmushi kawai yayi yabarshi a wurin yana babatu.
Sai kawai ya Fara fushi dashi.
Cikin bacin rai sadeeq ya samu Anas, Yana fada mishi abinda Anwar din yayi mishi Kashi na biyu akan Bilkisu.

Yaja guntun tsaki, kayi hakuri sadeeq wallahi *So* ke wahalar dasu duka for now ka bashi time zai nemeka.
Tun daga ranar Bilkisu ta koma sadeeq ke nuna mata, sun kyale Anwar.
Hankalin Anwar yayi matukar tashi ga exams na karatowa, hanya ma idan ta hango shi canzawa takeyi.
Ya rasa inda zai saka ransa.
Ko kallo bai isheta ba. Idan ta zo school amma tana komawa daki zata ci kukan ta tayi ma'ishi.
Yanzu fa kowa ya fahimci an bata Bilkisu da Anwar. Tsalle da Murna mufeeda ta ringa yi.
Tana zaune class za'a yi lecture ya shigo.
Yana ganin ta yayi saurin shiga sit din zai zauna kusa da ita...... Sai da ya karaso gaf! Daman can karshe take sai kawai ta kwashi kayanta ta dora waya a kunne , helllooo....yes inajinki.
Tayi waje kamar me amsa wayar gaske.
Tana fita tayi jimmm sannan ta dawo tare da canza layi ma gaba daya.
Ransa ya baci, hankalin sa ya Kara tashi, kowa ya fahimci abinda tayi.
Sam ta rage fara'a in kaga tana dariya to tare take da Suleiman.
Ana gama lecture ya tsaya bakin kofa yasa hannu duk Wanda zai fita sai ya mishi magana, tana ganin haka ta yi zamanta, Shima ya ayyana a ransa wallahi yau Kam sai dai su kwana haka.
Masu shigowa da masu fita kowa sai ya mishi magana sannan.
Ta dawo gaban sit suna magana da chinyere, tayi sa'a ya juya suna magana da wani dan aji daya da alama bayani yakeyi mishi har ya manta ya saki hannu Yana magana cikin nuni da hannu....tayi wuf, ta wuce ko alama bai lura ba sai da tayi nisa ya waiga class din da sauri ya tabbatar lallai ita ce.........wani mugun tsoki yaja tare da dunkule hannu ya daki bango har yaron ya tsorata.
Cikin tsawa yace yaron ya bace mishi da gani.....
Daki ya tarar da sadeeq nacin abinci. Yasa chokali kawai Shima, ya kalleshi malam zaka Sanya mun Rani.....dama jira yakeyi yayi magana ko sa shirya.
Anje an Sanya.
Ya Galla mishi harara kawai.
Anwar din ya rike kunnuwa biyu am sorry my friend pls sorry.
Murmushi sadeeq din yayi kawai.
Ya Fara magiya, har Anas ya shigo yasa baki.
Nan da nan aka koma normal.
Ya kallesu kamar zaiyi kuka. Dan Allah ku shiryani da Bilkisu yarinyar nan tayi fushi dani sosai.
Wallahi nayi tunanin bayan kwana biyu zata bani hakuri shikenan komai ya wuce ashe ita zafin nata yafi nawa......
Anas ya harareshi, kunfi kusa, a da idan kunyi fadan ku waye ke shirya ki?
Wallahi tsoronta nake yanzu, bana iya tunkarar ta ku taimaka ku shirya mu....
Zamu jaraba gobe....inji sadeeq.
Duk an Fara covering ana shirye shiryen tafiya sallah break ( babbar sallah ), da andawo Kuma da sati za'a Fara exam.
Tana zaune can baya sadeeq ya sameta.
Bayan sun gama gaisawa ya kalleta.
Bilkisu ya kamata ku shirya keda Anwar fadan ya Isa hakanan Dan Allah Kinga....... Mikewa tayi

tsaye, tace, sadeeq Ina ganin kimarka da mutunci wallahi duk ranar da ka Kara mun maganar Anwar kaima Zan daina magana dakai har nabar makarantar Nan.........ta kwashi books dinta lecture din da bata dauka ba kenan ranar.
Gaban Anwar sai faduwa yakeyi...... Tana fita ya koma inda ta tashi... Yaya?
Sadeeq din ya bata rai tare da fada mishi abinda tace, sai kawai ya dora Kai bisa table yayi shiruuuu!
Ya dan sunkuya da Kai Anwar idan kana son yarinyar nan ka sameta ku daidaita........mtseww Shima ya figi takardu yayi waje....ya bishi da ido yace ikon Allah!
Anas ya taso Yana dariya...... sadeeq ma ya kyalkyace da dariya suka tafa.
Ni naga karshen wannan girman Kan nasu, ko wane ta ciki na ciki sai wahalar da juna ake.... Laifin Anwar ne kasan Allah sadeeq maganinsa Bilkisu.
Bashi da aiki sai dai ya dauko waya yayi ma sunan ta zuruu Yana kallo. Text din da ta mishi na birthday ya Zama tamkar paracetamol ga Mai ciwon Kai.
Kwance yake ruf da ciki suka iso, Anas ya tabo Shi ...abokina barci kakeyi?
Ya tashi firgigi yace no, Ina jinku kawai na kwanta ne na huta Yaya?
Ya Mika mishi littafi exercise question din nan zaka solver Mana please...... Wallahi tallahi bazan kara koya ma kowa ba school din nan inbaku shiryani da Bilkisu ba.....hada rantsuwa sadeeq ya zaro ido.
Kana wasa ko?
Ya Kara Bata rai try me and see. Ya koma ya kife a katifa.
Nan da nan suka shiga damuwa, Anas ya kalli sadeeq lallai abun nan ya girmama.
Sadeeq ya nisaaa, kagane kamata yayi mu Sami Suleiman da Helen muje mu Kara bata hakuri kasan Dan iskan yaron nan fa zai Kira Mana ruwa mu shiga uku.
Yana zaune ya ajiye littafi alamar ita ya ajiyewa sit sakamakon ita ce lecture karshe kowa yayi covering shine yayi saura.
Suka Mika mishi hannuwa ya bisu da ido Yana mamaki saboda yasan clique din su basu daukeshi bakin komai ba har gara gara sadeeq suna gaisawa jefi jefi idan Yana tare da Bilkisu.
Suleiman wannan zuwan naka ne,
Toh, gani lafiya dai ko?
Da sauki gaskiya, akan Anwar ne da Bilkisu ya rantse cewa duk semester din Nan ba Wanda zai karu dashi matukar ba'a shirya su da ita ba Kuma wallahi ni dana Mata magana cewa tayi na Kara Nima zata daina mun magana.
Murmushi kawai yayi.
Anas yayi karaf! Yace, shine muka yanke shawara mu sameka Dan Allah kasa Baki muje mu Bata hakuri.
Ya Kara murmushi okay ba damuwa.
Har aka tashi class bata zo ba,kawai suka yanke shawarar zuwa gida su sameta .
Aisha ta Fara haduwa dasu ta fito da alama garin zata bari take shaida masu ai tun karfe bakwai Bilkisun ta tafi Kano zata hau jirgi ta tafi Abuja..........
Kofin dake hannun Anwar ya Fadi ji kake tartsatsatsa...... Lokacin da Anas ke Mata bayani.
Ya kallesu asanyaye... shikenan tunda ta tafi.
Washe gari Shima suka tafi.
Abinda yafi komai bata mishi rai shine bata chatting, ya Kira duk wadanda suke tare ko tana

da wani layin na daban Amma sunce layinta daya ne kwal!
Ba abinda ta boye ma mommy hada kukanta.
Yar dariya kawai tayi tace zaku shirya karatu ya gaji haka.......zumburar baki tayi kawai ta wuce ciki.
Shima ya kasa sukuni, ya gama ayyana ma ransa dole ya kirata ranar sallah ya Mata Barka da sallah tunda ranar kowa na cikin farinciki yasan dole ta saurareshi Kuma ta sauko.
Hakan kuwa akayi, misalin Sha daya na safe taci kwalliya tana tsaye kitchen tana zuba gasassar hanta a plate Kiran ya shigo.....
*Anwar* shine abinda true caller ta nuna Mata, kamar zata ki dauka sai Kuma ta tuna gara ta dauka ya gane cewar ko number sa bata dashi ........
Assalamu alaikum. Ta fada a hankali.......luuuuu ya tafi tare da lumshe ido kafin yace wa'alaiki Salam *Barka da sallah*....... Wake magana?
Ta bukata a dake,
Ya zaro ido kamar tana kallonsa.... Bilkisu kin goge number ta?
Tayi shiru kwalla sun taru idonta....
Kinji? Na ce kin goge number ta awayarki?
Kwallah suka shatato Mata tayi tsoki kawai ta kashe wayar......yace what???
Ya Kara Kira.
Tana kallo taki dauka sai da yayi missed call biyar amma Bata dauka ba.
Ya dankara wayar a kasa ta tarwatse sannan ya dafe Kai saboda juya mishi da yakeyi.
Ita kuwa sadadawa tayi zuwa dakinta taci kuka Mai isar ta tukun sai bayan azahar ta fito Shima fa'iza ce ta kirawo ta su fito zasu tafi millennium Park duka gidan.
Tambayar duniya gida Anyi ma Anwar cewar meke damunsa amma yace ba komai fargabar jarabawa ce .
Sati daya ya koma school ita kuwa sai ana gobe jarabawa sannan.
Don haka basu hadu ba sai dakin jarabawa, ya hangota can gaba, tun kafin su shiga sadeeq ya fada ma Suleiman ya tsaidata ko ta gama don su ganta.
Sai gashi ma duk sun rigata fitowa har Anwar din.
Ya tafi can nesa bakin bedi ya tsaya su Kuma suna gaban class suna jiranta.
Suleiman man ya Fara tarar ta sannan sauran suka matso aka Mata zobe .
Ya kalli kowa, sannan ya kalleta wannan zuwan naki ne fa, Dan Allah kiyi hakuri ku shirya da Anwar haka nan kinji yace matukar ba'a shirya ku ba ya gama koya ma kowa karatu........and then?
Sai su dage su koya da kansu Shima ba da iyawa aka haifeshi ba, Suleiman ka fita maganar Nan ba huruminka bane.......ta juya tayi tafiyar ta.
Anas ya zaro ido.... Suleiman ya kallesu Yana murmushi ku Kyaleta Zan lallabeta zasu shirya...... please try your best Dan Allah sadeeq ya fada tana wucewa Anwar ya karaso. Yaya? Anas ya dankara mishi harara yayi gaba kawai.
Hankalin sa ya Kara tashi jin ba wata nasara. Amma Suleiman din ya masu alkawarin zai shawo kanta.Hankalin kowa a tashe yake cikin department ganin da gaske Anwar yake bazai koya ma kowa ba matukar bai shirya da Bilkisu ba.
Ya daina ma kowa dariya tun su sadeeq na daukar abin wasa har suka ga lallai da gasken gaske yake fa.

Ba Wanda ke iya tunkarar sa,  idanun sa  cikin facing cap yake shigowa Yana rubuta jarabawar za a nemeshi a rasa.
Courses din ana Shan wahalar su, Bilkisu kuwa tuni ta sadakas, idan tana ta exam 3 tun 7 take shiga library sallah kawai ke fiddo ta. A cewar ta in kaji maraya raggo.
Bai taba tunanin Bilkisu zatayi wannan zuciyar ba Yana tunanin yanda ta Saba da tutorial din sa bazata taba karatu babu Shi ba.
Sun Sami interval na kwana daya, da marece tana class tana karatu Suleiman yazo.
Suka Fara karatun tare...... Wani wuri ya Dan kakare masu.
Yayi murmushi Kinga da kin huce da duk wannan wahalar bamu Sha ta gashi kinja ma kowa, Anwar...... Suleiman ka kasa ganewa na fada maka wallahi ko sunan Anwar bana son inji an fada.....
Saboda me?
Ni bakiyi mun adalci ba wallahi sai nake ganin kamar bani da kima ko mutunci a idon ki, tunda ya Baki hakuri Nima na Baki sai ki......yaushe ya bani hakuri? Wallahi bai bani hakuri ba.
Mutane nawa ya Aiko Miki?
To ai mutane kace Shi in person baizo ba ta Yaya Zan San cewar ya gane kuskuren sa?
...... Yanzu idan yazo da kansa ya Baki hakuri Zaki hakura ku koma normal?......
Tayi shiruuuuu.... Me yasa Suleiman zai Sanya ta kwana.
Kinji? Dan Allah Ina son Anwar yaci albarkaci na ki yi hakuri Kinga Yanzu idan ya dauke hannunsa ga kowa tabbas an Sami matsala Kuma kece sila...... Ni?
Yayi murmushi, kiyi hakuri Bilkisu Yanzu dai, Dan Allah kiyi hakuri.
Ya Gama daureta ta ko'ina, tafi mintuna hudu bata ce komai ba.
Ya Kara kallon ta, Ni zakiyi ma wannan alfarmar ba kowa ba kiyi hakuri.
Kwalla suka suka zuba Mata...... Ta mayar dasu da karfin tsiya sannan ta ce shikenan ya wuce...... Ya zaburo, kin hakura?
Eh, amma ka sani saboda Kai...... Na sani wallahi. Na sani Bilkisu na gode na gode words cannot express my gratitude.
Suka jero tare ya rakata har bakin gida sannan ya tafi.
Hostel yayi ma tsinke, kamar daga sama suka ganshi karon farko da ya taba zuwa dakinsu.
Anwar na kishingide Koda Suleiman man din ya shigo ya maida ido ya rufe kunnen sa like da ear piece, ba wani music da ya kunna duk Yana jinsu,
Sadeeq ya fadada murmushi wannan babban bako ne sannu da zuwa Suleiman. Ya ce yawwa tare da Mika ma kowa hannu Banda Anwar.
Ya kalli sadeeq muje in ganka...... Suka fita tare.
Anas ya kaima Anwar duka Amma Kai Dan iska ne wallahi. Yaron nannya shigo don wulakanci shine ka rufe ido Dan ubanka..... Mtsew yaja tsoki kawai.
Ya kalli sadeeq, na shawo Kan mutuniyar ku, ta hakura ta ce komai ya wuce sai ka fadawa Anwar din saboda kasan........ya riko hannunsa duka biyunKace wallahi......
Yayi murmushi wallahi kuwa. Amma Suleiman mun gode Allah yabar zumunci dama inata zullumi ranar juma'a za ayi econometrics gashi yayi burus da kowa.....Ya Mika mishi hannu suka Kara gaisawa sannan yace mun gode fa bari naje na mishi albishir .....ya koma daki da sauri.
Kallo yayi ma sadeeq ya watsar.
Ni kakeyi ma wannan Dan iskan kallon? To Suleiman zuwa yayi ya fada Mana ya shawo Kan

Bilkisu tace ta hakura zaku koma normal.......zumbur ya Mike... Are you serious????
Ya galla mishi harara na ban sani ba kaga wulakancin da kayi mashi da yazo ko kallo......forger about that please ta hakura????
Anas yaja dogon tsoki sai kaje ka fada Mata ka kusa mutuwa..... Ya kyalkyace da dariya a'a ka manta mutuwar nayi.
Eh Mana, Kuna ta wahalar da kanku a banza....... We are just friends jor what are you talking about???
Ai maganin sa Bilkisun, nifa yarinyar ta bala'in birgeni wallahi ta nuna mishi ita din ta daban ce......Anas ya fada Yana Kara doka mishi harara.
Ya lumshe ido ya koma ta baya ya kwanta...ku yau kuka San Bilkisu ta dabance ko?
Duk suka dunkule hannu suka Kai mishi duka ... sadeeq yace asirinka dai ya tonu munafuki.....ya Kara bushewa da dariya.
Washegari suna da exam 3, karfe biyu ta fito library jikin wata bishiya bisa kujera ta Kira Suleiman...... Hello ka shigo?
Eh, kina Ina ne?
Ina ta wajen library wallahi na kasa game wannan last part din, zo kamun dalla dalla please..... Okay Ina zuwa.
Ashe tun karfe tara suna tare da Anwar Yana koya musu a class, ya kalleshi cikin kosawa.......Yaya?
Dariya yayi kafin yace, last part din nan ne bata gane ba take so na nuna......tashi muje ya Mike.....
Anas ya kalleshi Dan uwarka mu Kuma fa ?
Ya dalla mishi harara ku gane ...yayi waje.
Daga nesa ta hangosu , tayi saurin boyewa bayan bishiya sannan ta saka wayar ta Airplane mode.
Tana kallonsu sai safa da marwa sukeyi amma ta boye. Har kusan uku saura kwata sannan ta hangosu sunyi hanyar class din da zasuyi jarabawar......... Watan Suleiman kiranshi yayi ko? Ta buga tsoki.
Lokacin da ta Isa har sun zauna invigilators sunzo, ta shiga...idon sa na kanta, Koda wasa Bata yarda ta kalli inda yake ba, Suleiman na bayansa ya Dan gyara alamar ta zauna sai kawai ta wuce kamar bata lura ba.
Ana gama jarabawar, tayi saurin submitting tabar shiyyar.
Suleiman na fitowa ya kamo hannun sa, kaga ta tafi ko?
Murmushi kawai yayi.
Abu kamar wasa har saura exam uku su gama amma Bata yarda sun hadu ba.
Ya Sami Suleiman kamar zai mishi kuka yace shifa bai gane ba.
Dole ya sameta yace Dan Allah tayi hakuri ta saurareshi.
Tasha mur, au ni zan sameshi bashine zaizo yaban hakuri ba?...... Ohhh toooo kiyi hakuri zaizo, ta wuce abinta tabarshi wurin saboda yama bata haushi.
Suna rabuwa ya Kira Anwar din yace tace Shi baida bakin bata hakuri ne?
Gaban sa ya Fadi.....Anya zai iya tunkarar ta Yanzu Kam har ga Allah tsoron ta ma yakeyi.
Haka ya kwana dardarce, ko barci kirki ya kasayi da ya tuna sai ya yi firgigi ya tashi zumbur.
Jarabawar ta safe ce, farar shirt ya saka Mai kwala tana da ratsin ja, da farin jeans sai jar

facing cap. Agogon hannun sa kirar *Rado* baka .
Ya rufe ido da makeken glass dinsa Baki. ( Anwar akwai kyau da iya wanka ).
Ba abinda gabansa keyi sai faduwa Anya zai iya mata magana?
Duk inda ya gitta sai an kalleshi ya wanku iyakar wanka sai kamshi ke tashi.
Yana tsaye jikin taga ya hangota sun taho tare dasu Aisha sai faman dariya sukeyi.
Ya bude littafi kamar Yana karatu amma ita kawai yake kallo.....tana matsowa kirjinshi na Kara bugawa.....kafin ta iso har invigilators sun iso, dole ya shiga hall din ya zauna.
Yana Zama tazo zata wuce yasa kafa tun daga nesa ta hango abinda yayi sai kawai tabi dayan layin.
Ya rigata fitowa, Banda faduwar gaba har Yar kyarma ya Fara lokacin da ya hango tana fitowa.
Ta zukunna gaban Helen tana fadin .....duba mun wannan shin sune characteristics din nan?.......
Kamar daga sama taking yace *Bilkisu*........
Gabanta ya bada rasss!!! Maganar ta makale Mata.......ya Kara kiranta a hankali Yana tsaye bayanta..... *Bilkisu*...........Zainab wowo ce✍🏼😄😄💖

Ayi hakuri da kadan
[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
1️⃣1️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

****************
*KADUNA RIGASA*

Ranta a bace amma Sam hankalinsa baya kanta sauri sauri yakeyi daman tun da ya iso an shigo Mata da tsarabun da yayo.
Gabanta ya fadi, wannan rawar kafar ta mecece?
Ta daure ta dan boye fushin ta, kafin tace : Wai lafiyar ka kuwa?
Yau ka dawo sai Yanzu ka shigo nan Kuma kana ta wani sauri sauri........ Nan da Nan guiltiness ya kamashi, ya Fara Yan kame kame..... Nan da nan ta gano bakin zaren tayi murmushi ko hada gajiya halan?..... Ya kakaro murmushi gajiyar ma ce gaskiya.
Gaskiya ne.
Ta Mike , mu kwana lafiya kaje ka huta......wuf Shima ya Mike Daman jira yakeyi yayi waje Yana fadin Allah ya tashe mu lafiya.
Ta bishi da ido kawai, lallai namiji akala ne, ta kuta zaka gane kirenka ka gama kwanakin ka

dawo...amma zanje in ga kalar wainar da ake toyawa.
Ummi nada tsawo Kuma doguwa ce tafi Amira .
Ita kuwa Amira irin Dan jikin Nan gareta Mai kyau da tsari, kallo daya Kai kace ummi keda Yara biyu ba ita ba.
Tana gyara jikin ta don ko tsakanin Ahmad da almustapha shekara biyar ne.
Ta bashi kamar mintuna arba'in kafin ta saka bakar jallabiya matsattsa tabi jikinta da turaren da ya fi so ta nufi sashen sa don ta San Yanzu suna can.
Ta danna karaurawa, ummin ce ta zo ta Dan leka.....ta kalleshi tare da yin Yar dariya *Yaya Amira* ce.
Oya bude ya fada Yana kishingide Yana Shan kankana.
Ummi na sanye da dogon wando jeans ya matse ta da Yar matsattsar Riga kanta ba kallabi ta yi kitso shuku Wanda ta daure da katon ribom saboda karancin gashi .
Ta kalli ummin sama da kasa sannan ta danyi murmushi sorry for disturbance please.....laaa ba komi karaso ciki.
Ya tashi zaune Yana Yar dariya Amira Yaya?
Tayi Yar dariya.....zuwa nayi in ji ka siyo mun book din nan kuwa dazun na mance in tambayeka......ohhh yes, Yana mota Bari na dauko Miki........ya yunkura..
A'a barshi kawo key din na dauko Yana ta wajen Ina?
Wurin Mai tuki jikin kofa Yana Nan....Ummi dauko key din.
Ta Mike.
Ya Kura Mata ido, Yana son tayi shigar doguwar Riga, wannan kamshin zuwa akayi ayi mun kwalele?
Good and fine, ta ce cikin zuciya, sannan tayi murmushi ta ce hmm kawai.
Kinji?
Gobe zanje kasuwa Dan Allah da safe ba dadewa zanyi ba, Zan biya gidan Salma.....me akeyi gidan salmar?
Ta dan mishi warrrr da ido, zumunci......duk sai ya diririce, Ni Zan kaiki ko?
Ta Dan Kara farrr da ido tare da Yar dariya, lokacin da Zan fita bana tunanin ka tashi cos by 8 nake son zuwa kasuwa Kuma Kai ba ma'abocin son zuwa kasuwa bane.....Zan biki please.
Saura kadan ta tuntsure da dariya yanayin yanda yayi maganar. Ta danyi murmushi.....Ummi ce ta fito da key.
Ta mike Bari na dauko book na.
Ya bita da ido Ummi ta dankara mishi harara Amma Sam bai lura ba.
Bude tabar kofar tana dawowa Bata shigo ba ta tsaya bakin kofa....ga key din Ummi, ....wuf ya Mike Bari na karbo.
Tana daga waje ya hada da key din da hannun ya rike in fito goben muje?
Nooo, kaga Ummi zata ji haushi kayi hakuri ka bata full time dinta don nima turn Dina.....ya murza hannun da karfi.
Tayi Yar Kara, ya dawo Yana dariya...... Ummi kamar zata fashe amma ta daure ta cije duk da haka sai da ya danga chanji amma sai kawai ya share.
Butique ta tafi, ta siyo rantsattsun English wear sabbi hada three quarters wando da skirt da crazy jeans.
Har ta dawo wajen Sha daya bai fito ba.

Ta fada wanka Yara sun tafi islamiya tahfeez, ta kulle kofar ciki tabar Mai aikin ta kitchen tana fita ta kofar baya.

Amira nada gashi sosai, kanta kananan kalaba ne duk sun zuba bisa bayanta wani sky blue crazy ta saka da wata crazy riga Mai hannu daya nononta kawai rigar ta rufe kasan ta Kuma bazace, ta cikin Bazar kana hango cibinta.

Kamshi kawai ke tashi gidan.

Sha biyu saura ya fito, motar ta kawai ya gani yasan ta dawo.

Ya nufi bangaren nata don agaisa.

Tana Jin motsin sa ta ruga daki ta dawo rike da littafi kamar me karatu ita a dole bataji shigowar sa ba.

Mutuwar tsaye yayi ya kusa sarkewa da miyau sai kawai taji Yana tari.....ta dago Kai da sauri irin ta razana din nan.......

*****************

*Federal University dutsinma*

.....Ta kasa dagowa ta amsa, jikinta ya Fara Yar kyarma.

Helen ta kalleta, Anwar na Miki magana...

A hankali ta juya kamar Mai ciwon wuya , idanun sa cikin glass Yana Dan murmushi........ Minti biyu. Ya fada kafin ya juya ya Fara tafiya can nesa wurin parking motoci.

Ta Mike jikinta duk ya mutu tabi bayansa.

Jingina yayi da mota hannuwan sa duka cikin aljihu ya kura Mata ido.

Kanta a kasa ta karaso fuskar ta babu yabo ba fallasa. Ta kasa magana.... Ya Kara nutsar da idanun sa gareta yace: Ranki ya dade ya exam din?

Ta danyi murmushi kadan Alhamdulillah...Ina kwana.

Lafiya Lau, na Aiko a Baki hakuri kina ta ba mutane wahala kince dole sai nazo da kaina to gani nazo.

Ta Kara kasa da Kai tana murmushi...... ban taba tunanin zakiyi fushi haka dani ba ko kadan.

Tayi shiru dai,

Har kiranki nayi da sallah without knowing u deleted my number....... Shikenan dai ya wuce. Ta fada a hankali.

Kin tabbatar ya wuce?

Eh,

Mun shirya?

Sai kawai tayi Yar dariya saboda yanda yayi tambayar kamar wani karamin yaro.

Yabi fuskar da kallo......  Ji yakeyi kamar ya kamota ya rungume... Yayi murmushi kinji mun shirya Yanzu ko?

Eh,

To na gode, Zan kiyaye daga yau Allah ya Kara Baki hakuri shikenan ko?

Um, tace a takaice.

Ina zakije yanzu?

Gida Zan tafi.

To muje na rakaki ..... A'a barshi kawai na gode, ta katse shi tare da yin gaba abinta.

Ya bita da kallo baya so ta tafi ko kadan.
Ya hura iska.... nawaoooo yarinyar nan miskila ce ta karshe.
Wani sanyi zuciyar ta keyi mata, tana zuwa daki ta fada bisa katifa ta rungume filo ta maida idanu ta rufe a hankali.
Su Anas suka bushe da dariya, ya cire glass Yana hararar su , Helen na bayansu, tana so taji yanda akayi.
Munafuki sai kace yau neman shiri zakayi Shi yasa tun karfe biyar ka yo wanka kana faman shiri.
Mtsew yaja guntun tsaki, suka jera suna tafiya.
Ya kalli Helen din dake kokarin jerawa da su yace ke kuma lafiya kike faman binmu?
Kamar za ta nutse dan kunya, ta juya kawai ta koma...... Sadeeq ya harareshi wallahi ka daina dizga mutane haka Anwar.
Ya maida glass din a idon sa, inba gulma ba ubanwa zatayi cikin mu?
Kasan tun dazun ina tsaye da Bilkisu hankalin ta na nan?
Kayi mamaki ne? Inji Anas.
Waye bai San ta mutu kanka ba...... Ban san abinda kuka mayar dani school din nan ba. Ko wace jik and jak Sona takeyi? Mtseww kada kusanya inci ubanta da kyau fa. Mufeeda ma ta gama haukanta ta shafan lafiya bare wata arniya....... Kada ka taba yarinyar mutane arnan can sun fika hauka..... Ko in gwada? Muga cikin mu wa ya darar ma wani?
.......Anas ya zaburo Kar ka Soma wallahi. Babu ruwanka da ita baka San tana yi ba kawai ka ci gaba da nuna Mata baka ganeba.
Naji! Ya fada a takaice.
Yaushe zaka Mana bayanin Economic of production?
4, yace a takaice.
4, Kuma?
Eh, saboda zanje wani wuri da daddare.......duk suka kalleshi.
Yanzu barci zanyi, 4 Kuma sai muyi zuwa magrib ko bai muku ba?
Amma ai yau ba ball ina zakaje ne?.... Murmushi kawai yayi.
Suka Kara binsa da ido.
Wai lafiya? Ya bukata Yana Yar dariya.
Ina zaka je muka ce?
Wanda zai bini ya shirya ban hanaku ba.....
Duk sukayi shiru, suna kallon kallo.
Ya kyalkyace da dariya wallahi ku munafukai ne...... sadeeq ya Kai mishi duka wallahi baka da gaskiya.
Ya kyalkyace da dariya.
Mashin daya suka hau.
Dakin acike bai samu ya yi barcin ba daga wannan sai wannan, ya gaji matuka. Shi ba koyawa ko bayani ke baya son yi ba, cin lokacin sa da akeyi ke sanya Shi kosawa.
Sai da yayi wanka sannan ya Fara shiri cikin farin boyel ya dauko hudaddun takalma ya saka na fata *masarati*, yana cikin sharce gashi suka shigo.
Duk suka zaro ido..... Ya fiddo turaruka ya shiga fesawa kusurwa kusurwa, lungu lungu.
Sadeeq ya kalleshi *Anwar Ina zaka je?*

Bai ma kowa magana ba ya Mike, har ya Kai bakin kofa ya waigo ku bakwa ganin karuwa da danta baku tambayi ubansa ba.
*Zance Zan je*....... Ya fice da sauri suka Fara surma mishi zagi.
Yana tafe Yana tunanin Yanzu kuwa Yana zuwa ya tarar tana tare da wani to ya zai yi?
Ya tofar da miyau, Wai kada abin ya Zama gaskiya.
Mashin din Salim, roba roba ya karba.
A bakin gidan yayi farking ya kafe mashin din tare da Zama saman Shi kamar kujera sannan ya Kira wayar ta, tana kwance da Yar shimi ta barci rike da littafi tana karatu wayar tayi Kara........
Tunanin ta mommy ce.
Ta muskuta, Ba tare da ta kalli screen din ba tace.
Mommy.....
Mommy Kuma? Ya bukata.
Ta zaro ido tare da kallon fuskar wayar sai akwai ta mayar a kunne....still Baki mayar da no. Ta ba ko?
Ya hakuri Ina wuni?
Gani waje Ina jiranki....... Waje Ina?
Kofar gidan ku.
Na shiga uku.....Bata San a fili ta fada ba sai da taji yace.....zuwan nawa ke da shiga uku?
Ta zaro ido. Duk ta diriri ce.
Ko baki maraba dani na juya?
Ina zuwa... Ta fada a hankali.
Jikinta yana ta Yar kyarma. Ohh ni Bilkisu ko lafiya?
Sauri sauri ta shirya ta zumbula hijabi har kasa ta fita.
Kallo daya tayi mishi tsikar jikinta ta tashi Yarrrr....
Anwar a manyan Kaya????
Tayi murmushi kunyar duniya ta kamata gabanta ya dunga faduwa tana zullumin me ya kawo Shi?
Ya tsareta da ido, yaki magana.
Ta dago Kai sai ta zumbure baki ta maida Shi kasa.
Yayi murmushi, haushi kikeji nazo saboda ba Suleiman bane ko?
Kallon sa tayi da sauri , ya Sha mur!
Kin tsaya kina ja mun class kamar irin nazo zancen nan.
Dariya tayi.
Yanzu dai Ina wuni, me ya kawo ka cikin tsohon Daren nan?
Yayi murmushi, zance nazo can baya na biyo mu gaisa ko ban kyauta ba?
Gabanta ya fadi, ta dan tsuke fuska. Hmm.
Ko ban kyauta ba?
Kayi daidai.
Ke baki iya tarar bako? Ko haka kikeyi wa Suleiman idan yazo?
Suleiman again? Ta ce cikin zuciya. Wai meye kake ta fadin Suleiman...... Ba Kya so long sunan sa na fada kada gabansa yayi ta faduwa?.
Ikon Allah ta fada.
Eh Mana. Gashi kin kasa sauraron kowa sai shine ya shirya mu....... Baka ji dadin hakan ba?

Ya Dan harareta meye tsakaninki dashi? Ki fada mun sirrin..... Anwar rigima kazo muyi ko kuwa zuwa kayi mu gaisa da gaske?
Duka biyun nazo yi.
Karatu nakeyi.  Nasan kayi covering gobe ka Fara ansar extra sheet ina page 2 ina zare ido......
Suleiman zai Baki amsa.... Na shiga uku. Ta fada tare da kallon sa. Yasha mur, ko ruwa bazaki bani ba da gaske......juyawa tayi kawai.
Ya bita da kallo. Kwalin fresh milk ta fito da Shi da cup a hannu, gashi amma ba sanyi.
Ya karbi kofin ya Mika Mata alamar ta zubo mishi.
Ya tsareta da ido sai Yar kyakkyarwa takeyi.
Nayi kyau da manyan Kaya?
Ta tuntsure da dariya...... Yau naga ta kaina.
Shima dariyar yayi, to naji kin ki yabawa ..... Ta dalla mishi harara ita wacce kaje gurinta Bata yaba bane?.
Ya Kai kofin bakinsa yasha kafin yace, ta yaba tayi comments kema kiyi naki.
Har zata ce ni budurwar ka ce sai Kuma tayi shiru kada yace *Eh* tafi so *YA FURTA* Da bakin sa.
Me yasa baki WhatsApp?
Hakanan.
Bai yiwuwa , saboda duk Mai hankali baya abu babu dalili. Me yasa bakya yi?
Allah kawai bana son abun da zai daukar mun hankali daga karatun nan.
Muga wayar.......ta kalleshi.
Ya nutsar da idon sa cikin nata tayi saurin kawar da Kai.
Kada Inga text din Suleiman? Bazan shiga can ba......ta Mika mishi da sauri, yayi murmushi.
Zan dawo Miki da ita gobe ya saka aljihu. Meye password din?
Ta zaro ido, Daddy na kirana every asubah..... don't worry I'll talk to him meye password din?.
Dan Allah ka bani saboda....... Saboda Suleiman bazaiji dadi ba? Sau nawa nake ganin ta a hannun sa?
Wai lafiyar Anwar kuwa meye Yanzu magana daya sai ya ambaci Suleiman????
Na rantse da Allah sau biyu ne, Kuma duk chargy ya kaimu ya Kuma karbo.......
Yasha mur meye password dinki?.
Gabanta ya Fadi duk ta rikice saboda ANWAR ne password din. Ya kalleta wallahi wurina wayar Nan yau zata kwana Kuma sai kin fada mun password din..........✍🏼😄

Zainab wowo ce 💖

Ayi hakuri da kadan. An dameni da cigiya 😄
[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
1️⃣2️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

👉🏼 *Godiya ta musamman ga :*
*Mowa ( maimuna Nasir )*
*Hauwa'u, ( mum khady nima Ina kaunarki matuka*
*Da masu mun waya, text da kirana direct ku sani cewa zainab wowo Bata Raina masoya wlhi Ina kaunar ku sosai*
👉🏼 *Unex*💖

***************
*KADUNA RIGASA*

Ta dan rike kugu tana Yar rangwada.... Mura kakeyi haka?
Wuffff.... Ya riko kugunta, kece Zaki Sanya mun ita Yanzu, Ina Kika Sami kananan Kaya haka?
Sai faman shinshinarta yakeyi ya nutsar da kansa cikin wuyanta.
Tayi wani juyi tare da mayar da fuskar ta gab da tasa saboda ya sunkuyo tayi warrrr...... Kawai taji ya hada bakin sa da nata...... Fittt... ta fizge. Ta danyi baya tare da buga wani makirin tsalle rigar tayi sama cikinta ya fito fili..... Kanka qalau kuwa?
Ya yunkura zai Kara chafko ta tayi baya tana Yar dariya idanunsa sun kada sunyi jawur.... Ya kalleta kamar Mai Shirin yin kuka *Dan Allah ki tsaya bani da karfin binki ko'ina*.......
Amma kasan ba anan kake ba ko?
Ya langwabar da Kai, please one kiss.... Tabbb wlhi Haram. Ta fada tana wata karairaya.
Ya kura Mata ido duk hankalin sa ya tashi.... Amira kada ki hadu da fushin Allah ki tsaya....
To Yanzu....... Charaf! Taji ya damke ta cikin taku daya. Yana riketa ana dukan kofa da karfi.
Kafin yayi wani motsi ya jiyo muryar hajia ( mahaifiyar sa ) tana fadin Amira ko Bata ciki ne?.
Ya buga wani uban tsoki ya ingijeta ya wuce bedroom dinta da sauri.........

***************
*Federal University dutsinma*

It seems like baki da gaskiya fa!. Ya fada tare da tsareta da ido.
Ta dake ta kalleshi Yanzu dai Wayata ce zaka tafi da ita ko?
In shaa Allah, ya fada Yana murmushi.
Wai meye zakayi da wayata ne Anwar?, Bincike......., Ya fada Kai tsaye Yana kallonta, tayi shiruuuuu.......
Naji Zan baka, kawo na goge abu daya shikenan....menene?
Wallahi dana goge Zan baka hoto ne.....hoton Suleiman?
Ta doka tsoki Wai Kai komai Suleiman??????
Eh, ai kema komai shine....mtsewww to ba nashi bane nawa ne.

Kiyi hakuri bazan Baki ba don Ina son ganin hoton.
Ta Sha mur bani da Riga ne, Shi yasa da best Aisha ta daukemu muna cin abinci akwai hotuna da yawa nawa sai ka gaji da gani amma wannan bana son ka ganshi.......Ni Kuma naji Shi kadai nake son gani ma .....ta zaro ido. What?
Cikin fushi ta juya gara ta nade tabarmar kunya da hauka... shikenan sai da safe ka cinye wayar ko kaje wurin Yan gyaran waya su bude.....dawo dawo....zo ...zo..zo please. Gashi zo ki goge ya fada da sauri Yana fiddo wayar daga aljihu.
Ta kusa sakin dariya Amma ta daure ta Mika hannu okay bani.
Ya rike wayar yaki saki.....ki rantse da Allah ba text ko hoton wani Zaki goge ba...... Wai me ka daukeni ne?
Ya langwabar da kai hoton nawa Zaki goge?.... Ikon Allah ta fada duk ta Fara kosawa, guda daya ne ko?
Ta sakar mishi wayar ganin baida niyyar Bata..... Ya Kara mikowa ungo amma kiji tsoron Allah kada ki gudu da ita Kinga na rantse.
Wallahi Zan baka Yanzu.
Ya sakar Mata ta Dan ja baya ta fidda key din sannan ta shiga setting ta chanza password din, tana dannawa zata Kara confirming yayi fit!!.... Da wayar, Wai meye kikeyi?.
Kawo na karasa please baka zanyi...... Password kike canzawa??????? Ya fada Yana Mata wani kallo.
Tayi murmushi, Yanzu dai Kara confirming ka Sanya *Balky02* shikenan.......
Dirowa yayi bisa mashin din saura kadan ya fada Mata tayi saurin ja da baya, kawai ya Fara binta Yana magana cikin daga murya.... password Kika chanza? Hankalin sa duk ya Fara tashi cikin bacin Rai....... Ai ...ai ....tanayi tana ja da baya Yana binta.
Gama korar awakin na rantse da Allah sai kin sanar Dani tsohon password dinki da dalilin da ya Sanya Kika canza....au ni Kika mayar photo?
Bayanta ya daki bango ta daga hannuwa sama Dan girman Allah ka ja baya Anwar......waye password dinki?
Ta runtse ido...... Dan Allah kaja baya Zan fada maka...... Kina fadawa Zan koma inda nake meye tsohon password dinki?
Dabara ta fado Mata, sunan da ake kirana gidan mu ne Kuma bana so ka ...... *Balky* shine abinda ake kiranki saboda har daddy da mommy suka tafi banji sun kiraki da wani suna ba bayan haka wane password ne Kika goge Wanda bakya so na sani?
Ka koma yanda kake kada wani ya ganmu a...... Suleiman kike gudu da samarinki ko? Ya Kai hannu daya a bango.
Ta runtse ido na shiga uku.....sai kwalla sharrrr....... Ya kura Mata ido jikinsa yayi sanyi sosai, ya sauke hannun a hankali ya Dan ja baya tare da saka hannuwan sa duka ga aljihu ya kura Mata ido.
A hankali ta bude ido, ita kanta Bata iya fadin ga dalilin kukan, saboda wani yanayi ne ta fada Mai rikitarwa.
Ke shagwababbiya ce?
Kamar ta shako wuyansa,
Tayi mishi banza.
Meye tsohon password dinki?......woohoho, Anwar idan maye ne ya Kama mutum tabbas sai

mutuwa.
Kina so kiga irin tawa rigimar ko?....... *Yar Fara* ta fada a hankali, kakata ce kafin ta rassu take kirana da haka shine na saka........ta karasa maganar tana addu'a a zuciya ya Allah ya ceceta ya yarda da hakan.
Yayi jimmm, sannan yayi murmushi me yasa baki so nasan haka?
Ta galla mishi harara ban sani ba .....Nima meye zakayi da wayata?.
.......yayi Yar dariya, bincike....ai Ni ban boye Miki ba.
Karfe nawa?
Ina ruwanki da ko karfe nawa keda kike bakin kofar gida fadawa kawai zakiyi?.
Ina binki bashin abinci Wanda aka mun kwalele lokacin da mufeeda tasa nayi laifi......ta doka uban tsoki, kaje ta dafa maka mana.
Saboda me?
Saboda yarinyar ka ce.
A'a na kawata nake so my best friend Bilkisu.... Hmmm.
Ko ni ba babban abokin ki bane?
Shine, ta fada a gajarce.
Kika ce mun bakya fitar dare ya akayi yau Kika fito ??? Wannan karon Yar dariya tayi Wai haka kake da masifar tambaya?
Ya bi kumatunta da kallo, yau Kika San haka?
Tayi hamma ,
Barci yazo?
Da sauri ta daga Kai.
Yayi murmushi, to jeki kwanta...... Ta juya da sauri daman kafafunta duk sunyi dayi saboda tsayuwa.
Tace sai da safe.......ya bita da kallo Jin bai amsa ba ta Dan waigo....ya tsareta da ido ta dalla mishi harara.....wallahi  ka fiye kallo da yawa. Ya matso da sauri me?
Ta kwasa da gudu ta fada gida tana fadin Wai yau meke damunka ni Bilkisu??????
Ya Kama dariya kawai ya juya ya haye mashin. Tana jinsa ya tada ya tafi sannan ta shige daki.
Ta cire kayan ta mayar Dana barcin da ta cire ta kwanta.......akwai tambayoyin da nake son yiwa Anwar amma inajin nauyi.
Ta lumshe ido.....yau dole ta kwana karatu kada gobe taci kaniyarta, abubuwan da suka faru suna dawo Mata a hankali.
Ya Allah kasa Anwar mijina ne....ta fada a hankali.
Tayi tagumi, nasan Yana Sona.....Amma Ina son ji daga bakin sa, ya Allah yasa da gaske abinda nake gani a idanun sa har cikin zuciya ne ya bashi ikon *FURTAWA*........ Ta lumshe ido........

Sha biyu saura ya shiga daki.
Dakin a cike ana jiransa.
Ganin hada Yan 100level yasa bai saki fuska ba kada su Anas su kawo mishi wasa( .....Kai Anwar case ne ).
Kowa jinin sa akan akaifa don karamin aikin sa ne ya fatattaki kowa yace barci zaiyi.

A hankali yake kallon kowa daman duk dudumar za'ayi dakin Babu Mai hawan gadon sa,
Ya zauna bakin gado yace to bisimillah....... Duk suka zaburo.
Bai Sami kansa ba sai uku saura.
Tuni su Anas sunyi barci.
Ya kwanta daga Shi da best Daman akwai wuta ya janyo laptop dinsa yayi connecting da wayar Bilkisu ta nuna mishi option ya shiga *transfer file*...
Gallery din ya shiga, a screen din system din yake kallon pictures din......ba karamin tashin hankali ya shiga ba ganin hotunan ta da yayi ba Wanda ta dauka babu hijab.
Duk duniya ba abinda yake son gani a kullum irin ya kalleta ba tare da hijabi ba.
Tsikar jikinsa sai tashi takeyi yayi ma wani hotonta kuri da ido Yana kallon kirjinta........hazbunallah ya fada.
Ya zaro ido ganin wani hoton Shi Kuma ba kallabi gashin ya zubo Mata a kafada ya zarce kirjin ta...... Attachment ne ko nata? Ya fada Yana rike Baki......
Wannan yarinyar anya Bata fi karfina ba?
Zumbur yayi ganin ta cikin kanan Kaya riga da wando tana rungume jikin daddyn ta, gefe mommy ce da kannen ta biyu maza. daganin pic din kasan ba Nigeria bane......yayi Mata kuri da ido Yana kallon kugunta..... Ya fadada murmushi *this is Dubai*....... Nawaoooo.
A hankali yake ingiza hotunan a system din sa. yarinyar nan gaskiya ta gama haduwa.......kutt!!! Ya Kara rike Baki.
Duk wani hotonta dake cikin wayar sai da yasa a system dinsa.
Ya shiga videos, mafi yawa Indian music ne.
Ya shiga text nan yayi karo da text din Suleiman Yana kyarma ya Buda.
```Aslm, Dan Allah lecture din yau karfe nawa ne ?```

Ansa: ```Four```

Na biyun

```Bilkisu ya murar? Allah ya Kara lafiya?```

Ansa:
```Amin thank```

Ya buga tsoki...... Dan iska uban chusu..... I hate this idiot.
Ya bincika ba wani sauran text daga na kawayenta Mata sai nasu Daddy da mommy.
Ya tafi dialing calls, mafi yawan Kiran Suleiman shine yake Kira kusan idanun sa Kira biyu ya gani tayi mishi.
Ya Kara doka tsoki.
Ya Kara komawa message baiga text din da ta mishi na birthday ba.
Ya doka tsoki watan ni ta goge ni ko?
Ya Fara dialing number sa Nan da nan sunansa ya bayyana ```ANWAR```
Ya saki ajiyar zuciya ya Danna sunan ya bi ta message sai kawai yaga text din ya fito, Nan da nan ya gane ta saka Shi secret conversation ne.
```

Yayi tsammmmm! To me take nufi da hakan?
Bana son Mata yawan tambayoyi ko don munyi fada tayi hiding?...
Ya kada Kai kawai.....hmm.
Ya hada xender ya tura Mata GB WhatsApp ya Mata installing.....
Ya rubuta Mata a wall status din ta *You can hide what is on your mind not eyes...*
Profile picture din Kuma ya saka Mata hoton Mommy da daddy Wanda suka dauka tare cikin jirgi......
Kiran sallah yaji an Fara ..... Ya zaro ido....yau akwai chakwakiya fa.....ya rufe da sauri, ya kashe wayar ta sannan ya dauko littafi saboda 8 suke da exam.
Rutsum , itama bata runtsa ba, Rabi karatu Rabi tunani.
Shi ya tayar dasu sadeeq sallah.
Daga masallaci Basu Kara ganin sa ba ashe school ya gudu ya boye Yana karatu.
Babu abinda idanun ta keyi sai zafi. Tana zaune can baya ana shirya su har an Fara raba question paper babu Anwar.
Hankalinta a tashe ga sadeeq ya Mata nisa bare ta tambayeshi.
Tana Shirin mikewa ta dauki excuse ta ari waya ta kirashi ya shigo, Yana ta mazurai Yana Bata rai...... Malamin ya bashi question dinsa da booklet ya ce biyoni..... Sukayi baya.
Yana zuwa dai dai inda take zaune ya sa biro ya zunguri hancin ta malama kalli paper karki sa in Fadi.....ta rasa inda zata sa kanta saboda kunya saboda hatta malaman kowa yaga abinda yayi Kuma Harga Allah ita ba Shi take kallo ba. Tayi sauri ta sunkuyar da Kai bisa table.
Kowa addu'a yakeyi Allah yasa akawo Shi kusa dashi amma malamin nan ya kaishi can karshe last.
Jarabawar tayi zafi, matuka.
Tunda yaga questions din Shima hankalin sa ya tashi yasan sunyi wahala though Shi ba wacce bazai amsa ba.
Bilkisu kawai yake tunani saboda jiya yayi obstructing karatunta.
Yana rubutu Yana dago Kai. Sai ya hango ta tayi zugummm.
Addu'a kawai yakeyi Mata Allah yasa ta Sami mafita...... Da kyar ta iya amsa tambaya daya *b* part din ma da kame kame ta karasa...... Na shiga uku ta fada.
Na kusa da ita kowa yayi zugummm.
Wadanda ke gaban Anwar suka Fara juyawa Nan ya Fara fada musu kwatsam..... invigilator ya hango su.....hey.....hey....yayo baya.
Come....come.....come....ya nuna Anwar taso daga Nan zonan....
Ya tashi a hasale Yana jiyawa na kusa da Bilkisu na Mata magana ko ta gane question 2? Ya hangoshi yace Shima ya taso.......saura kadan Anwar ya taka rawa yace Alhamdulillah a hankali.....suka hada ido da sadeeq ya daga mishi gira sadeeq din ya mishi dakuwa kasa kasa......ya danyi dariya. Ya fiddo wurin yace ma Bilkisu matsa ciki ya ce Kai Kuma zauna.
Yana juyawa Anwar din kafin ya zauna ya ajiye Mata booklet dinsa Shi Kuma ya dauki nata sannan ya zauna kawai ya Buda .
Ya Fara karanta shirmen da ta rubuta kawai ya soke ya bude sabon shafi.....
Tsoro gareta....jikinta ya Fara karkarwa, ta bude tana karantawa.... Ya cika booklet din tabbb...kaiii Anwar *guru* ne wallahi. Ta fada cikin zuciya.
Ya iya bada amsa ga turanci Shi yasa kullum cikin photocopy din C.A din sa akeyi Yan aji.

Tunani kawai takeyi ta Yaya zai karbi tashi ya Bata nata?. Tayi sukutiiiii........ Chinyere ta hango zata you submitting...... Ya daga kai, idan kin gaji go and submit..... Bata San ta mishi wata uwar harara ba......shin nashin zata bayar amatsayin tata?
Dukewa yayi Yana Yar dariya yaci gaba da rubutu.
Sit biyu ne tsakanin ta da Suleiman tana son daga mishi na Anwar Amma sunyi nisa.
A hankali aka Fara submitting...... invigilator din nan yazo yayi tsayi tagar kusa da su.
Anwar na gamawa kawai ya Mike yaje yayi submitting yayi signing out ya fice.....
Kaiii Anwar karshe ne.
Ta kasa tashi. Har sai da akace time out....stop writing, aka bi ana karba...... Ta saki ajiyar zuciya a hankali sannan ta mike taje tayi signing out.
Yana can zaune bisa taga..... Ya kura ma kofar fitowar ido. Tare suka jero da Suleiman.... Bilkisu yau Nasha wahala Allah dai ya kyauta..... Bilkisu kinyi duka ko? Naga Anwar aka maido miki.....Helen ta dafa kafadarta.
Tayi murmushi eh.
Suleiman yayi karaf, da kyar na amsa question one *b* da question three *a*.
Sai na tafi question 4 na buga mishi kame kame ya Allah kasa ko *e* mu Samu na gaji da carry over wallahi....ai Bata da dadi ta fada tana Mai jajanta mishi.
Wallahi Suleiman *Anwar* dan rigima ne Wai kasan Shi yamun jarabawa yayi submitting Ni kuwa yaban tashi na bayar?
Ya zaro ido ban gane ba.
Ta bashi labari...yayi dariya yace *Hmmm* kawai.
Yana ta kallonsu...ji yakeyi kamar ya je ya Shakure Shi.
Na Miki Barka wallahi Allah ne ya duba Miki.
Wallahi kuwa Alhamdulillah ai jiya na kwana du'a'i wallahi saboda daman na tabbatar Ina ruwa....... Karaf suka hada ido dashi.
Ya bata rai,....Ina zuwa Bari na karbo wayata wurin Anwar....... Okay sai gobe Nima zanje waje wani ke jirana.
Ya wuce, saboda yasan ba dawowa zatayi ba dan Yanzu.
Kun gama? Idan baku gama ba kije gashi can zai tafi.....Anya ba kishin Suleiman Anwar keyi ba?
Ta fada a zuciya. Shiru kawai tayi.
Baki da lokaci na?
Ta kalleshi, wallahi duk ka sauya Mani, Yanzu Abu kadan sai ka Fara fada kana sako Suleiman, Yana fada mun yanda yasha wahalar exam ne shine fa ka ganmu....... Bana sonji.
Kina son fada mun cewa kowa baisan Shi din saurayinki bane.?
Zatayi magana ya Mika Mata wayarta, ungo idan daddy ya tambayeki kice wayar ba chargy ta kwana saboda na kasheta b4 ya Kira don't know what to tell him.
Fishi kayi?, Ta ce ba tare da ta karbi wayar ba.
Akan meye zanyi fushi, Ina abinda ya dameni, na Isa in rabaki da Suleiman ne while Nima albarkacin sa nakeci na........ *Anwar*..... Ta Kira sunan sa.
Ya kalleta,
Wallahi ka canza, bana Jin dadin abubuwan nan har ga Allah.
Magana takeyi kamar me Shirin yin kuka.

Yayi shiru kawai,
Amma kayi hakuri idan na bata maka Rai shikenan ko?
Naji karbi wayar ......
Ta danyi murmushi ta Kai hannu.
Kina Sanya attachment?
Da sauri ta kalleshi, ya kura Mata ido....
Ta sunkuyar da Kai Allah ya sawake ban taba ba...... Gashin ki ne haka?
Haka me?.... Daman ka karbi wayar ne don ka man kwakkwafi kazo ka addabeni da tambaya?
Ya bushe da dariya...... Me yasa anan bakya sa ko gyale bare ki kwatanta saka wando mu gani........ Juyawa tayi ta Fara tafiya, ya dirko da sauri ya bita....Ina zakije?
Yasha gabanta.... Dan Allah kiyi hakuri na daina.
Hmmm, ta ce.
Na ce na daina ko?
Shikenan, bani wayar.
Tafiya zakiyi?
Eh, tace,
Suka jera suna tafiya,
gobe ne last paper kuma morning ana fitowa Zan gudu......... Nima gobe Zan tafi. Ta fada mishi.
Haba, Abuja ko sokoto.
Tayi Yar dariya Abuja..... Shikenan na Sami lift har gida ke zanbi ko? Ance Kano kike kawa jirgi Yar gayu ......... Tayi Yar dariya.....inji wane magulmacin.?
Ke fada mun Zaki tafi dani na shirya ko..... Shatar mota zanyi fa ba zuwa akeyi daukana ba....... Shatar mota?
Eh,
To kawai ki Bari mubi motar gidan su sadeeq idan anzo......Kai nifa bana son rabe rabe..... Ba damuwa nida sadeeq daya ne kada ki damu we are now family.
Shikenan Zan fadawa mommy yanda tace ....... Ya watsa hannu fine.
Ta harareshi Kai wallahi Anwar din Nan ka fiye yanga kamar mace......
Ya tuntsure da dariya a'a kin manta nine Bilkisu.
Barci kawai kowannen su keji. Koda suka suka rabu gado kowa yabi lafiya..........
Shako wuyansa yayi suka yi bayan daki.....Kai lafiya ....Wai Anwar kana da hankali kuwa?????
Warning Zan maka wallahi tallahi idan kayi kuskure *you are dead* ya mishi nuni da yanda a wuya.
Da Bilkisu zamu tafi gobe na fada Mata Kai zamubi idan ka saki ka nuna Mata inada alaka da tafiyar you are sorry Dan ubanka.
Zan ma Umar waya in mishi bayanin komai...... Kaji ko?
Naji banza....sakarni toh.
Yayi murmushi. Good and fine.
Wace karyar ka shirga Mata?
Ya tabe baki wallahi bance Mata komai ba Kuma nasan bazata tambayeni ba.....
To kaja ma Umar kunne wallahi......bai da matsala. Kuma wannan karon Shi kadai zaizo ba wani security saboda Kai zaka zauna gaba nida Bilkisu a baya ...... Dan ubanka ni oga Kuma a

gaba? Eh, Kai zakayi arranging hakan.......mtsew naji.
Cikin kwanciyar hankali tayi wa mommy bayani. Tayi Mata nasiha da addu'a , ganin Bata boye Mata hakan ba, (munafunci ga yaro Shi keda ciwo).
Umar yasan dakin su, can ya biya aka Sanya musu kayansu kafin ya karaso cikin makarantar.
Suna fitowa ya tareta Yaya?
Ta ce ta shirya.
Haka suka biya ta dauki jakar ta suka wuce.
Sadeeq ne oga ya kame a gaba.
Shida ita baya..... Ya kalleta. Kinga WhatsApp???? Tayi murmushi eh,
Zamu ringa chatting kinji?
Toh,
Ko Baki da time?
Me zai hana......
Good, ya fada.
Kinyi break?
....tambayo. Ta fada a zuci. A zahiri tace Nasha tea.
Tea?
Umar akwai abinci motar nan?
Eh, yalla....... Yayi saurin datse maganar ya canza da cewa, Yana daga Nan baya.....
Sadeeq ya juyo Kai bana son hauka abincin nawa zaka cinye?
Bilkisu zata ci ko zaka Mata rowa ne......Ni na koshi ma ta fada tana Yar dariya....... Au Bilkisu waa nakeyi I tot koshine keson ci.
Ya yunkura ya dauko cooler sadeeq ya Miko mishi spoons biyu, yabude.....kamshi ya buge motar... Gasassun kaji ne da soyayyen dankali da kwai.
Ya kalleta kici ....
Tayi murmushi.....na gode.
Wani kallo yayi Mata....bakici?
Ta tabe baki Alhamdulillah.
Ya daga kafada, kufa wadannan an Saba haduwa ko? Wurin mu ne sabbin zuwa ya waxgi kaza ya Fara ci.
A hankali a hankali yaci ya koshi tana kallonsa ........Kai namiji baida kunya ita Ina zata iya Shan ko ruwa a nan?.
Ya Mika ma sadeeq ungo...... Miko mun maltina Mai sanyi gaban ban......Ashe Yar cooler ce ta ruwan sanyi dankare da lemuka .......
Ya kalleta me zai Miko Miki?
Ta girgiza Kai na koshi...... Ke kuwa Dan Allah hajiya Kisha ko Mai sanyin ne.......Kyaleta umar tana tsoron kada mu saka Mata baliyan....... Ta zaro ido....yasha mur...... sadeeq bani maltinar Nima...... Ungo wannan Kisha Ni ta isheni. .....ya Miko mata tasa.
Kurba biyu tayi da kyar, ya tsareta da ido.....ko kadan baijin kunya ko nauyin kallonta, taci gaba da rikon ta.........tana jujjuyawa.
......... Kina tunanin Suleiman ne?...
Wohohoho Kai kuwa a Rana sau nawa kake ambaton Suleiman a rayuwar ka Wai meye ya tsare maka?.

Inba tunanin sa kikeyi ba Kisha.....na koshi ne kaima ka kasa shanyewa bare Ni?
Kuna da Yan uwa a Kano?
Um, um.... Ni ban ma taba zuwa Kano ba sai ta dalilin karatun nan.
Da gaske?
Allah kuwa.....
Kai Dan asalain Kano ne?
Yayi murmushi ciki da bai kuwa.....ya bangan ka da tsagen kanawa ba?
Yayi Yar dariya, daga kaina aka daina gidan mu kinsan nine auta gidan mu muna da yawa.....
Ya sunan anguwar ku?.
Keda Baki San Kano ba Ina ruwan ki da sunan anguwar mu kuma?.
Eh, Ina son sani.
Yayi Yar dariya ni ba cikin garin Kano nake ba kauyen Kano karkashin karamar hukumar *Rano* kin San wani gari *Dagama*?
Nope, ta fada.
Yayi Yar dariya.
Suna shiga Kano ya ce a tsaya ya sauka.
Ya Dan fita can gefen hanya.....ya Kira Alhaji Mubarak a airport.
Hello an Gama komai?
Ya rusuna, angama Allah Shi taimakeka.
Yawwah.
Ya shigo motar da sauri, Umar airport muje Airport da sauri please....... Ta kalleshi zakewa????? Shi Dan karo sai instruction yake badawa tun dazun.
Tun daga bakin gate ake Basu girma. Ko kadan Bata kawo wani Abu a ranta ba.
Ya tokare bakin kofa zan koma mota, sadeeq sune Yan gari zasu raka ki har ciki......
Toh, na gode sai munyi. Sai Yan waige waige kamar marar gaskiya......zamuyi chat kinji?
Tayi murmushi ba damuwa....... Manyan mutane biyu ta gani sun zube gabansa Allah Shi taimakeka Barka da sauka.........
Ya zaro ido ita Kuma tabi fuskar sa da kallo........✍🏼😄😄💖

Alawiyya ma na gefe...😝

*ZAINAB WOWO* 💖💖
[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
1️⃣3️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

👉🏽💖💖💖💖 *For Gaje Abu*
👉🏽 Alaweez😍😘🥰🥰😘😘 Ana mugun tare.

*Ya Allah ka Kara Mana katangar karfe da masu bakinciki damu* *Hassada ga Mai rabo taki ce duk Wanda Allah ya tarfa ma garinsa nono wallahi ko ana mazuru ana shaho sai yasha* masoyana ga taku👉🏽💕💞😘

***************
*KADUNA RIGASA*

Tayi zaune falon suna labari da hajiya bayan ta sako doguwar hijab.
Ta kawo Mata lemu da naman kaji......gidan Alhaji shamsu naje shine na biyo ni in ganku tunda Shi ya kwammace yayi ta kullenku da ya barku zumunci.
Murmushi tayi kawai.
Ya kuke ba wata damuwa dai ko?
Babu damuwa, ta mike tsaye bari na Kira ummin ku gaisa.
Da gasken gaske hankalinsa ya tashi sha'"awar Amira ta addabeshi.
Da farko yaji haushin kwalelen da ta mishi amma da ya tuna haramcin yin haka saboda ya shiga hakkin Ummi, sai ya bata uxuri.
Ya shiga toilet dinta yasa ruwan zafi ya warwatsa a jiki saboda ya Sami sauki, sannan ya fito.
Zaune suka tarar dashi suna labari da hajiar, ya kasa dauke idonsa daga Amirar duk inda tayi idanun sa na kanta har Ummi ta Shaka.
Koda suka raka hajiyar Sashen Amirar ya koma.
Ya riko kugunta wallahi gobe sai kin gane kurenki......
Wai Ina Kika saki Kaya haka bayan nasan ke ba ma'abociyar su ba ce?
Inji waye? Ina ra'ayi Kaine naga kamar basa birgeka.......wallahi Ina so. Da kin tsaya dazun tabbas da ba kiss kadai zanyi ba........... Maganar ta makale ganin Ummi ta banko kofa kamar an biyo ta....

**************
*Federal University dutsinma*
......Malam ba Wanda kake tunani bane get lost.... Ya bude baki zai Kara magana ya fiddo mishi idanu I said get lost ya fada cikin tsawa.......... Wai Kai baka girmama manya ne?
This is not your business mutane fa Yanzu kasar nan a firgice suke kamar.....kamar kowa ya haukace irin ka?
Da sauri mutumen ya kalleta, sai kawai ya tashi yabar wurin.
Ya kamata kasan darajar mutane fa......naji kiyi hakuri go....ya Mata nuni da baki.
Kana korata ne don na Fara fada maka gaskiya....... Bilkisu muje...... sadeeq ne ya karaso da sauri.
Sadeeq kayi ma Anwar fada abunsa ya Fara wuce gona da iri ta Yaya zai ringa yi wa magidanta tsawa babban mutum mai kima...... Dan Allah kiyi hakuri ban karawa...ohhh my God.

Ya akayi ne? Inji Sadeeq.
Ta juya suka jera suna tafiya tana magana cikin fada fada, Shi ya raina kowa, mutum da kimarsa yayi mishi magana mistakenly it might be ya mishi Kama da wani ne Wai kaga wulakancin da ya mishi? Haka kawai ya janyo ma kansa dauri a banza........ Kiyi hakuri Zan Kara mishi nasiha don Anwar Kam sai dai nasiha ba fada ba.
Suna wucewa ya saki ajiyar zuciya....... Ya ruga mota.
Yana Zama ya kirata a waya, kamar bazata dauka ba tana kokarin hawa jirgin bayan sun rabu da sadeeq.......
Hello...fly mode Zaki Sanya wayar ki Kuna landing in the next 40-50 minutes I'll call..okay?
Naji, thank bye....ta latse wayar.
Yayi dariya, Bilkisu rigima.
....... Yana bude mota ya shako wuyansa.....Dan ubanka me yasa kakeyi Mata boye boye?
Ya kyalkyace da dariya,
Wane babban mutum ne kayi ma wulakanci a gabanta...... Wallahi su Alhaji murtala ne kasan Shi ya cika shisshigi Ina Jin saukarsu kenan.
Ya zaro ido? Shi ka yankwana???
Kwarai kuwa......anjima idan yazo lissafi Kuma fa me zaka ce mishi?.
Inaaaa bazan bashi fuska ba yasan bana son haka gaban mutane.
Ya kalleshi, jirgin kayan nan fa ya iso tun last week, jibi zanje Lagos nayi clearance a Fara distribution.......
Masha Allah.
Amma me yasa baka son Bilkisu tasan Kai wanene?
Yayi murmushi saboda Suma suna da kudi Kuma...... Kuma ubanwa??..... Ko makaranta kaki nuna ko Kai wanene Wai me yasa kake haka?
Yayi Yar dariya, Kuma fa yarinyar ta gane Zan masifa amsa questions irin lokacin da tasan ni first class ne.
Kana son Bilkisu ko Anwar?.....
Ya kalleshi bana son irin wannan tambayar taka na Fara gajiya da ita, saboda ka kasa fahimtar baka da amsarta Yanzu......mtseww nonsense. Ya Kai mishi duka.
Tarihinka Zan Bata Dan ubanka, Zan fada Mata Kai din wanene..... Da kayi nadama irin Mai ban tausayin nan wlhi.
Sadeeq din suka Fara ajiyewa sannan so gida unguwar makil da jama'a Yan maula kofar gidan ba masaka tsinke .........

*TUSHEN LABARIN*
Babban gida ne a Kano, Alhaji Hamza hamshakin Dan kasuwa ne Wanda aka sani ko'ina a fadin duniyar.
Yaranshi shidda hudu Mata sai biyu maza.
Matansa uku, Allah bai azurtashi da yawan yaran ba,sai yawan dukiya.
Ta farkon hajiya maimuna keda Yara hudu, maza uku mace daya, ta biyun Allah bai Bata haihuwa ba hajiya Jamila, sai karamar keda Yara biyu mace daya namiji daya Kuma Wanda ya kasance Auta a gidan watau mahaifin Anwar (Alhaji Yusuf ).
Ya tashi cikin tsana da tsangwama ta Yan uwa, ganin hakan yasa mahaifiyar Shi ta maida

hankali ga karatunsa fiye da harkar kasuwanci.
Babu Wanda mahaifinsu bai jaraba ba cikin yaransa maza 3 Amma dukkan su sai da suka ha'ince Shi.
Yusuf bai da lokaci ma bare a kwatanta kullum Yana makaranta.
Ya gama jarabawar aji shidda suna jiran sakamako mahaifin su Allah yayi mishi rasuwa daga ciwon ciki.
Nan da nan rikicin rabon gado ya taso.
Aka raba rabo na son zuciya.
Cikin gidajen da suka gada shida Yar uwarsa da mahaifiyar sa suka koma can wata unguwa.
Allah ne gatanta shine jigonta.
Ya ce zai ci gaba da kasuwanci kawai tunda ga jari sun samu.
Nan da nan ya Fara fita China Yana saro turaruka Yana rabawa manya manyan shaguna a garin Kano.
Tun Yana tsayawa Kano kadai har ya Fara kaiwa kaduna, zariya......wasa wasa sai ya bulla har Lagos, Abuja da sauran wurare.
Arziki Kashi........ Nan da nan ya Kara da cosmetics, takalmomi, jakunkuna.....Kai kayan masarufi........kafin kace kwabo Yusuf ya taso da zafi....hakan yasa mahaifiyar sa bata duba karancin shekarun sa ba tace lallai sai yayi aure.
Bai da ko budurwar ma saboda bashi da wannan lokacin.
Itace ta nemo mishi diyar kawarta Yan asalin Yola Fulani basa ko hausa cikin gidansu, lokacin duka bai wuce shekara ashirin da biyu ba.
Shekarar su daya cif da Aure aka haifi Anwar.....bayan ta haifeshi kuma tace ga garinku nan Shi bai San mahaifiyar sa ba.
Tunda ga lokacin ko maganar Aure baya so.
Anwar ya tashi hannun kakarsa, Yana Dan shekara 2 bayan an yaye shi yayar babansa Aunty murja tayi Aure.
Ya kasance gidan daga Shi sai kakarsa mahaifinsu ba mazauni bane sai Yan aiki dake kula dasu suna musu dawainiya.
Duk Yan uwansa arzikin ya tsiyace sun dawo karkashin sa.....
Cikin kankanin lokaci ya nunka mahaifinsu kudi linkin baninkin.
Yan uwan cutarsa sukeyi amma kullum kudin kamar ana Kara musu taki.
Ya mallaki kaddarori iyaka, kamfunna a Nigerian ba inda baya dashi komai Yana shigowa dashi Kuma ana yi na cikin gida.
Anwar na primary school ya Kara Aure, ba hausa Amma mazauna saudiyya yarinya Mai hankali da sanin ya kamata.......watansu uku da Aure hatsarin jirgi ya rutsa da Alhaji yusuf.
Anji mutuwar sa a kasa Baki daya, sanarwar rasuwar ya barar da tayin cikin Amarya.
Illahirin dukiyar Anwar da kakarsa suka gaje ta, Nan take ta ce ta yafe ma Anwar komai na mahaifinsa amma nata na mijinta a fiddo Mata, haka akayi kuwa aka Bata ta karawa yarta murja.
Kafin marigayin ya rassu Yana yawan fadawa mahaifiyar sa amintattun mutanen sa da wadanda ke cutarsa. Baya boye Mata komai.
Cikin amintattun hada Alhaji murtala ( wadanda suka hadu da Anwar airport ), shine kan gaba wajen Jan ragamar kasuwancin.

Tsaron shaguna aka ba wasu daga cikin macuta.
Allah da nashi iko, sai ya dubi maraitar Anwar ya Kara bunkasa dukiyar........
Yana j.s one wata Rana an dauko Shi school sun shawo layin gidan su kawai suka ga yaro gabansu da Keke......da karfi suka taka birki ji kake kuuuuuu.... Yaron ya Fadi da karfi lokacin da keken ya daki motar Kan ya karye tayar ta lauye....Shi Kuma ya karya musu madubi ya karci motar.
Anwar na kwance bayan sit, yaki ko motsi tunda yaga abinda ya faru ya kishingida bai Kara dagowa ba....... Drivern ya fita mutane suka taru sosai, ihu kawai yaron keyi Yana kururuwa wallahi sai an biyashi keken sa, kowa yasan laifin yaron ne amma sai aka goya mishi baya.
Shurun tayi yawa hakan yasa Anwar din fitowa, ya kalli Umar driver yace ya akayi?.......
Sai kawai yaron ya cakumo wuyan Anwar, na rantse da Allah ban sakin sa sai an biyani kekena........ A hasale Anwar din ya kalleshi cika ni ko Kuma wallahi in maka mugun duka anan...ya fizge tare da ingijeshi yayi taga taga.....Nan Yan unguwa kowa ya Fara darewa an San Hali.....
Ya Kara shako wuyansa..... Umar yayi wuf ya fizgeshi...... Sai abun ma yaba Anwar dariya.
Keken nawa yake?
Koma nawa yake wallahi sai kun biyani, don ba inda zakuje ya babbake hanya Yana ware kafafu.
Shigo muje .....Akan wannan shegen keken.....wani nushi ya Kai mishi a gefen fuska, Nan da Nan suka rukume fada...kichaaa...kachaaaa.
Mutane suka yo kansu da gudu.......kowane sai haki yake.
Yau naga bala'i Kai wane irin Dan iskan yaro ne?....... Mugun bugu Zan maka, wallahi na gane fuskar ka matukar ka Kuma zagin keken Nan sai nabarka kwance saboda zufar ubana ce....ita wannan motar zufar uwarka ce da ka fado Mana ko baka ga ka Mana barna muma......
Sunfi awa ana abu guda daya Anwar yace Basu biya Shi Kuma ya hanasu tafiya......har hajiya ta Kira waya taji shiru.
Hankalin ta a tashe ta fito...... Tasa aka iso da ita wurin da ake rigimar .
Yaron ta kalla lokacin da ta iso tace zo muje a siya ma wani keken....ta kalli Umar saka wannan mota......Yanzu naji magana...ya figi hannun Anwar zo muje tare kada a yaudareni.......suka fada motar hajiyar da tazo ciki.
Anwar na shakkar hajiya baya kaunar bacin ranta duk duniya.
A motar yaji tana waya..... hello Yanzu Yanzu Aiko da sabon Keke Mai inganci na Dan samrayi sa'an Anwar .
Suna shiga Anwar yayi saman bene da gudu cikin bacin Rai.
Suka zauna falo Shi da ita.....ta kalleshi ya sunan ka?
Yace *sadeeq* da sauri.
Babanka ya siya maka ne?
Eh, ya zumburo baki cewa yayi idan nayi na daya a makaranta zai siya mun, yau kwananshi biyu fa da saye!.
Tayi murmushi.....to ba sai ya Kara siya maka wani ba idan yaje kasuwa?......ai ba a kasuwa yake yin faskare ba nan kusa da gidan mu ne kullum.....dai dai Anwar na saukowa bene....ta ce innalillahi faskare yakeyi?
Eh, shine yayi ta tarawa ya siyo mun keken.

........hansa'u!!!!!!! Ta kwala ma cikin Yan aikin Kira. Da sauri ta karaso, kawo ma yaron nan abinci.
Ya washe baki Yana Murna,Nan da Nan Anwar yaji tausayin sa musamman da aka kawo abincin yanayin yanda yakeci.
Ya tashi kawai yabar gun.
Da gudu Anwar din yayo baya cikin firgici jin ihu ba kakkautawa........Ashe sabon keken ne aka shigo dashi..
Kawai ya dunga buga tsalle Yana ihu da rawa..... Da hajiya da Wanda ya kawo keken sukayi ta dariya...... Kai Wai baka da hankali ne ? Ya daka mishi tsawa ka bani tsoro a banza wajen hauka......Allah ya baka hakuri Yanzu ko duka na kayi bana ko kallon ka...mtsew ya yi hanyar daki.
Ya ruga ya kamoshi.....zo muje mu dana tare kafin na tafi a titin cikin gidan Nan...... serious ya kalleshi...are u mad?
Baya jin turanci ko kadan ya figi hannun sa kazo mu je ka tukani in tuka ka kowa ya Rama ma kowa sannan in tafi...... Sai kawai Anwar din ya bushe da dariya....Ni yau na hadu da matsala. Hajiya ta Sanya musu ido kawai da tsiya ya fidda Anwar din.....
Ta kalli labaran da ya kawo keken.....yaron can dole ya Zama abokin Anwar saboda zasuyi dai dai........ Shi yasa na tsani karatun kasar waje Ina so yayi anan yasan duniya....... Arziki irin na yaron nan Yanzu Yana da hadari a gareshi....... Hayaniyarsu take jiyowa suna ta wasa.
Da abu yayi dadi a mota aka Kai sadeeq har gida da sabon keken sa da ma tsohon Basu da nisa sosai.
Mahaifansa sukayi ta godiya, tun daga ranar kullum sadeeq sai yaje gidan su Anwar wasa su hau Keke, shillo kamar kananan Yara.
Shakuwarsu yasa Anwar din kawai yace a maida su school daya suka dauki nauyin karatun sa.
Abin mamaki tun a lokacin sai Anwar din ya ringa mishi kandakun kada yaje Yana bada labarin gidan su.
Aka ba iyayen sadeeq jari Mai tsoka Banda taimako da zakka sannan hatta Kaya sutura Anwar ke ba sadeeq tun Yana bashi kwance har ta Kai Shima nashi ake siya mishi.
Suna girma Anwar na Kara miskilanci sadeeq Kuma na Kara lakantar sa ciki da bai.
Yana ss 2 ragamar dukiyar sa kaf! Ta dawo mishi mafi karfin kasuwancin yafi karfe a *Dubai* sai ya kasance da anyi hutu yake tafiya sadeeq Kuma ya tsaya Nan Yana wasu ayyukan.
Ko kadan Anwar baida fahari.
Ko a Dubai yasha Kira cikin yaransa yayi acting as shine Anwar din wajen wata Hulda idan tazo.
...... Babu kasar da baya zuwa da sunan kasuwanci.
Shi yasa da jarabawa ta fito ya cike Nigeria jihar katsina Kuma, don ya na son surveying area din ciki da bai, saboda suna da karancin kasuwa a katsina matuka......
Jiragen sa shidda sannan ya na da share a Abu Dhabi airlines suna bayar da hayar jiragen su.
Anwar hamshakin Mai kudi ne Amma duk duniya ba abinda ke birgeshi irin ya boye Identity dinsa Yana acting as normal person hakan na saka Shi nishadi Shi yasa karatu kasar waje bai taba birgeshi ba yafi so yayi cikin normal mutane cewarsa masu kudi naturally suna da wani abnormality Wanda basu fiye sanin hakan ba........ Duk wani taimako da ake bayarwa makarantar fudma daga miliyan daya zuwa sama Anwar ne ba tare da an sani ba.

Yana da tausayin talaka, Abdul Mai shop yasan Anwar masu kudi ne saboda kyautar da yakeyi mishi na ya Kara jari Kuma ya mishi mugun kashedi Koda wasa kada ya fadawa kowa.
Yana da gadara haka ya tashi fil azal............
*wannan kenan*

Falon cike da mutane ya shigo duk suka Mike Allah Shi taimakeka.......
Wayarsa tayi Kara , *Bilkisu ce* da sauri ya daga Ranki ya Dade Kun sauka?
Um, gashi ma har na Kama hanyar gida....good nima shigata gida kenan mun biyata gidan su sadeeq....Ayyah, ka Kara mun godiya ga sadeeq Allah ya Kara arziki.....Baki da matsala.
Zamuyi waya Anjima please.
Okay bye....ta latse wayar.
Ya kalli Alhaji murtala....... Yallabai yau ka dawo ne?
Ya rusuna Allah ya Kara ma daraja eh wallahi.
Yayi Yar dariya Dan Allah idan Kun ganni da jama'a ku daina irin haka bana so Kun San haka, za a ringa kallona bani da tarbiyya matukar Ina tsawatawa Kuma tabbas bana Jin dadin hakan......kuskure ne ayi hakuri in shaa Allah...... Ina takardun jirgin da ake gyara Jidda??
Ya Mika mishi file gashi............. Sai karfe shidda da Rabi ya shiga ciki.
Tana zaune bisa abun sallah ya shigo........ Yaro da akidar manya....tsohuwar ta fada.
Yayi dariya hajiya tuwo zanci akwai ko?
Eh, ........ Ya Mike a hada mun kafin na watso ruwa na gaji yau Zaki Sha labari.....
Tana kwance bisa kafar mommy falo kiransa ya shigo......ta daga hello Anwar.
Ranki ya Dade......ya gajiya?
Ba gajiya yasu mamah?, Ya danyi jimmm, kafin yace Hajiya lafiyarta kalau,
Ohhh, hajiya yake Kiran mamansa?
Yasu mommy ya katseta. Ga mommy nan kusa dani...Ina gaisheta please.
Tana amsawa.
To meye labari?
Labari na wurinka ni na iya labari ne?.....mommy ta zameta tare da mikewa...
Ki koya Mana sai ki bani.
Me yasa gidanku babu hayaniya ko yaran sunyi barci?
Auwal da musbah ne suna can dakin su.
Ke Kuma kina makale da mommy ko?.... Tayi Yar dariya ai ta tashi ma ta shiga ciki.
Ya Kano din?
Kauyen Kano dai? gamu ciki ya fada Yana dariya.
Ta ce hmm.
Zan Fara fita kasuwa gobe kin San talaka baya Zama......kana kasuwanci ne?
Eh, Ina bin wani ubangidana Ina mishi tsaron shago cikin sabon gari a garin Kano......kin San kasuwar sabon gari?
Naji dai ana fada.
Okay toh can.
Tausayin sa ya kamata.......rashi bai hanashi gadara da izzah ba, Mai Hali baya barin halinsa....kinyi shiru.
To Allah ya bada sa'a ka samo kudi da yawa Wanda zamuci biscuits next semester....ya

kyalkyace da dariya ni Zan siya Miki?
Kwarai kuwa a rama wa kura aniyarta nima sai na ci kudin ka next semester.....hahahaha ya Kama dariya.
Naji Zan dage na samo da yawa.
Ke me Zaki kawo mun tsaraba?
Abinda kake so,
A'a kawai ki dai kawo man ko menene.
Hmmm, tace.
Ko bazan samu ba?
Zaka samu in shaa Allah.
To me Zaki kawon?
Ka fada Mana me kake so?
A a bani da zabi.
To shikenan ka jira zaka gani.
Na gode.
In kyaleki haka ko?
Okay gudnight ta kashe kawai....... Ya doka tsoki jira takeyi ne?
Yarinyar nan tafini
gadara wallahi.
Washe gari bai Sami kansa ba ko kadan, abubuwa sun taso, ba shiri karfe shidda ya bar kasar......
Yanayin abubuwan sai da ya kwana biyu bai samu yayi magana da Bilkisu ba.
Ta nemeshi a waya har ta gaji.
Da ta Kira sai a Fara nata faransanci Ashe France ya tafi ya Kuma chanza layi.
A Rana ta biyu ana ta meeting a katon office din sa Kira ya shigo through WhatsApp ya kalli turawanya ce kowa yayi shiru,
Ya daga... Hello Bilkisu.... Duk kasuwar ce wayar ka Bata shiga? Ina Kira sai wani yare ko ka Sanya Ni voice mail ne?..... Voice mail Kuma ? Yayi dariya kiyi hakuri wasu kayukane muke shiga Saro tattasai Kuma ba service wurin kiyi hakuri muna lissafi da Mai gida anjima zamuyi chatting......
Hakan kuwa akayi tun Sha daya suke chatting har kusan biyun dare.
Amma ita dashi lokutan sun banbanta.....
Daga ranar kuma bai Kara samun lokaci sunyi magana ba.
Fushi tayi Bata nemeshi ba, Suleiman kuwa duk bayan kwana biyu sai ya nemeta sun gaisa.
Ranar da zai baro France aka mishi waya zasuyi meeting Abuja da managers din, *Next, ShopRite da Sahad*
Dole sukayi landing Abuja.
Motoci shidda kebin bayan tasa biyu na gaba. Saboda tafe yake da nashi mutanen.
Ko a cikin motar waya kawai akeyi.
Bayan an gama meeting din suka zagaya ta kofar shiga ShopRite wurin ice cream security sai kyarma sukeyi yau ga Anwar...... An cunkushe kofar an tsaida masu shiga.
Ya Kira Angelina suna magana.........Ai sai ku bamu wuri mu wuce ko?
Da sauri ya waigo *Bilkisu ce* rike da iyayen ledoji..........😄✍🏼

*Ayi hakuri a hankali za a ji yanda labarin ya ke da yanda zai Kare* Banda sauri please mubi komai a hankali.
Zainab wowo ce💖💖😄
👉🏼💖
[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
1️⃣4️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

*****************
*ABUJA NIGERIA*

........ Ya juya da sauri ya kalli Anjelina Yana magana kasa kasa..... Jeki ce su bude kofa ta fita da sauri...
Ta rike kugu tana ta faman masifar su bude kofa zata wuce.
Ya juya a hankali, yana kallonta ta wutsiyar ido. Matsattsar doguwar Riga light pink ta saka da Dan karamin gyale fari iya wuya, kafarta cikin dogayen takalmi....
Anjelina na fada musu sukayi saurin bude Mata..... Ta bude baki iyyehhh ikon Allah yau Allah ya kawo mu ShopRite shiga da izini fita haka..... mtseww ta buga tsoki ta wuce..... Ya tuntsure da dariya....yarinyar can wata Rana sai ta janyo mun rigimar da za a daureta.
Ya fito a hankali Yana leke duk aka bishi da ido..... yallabai lafiya?
Yayi murmushi Ina zuwa ya fita da sauri.
Tana faman zuba kayan bayan mota.
Ya fiddo waya da sauri ya kirata, ya lafe bayan wata mota.
Ta zumburo Baki kafin ta dauka alamar tayi fushi ya kyalkyace da dariya Yana hangenta.
Sai yau ka tuna dani?
Allah ya Baki hakuri ayyukan ne sunyi yawa Kuma kinsan kauye service din waya sai a hankali... always excuses mtseew.
Yayi murmushi kiyi hakuri ai Yanzu na dawo gari Daman wasu Kaya ne muka siyo......
Naji dan kasuwa, Ina wuni......ta fada tana kokarin shiga mota ya musu nuni da hannu, alamar motar can zasu bi.
Ya manta ma da abinda ya kawo Shi,ya Abuja kina Jin dadin ki fa.
Hmmm kawai tace.
A hankali Yana janta da labari suna bin su a baya har suka je gwarunfa a road *111* gidan yake flat 4 Nan ne gidan su Bilkisu..... Next week fa za a koma school nasanka da Kara kwanaki

wannan semester din ka Kara Alalh sai munyi fada...... Amma dai ba ranar da aka koman Zan dawo ba ko? Na Kara ko sati biyu.....daya dai wallahi Nima ranar Zan dawo......
Ya kyalkyace da dariya Hajiya kice kawai kina neman lift Kuma matsalar ba tare da Sadeeq nake dawowa ba Mai rabo ni har na gayyaci wasu.....mtsew a a ka manta... shikenan kayi zamanka....ta ajiye wayar daidai lokacin da motar ke kutsa Kai cikin gate din gidan.
Ikon Allah har taji haushi?...... Kamar yaje gidan yakeji Amma baya so yayi hakan Yanzu. Komin dare yake son komawa kano, haka suka juya Yana waigen gidan.
Bai kirata ba, ya Bari sai zuwa anjima........
Suka kura ma jaridar ido, daddy yayi murmushi ai yaron nan ne wallahi. Na fada Miki kinki yarda Amma Bari Bilkisun ta dawo muji cikakken sunan sa a bakinta Amma tabbas prof. Hamza yace mun lokacin da na saka ayi binkice Kan dabi'un sa da irin rayuwar da yakeyi makarantar...... Da gudu ta shigo, mommy na samo cheese din kuwa....... Ba sallama?
Assalamu alaikum...ta fada tana dariya.
Gardama mukeyi da dadyn ku akan Anwar meye cikakken sunan sa?
*Hamza Yusuf Hamza*...... Duk suka kalli juna shida ita da sauri,..... Ta zaro ido lafiya? Yanzu Ina fitowa ShopRite ya kirani kuwa.....yace me? Duk suka hada Baki.
Ta tabe baki gaisawa kawai mukayi da yake kwana biyu bamuyi magana ba ya ce sunje kauye siyo ma ubangidan su wasu Kaya..... Nace damuwata ya koma school da wuri kada ya barni da tararrabi inyi ta zare ido saboda idan Yana kusa da anyi ban ganeba ya mun bayani shikenan.....
Aikin meye yake?
Daddy ya Kara bukata...... Daddy hoooo nace maka wani yake mawa fa tsaron shago sukeyi a sabon gari market...this is what he told me na.....
Tohhhhh, ai Yanzu muka fahimta. Jeki ciki abinki.
Kin yarda Yanzu da maganata?
Ta zaro ido shine da gaske wallahi.....baya son fada Mata Shi wanene Kuma makarantar ma badda sawu yayi.
Ba tace first class din ma boyewa yayi ba?.... Tabbas.
Yayi murmushi, shikenan mu Sanya su addu'a Kar ki saki Koda wasa ki sanar da ita, wata kila Yana da dalilinsa nayin hakan....
Hmmm. Tace duk jikinta yayi sanyi tana Kara maimaitawa a zuciya *Hamza Yusuf Hamza bushara* Shi ne *Anwar* ikon Allah.
Karfe biyun dare ya sauka Kano.
Bai Sami kwanciya ba sai uku saura, Shi yasa ya makara washe gari wurin tashi.
Sha biyu saura ya farka tun bayan da yayi sallar asubah ya koma.
Ko juyin farko batayi ba ya mirgina ya janyo wayarsa....... Cikin magagi ta dauka hello.......shine Kika ajiye mun waya jiya ko?.
Hmmm, ina kwana..... Duba agogo ki gani Sha biyu ta wuce kike faman ina kwana.
Ina labarin Suleiman,
Lafiya Lau.
Shi Dan wane gari ne....Ina ruwanka ta fada tana tashi zaune.
Yayi murmushi lallai dai Kam, babu ruwa na.
Next week result zai fito waye zai Miki registration?????... Suleiman nake turawa kudi Yana

mun.....kenan yasan password din portal dinki....why not?
Shine ni ban sani ba?
Tayi dariya kawai.
Kinji?.
Nawa ka samo kasuwar? Nawa ne share na Kuma?
Ya kyalkyace da dariya....sai nazo zamuyi lissafi.
Ehee, hakan ya kamata.....tana so tace mishi suyi video call tana Jin nauyi.
Sun kusa awa kafin suyi sallama.

Tunda ya dawo Kano ayyuka sukayi mishi sauki a Rana sai suyi waya sau hudu, chatting kuwa Koda yaushe suna online.

Ya rasa inda zai Sanya kansa da tayin Yan mata.

Sati daya da komawa Bilkisu ta koma, Shi Kuma yace Mata sai satin sama, Amma duk Rana daya suka dawo Yana son Bata surprise ne banbancin shigar dare sukayo sosai don lokacin da suka zo dutsinma daya saura na dare.

.......ya kalli sadeeq an dawo fagen fama.
Suka kyalkyace da dariya.
Sadeeq ya Kara langabe Kai ka dubi girman Allah ko roba roban ne ka sai Mana muma wannan semester din...... Allah ban saye ka Bari kawai muyi ta aro muna 3 in1 hakan Yana matukar birgeni da saka ni nishadi......mtsew..kada Allah yasa ka siya mugu, ya wuce.
Ya bishi Yana dariya, inba kaiba Bilkisu duk duniya Yanzu kunfi sanyani ciwon Kai.

***************

*Federal University dutsinma*
Hutun ya amshe ta, tayi kiba ta Kara yin jawur, Bata son zuwa lecture din Dr Richard munafuki saboda ta tsane Shi. Kuma Yana iya bada test idan yaga ajin ba mutane.

Milk lace ne ta saka Yana da ratsin flowers orange dinkin Riga da skirt, sannan tabi da doguwar hijab.

Agogo kawai ta daura sai zoben azurfar da ke hannun hagu.

Tafiya take kanta a kasa, wani haushi take ji har cikin zuciyar ta idan ta tuna class din yau ba Anwar.
Ga mamakin ta ajin cike fiye da rabi duk an dawo.
Daga nesa Helen ke ihu oyoyo Bilki beauty....
Tana Yar dariya tana Kara sauri tare da ware hannu suka rungume juna.
Kinje America ne irin wannan fresh haka?....
Ta tun tsure da dariya suka fada aji........ Karaf sukayi tozali, ta zaro ido Anwar??????
Ya sakar Mata murmushi kawai, wani dadi ya ziyarce ta kamar ta ruga ta rungume Shi takeji, ya Kara kyau shima yayi haske, tayi kasa da Kai kawai tana murmushi.
Tana Shirin Zama ya taso... Helen move, ya janyota da hannu ya fiddo ta sit din, Shi kuma ya zauna.
Wani mugun kishi ya turnuketa ta kalleshi a hasale ji yanda ka wani kamata ba ka iya cewa ta wuce ko ta gafara dole sai ka cacukumota? Ta Kara sa maganar tana maka mishi harara......
An Kuma dawo fa, yau din nan har na Fara tabka laifi?.
Au hakan da kayi daidai ne??? To ka je Kama kadaddabeta Anwar mtseww ta doka uban tsoki.
Ya dafe Kai, ohhh my God, naji ban kyauta ba kiyi hakuri bazan Kara ba shikenan ko?

Kinji?
Naji, ta fada.
Ina tsarabata?
Ya Mika Mata hannu....... Tana daki na yi tunanin baka dawo ba.
Jeki daukon Ina jiranki.
Kana jirana a Ina? Lecture din Kai zaka mun?
Ai ba zai zo ba Yanzu ya Aiko kafin ya karaso...... Mtsew mutumen nan baiyi ba wallahi.
Tashi muje in baka......ta mike.
Ya shafa Kai da hannu, kije ki dauko mun Ina nan ki dawo.
Inje in kuma dawowa?
Eh, Mana.
Idan na biki muka je kina bani zaki gudu......ta yi Yar dariya in gudu kamar wata marar gaskiya?
Eh, nidai jeki dawo Ina Nan..... Me zakayi anan din?
Jiranki zanyi kawai har ki dawo, a a idan na tafi ka gama sai ka biya ka karba kawai.....wallahi bazan karba ba kuwa, ki je ki dawo akwai labarin da Zan baki.
Ta koma ta zauna, mu gama labarin tukun sai mu tafi tare ka karba.
Ya kalleta better.....
Ina Suleiman Shi bai dawo ba?
Wallahi ban sani ba.
Yasu mommy?
Lafiya Lau.
Meye Kika siyo mun tsaraba?
Tayi Yar dariya kana sauri ne? Ka jira zaka gani Mana..... Ina salalar business dina?
Ba kince zamuje na siya Miki abinda kikeso ba?
Tabbas, Amma dole inji dumus Kuma.....ya kyalkyace da dariya har Yana dukan table....Yan aji duk suka maido hankalin su sai dai ba Wanda kejin me suke cewa.
Watau kiji dumus...... Ta kalleshi tana murmushi eh Mana....... Ashe da gaske ka dawo.... Sukaji magana daga sama kwatsam, duk suka dago *Mufeeda ce* tsaye tana murmushi Tasha wanka..... Ya Dan Sha mur kamar bashine ya Gama dariya Yanzu ba.... Eh na dawo ya kike?
Qalau, ya hutu?
Lafiya.
Dan Allah kazo minti biyu Ina son magana...... Kodai ki Bari sai anjima ko Kuma ki fada anan.
Anjima yaushe.
Evening may be.......
To anjiman zamu hadu, ta juya ta wuce....
Mikewa tayi,
Ina zakije? Ya bita da idanu.
Ta tsuke fuska, daki.
Saboda mufeeda tazo?
Ta dalla mishi harara ta Isa ta koreni ne?
Idan Bata Isa ba ki zauna to, ko don kinji nace Mata anjima? Wallahi don ta kyaleni Ina zata ganni anjima din?.....
Na sani? Ai zata maka waya ko baka zo ba ko?

Wallahi na Miki alkawari bazan dauki wayar ta ba ko da ta kirani.
Kiyi hakuri zauna.......
Ta koma ta zauna. Ya kalleta Yana Yar dariya, saurayin ki ya shiga uku don kina da kishi sosai da sosai.
Tasha mur batayi magana ba.
Wayarsa tayi Kara, Yana dubawa yaga Alh. Murtala. Ya mishi text cewar zai Kira anjima.
Ya kalleta, haka shima Suleiman kike saka mishi doka da horashi Akan kula Mata?
Murmushi kawai tayi tace humm.
Ina ruwana da su? Kawai bana son raini ne?
Kiyi hakuri Zan Mata fada sai ta ringa Baki girma........
Ta kalleshi, ya gyara fuska alamar ba wasa.
Cikin semester din nan Zaki fiddamun gwana cikin su, Aure nakeso gaskiya.....
Saura kadan ta dora hannu a ka.
Ta ce hmm.
Ko bazaki fidda mun ba?
Ta daure ta cije ba tare da ta kalleshi ba tace cikin su wacece tafi birgeka?
Yayi jimmm, ai ruwan ido bazai barni na tantance ba, wace kike ga tafi?
Ta harareshi ban sani ba ta Mike Ina da aiki daki...... Ya gumtse dariya shima ya Mike.
Suka jera kamar ta kwasa a guje tabarshi agun takeji....... Kin San rayuwata Ina son mace wacce Bata da tsoro, .....,..ai shikenan bani ciki kawai, ta fada cikin Rai saboda nikam kamar farar Kura nake don tsoro.........Mai kyau, Mai ilimin addini, wayayya, fara Mai dogon hanci, Mai tsawon gashi, Yar gayu.......shin Wai ni Yanzu Ina ruwana kake ta faman lissafo mun kaje can ka Nemo Mana....
Yayi Yar dariya ke nake fadawa irin wacce zaki nemo mun..... Mufeeda kaje na zabar maka mufeeda ita ce keda duk qualities din da ka zayyano...... Ya Kara gintse dariya mufeeda ba Fara bace Kuma Bata da gashi dogo attach........ Har ma ka sani? Ta zaro ido.......
Eh, Mana kowa ma yasan haka tana boye gashin ta ne?
Mtsew....sai kaje sadeeq ya Nemo maka...... Ke Zaki Nemo.
Tayi murmushi ikon Allah dole ne?
To ai kece babbar kawar tawa ko?
Kema sai in taya ki zabe......Ni an mun miji..... Ya bazga uban tuntube saboda tashin hankali saura kadan ya Fadi tayi saurin tarewa kamar zata taba Shi tace subhanallahi sannu....
Ya Mike idanuwan say duk sun Fara chanzawa daga farare zuwa jajaye.....
Da gaske an Miki miji?
Ya fada Yana gyara takalmin sa, ta kakaro murmushi ta ce aikuwa dai Ina da Wanda Zan aura......
Bai Kara magana ba har suka je kofar gidan.
Ya tsaya kansa juyawa kawai yakeyi, ta fito da Yar karamar leda ta Mika mishi ga tsarabar.....ya kasa Sanya hannu ya karba.
Ta kura mishi ido ya sunkuyar da Kai kasa kawai.
Lafiya dai ko?,
Yayi shiru.
Gabanta ya Fadi...... Anwar lafiya?

Ta Kara fada a hankali .
Ya dago Kai, kirjinta ya buga duk ya wani gigice yayi kicin kicin da rai, ya sunan Wanda Zaki aura?
Ta kalleshi........ Wai shine abinda ya sanyaka damuwa......
Ya Mata wani kallo dole ta kawar da Kai saboda ta tsani kallon banza da rainin wayau.......
Akan meye zai dameni?
Tayi murmushi to naga ka chanza lokaci guda.......
Kaina ne yake mun ciwo.
Ga tsarabar.....ta Mika mishi ledar.
Ya juya ajiye wurin ki Zan karba......
Wallahi bai yiwuwa. Ina ce shine dalilin biyo ni.
Ya kalleta nace ki ajiye Kuma bana bukata.......
Ta tari gaban sa da sauri Wai me ya faru?
Bani wuri in wuce please.
Wallahi baka tafiya sai ka fada mun me ya Bata maka Rai....... ( Cikin zuciya kuwa sai dadi takeji watau Anwar ita yake so yake ta gewaye gewaye. )
Ya kalleta sai ya koma jikin bango ya harde hannuwa ya sokar da Kai .
Kai nake sauraro ta rike kugu.....ya yi shiru.
Ta Fara magana cikin fada fada.
Kace in nemo maka matar Aure na zabar maka ni Kuma bani da ikon da Zan ce Ina da Wanda nake so......... Ke ! Ya daka Mata tsawa.... Na ce kada kiso wani?
Tayi baya da sauri, cikin razana. Ya matso kusa da ita, da kiso wani da ki tsaya haka bai Dame ni ba, I have nothing to do with that, and it doesn't make any difference to me....... ikon Allah ta fada.
Kamar Yana jiranta?
Cikin bacin Rai ta kalleshi, Ni ya dameni ne? Ko mufeeda Shi yasa da ta tare ni tamun rashin wayau na Bari sai a gabanka na Mata warning... saboda bana tsoron ka baka gaba na.....
Damko kafadunta yayi da hannu biyu ya buga bayanta da bango....... Wallahi tallahi idan Kika Kara........kwallah suka zubo Mata sharrrr ta fashe ta runtse ido.
Allah yaso duk ba a dawo sosai ba, kofar gidan ba kowa.
Ya runtse ido da karfi ya saketa a hankali......
Ta yunkura zata ruga gida ya tare ta da hannu idan Baki so in Kara taba ki kada ki motsa...... Ta fashe da kuka.... Hankalin sa yayi kololuwar tashi...... Bai San ya Fadi *Na shiga uku ba*
Bilkisu...... Tasa hannu ta toshe kunnuwanta....
Kiyi hakuri Dan Allah na gwadaki ne kawai.
Ganin yadan matsa baya ta yunkura zata Kara guduwa ya kuwa kamota da karfi ....... Yaya Zan ta Miki magana Baki ganewa? Nace idan Baki so na Kara taba ki kada kice Zaki gudu ko daman kina son hakan ne?
Ya fada cikin tsawa.
Ta Kara rushewa da karfi....na tsane ka wallahi bana son ganin ka , ka kyaleni.
Har cikin kasan zuciya yaji maganar. Ya daure yace ....naji kin tsaneni, kiyi hakuri nayi kuskure bazan Kara ba.....wasa nakeyi.
Nima ai da wasa nakeyi ka Fara .......wasa kikeyi ba a Miki miji ba?

Ta mishi banza...... Saura kadan ya Kara kamota don ya rungume ya saki wani murmushi: nasan wasa kikeyi Nima. Kawai Ina son ganin fushin ki ne don Shi kadai nayi missing cikin hutu.......kiyi hakuri I'm sorry ya rike kunnuwa.
Kinji?
Dan Allah kiyi hakuri wallahi bazan Kara ba....
Ta goge hawayen da kasan hijab dinta. Kawai tayi shiru kanta a kasa.
Baki da wahalar yin kuka meye na kuka anan Bilkisu....kina da shagwaba ko?.
Um? Baki magana?
Yau ni Kuma tawa ta sameni an Kara yin fushi Dani...... Dan Allah kiyi hakuri kinji.

Bani tsarabar ya Mika hannu........ Ta maida duka hannuwanta baya ta boye ledar har lokacin Bata dago Kai ba .
Ba zaki bayar ba?, Zan Kara taba ki wallahi don Zan karba da karfi kibani da arziki kawai....
Zan ajiye sai lokacin da ka nema....
Yanzu na nema saboda haka bani....ya Kara Mika Mata hannu.
Yasa hannu zai janyo hannayenta tayi saurin fiddowa ta Mika mishi. Ta kalleshi Rai bace idan ka Kara gigin taba ni wallahi zakayi Dana sani....... Ya karba Yana murmushi naji bazan Kara ba.
Mun shirya ko?
Ya fada Yana kallonta.
Kinji?
Mun shirya?
Ba zakiyi magana ba?I prefer kiyi mun masifa da wannan shirun fa.
Bani da wannan lokacin......
Me yasa kike da wuyar lallashi haka?
Kai Kuma ka fiye naci ko?
Ya yi Yar dariya. Wallahi naci gareni tabbas ko zamu kwana anan sai kince mun shirya sannan kinyi dariya.
Matukar babu wadannan wallahi kinji na rantse a nan zamu kwana.
Idan Kuma kikayi kokarin guduwa Zan rikeki a hannu na bazan sakeki ba har sai na tashi tafiya, idan Kuma kika Sami damar shiga gida da gudun nan naki binki zanyi har ciki in kamo ki........
Na shiga uku ni Bilkisu akan meye Wai wannan dokokin????
Ya Kara Yar dariya, akan Ina so mu shirya kada mu Bata.... Na ce mun Bata ne? Ko kaji nace nayi fushi?
Au haba? Wai babu ko daya ciki?.... Ta harareshi kawai.
Ya Kara Yar dariya, shikenan.
Maganar lecture, wannan semester din idan na saki na ganki da Suleiman na rantse da Allah zan dauki mataki akansa........ A wane dalili?
Very good question ya gyara tsayuwa....
Na farko ni nake koya Miki karuwa ba Shi ba, na biyu ko Kun zauna a jarabawa ke kike bashi amsa bashi ne ke Baki ba, na uku.....idan ba zaman class din ba ka taba zuwa ka ganshi anan?
Ta rike kugu akan wane dalili zaka Sanya mishi doka akaina?
Na taba hanaka tsayuwa ko magana da ajabon Yan matanka?.

Ya kyalkyace da dariya Yan matan nawa ne ajebo?
Tayi shiru,
To ki ci gaba da kulashi kiga idan bai bace ba bat!
Ta danyi dariya ........ Ya kura Mata ido, lallai mun shirya. Ya daga hannu sama Alhamdulillah!........ Wayarsa ta yi Kara akayi ta Kira yaki dauka....
Kina ganin wasa ko?
Allah sanyawa zanyi ayi kuku dashi....... Matsayinka naa???
Ta tsareshi da ido, matsayin abokin Bilkisu Wanda bai son kowa ya rabe ta....... Maganar ta makale da alama ya kusa yin *subul da baka*.
Shima abokina nane kamar ka nafi sakewa dashi fiye dakai saboda bashi da fada ko kadan ni Kuma na tsani fada rayuwata wannan abotar da kyar zatayi lasting.....
Ya zaro ido da gaske kikeyi ko wasa?
Tayi shiru tana murmushi,
Ke!, Dago Kai ki kalleni ki Kuma maimaita abinda Kika ce Ni da Suleiman duk matsayin mu daya?.......
Ta Dora hannu bisa Kai *wallahi idan akwai abinda ya fi shiga uku a yau to cikin sa nake*....
Dan Allah Anwar kabar ni haka nan na gaji yunwa nakeji har an kusa Kiran sallah.......
Zan dawo anjima.....
Basai ka dawo ba zamuyi magana ko ta waya ne....... Zan dawo da karfe 8 idan Baki fito ba Zan shiga har ciki in fiddo ki.....
Ta bude Baki, sannan ta tsuke fuska, nifa bana fitowa da dare na Kuma fada maka tun last semester.
Na fi kowa sanin haka sai nidin Anwar ne dole ki fito saboda....... Maganar ta makale. Ita Kuma ta tattara hankalinta kaf akansa......
Yayi murmushi, kije ciki sai na dawo anjima.......
***************
*KADUNA RIGASA*
Tayi turus, duk sukayi tsuru tsuru ba kamar Shi guiltiness ya kamashi........ Ta kakaro murmushi Wanda yafi kuka ciwo kafin tace .... Ohhh sorry ta juya yayi Kiran duniya amma Bata dawo ba, Ya saki Amira da sauri yabi bayanta Nan da Nan kishi ya turnuke ta itama.....hawaye suka shatato Mata sharrrr.......✍🏼✍🏼😄
*Zainab Dahiru wowo* ce💖

Ayi hakuri da kadan
[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
1️⃣5️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

*****************

*Federal University dutsinma*

Anwar din nan ya mayar dani sakarai. Shi girman Kai ya hana ya fito yace Yana Sona shine yake ta gewaye gewaye, bai San halina ba, a dole yanda banzayen Yan matansa ke zubda class suna crushing din sa nima haka yakeso nayi..... Ba dai Bilkisu ba, ko Zan mutu bazan ce Ina son sa ba.

Zan daure na cije na nuna mishi ban San inda ya dosa ba inaga idan yaji uwar Bari *Zai furta*.

Ya fada bisa gado...... Ya kalli sama .

Sadeeq ya kalleshi an dawo fa!

Baka ga missed calls Dina ba?

Ina so ince ka amso Mana abinci *M&M*...... Abdul din fa ya daina dafa indomie ne?

Kai ubanka da indomie din Nan, Wai me yasa kake son gana Mana azaba?......

Ya kyalkyace da dariya azabace cin indomie?

Nifa bazanje wani *M&M* ba kawai muyi normal life na student kada mu banbanta...... Ubanwa yace to baka sai Mana gida ba ka kawo mu hostel?

Ya Kara murmushi....ba za ka gane ba..

Ban ganewa wallahi....

Ranar da aka ganoka tabbas ka shiga uku.....in shaa Allah har na gama babu wanda zai sani, Ya bude ledar da Bilkisu ta bashi kamshi ya doki hancin sa, rantsattsen agogo ne Mai tsada cikin cover....... Kai ya tashi zaune.

Menene?

Bilkisu ta siya mun agogo wallahi.

Ya fada Yana daga Shi sama.......

Hmmm, wannan babbar kyauta ce, ka daina cinyewa Yar mutane kudi fa.

Yayi murmushi ya cire na hannunsa ya mayar da nata.......

Anwar a fidda maganar wasa ka dubi girman Allah ka sai Mana gida ko ka Kama Mana haya mubar wannan kwamachalar......

So kakeyi nayi ma wata ciki..... Ya zaro ido.

Yes! Bari na fito maka a mutum sak!

Dan ubanka yanda Yan matan nan ke kawo man hari kana tunanin idan na ware baxasu bini daki ba? Ko ni katako ne da Zan ga mace daga ni sai ita na....... Shikenan, ai shikenan next year by now mun Fara bankwana ma.

Wayarsa tayi Kara ya dauka....... Ya Dan kalli sadeeq buga mun sixteen million times 42 please..........

Bayan ya ajiye sadeeq ya hado musu oat suka Sha sannan suka tafi masallaci.

Akan hanyar su ta dawowa yace sadeeq Ina son ka Sami Suleiman kace kada na Kara ganin sa da Bilkisu....... Dalili?

Ya katseshi.

Haka Nan.....
Zancen banza kenan, haka kawai sai ka raba su babu dalili?
Yaron banza ne bana son sa.....kada ka tsani Dan mutane. Kowa yasan Shi mutumen arziki ne idan kana da wata hujja ka fiddo kafin ka yanke zumunci.
Kana ganin wasa nake ko?
Wallahi semester din nan takunkumi Zan sakawa Bilkisu akan Shi saboda Shi kadai take kulawa yaron Yana da mugun shisshigi.
Anwar! Anwar!! ..... Idan son yarinyar nan kakeyi........ Wai Kai me yasa baka ganewa? Dole sai Ina son ta Zan Sanya doka akanta????
Ni Sona takeyi da take Sanya mun doka inabi?
Ko kasan yarinyar nan juyani takeyi kamar waina?( Masa ).
Kuna dai juya juna.
Kuma duk laifinka ne, ka zauna wurin kallon ruwa kwado yayi ma.....
Sadeeq Banda wani personal business da yarinyar nan da ya wuce friend, kawai bana son tana kula Suleiman period.
Mtseew to ka jaraba ai Bilkisun ba bakuwar ka bace na tabbatar akan Suleiman tana iya kyaleka kwata kwata...... Da gaske? Ya zaro ido.
Lallai dole naci uban yaron nan.
Sadeeq ya tuntsure da dariya, Allah gamu fareka.... Sai ka maida hankali toh.
Kai da Bilkisun duk munafukai ne kowa Yana fama da ciwo ya gwammace ya mutu da ya fitar da cutar......
Kamar ya?
Kai ba bahaushe bane?
Ya doka tsoki....... inyamiri ne ni.
Yaushe Anas yace zai dawo?
Sunday.
Ai Kaine ka kwaso mu badon na shirya ba wlhi.
To ya zanyi?
Ya kalleshi ya zakayi? Wani ya tilasta maka?
Ya kada kafada tare da watsa hannu yace ko daya.
Zaku kaisu idan Kaya ne.
Ina tausaya maka ranar da wani zai maka shigar kutse......
Ku bakwa ganewa, yarinyar nan tana Sona fiye da duk wata yarinya da ke hauka a school din nan, na rasa girman Kan da ya ke hanata *FURTAWA*....... Kai ba sai ka *FURTA* ba?
Mtsew....your are not well.
Ya kwanta bisa gado, ka dafa Mana shinkafa muci da miyar can Mana.yayi murmushi ka canza maganar Kuma? Toh
Yanzu kuwa ya Fara Shirin aiki.

Ya janyo waya ya Kira Bilkisu,
Tana kokarin fere doya Aisha na warming Miya daga gefe Kiran ya shigo,
Ta ce hmm sannan ta daga .....
Hello, Ina wuni......

Ya lumshe ido Yana son gaisuwar ta yarinyar nan nada da'a sosai.
Lafiya, ya kike?
Qalau.
Keda waye nake Jin motsi?
Aisha,
Kuna meye?
Girki.
Me ye ne ?
Kai ai da gangan akai tamabayo......
Doya da Miya.
Zanci.....
Aikuwa baka cinsa sarkin roko....... Ya tuntsure da dariya har Yana sarkewa da miyau.... Aisha ta kura Mata ido tana kallonta. Keda waye?
Ta bude Baki ta Mata alamar Anwar ne ba tare da sautin ya fito ba.
Rowa Zaki mun?
An maka........
Shikenan. Ki shirya anjima zamu je na siya Miki wani Abu cikin kudin Dana tara ko kuwa?
Ka dai ka siyo ka kawon ba sai munje tare ba.
Saboda me?
Haka Nan.
Karya kikeyi ba Kya son samarinki su ganki Dani........ Sadeeq ya kalleshi Kai da wa??????
Harar sa kawai yayi.
Kinji?
Ni nakeyin karya?
Eh, ko gaskiya Kika fada?
Kai Ni ban iya abinda ka iya ba..... Meye na iya Wanda Baki iya ba?
Neman magana...... Ina mamakin yanda ake cewa baka magana kana da jiji da Kai amma Ni wallahi nace surutu gareka ga roko....... Ya Kara yin dariya.... Ke Kuma rowa gareki ko?
Rowar me?
Meye ka ce na baka na Hana?
Abinci.
Mtsew...tayi murmushi badai zance kazo kaci ba .
Muma ga sadeeq na dafa Mana shinkafa Mai dadi Ni na kawo Miki?..... Na koshi aci lafiya.
Allah kuwa..... Bana ci na gode malam .
Kai lazy baka dahuwa sai an dafa an baka ko?
Inji waye? Nafi sadeeq  iya girki ko kina musu?
Eh.
In dafo in kawo Miki Zaki ci?
Noooo, ta fada da sauri. Yayi murmushi yarinyar da kinji akul.
Ta ce hmm.
Zan zo anjima kinji ko?
Okay.
Ki gaishe mun da Aishar Bari na dauki wata waya...... Ya katse Kiran.

Ta kalli Aisha Anwar case ne.
......... Gaskiya ai Yana bala'in yinki. Anwar Dan gadara Shi yake Kiran mace kinji yanda ake surutun miskilancin sa kuwa?
Inaji amma nake ga kamar hada Sheri..... Wallahi da gaske ne.
Yan matan ne basu da zuciya. Kinga wulakancin da ya ringa yi ma khausar har kuka take mishi.... Jakka kuwa ki Sami fareeda yarinyar nan Bata da zuciya wallahi..... Ke Aisha namiji munafuki ne kedai baki sani ba ko Yana gewaye wa.
Last semester gab da za ayi hutu da yazo cewa yayi zance ya fito ya biyo wurina Kuma kema kinsan kilan bai wuce mufeeda ko wannan dayar banzar Yar aji hudu.
Hmmm, kawai Aisha tace.
Salim bai dawo ba Ina Zan Sami aron mashin?
Sadeeq ya Fara maka mishi uwar harara ai taurin Kai da wulakanci ya Hana ka siya Mana sai kaje ka hau kabu kabu......... Wohohoho..... Wai nawa mashin din yake in siya a huta?
150-200k wannan range din.
Mtsew...... Ka shirya gobe ka shiga katsina ka siyo Mana...... Ya buga ihu.
Ya shako wuyansa..... Koda wasa ka nuna inada alaka da hakan ubanka zanci..... Bazan fada ba cika ni mugu...... Ya wuce har ya Kai bakin kofa ya waigo wane police station ne DPO ke Zama a garin Nan??....... Ya zaro ido DPO? Lafiya meye zakayo wurin DPO?
Zan sa ya ma Dr Dan Musa warning da Suleiman akan Bilkisu.......... Wata muguwar dariya ya saki munafuki karshen tuka tika tik... Yanzu ka *FURTA* mun abinda nake son...... Dawowa yayi zai Kara shako Shi yayi bisa gado.... Allah ya baka hakuri.
Amma Ina baka shawara zaka tona asirinka a banza saboda zasu so sanin wanene....inji waye?
Ba zai fada ba. *This is legal warning* ...... Ya fice da sauri Yana duba agogo.
Ya daga murya inzo in raka ka??....... Da ga can waje yajiyo Yana surfa mishi zagi.
Yana sauka achaba Aisha na zuwa zata tsallaka titi..... Aisha. Ya Kira sunan ta.
Laaa Anwar Barka da dare an dawo lafiya?
Qalau, je Kira mun Bilkisu..... Tayi jimmm sannan ta ce toh ta juya Shi Kuma yayi tsaye maimakon yabi bayanta.
Tana tafe tana masifa, je Kira mun Bilkisu kamar wata barar sa..mtsew. Haushi na da Shi Sam bai da manner of speaking Yana magana a gadarance da Isa na tsani wannan wulakancin wallahi.
Tana wankin toilet ta shigo.... Kizo inji Anwar.
Ta dafe kirji...kin ban tsoro wallahi.
Ta harareta kawai zata juya..... Aisha Wai ya akayi?
....... Pad Zan jarbo Ina sauri ya ganni kawai ba wata magana Wai *je Kiran Bilkisu* irin yarinyar nan wacce ya ajiye....
Kiyi hakuri kin dai San Hali...... Eh amma ki ringa kwatanta mishi wata rana Zan yankwana Shi..... Kiyi hakuri dai, jira mu fita tare Dan Allah. Idan mun Gama Zan rakaki..... Wai injira ki wurin sa?
Baki da hankali wallahi idan yamun wani dizgin inyi Yaya dashi?,
Bazaiyi ba, idan ya ganmu tare bazai...... Wallahi bazan je ba. Kina tare da Anwar seems like you don't know him ko? Mtsew taja guntun tsoki ta fice abinta.

Ikon Allah. Kai Anwar nikam tawa ta sameni........ A yanda yayi rantsuwa tabbas idan ban fita ba shigowa zaiyi.

Ta dauraye hannun ta, Daman Riga da wando ne jikin ta, ta zumbula hijab har kasa ta Dan fesa turare kadan ta fito.....

Bashi babu alamar sa, ta juya ta waiga ba kowa, tana niyyar komawa ciki har ta saka kafa daya ciki kiransa ya shigo...... Ta dauka hello....... Kin fito Kuma kin koma.

Ni Banga kowa ba kana Ina?

Bakin titi..... Bakin titi Kuma?

Eh. Ki karaso.... Meye zanyi a bakin titi?

Kina da gardama ne Wai? Just come here simple and short why are you arguing?? Ya kashe wayar.

Wai ni zai mulka? Irin yanda yake juya Yan matansa Nima haka zai juyani? Ta doka tsoki ta wuce ciki.....

Kofar taki buduwa daman tanayin haka some times, da kyar ta bude tana saka kafa Yana saka tashi...... Ta firgita, ta tsorata sannan ta razana ainun. Gabanta yayi mummunan faduwa ta zaro ido tare da bude baki zatayi magana .....ya riga ta, kina daukar maganata wasa ne?

An fada Miki akwai Wanda nake tsoro ko shakka duk dutsinma?..... Babu, Dan girman Allah kayi hakuri muje tayo hanyar fita yasa hannu ya maidata... Ban gama ba....... Sai kawai tayi kneel down na tuba Dan girman Allah muje waje idanunta sun Fara kwal kwal alamar zata Fara kuka...... Ya buga tsoki ya juya.

Ta Mike da sauri ta janyo dakin ta datse ta bishi da gudu.

Tafiya yakeyi yaki tsayawa.....

Ta Kara sauri ta tari gabansa Wai Ina zame je ne saboda Allah?

Me yasa kika zabi bani wahala da bin yarda nake so?.

Kayi hakuri wallahi daddy ya ce baya son fitar dare Anwar kada a sanar dashi zanji Babu dadi....... Da Yan iska yake nufi ni Kuma ba Dan iska bane...... Ikon Allah ba haka nake nufi ba.

Okay to wuce muje..... Zan siya miki sweet ne da kudin aikina...... Wallahi da wasa nakeyi maka kawai na fada ne..... Ni Kuma da gaske na dauka saboda haka wallahi sai munje.

Shikenan, suka jera.

Tayi murmushi ko ke fa? Amma ke komai sai anyi tsiya tukun.

Me kike so?

Duk abinda ya maka.......

Kinga agogon ya mun kyau? Ya nuna Mata .

Um, kawai tace .

Na gode fa, Allah ya Kara dalili.

Amin.

Zaki ci nama suya?

A'a na gode.

Kaza fa?

Bana ci.

Shawarma...... Nifa bana bukatar komai.

Lallai yau zamu kwana a titi...... Ta kalleshi da sauri. Ya bita da ido Daman so kawai yakeyi su hada ido..... Allah matukar Baki ce ga abinda Zan siya Miki ba haka zamu kwana...... Biscuits.

Tayi saurin cewa. Muje ka siya mun biscuits.
Ya yi Yar dariya ko kefa?.
Napep! Ya daga murya. Shi Kuma ya tsaya. Ta kalleshi da sauri...... *Abis supper market* zamu je Nan kadai Zaki Sami biscuits din da kike so..... Anwar, biscuits ko anan akwai Dan Allah...... Mtsew Allah ya raba ki da gardama. Muje ko in daukeki...... Kafin ya rufe Baki har ta tsallaka titi.
Ya dunga mata dariya. Ta turbune fuska..... Gaskiya bana Jin dadin abubuwan nan Anwar bana son abinda kakeyi mun..... Kiyi hakuri.
....Ina zakuje ne?
*Abis supper market* Anwar din ya fada Yana kallonta .
Ta harareshi kallon Kuma na menene?
Wallahi na tsani kallo rayuwata...... Na sani. Yace Yana dariya.
Ka sani Kuma bazaka daina ba?
Ya kyalkyace da dariya Nima na tsani kallo fa ta Yaya Kika San Ina kallon ki?.
Yanzu Ina amfani wani ya ganmu a Sanya Ni a bakin fudma ace har mun Fara fitar dare sai ma a ba abun wata fassara wallahi. Mtsewww.
Fassarar me?
Ta mishi banza.....
Kinji?
Ta harareshi, ya kamata ka daina zuwa mun da dare gaskiya bana iya masifar Yan matanka kullum sai an mun zobe kamar za a dakeni...... Basu iyawa. An fada mun tsoronki sukeyi tun lokacin da Kika Mari kawar mufeeda...... Au ka sani ma ashe.
Yap. Yace Yana murmushi.
Dai dai sun kawo ya Mika mishi kudin suka shiga.
Ranka ya dade..... Ma'aikatan suka taso .
Ta kalleshi da alama regular costumer ne Kai.
Murmushi kawai yayi.
Kije ki zabo biscuits din da kike so.
*Short bread* daya is okay..... Ke bana son gidadanji kije ki kwashi Kaya kinji ko idan kina Jin kunya Kuma muje na Taya ki ya zungureta da hannu.... Kamar ta bude kasa ta shiga don kunya yanda aka Mata ratai da ido.
Sam ta kasa nuna ko daya...... Ya Kira yaron ya ce duk layin Nan sauko shi, tayi Yar dariya tunanin ta zolaya ce yakeyi.
Da sun Kara gaba yaga wani kalar biscuits din sai yace wadannan ma duk safko dasu.......
Wasa wasa ta ga abu da gasken gaske bata San lokacin data janyo Shi baya ba *Kana qalau* kuwa?.
Ya Kai fuskarsa daidai saitin tata kamar zai yi kissing dinta...tayi baya da sauri yayi kasa kasa da murya *Yi kokari ki dizga ni*..... Kamar zatayi kuka ta kalleshi ka dubi girman Allah..... Me yasa kike son yi mun irin wannan magiyar Mai tsada?
Ya katseta hannuwan sa duka a kirji.
Ka ce su mayar da biscuits din can..... Wallahi duk wadanda suka sauko bazasu koma ba, idan Baki sa hannu kin dauki Kaya ba Zan siye duk biscuits din dake super market din Nan...... Ta zaro ido....

Kamar me Zan Dauka?
Na bani ni Bilkisu kawai take nanatawa a zuciya...... Duk abinda kike so perfumes, cosmetics, drinks... everything.
...... Dabara ta fado Mata, okay na amince amma kaga Yanzu duk Ina dasu ka Bari semester tayi nisa Zan biyoka...... Yau fa sai kin dauka Kuma zamu Kara dawowa hakan ma ba laifi bane.
Kamar ta daura hannu a ka ta yi ta ihu.... Ta kalli yaron kaga zo daukon *women million din can please*, Kuna da Apple juice? Eh hajia Mai sanyi ko marar sanyi..... Kamar ta zageshi don takaici, ta daure tace bani marar sanyi.
Suka Kara zagayawa ta dauki robar chewing gum banana.
Ta kalleshi wadannan sun isah na gode.
Are you sure?
Um. Tace da kyar.
Biscuits din da yasa aka kwaso anata packaging a kwalaye manya...... Assorted biscuits ne na kwalaye da gwangwanaye...
Tayi tsuru duk da diririce.
Watau Anwar gidansu akwai kudi shine yake boyewa yace karkashin sadeeq yake komai sai ya nuna sadeeq ke dashi ko zaiyi.
Hmmm, kawai take cewa.
Yasa hannu ya fiddo ATM wasu dunkulallun dollars suka fado........ Ta bishi da ido jikinta sai karkarwa yakeyi ta Fara tsorata da al'amarain sa.
Ya Dan kalleta Yana Yar dariya, ajiyar sadeeq ne.....mtsew taja guntun tsoki tayi gaba.
Ya biyota da sauri ki jira zasu bayar da mota akai mu kayan sunyi yawa....... Ta rike kugu ta tsare Shi da ido sannan tace *WHO ARE YOU??gg?*

****************

*KADUNA RIGASA*
Ta fada bisa gado ta saki kuka..... Ya karaso Ummi tashi ya dagota.... Kiyi hakuri wallahi ba abinda kike tunani bane I just hugged her..... I don't want hear about it.
Naji but kiyi hakuri ya rungume ta, I was confused these days.
Tsakanin Miji da Mata sai Allah cikin second zancen ya sauya launi ya shawo kanta ....
Kuka sosai Amira keyi tana cewa tabbas na ma kaina wauta me yasa na bayyana Mata abinda yake so da Wanda baya so? Me yasa na sakar Mata ragama...
Tabbas ya shiga rudani ya kasa tantance daya cikin biyu... Ta Kara rushewa da kuka.
Yayi lamooo bisa cikinta, ita Kuma tana shafa kansa.... A hankali take magana.
Kafi son matarka Dani, har Yanzu ka kasa sabawa da ni matsayin matarka, a kullum...
Ya rufe mata baki da hannu, I'm sorry baby, Ina sonki musamman Yanzu da Kika dawo normal wife kina biyayya ga sharudda na sannan kina kula dani....
Me yasa kake saurin kamuwa Koda kuwa wani abun munyi shine saboda makircin mu na Mata?..
Yayi shiruuuu..... Ya kasa magana hakika ya gano inda zancen ta ya nufa, ta yi murmushi hakika Yana da kyau ka Zama jarumi Mai iko da bukatar sa.
Kiyi hakuri please I'll change..... Hmmm Allah yasa zaka iya.
Kuma Ina rokon ka Dan Allah idan kasan har Yanzu kana kokwanto akan son da kakeyi mun....

Ba wannan maganar Ummi ya fada tare da janyo ta jikinsa..... Wallahi Ina sonki fiye da yanda kike tunani sometimes Ina rasa meke damuna amma na gano bakin zaren na Miki alkawarin zakiga canji.
Please am sorry dear.
Ya Kara rungume ta........✍🏼

*Zainab wowo ce*💖[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
1️⃣6️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.* ( Allah ya Kara tsareki daga sharrin munafukai Kuma azzalumai ).

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

************
*Federal University dutsinma*

......Ta rike kugu ta tsare shi da ido sannan ta ce *Who are you?*
Ya kyalkyace da dariya *Nine Anwar*..... Wallahi ka Fara bani tsoro ni ban yarda da Kai ba,kawai ta firgice mishi tana baya baya...... Tana neman Tara mishi jama'a ya Fara magana a hankali ```look calm down please I'll explain let's go```.......ba inda Zan bika sai kwallah sharrrr, duk jikinta ya tsinke da rawa.
Ya zaro ido yace ```this is serious```....... Yallabai an saka a mota.... Please zanyi magana bani minti biyu just go away...
Bilkisu please kizo muje Zan Miki bayani.... Wallahi bazan bika ba. Kai Bari na fada maka ni ban ma yarda da dakai ba......sai kuka.
Ya runtse ido yace ohh my God this girl nawaoooo.
Ya fiddo waya, ya Kira sadeeq.... Sadeeq please come to Abis super market now am there with Bilkisu... Ya latse wayar..... Kiyi shiru Dan Allah ke ba ki wuyar kuka what's wrong with you??? Ta mishi banza...
Ya sa hannu zai kamota tayi baya saura kadan ta fada cikin kwalayen lemuka.... Zaki Fadi fa ya daka Mata tsawa.
Ta makure wallahi kana tabani Zan maka ihu.
Ya kura mata ido kawai ya maida hannuwa ya rungume.
Yana hango sadeeq mashin ya ajiyeshi ya fita da sauri..... Please save me she's suspecting me...mtsew ya doka tsoki ya wuce Shi.
Tana tsaye ko motsi ta kasayi, sadeeq ya kalleta zo muje Bilkisu kinji.
Duk jikinta ya mutu ta biyo shi, ya bude Mata mota tana Zama shima ya shigo ya rufe kofa,

Sadeeq ya shiga gaba suka tafi.
Bayan an sauke kayan kaf, sadeeq ya kalleta ya akayi ne Bilkisu me ya faru?
Kwallah suka zubo mata, Dan Allah kiyi hakuri kiyi shiru menene ya faru? Idan Kuma kina da tamabaya akan Anwar kiyi mun Zan baki amsa wallahi...... Wanene Anwar?, Wallahi ni ban yarda dashi ba, duba ka gani ta nuna mishi tulin kayan da hannu wannan siyayyar hankali ce? Kuma naga dollars sun fado aljihun sa yace ajiyar ka ce he's always hiding something from me why?…...
Kiyi hakuri...... Wallahi bazanyi hakuri ba yace mun Shi a kauyen Kano yake Yana business da wani ubangidan sa Kuma...... Karya yakeyi. Sadeeq ya katseta.
Ya kalleshi da sauri, me kake nufi?
Ina nufin gidan ku akwai kudi Kuma cikin garin Kano kake ba kauye ba. Ya kalleta what else do you want to know?........ Ya ingijeshi shikenan ka tafi tunda taji daga bakin ka Zan Mata bayanin saura.
Ya yi dariya, wannan rawar kafar da kakeyi Shi ke tona maka ASIRI..... I said go ya Kara tura shi.
Allah ba inda zanje.
Bilkisu karya yakeyi babba gida ya fito.
Ni meye nawa a ciki da yake boye mun? Ta fada tana hararar sa, ya yi murmushi hankalin ki ya kwanta Yanzu?
Ban sani ba ta juya...... Ya kamota, me yasa baki ganewa ne ke? Nace idan Ina Miki magana ki daina tafiya bazaki daina ba ko? Sai ranar dana kamaki gaban wadanda kike ji ma kunya Zaki.....Amma Kai iyakar Dan iska ka Kai.
Saketa wallahi.
Ya saketa Yana Yar dariya.
Kinga Bilkisu je kirawo kawayenki su shigar Miki da kayan Nan.....bazata dawo ba Kuma wallahi binta zanyi ciki Kama fada Mata.
Don't mind him jeki abinki.
Ya bita da ido.......
Zaka rikita Yar mutane Anwar wallahi ta tsora fa da gaske...... Ya kwashe da dariya kawai.
Asirin ka ya Fara tonuwa sai ka yi kokari Kuma Yanzu ka *FURTA* Mata.... Uwarka.... Yakai mishi duka.
Yarinyar can sadeeq rigimammiya ce Kuma shagwababbiya...... Komai sai ta bude Baki tana kuka.
A gaskiya ka takura mata..... Fitowar su yasa ya tsayar da maganar.
Ko kallonsu baiyi ba ya ce Bilkisu minti biyu..... Ya danyi gefe can nesa.
Tayi tsaye, sadeeq ya kalleta kije kada ya Kara Mata Mana lokaci I'll talk to him please.
Ta wuce kanta kasa, ta rasa inda zata sa ranta.
Ta tsaya nesa dashi,
Ya kalleta ki matso koni nazo Nan.... Ina jinka daga na...... Taku daya ta ganshi gabanta wallahi kina motsawa Ina kamaki, ya fada.
Tayi kasa da Kai.... *tawa ta sameni ni Bilkisu* tace a zuciya.
Ya kamata kiyi mun godiya ko?
Ko nayi laifi ne?

Hmmm, na gode Allah ya biya.
Good, yace Yana murmushi.
Ya kalli hannun sa *I really like this watch honestly*
Ta ce hmm, kawai.
Yanzu hankalin ki ya kwanta kin Kuma yarda dani tunda kinji na fito daga babban gida?
Um, ta ce a takaice.
Gobe ba lecture ko?
Ta ce um.
Sai dare kenan zamu hadu?..... Anwar Dan Allah ka rage zuwa wurina bana son abinda zaiyi affecting karatu na gaskiya.
Ya kura Mata ido yayi shiru.....har sai da ta dago ido ta kalleshi.
Ta mayar da Kai kasa.
Kamar zaice wani Abu sai Kuma ya fasa yace okay I'll try.
Ta ce na gode, sai da safe.....
Ya matsa baya kawai ya bata wuri ta wuce.
Ta Dan kalleshi kadan fuskar sa ta canza alamar damuwa.... Kirjinta ya buga da karfi.
Kamar tayi magana Kuma ta fasa ta wuce.
Sadeeq na tsaye su Aisha Kuma sun shiga da kayan, ta mishi sai da safe ta wuce....
Har ta shige idon sa na kanta ya kalli sadeeq shi Kuma ya banka mishi harara, wannan rawar kafar ita zata......I don't know how to control my self. Abun ya Fara damuna.
Wata muguwar dariya sadeeq ya saki tare da fadin *Anzo wurin.*
Murmushi kawai yayi.
Kana hauka ne kayi Mata irin wannan shopping din?
Mtsew wallahi Bilkisu da kake gani ta banbanta da ko wace irin mace class din yarinyar yayi yawa could you imagine she refused to take abinda takeso sai da taga da gaske Zan kwashe kayan shagon?.
Da sai ka bita a haka for once gaba gaba idan kun Kara sabawa sai ta dauka...... I don't think so.
Kuma wadannan banzayen dollars din ne suka rikitata cos har muka Kare she was shocked but couldn't..... Gaskiya ta firgita.
Ya kamata fa ka Kama kanka gaskiya wallahi kada ta birkice maka kuma ko ta tsorata tsoron yasa ta gujeka.
Mtseew.... I said I'll try. Ya fada Yana yarfa hannu.
And ka rage kakkamata fa..... Ba laifina bane wannan fa, sadeeq yarinyar nan fa baza ka gane ba. Wallahi sai muna tsaka da magana sai ta nemi guduwa I told her this is what will happen idan tayi she refused to listen....and I have no choice than.... This is not an excuse idiot. Ya katse Shi.
Ya kamata fa ka duba kada kazo ka kasa shawo kanta bayan ta rikice maka..... Mtsew naji Zan jaraba.
Yanzu ai hankalin ka ya kwanta ka fada Mata Ina da kudi..... Kuna da kudi dai ba kana dashi ba. Bari kaji na fada maka a yanda kayi Mata Yanzu wannan kadai ce hanya da zata fisshe ka.
Kana tunanin Koda kudi nane da gaske kana iya wannan gabatar? Kayi abinda hankali zai dauka Mana. Amma Yanzu na fada maka Kuna da kudi komeye ta dauka zata ajiye.

A yanda ta firgita some muka fada Mata bayan wannan wallahi Koda ta yarda a fili a zuciyarta zata ci gaba da wasi wasi Kuma hakan zai haifar Mata da bincike akanka... Kayi tunani Mana.
Kuma fa hakane.
Yawwa.
Amma Yanzu kaga tasan Kai Dan masu kudi ne zaka iya komai shikenan.
Yayi ajiyar zuciya *I too much like you sadeeq*
Suka kyalkyace da dariya tare da tafawa......

Aisha kadai ta tarar dakin a zaune ta tasa Kaya gaba tana kallo.
Ko takalmi bata cire ba ta fada bisa katifa....... Aisha na shiga uku.
Wai ya akayi ne? Fada kukayi da Anwar din bayan fitar ku? Naga alamun kinyi kuka Shi Kuma sai babbata Rai yakeyi...... Aisha Anwar yafi ciwon ciki.... Ta kwance Mata zance kaf!
Ko kadan Aisha bata razana ba. Sai tayi murmushi tace, ni wallahi nasan Anwar Dan manyan mutane ne. Haba kiyi tsam da Rai ki kalleshi da kyau ya Miki kama da mazauni kauye?
Ko fatar jikin Anwar Kika kalla kinsan ana rayuwa cikin A/C da Jin dadi.
Bari in Baki karamin takadiri ki kalli yanayin shigar da yakeyi duk kayan Anwar tsadaddu ne daga manyan kamfuna manya manya irin su *Gucci, M&S, C&K* ke gasu nan. Ji takalmomin da yake sawa..... Haba mutane, Ni wallahi nasan karya ne ace duk sadeeq ke musu sai dai na yarda shikeyi ma sadeeq saboda ko dressing yanayin dauka a jiki ma ba daya ba Koda kuwa iri daya suka saka .
Ji lokacin zuwan su daddy ke baki lura bane Amma wallahi wani taku da Anwar keyi nasan yaron yaji bariki wallahi.....
Ke ni al'amarin sa ya Fara bani tsoro Aisha...... Hakuri zakiyi sonki yakeyi Kuma ya kasa *FURTAWA* kawai idan ya Miki kina sonsa Ina Baki shawarar kada ki Bari wata tayi Miki shigar kutse sannan kada ki yarda ki nuna kin San inda ya dosa ki barshi har ya gaji ya *FURTA* idan da gaske yakeyi.
Koda yake wannan hauka haukan da ya Fara tabbas saura kiris ya *FURTA*....... Aisha bana iya wa Anwar har ga Allah..... Ba Kya son sa?
Ta tsare ta da ido...... Tayi shiru ta kasa magana.
Kinji?
Idan bai Miki ba ki fada mishi ya rabu da ke, naga dai yanda Yan Mata ke neman kashe kansu saboda Shi Amma ke ya zabe ki kamar tumun dare Zaki..... Understand me please.
I'll never understand you. Namiji kowa da kalar soyayyar sa, Anwar miskili, gadararre, Wanda ya Raina kowa kije kina bada labarin da kike bani Yanzu wani sai ya mare ki saboda cewa zasuyi karya kike yi amma Ni ganau ce ba jiyau ba.
Amma ji yanda yake Miki rawar kafa.
Wallahi Yanzu dan ana farkon dawowa ba mutane Amma tabbas ni nasan wannan semester din akwai daru za 'ayi kallo. Sai ki dage..... Abinda ke tayar mun da hankali kenan wallahi.
Tayi dariya zai tare Miki nasan dole ya..... Wani abun ba agaban sa zai faru ba Aisha.... Yanzu ni ya zanyi da wadannan Kaya ni Bilkisu.... Ci zamuyi. Yanzu fa aka dawo.
Ai wallahi mun gode......... Wayarta ta Fara Kara.
Ta kalli Aisha Anya Anwar zai barni nayi abin kirki wannan semester din?..
Tayi dariya ta kwashi biscuits da wasu tarkace tace keni sai da safe...... Taja Mata kofa.

Ta kanga wayar a kunne ba tare da tace komai ba...
Ko har wayar ma an Sanya Mata doka?.
Ya fada Yana Yar dariya.
Hmmm, kawai tace.
Ke na gaji da hmm, dinnan da kike neman ki ringa kawoshi bana son sa ki bude Baki kiyi mun magana kinji ko?.
Toh, tace a hankali tana murmushi.
Da gaske ba Kya so Ina zuwa wurinki?
Eh, tace da sauri.
Saboda me?
Ta runtse ido anya mutane sun San Anwar kuwa da ake mishi shaidar baya magana?... Kinyi shiru. Ya katseta.
Haka Nan,
Baiyiwuwa ki fada mun dalili ko Kuma gobe ki ganni...... Dokar daddy ce, sannan zuwan naka zai rinka haddasa mun fitina tsakanina da Yan matanka, idan Kuma aiki yayi nisa Zan Sami raunin karatu...... Zuwa gidan naku?
Eh,
Fine. Zan daina zuwa shikenan ko?
Eh, ta ce tana murmushi.
Idan Zan ganki muyi magana Kuma fa?

Sai na sameka class....fine, gobe mu hadu new lecture rooms by four. Yana fadin haka ya kashe wayar.
Ta bi wayar da kallo tace ikon Allah..... Allah ya kawoni ni Bilkisu.....
Tayi shiri daga sallar la'sar, a hankali take tafiya ga nisa daga masallaci zuwa classes din, kanta a kasa kadan kadan take gaisawa da mutane.
Kugin mashin taji a bayanta tayi saurin Kara matsawa gefen titi, gabanta suka tsaya, ya sauko sanye da kananan Kaya kamar kullum ya rufe ido da facing cap... Ajiye ni a nan.
Ta dago ido da saurin Jin maganar sa. Shida sadeeq ne bisa sabon mashin fari duk leda jikinsa. Sadeeq Ina wuni ta fada tana murmushi.
Lafiya Lau Bilkisu.
Ta Dan kalli gefen sa Ina wuni.
Yayi kamar baiji ba, ta ce ai kaji tsiyar Shi dizgi wurinsa bai daukeshi bakin komai ba.
Ka kawo man upstairs Yanzu please ya fada Yana kallon sa ya juya da mashin din Shi Kuma ya jera da ita suka ci gaba da tafiya bai ce komai ba,
Ina gaishe ka amma kayi shiru.
Ya dago ido cikin facing cap kince sadeeq Ina wuni Ni Kuma kin wani ce Ina wuni sunan nawa Yana Miki wahalar fada ne?
Murmushi tayi kaii ikon Allah Wai haushi kaji?
Anwar Ina wuni?
Sunana Hamza.... A'a Nan Kuma daya fa. Sunan da kowa ke kiranka Zan ambata sai dai idan kana neman magana ne sai inji.
Shiru kawai yayi Mata.

Tayi Yar dariya yau gadara ake ji, ta fada cikin zuci tana satar kallon sa Yana ta faman Shan kamshi Yana Bata rai.
Maganar meye zamuyi kace mu hadu yau?
Kina sauri ne?
Tayi dariya ohh ni Bilkisu halan bani da ikon tambaya.
Murmushi kawai yayi ta gefen kunci.
Suka shiga class din ba kowa sai mutum daya shima da alama chargy yakeyi, kasancewa farkon semester ne.
Ta toge bakin sit....ya kalleta wuce ciki ko ni Zaki saka cikin kujera?
Ka zauna ni Bari....... Ya ingizata da karfi tayi ciki ya bita dole ta matsa da sauri kada ya Kara kamata...... Kina da gardama, na fada Miki idan Baki son Ina kamaki ko taba ki kada kiyi mun gardama amma da alama kina da kunnen Kashi...... Ya karasa maganar Yana Zama kujerar kusa da ita.
Da sai ka bada tazarar kujera daya tunda magana ce zamuyi ba karatu ba...... Bazanyi hakan ba.
Tayi shiru tare da sunkuyar da Kai tana wasa da yatsun hannunta.
Yasu daddy?
Lafiya lau, dazun munyi waya yace mun zasu tafi Paris da mommy.
Haba?
Allah.
Yayi murmushi *Yan gayu*.
Ta Dan harareshi.
Dafatan baki sanar da kawayenki abinda ya faru jiya ba, kin San bana son yawan surutu ne yasa bana nuna ni din wanine.....
Aisha ce Kuma ta rigani sani... Tasan meye?
Kuna da kudi?
Kice wallahi.... Tayi murmushi Allah kuwa, ta bashi labarin yanda sukayi.
Ya danyi tsoki, kawai don Ina sa Kaya masu kyau Shi zai nuna muna da kudi? She's not well.
Eh din. An dai gano ka.
Ya danyi dariya kawai.
Wace magana zamuyi kace nazo?
Ba gashi munayi ba?
Ko wata ta daban kike so muyi?...... Tsayuwar mashin din sadeeq yasa maganar da zatayi ta koma.
Ya dora Kai bisa table ta bi bayanshi da kallo.
Ko baka lafiya ne yau? Naga duk kayi sukuku Anwar..... Sadeeq ya shigo ya ajiye ledoji bisa table din gashi nan Zan je na karbo sako isah kaita idan ka gama ka kirani.
Bai dago Kai ba Yana duke ya rufe ido kawai.
Tayi shiruuuuu tana kallonsa...
Anwar..... Ta kirashi a hankali.
Ya dago Kai ya akayi?
Baka lafiya ne?
Ya yamutsa fuska yunwa nake ji ..... To ba gashi nan sadeeq ya kawo maka ba Kuma kana Jin

sa Anwar kamar karamin yaro kayi shiru.
Fiddo ki ban ya fada tare da kokawa ya kife..... Bata San lokacin da tayi dariya ba ta Mike tare da saka hannu ta janyo ledar sai gogar jikinsa takeyi yaki Kuma gyarawa.
Ta fiddo hollandia biyu milk and strawberry, tashi gashi ta fada tare da fiddo wata leda, katuwar gasassar kaza ce taji cabbage da kayan miya nade a foil paper.
Ta bude ikon Allah dadi za'aci Alhaji Anwar..... Ya dago Yana Yar dariya keni wallahi tuwo nake son ci miyar kuka..... Ta kalleshi ka iya tukawa ko?.
Yayi murmushi Allah da gaske nake Ina son cin tuwo Bilkisu ya langabe Kai.
To ka je ka siyo Mana.
Ke zakiyi mun. Zan siyo semo kiyi mun anjima...... Kam wallahi kada kasa ma ranka abinda bazaka samu ba. Zan samu yau sai naci tuwo Kuma ke zakiyi mun.
Ya bude kazar ya cire wurin cinya ya Fara ci.
Tayi shiru kawai.
Wane kike so milk din ko strawberry?
Kai wane zaka sha?
Bani da choice as long as nidai cikina zai cika..... Ta yi dariya kawai ta dauko milk din ta Fara Sha a hankali.
Zakici kazar ko kunya kike ji?
Ta Kara Yar dariya, na ci abinci na koshi.
Me Kika ci?
Taliya muka dafa.
Zaki mun tuwon?
Zan maka Amma ka Bari sai gobe yau dai marece yayi sosai.
In siyo semo din?
Ina dashi Kar ka damu.
Good.
Ba za kici ba da gaske?
Allah na koshi....... Zan baking baki matukar Baki sa hannu kinci ba..... Rage mun idan naje daki zanci da dare.
Mtsew, Allah ya raba ki da gardama.
Yaci gaba da cin abinsa.
Mamaki kawai takeyi Wai me yasa maza Basu da kunya ?
Kamar ya karanci zuciyar ta ya kalleta...... Ni banjin kunyar ki.
Ta danyi dariya ....yabi kuncinta da kallo....
Kin San cewa kina da kyau kuwa?....... Ta kalleshi da kyau me kace?
Yayi murmushi kina son in maimaita abinda Kika Riga kinji?
Hmm, tace.
Samarin ki nawa?
Zaka Fara ko?
Ana zaman lafiya ka Fara tamabayoyi marassa amfani kuma azo ayi fada ko?
Ba Kya so na sani ne?
Ina ruwanka da samari na an fada maka irin ka ce da kowace jik and jak ...... Ya sa hannu ya buge Mata Baki...... Kai Kai Kai ta rike Baki.... Sai tayi kwal kwal zatayi kuka.

Ya harareta wallahi yau kikayi mun kuka Zan baki mamaki ke baki da aiki sai shagwaba.? Gaskiya bana son abinda kakeyi mun Anwar..... Gaskiya bana son abinda kake yi mun Anwar ya maimaita Yana kwaikwayonta.

Karfe nawa Zan zo na karbi tuwo gobe.... Zan Aiko maka Dan Allah ba sai kazo ba ko ka turo sadeeq ya karba.... Wani kallo ya jefe ta dashi kafin yace *why are you pushing me away?*

Ba haka bane...... Haka ne.

Bazan zo ba, ki Aiko mun ya Miki ko?

Tayi murmushi eh,

Duk ya kware tsokokin kazar ya tura Mata kasusuwa ga naki..... Ta danyi dariya wallahi kana da ci Anwar...... Ya yunkura zai Kara buge bakin ta tayi baya tana dariya.

Tashi muje kada six tayi na gaji tunda ka gama.

Ki shanye tukun.

Tabbb bazan ya ba.

Shi yasa ba Kya kiba.

Hmm, kawai tace.

Wayarsa tayi Kara Yana dubawa ya Mike please Ina zuwa...... Ta mishi wani kallo ya nuna Mata fuskar wayar Alhaji Abbas ne kin gani?... Ya fice Yana dariya kunya ta Dan Kama ta ganin zai fassara ta.

Ya Dan dade kafin ya dawo tana ta latsa waya taji yayi fit da ita.......

Bani naga suwaye samarinki.......Aka Kara kiransa a waya.

Ya kalla sai kawai yayi tsoki, sai ka bar nan ka kirata ne?...... Sai bani kawai yayi picking yasa handsfree.....

Ya akayi?

Haka ma zaka ce?

Baki bani amsa ba nace ya akayi ne?

Jiya an Kai maka abinci ka dawo dashi, tun jiyan nake kiranka kaki dauka Wai me yasa..... Nace kiyi mun abinci?

Sai kace sannan zaka ci?

Ke idan Baki da abin fada Ina da abinyi ya kashe wayar.

Ya kalleta kin yarda Yanzu ita ce ke damuna bani nake binta ba?.

Kai ji Ni me nace toh?

Sai kince? Rigimar ki ai nasan ta.

Wannan semester din na ganki da wani Kato wallahi sai naci ...... Maganar ta makale ta zaro ido ya Mike da sauri tashi muje na rakaki.

Ka karasa abinda kake son fada?

Yayi murmushi kawai,

Ya daure fuska ta mike ka Isa ka hanani gaisawa da mutanen arziki na?

A matsayin a na wa to da zaka Sanya mun irin wannan dokar?

Ke ya Isa tunda nayi shiru kuma Dan Allah ki kyaleni.

Suka jera suna tafiya.

Suna karyo wata kwana su mufeeda na tahowa ta tsaya gaban sa kutumar uba Wai kana cikin school din Nan...........???????✍🏼

*Zainab wowo* 💖💖

Zan kawo muku wani true life story anjima Dan Allah Ina bukatar comments din ku please. Na gode masoyana Ina kaunarku.💖
[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
1️⃣7️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

***************

*KADUNA RIGASA*
Duk ina son ganin ku falona da karfe takwas...
Ya tura ma kowace sako.
Duk sun you zugum suna mamakin wannan Kira , abinda bai taba ba.
Ya rage karar TV.
Agurguje ba lokaci maganar zata dauka ba, da farko Ina godiya da Jin dadin yanda ko wace ke kokarin faranta mun da Kuma dagewa wurin kyautatawa, hakika naga canji a gidan Nan. Allah ya saka ma ko wace da mafificin alkhairi.
Magana ta karshe doka ce Zan saka na neman shawara ko neman izini ba.
Daga yau na Hana ko wace ziyarar dakina matukar ba ita ce da girki ba. Sannan daga yau kada wacce ta Kara bina ko ta shiga sashen dayar ku matukar Ina ciki.
Wannan shine.
Ummi kina iya tashi ki tafi sai da safe...... Ya Mike yayi ciki.

***************

*Federal University dutsinma*

Gaban Bilkisu ya fadi ita Kam ta tsani fitina a rayuwar ta, tayi kasa da Kai tare da wucewa a hankali..... Ya chafko hannunta ya rike gammm, ba Bilkisu da mufeedar ba duk wadanda ke wurin sai da suka fiddo idanu waje.
Yasha mur ya Kara janyo facing cap dinsa ya rufe idanun sa Yana kallon kowa kasa kasa sannan ya maida kallon sa ga Bilkisu Yana janyota baya a hankali Yana fadin ```yaya Zaki tafi ki barni bayan kin San...``` Amma Anwar ka maida mayar dani Yar iska. Au daman saboda wannan sillan Karan kake Mana yawo da hankali....tabbas yau na gane ma ido na.....
Sake mun hannu Bilkisu ta fada tana doka mishi harara, yayi kamar baiji ta ba.
Ya kalli mufeeda kin gama mu tafi?...... Na gama ai daman ban tsayar da Kai ba ko?
Ta fada tana huci.... Ya ja hannun Bilkisu suka wuce..... Kwallah suka zubo Mata sharrrrrr ta

fizge hannun ta da karfi yayi saurin kallonta cikin hula Yana Mai daga kansa sama..... Kuka again?
Ya fada Yana kallonta.
Ni zaka zubda wa mutunci a gaban bainar jama'a? Ana ganina da kima da mutunci.....ke! Wai me nayi?
Hannu na da ka rike ni muharramarka ce? Ta zaro mishi ido. Yayi murmushi Bilkisu rigima, na lura duk duniya ba abinda Kika fi so da kauna irin na taba ki saboda na fada Miki cewar matukar Ina tare dake ban sallameki ba Kika nemi Bari na ki tafi wallahi ko a gaban waye Zan Kama ki, me yasa ke baki ganewa kiyi mun biyayya?......
Bazanyi biyayyar ba, na ce bazanyi biyayyar ba.... Ta nuna Shi da yatsa jira kaji Anwar na lura da take taken ka kana son mayar dani irin su mufeeda da ke binka suna maka biyayya kana musu yanda kaga dama ko?
Saurara da kyau, bana tsoron ka , bana shakkar ka na gaji da wannan dokokina naka marassa Kan gado.
Ka tafi kaje mufeeda is ready for that not me.....ta hada hannuwa alamar tana rokonsa abeg leave me alone.... Ya rungume hannuwa duka a kirji ya tsareta da ido kawai Yana kallo.
Ta mishi kallon up and down ta wuce tabarshi a tsaye.
Yabita da ido har ya daina ganinta...
Yayi shiruuu, me yasa bazan kyale yarinyar can ba?
Anya Bilkisu ta damu dani kamar yanda nake jinta azuciya?
Me yasa ta fita daban cikin matan jami'ar nan take bani wahala ta kasa gane irin qimar da nake da ita.?
Wai ko wannan haukan da Yan Mata keyi a kaina me yasa ita bazata ringa mun yanda nake so ba don su fahimci tafisu?
Mtsewww yaja dogon tsoki, sannan ya fiddo waya ya kira sadeeq, *zo ka daukeni*
Yanayin muryar sa kawai yaji yasan an Kara kwafsawa .
Kicin kicin ya iskeshi bakin gate ya hau mashin din kawai suka tafi.
Yana zuwa daki ya fada bisa gado yayi ruf da ciki....

A bakin kofa ta hadu da Aisha ta bita da kallo kafin ta rufa Mata baya suka nufi dakin Aishar........ Yau ma kuka?
Kuka Zaki ringa mishi lallai kina da aiki...... Aisha bana son abinda Anwar kemun kawai a gaban su mufeeda ya rikon hannu Kuma ya rikeni yaki saki saboda Allah me zasu daukeni?
Ke yau ai na shiga uku Kinga kallon da kawayenta ke mun da ita kanta....... Ai dole. Kut! Wallahi dole su kalleki, Al'amarin Anwar ya Fara ta'azzara gaskiya Kuma Shi yaki fitowa ya Fadi ainahin abinda ke ransa ...... Yana jiran ni na bishi irin su mufeeda haka na lura amma wallahi ki barshi idan yasan wata bai San wata ba.
Ta wuce dakin ta don ta gabatar da alwalar magriba.
Ta kashe wayarta kada ma ya kirata,
Washe gari tara suke da lecture, akayi sa'a malamin ya zo. Ya bayar da first assignment cikin part of outline din da zasuyi semester din, Anwar na baya can karshe idanun sa na Kan Bilkisu dake tsakiya ita da su Joseph, lokacin da ya fita ne ta karbi littafin Joseph din tana rubuta inda aka wuce ta. Tana gamawa ta mike Anwar ya kwada Mata Kira.....

Bilkisu.... Ta waiga da sauri saboda yanayin yanda ya daga murya duk ya janyo hankalin wadanda Basu Kai ga fita ba.
Zo ki zauna anan ya nuna Mata kujerar dake gefensa ..... Kowa ya tsareta da ido Yana jiran response dinta,
Me Zan maka? Ta fada tare da tsuke fuska.
Kawo mun note dinki zanyi using ...... Bai rufe baki ba ta jefa mishi littafin har ya daki fuskar sa, gashi nan idan ka gama gobe Zan karba Ina sauri ta yi hanyar waje.....da gudu ya fito har ya ba wasu tsoro.
Ita kanta sai da gabanta ya Fadi lokacin da ta wurga mishi book din saboda tasan cewa ta debo ma kanta wutar dafa kanta.
Ta yi sauri ta tsaya tare da rike kugu....... Ni Kika jefa?
Ya fada Yana zaro ido.
Ta mishi kallon up and down kafin tace idan kaji haushi ka maido mun littafi na Mana.... Jeki dauka bana so ya fada Rai bace .
Fine , ta fada tare da wuce Shi ta koma class din.
Duk aka kawar da fuska ganin ya biyo bayanta, samm bata lura ba Bata Kuma ji takunsa ba.
Littafin ya fada can karkashin desk ta kutsa can ciki ta Kuma duka tana kokarin dauko Shi, ya shigo sit din ya zauna, ita kuma tana ciki.
Dagowar da zatayi taji ta fada bisa kafar mutum ta mike da sauri innalillahi.... Wai kanka daya Anwar??? Ta daka mishi tsawa.
Idan baki so na Miki abinda Kika tsana ki zauna silently muyi magana wallahi idan Kika kuskura anan zan Miki abinda...... Bazan zauna ba bani wuri in wuce.
Naki na bayar ko Zaki daukeni da tsiya ki fitar? Me yasa kike da gardama Bilkisu???
Kai Kuma me yasa baka da zuciya?.
Yayi murmushi nima Ina neman amsar nan wallahi..... Ta ja tsoki kanka akeji bani wuri.
Ya kalleta alamar ba wasa yayi baya da hular sa , kin san Allah idan Baki zauna ba Zan daura ki a bisa cinyata ki zauna in kuma rikeki har sai na gama maganar da zanyi ko bazan iya ba?
Tayi shiruuuuu, sai Kuma ta zauna saboda tasan karamin aikin sa ne sai dai idan ya aiwatar daga baya ya bada hakuri.
Ya bita da ido Yana murmushi..... Ta Kara tsuke fuska Ina sauraron ka ba ka tsareni da ido ba......
Me yasa Kika tafi Kika barni jiya?
Saboda ka gane baka gabana bana son wannan shisshigin, Kuma na Kara fahimtar fakai bana son kana taba ni na tsani hakan .
Kin tabbatar bana gabanki?
Ta kalleshi shekeke Zan ma karya ne don Ina tsoronka ko kana nufin...... Ina nufin mufeeda ce ta Kara Bata Miki Rai ko?
Mufeeda? Mtseww a'a ka manta.
Idan ba ita bace me yasa Kika hasala sosai Kika tafi Kika barni?
Saboda ka rike ni na kuma fada maka bana so..... Me yasa ke bazaki daina abinda nima bana so ba?
Ajiyeni kayi? Ko kana iko dani da zaka Sanya mun doka kace kuma dole sai na bi?
Kiyi hakuri, ya fada a hankali.

Tayi sokoko ta kasa ci gaba da masifar.
Ya tsareta da ido, Dan Allah kiyi hakuri naji nayi kuskure bazan Kara ba I'm sorry please.
Tayi shiru,
Bana son fadan nan wallahi, bana son kina wannan tada jijiyoyin kina fushi dani bana so ko kadan please kiyi hakuri shikenan ko?.... Ba shikenan ba, sai ka mun alkawarin bazaka Kuma taba ni ba sannan.
Yayi shiruuuu, gaskiya ban yi alkawari ba amma Zan kiyaye.
Ya wuce ko?
Eh, ta fada a hankali.
Mun shirya?
Ta dan harareshi.
Yayi Yar dariya. Mun shirya ko?
Um, ta ce tana murmushi.
Hmmm, Bilkisu kenan kina yarda Kika ga dama.
Karfe nawa Zaki kawon tuwo?
5, ta ce .
Lokacin na gama mutuwa da yunwa ko?
Ba abinci dare zakaci ba?
Waya fada Miki?
Shi zanci a matsayin lunch..... Tuwon???
Yayi Yar dariya yes!
Hmmm,
Zaki kawon irin two din nan?
I'll try. Ta fada a hankali.
Waye Zaki Aiko ko nine Zan turo?
Zan kiraka idan na gama dai.
Ya Mike tashi muje.
Ga book din ta Mika mishi .
Yayi Yar dariya daman ke nake bukata ba Shi ba...... Ta zaro ido what?
Ya Kara yin dariya ya ce Ina nufin ke nake so kizo inyi magana dake ba littafin ne a gaba na ba.
Tace hmmmm.
Suka jera suna tafiya..... Tana tsallaka titi sadeeq ya karaso suka wuce.
Ta zagaya can baya wurin Mai nama ta siyo tsoka Mai kyau ta Shani kilo daya.
Tana shiga ta cire hijab ta Fara hada Miya...( Duk kudi irin nasu Bilkisu baisa anyi sake da koya Mata girki ba ) har catering school tayi ga karance karance da tambaye tambaye saboda girki na daya daga cikin abinda take so a rayuwarta.
Ta shirya miyar kuka Mai Rai da lafiya, naman yayi ruguf a ciki wurin Aisha ta Samo kukar da daudawa saboda bata dasu Kuma Bata Kai ga ta siya ba, anan daman take siye.
Duk wacce taji kamshin sai ta leko. Tana gamawa ta daura tuwon bai wani dauki lokaci ba, karfe daya da kwata ta kullashi a leda, ta janyo sabbin coolers manya cikin kwali Wanda batayi amfani dasu ba daya kawai take amfani da ita karamar tana zuba Miya.
Ta jera tuwon guda Sha biyar aciki.
Ta zuba Miya ga Mai bi Mata duk naman ta kwashe musu kaf! Ta bi da manshanu saboda bata

rabo dashi ita ma'abociyar taliyar hausa ce dahuwar daudawa Tasha manshanu.
Ta kwalala mishi ta rufe.
Ta jera a basket ta Sanya mishi gwangwanin biscuit biyu cikin wadanda ya siya Mata da lemuka kala kala, ta dauki basket din da 200 ta fita.
Napep ta tsaida tare da mishi kwatancen hostel..... Zan kirashi ya fito sai ya karba sunan sa Anwar..... Anwar? Ya zaro ido... Anwar din zai fito ya karba? Ta banka mishi harara ka San sa ne?
Ni kuwa na sanshi an bani abinci na Kai mishi kwanaki nafi awa banga kowa ba na Kira abokin sa da aka bani number sa Koda yaji zancen nawa ya kashe waya bai Kara..... Malam zaka Kai mun sakon Nan ko na nemi wani?
Zan Kai Hajiya Amma idan bai karba ba Ina Zan ganki saboda wadancan kayan har Yanzu suna gidan mu...... Kaga compound gashi can??? Ka ce Bilkisu kake nema ta ajiye mishi basket din ta bashi 200 ta juya kawai.... Ya kalleta a yamutse wahalallu.....
Ta kanga waya a kunne tana Kiran sa..... Barci yakeyi kasa rika Kuma yanajin dadin barcin.
A hankali wakar *Because you love me* ta Fara tashi ta cylindion.
Yayi firgigi saboda Bilkisu kadai keda ring tone din.....
Hello ya fada cikin muryar barci.
Ina hanya Zan kawo maka tuwon na kusa karasowa na sameka bakin gate din ku kada ka barni Ina jira......ta kashe wayar.
Idanun sa suka bude tangaran ya bi fuskar wayar da kallo..... Ya Mike zumbur ya zura jallabiya ya fice da silifas kafarsa.
Dai dai tsayuwar Mai napep din Yana hango napep yanufe ta da sauri Yana lekawa..... Kai ne Anwar?
Sai kawai yayi murmushi watau yarinyar nan dabara tayi mishi don ya fito?
Ya kalleshi eh, tare da Mika hannu ya karbi basket din.
Yasa hannu aljihun jallabiya ya fiddo 500 ya Mika mishi.... Ta biya yallabai.
Yayi Yar dariya to in mayar kenan baxaka Kara ba tunda na fiddo?..... Yayi charaf ya karbe Yana fadin wazai mayar da alheri?.
Na gode yaba napep wuta Shi Kuma ya nufi hostel Yana murmushi.
Ya bishi da kallo Yana jinjina Kai. Yanda suke fama da student wurin neman ragi da amsar chanji amma ga wani na kyautar 500, ita Kuma ta biya 200 zuwa kawai..... Wurin Nan akwai magana ya ce kafin ya chilla keken titi.
Sadeeq nata barci bai motsa ba. Yasa kafa ya Kai mishi harbi.... Tashi Dan ubanka Bilkisu ta Mana girki..... Zumbur ya Mike Yana kallon basket din.... Yayi dariya wallahi tuwon ne ta kawo .

Yunwa sukeji Daman, sadeeq ya Fara kwashe lemukan Yana ajiyewa kasa, sannan ya fiddo coolers din, kamshin manshanu ya buge dakin Anwar ya hadiye wani tsinkakken miyau ya gyara Zama .
Baiwar Allah hada biscuit ta debo da lemuka...... Tana so ta rage su ne sun Mata yasa Anwar ya katse Shi Yana murmushi.
Sun kwashi tuwon sosai musamman Anwar kulli hudu suka Bari.
Amma fa yarinyar ta iya girki in har itace tayi.... Ita tayi nasan bazata ba kowa yamun ba ya janyo waya .

Hello ta fada tana Yar dariya..... Ni Kika mayar gaki nan zuwa ko?
Ta kyalkyace da dariya.... Tuwon nan yayi dadi fa ga Sadeeq nan Yana lasar kwano.... Shi na Bari Yana lashewa karya yakeyi ya fada da karfi.
Ta tuntsure da dariya..... Na gode sai na maido kwanonin Allah ya biya thank you so much Bilkisu Mai gadon zinari...
Ya fada Yana dariya.
Ta ce hmmm.
You and this your hmmm. Bye wanna baf. Ya kashe wayar.
Haka kawai taji ranar ta Mata dadi tana nishadi. Wunin ranar wani nishadi takeji.
Akan hanyarsu ta dawowa daga masallaci isha'i take ba Aisha labarin wayar da sukayi cewar yaci tuwon.
Kamar daga sama suka ga mutane gewaye dasu hada maza..... Gabansu ya Fadi suka tsarata ainun Aisha tayi karfin hali tace lafiya?
Mufeeda suka gani ta fado gabansu tana taunar chingam.
Ta kalli Bilkisu ke karamar Yar iska ce wallahi.... Ni zakiyi ma karuwanci?
Akan Anwar har kisan Kai Ina iyayi na rantse da Allah ta daga hannu zata kwada Mata Mari akayi charaf da hannun aka rike Shi ta baya.... Kowa yabi hannun da kallo zuwa inda aka Kama don suga waye?
Anwar ne yasha boyel fari kansa da hula kube ya murzata irin sa hular kanawa sai kamshi ke tashi, hannunsa dayan rike da basket........✍🏼
*ZAINAB DAHIRU WOWO DUTSINMA*💖

*KAUNAR KI AZIMUN CE Ina yinki over RUKAYYA BAKO DANBATTA* *ZAINAB WOWO NA JIN JINA MIKI ALALH YA SHIRYA ZURI'A AMIN*

A ringa mun uzuri, Ina zuwa aiki, Ina da miji Ina da Yara kafin na Fara rubutun na fada I won't be able to post all the time na Fadi haka saboda Ina da hidindimu.

Alawiyya ciwon ciki🗣🗣🗣🗣🙄🙄
[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
1️⃣8️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

👉🏽💞💕💕 *RUKAYYA BAKO DAN BATTA i love you so much, remember this always*🥰😍😘.

***************
*Federal University dutsinma*

```Ya juya hannun da karfi, wallahi duk ranar da wannan hannun ya yi gigin taba Bilkisu sai na karya shi, nima akanta Zan iya kisa```......... Ya wurgar da hannun. Sannan ya kalli wadanda ke tsaye *What the hell are you doing here?* Ya daka musu tsawa...... Suka Fara darewa, mufeeda ta juya zata tafi ya fizgota..... ``` Bata hakuri```....... Tayi saurin kallon sa, Jin haka yasa kawayenta Suma suka Fara yin baya,
Bakiji abinda na fada ba?
```ki Bata hakuri ko Kuma wallahi....```
Ta fizge hannunta, bazan bayar ba..... Ta wuce da sauri kamar zata tashi sama.....
Aisha ta rike hannun Bilkisu tamau.
Ita kuwa kanta a kasa kawai tayi shiru......
Ya kalli Aisha, me ya hada su ne?
Me kuwa zai hada su inba kaiba??? Ita har Yanzu tana zargin akwai wani abu tsakanin ka da Bilkisu shine fa suka tare mu Yanzu mun dawo sallah..... Mtseww ya doka tsoki.
Ya Mika ma Aisha basket ungo je Mata dashi ciki..... Ta juya kawai zata tafi ya yi saurin fizgota ta fada jikinsa kanta ya daki kirjinshi........ Yaushe Zaki fahimci da gaske bana so ki ringa tafiya idan nazo wurinki ko muna tare?
Ya hakuri sakeni please..... Ya Kara manneta jikinsa..... Aisha jeki tana zuwa.
Ta wuce tana dariya da mamakin wannan rigimammiyar soyayya.
Wai Anwar Kan ka qalau? Na shiga uku ni Bilkisu ka dubi Allah ka sakeni..... Yana rungume da ita ya Fara tafiya a hankali ..... Na shiga uku Anwar..... Ya sunkuyo Yana kokarin hada fuskar sa da tata tayi saurin sunnewa jikinsa tana Kara fadin na shiga uku ni Bilkisu..... Ya manna bayan ta da Bango sannan ya matsa baya kadan ya rabu da jikin ta yasa hannuwa biyu ya tokare bango tare da Dan sunkuyawa fuskar sa daidai tata suna shakar numfashin juna ya kafa Mata idanu.......
Innalillahi Anwar Wai meye haka? Ta fada tana faman yin kasa da Kai.......Haka zamuyi firar tunda ita Kika zaba..... Na zabi meye? Ka gyara Mana dan Allah ka matsa..... Allah ba inda zanje, ba dai taurin Kai gareki ba? Wallahi zanci gaba da binki yanda kike so, ke me yasa baki da tausayi?...... Tausayin me Wai? Ta fada tana kallonsa kamar zatayi kuka.
Gashi yauma saboda mufeeda zaki Kara guduwa kibar ni anan Kuma kin san zuwan naki ne....... Nayi Alkawarin Zan tsaya I'll give you the time you...... Never mind, I'm okay like this.....Anwar am not okay please shift back na tuba kayi hakuri Dan ...... Ke nafiki wuyar lallashi fa ki natsu muyi magana nafi Jin dadin hakan ma..... Tayi kwal kwal, ya kamata..... Na rantse da Allah kina mun kuka Zan mayar dake Nan... Ya nuna kirjin sa.
Ta hadiye kwallan ba shiri , kayi hakuri Anwar bazan Kara ba I promised.
Yayi murmushi naji but next time.
Kina da sauran tuwon nan?
Babu.
Yayi Yar dariya Yana kallon Dan karamin bakin ta da take ta faman turowa.

Duk kin cinye?, Amma fa yayi dadi. Zuwa nayi godiya waccen useless din ta Bata mun plan....
Ba komai nidai jeka sai da safe.
Ya kyalkyace da dariya kina korata ne?.
Ya Mike ya tsaya daidai ta saki wata ajiyar zuciya Mai karfi ya bita da ido Yana murmushi......
Matsoraciya kina motsawa Zan.... Ba inda zanje ta fada tare da makurewa jikin bango.
Kiyi hakuri ya fada a hankali, wallahi Nima fa bana son Ina taba ki Bilkisu ki daina mun gardama kinji?
To, ta fada a kagare.
Sadeeq ma yaji dadin tuwon nan. Ina Kika Sami manshanu?
Ina dashi. Ta fada a hankali. Duk jikinta yayi sanyi....ya Kara tsareta da ido sai ta bashi tausayi.
Bilkisu.....ya kirata a hankali.
Taji wani Yarrrr, tsikar jikinta duk ta tashi, ta kasa amsawa.
Ya Kara cewa Bilkisu......
Na'am ta fada tana murza yatsunta.
Dan Allah kiyi hakuri kinji ko?
Ba komi ta ce a hankali.
Da komai. Gashi naga duk kinyi relax, please I'm sorry.
Ba Kya so Ina taba ki ko?
Ta daga Kai alamar eh, yayi murmushi to duk laifin da nayi Miki idan muna magana ko Ina a wajen don't leave me, kinji ko?
Ta Kara daga Kai .....yayi murmushi Baki magana?
Ta ce hmmm.
Dan Allah ki daina bana so kinji?
To Wai me yasa baka iya kyaleni in tafi?...... Saboda.. sai Kuma yayi shiru Yana murmushi.
Saboda me? Ta tsare shi da ido.
Bazaki gane ba, yace Yana Yar dariya.
Zata Kara magana ya yi saurin cewa na saka Miki turaruka a basket din da na maido Allah yasa kamshin suyi miki.
Biyana kayi kenan?
Ya zaro ido na Isa in biyaki? Allah kadai zai iya biyan ki Bilkisu.
Na zo dasu ne tun daga gida ban dai kawo Miki bane ....... Turaruwanka Zan saka ajikina?
Nope, na Mata ne musamman na siyo Miki.
Hmm, na gode sosai.
Yaushe Zaki Kara mun tuwo?
Sai an kwana biyu kuma .
Gobe me Zaki dafa?
Ina ruwanka, Kai fa abinci ne damuwanka ni kuma ba girki nazo yi ba karatu..... Dariya yakeyi har Yana dukewa...... Wannan tsiwar taki na bir.... Sai yayi saurin canza magana yace tana bani dariya.
Ta ce hmmm, ai gara na fada maka na lura Kai baka san ayi abu Dan marmari ba.
Dan Allah kiyi abinci dani gobe.... Indomie Zan dafa malam..... Zanci indomie din please ki taimaka.
Mtsew taja guntun tsoki.

Amma ki bari Zan Miki waya ten minutes before yanda Ina zuwa kin karasa naci da zafi..... Kaci a Ina? Ka Bari Zan Aiko maka.... Bana cin indomie idan ta shiga wani kwano ba plate ba daga tukunya..... Kiyi hakuri zanzo nan in ci..... Anwar! Ta Kira sunan sa.
Ya kalleta Bilkisu!
Shima ya fadi nata .
Idan na tambayeka zaka bani amsa saboda Allah?
Ya danyi Yar dariya in shaa Allah.
```me yasa yake son takura mun bayan ga wadanda keson attention dinka kaki basu sai ni da ban nema ba?```
Ya fada murmushin fuskar sa ya zuki iska ya hurar..... Saboda kece best friend Dita. I'm More comfortable with you than any other girl in this school.
Tayi shiruuuuu, ya kalleta ko ba wannan amsar kike son ji ba ya karasa maganar Yana dariya. Ta galla mishi harara.
Kin San fa a tarihi abincin ki daya na taba ci duk school din Nan apart from sadeeq da ke Mana girki sometimes da Abdul Mai indomie...
Yanzu kuwa I don't think ko na sadeeq zan Kara ci....... Ta zaro ido sai nawa?
Naki zanci. Gaskiya gara na fada Miki Zaki ringa Mana girki once in a day ko twice idan kina da lokaci...... Amma ka debo dala ba gammo ..... Ya kwashe da dariya.
You are my personal person am sure you'll do it.... Bazan yi ba.
Naji bazakiyi ba shikenan Amma gobe zanci indomie ko?
Eh, amma daga ita karka Kuma cewa don bazaka samu ba....
Yayi murmushi is alright!
Zan koma ciki, na gaji da tsayuwa....... To muje ga bench a can mu zauna akwai sakon da Zan fada Miki...... Tana son mishi gardama tana tsoron ya Kara damkar ta, ta yi Dan jimmm ya tsareta da ido...... Muje ta fada a hankali.
Kaiiii, amma fa kin bani mamaki na ji dadi sosai ko kefa? Ai gardama bata da amfani..... Suna tafiya Yana surutai kamar ta shako wuyansa takeji.
Suna niyyar Zama wayarsa tayi Kara.
Ya dauka hello.....
Ya zauna tare da Mata nuni da hannu alamar ita ta zauna. Ta Dan raba can karshe a dosane. Ina jinka ya fada Kai tsaye.
Ta Dan saci kallon sa sai taga hankalin sa na ga babbar wayar sa Yana latsawa lokacin ne ta lura da iPhone 11x+ yake rikewa ta Dan zaro ido tana satar kallonsa.
Wai ita yau wannan tsadadden yaron ke bi.... Ikon Allah, Ina ma zai *FURTA* Yana sonta? Wallahi zata bashi amsa da gaggawa.... Har Yanzu tana wasi wasi shin da gaske friends din ya tsaya ko kuwa ita ya mayar friends???
Ko in jaraba cewa Ina sonsa?...... Tabb idan Kuma yace baya Sona hakan ya kawo karshen friendship din mu?
Ko Yanzu a tafi a Haka nasan wasu zasuyi ta misunderstanding irin su useless mufeeda.... Ko banza dai a FUDMA nabar record............ Ke kici kanki tubbb ya tofa Mata miyau... Tayi firgigi innalillahi...ta sa hijab tana gogewa... Wannan wane danyen wulakanci ne haka zaka tofan yawu?.... An tofa sai tsareni da ido kina kallo?
Ya harareta..... Bata San lokacin da tayi dariya ba, lallai wanzami baya son jarfa, Kai duk kallon
```

da kakeyi mun nace me?
Eh, aini bana munafurci nake ba ke kuwa sai kin lura bana kallonki sai kina dan sacewa kina.....
Mtseww ta doka tsoki.
Ya kyalkyace da dariya.
Ke bakya gajiya da hijab kamar matar liman?
Kai Kuma baka iya gani ka kyale???
Ya langabar da Kai don Allah gobe kisa gyale ki fito idan na zo cin indomie....... Bani da gyale.
Anan ko?
Abuja kina sa.... Maganar ta makale ta bishi da kallo.
Abuja ma bana sawa ni hijab nake sakawa ko gida..... Dan Allah Bilkisu... Ta kalleshi Kai bana sa gyale fa.
Saboda me?
Saboda Ina kishin mijina!!!
Waye mijinki???
Mai rabo.... Ta fada tare da Dan kallon sa....
Yayi murmushi, lallai ya more ko wanene.
Ta ce hmmmm.
Amma fa mijinki zai Sha rigima.
Ko? Ta ce tana murmushi.
Eh, Mana.
Hmmm.
Kaima matarka zata rigima..... Ni Ina da rigima???
Kwarai kuwa.
Wace iri?
Na ci, magiya, damuwa....Kai komai ma.
Amma Kuma I'm sweet ko?
Ta harareshi a'a chewing gum.... Ya kyalkyace da dariya.....
Tashi muje ki shiga gida idan Kika biye mun zan iya kwana haka dake ban gaji ba..... Tayi zumbur kamar tana jira.
Ya Mata kallon kasa kasa har taji Yar kunya.... Ta Dan juya tana murmushi.
Kin gaji dani already ko?
Um um.
Eh Mana .
Hmmm. Tace.
Zan tura miki assignment din nan ta WhatsApp kinji ko?
Har kayi?
Yayi murmushi kawai.
Har bakin kofa ya raka ta sannan yace okay have a pleasant sleep....
Same. Ta fada tare da shigewa......
Ta biya dakin su Aisha ta dauki key ta wuce.
Kagare take taga turarukan da yace.
Ai kuwa ta gansu don tsadaddu ne designers Kai Anwar babba ne ta fada tana juya daya Wanda yafi daukar hankalinta.

Mashin ya hau bai Kira sadeeq ba.
Kai Yanzu ka gane firar dare ko?
Kai Kuma ka gane sa ido nonsense ya Kai mishi duka.
Allah Anwar Kai munafuki ne....... Ya kyalkyace da dariya Kai Allah ne ya fiddani da wuri ina zuwa na tarar da mufeeda ta janyo gardawa zasu daki Bilkisu..... Ya dauki waya ya Fara nemanta.
Da gaske??? Sadeeq ya fada Yana mamaki.
Wallahi, yarinyar Bata da tarbiyya....kaga Ina Kira taki dauka gobe Zan buge Mata warning na karshe idan Kuma bata ji ba nasa a koreta ko waye ubanta.....
Anwar kabi sannu, fitina kwance take....
Sannan yarinyar nan kada ka takura Mata fa.
Naji. Ya fada Yana kokarin tube Kaya.
Washe gari ta tashi da wani ciwon ciki Mai tsanani ta kasa zuwa class.
Suleiman na ganin an Gama lecture ya kirata saboda yasan ta dawo.... Anwar na bayansa Koda yaga yasa waya a kunne sai ya kura mishi ido yasan tabbas Bilkisu yake nema.
Hello....
Lafiya dai ko? Naji muryar kamar Mai bacci kamar Kuma wacce bata lafiya....
Ciki?, Subhanallahi..... Anwar najin haka yayi zumbur ya mike ya ce zo muje sadeeq... Sauri yakeyi sosai, sadeeq ya fito da gudu, Ina zamu je?
Bilkisu ce Bata lafiya.... Me ya sameta?
Kamar naji Yana ambaton ciki it might be ciwon ciki... Suna zuwa bakin titi yace tare Mai napep ka taho dashi.... Ya tsallaka da sauri.
Allah ya rufa Mata asiri akwai doguwar Riga a jikinta , Aisha na ta faman dama Mata oat ya shigo dakin..... Kanta ba kallabi gashi ya bazo a gadon bayanta ta kifa Kai a filo tana ta murkususu Aisha kuwa daga ita sai shimi.... Ya fado dakin.... Duk suka firgita.
Aisha tayi saurin janyo bargo .
Ko kallonta baiyi ba ya zauna bakin katifar.... Ciwon ciki ke damunki? Ya fada Yana kallon Bilkisu cikin damuwa....
Firgigi ta dago tare da janyo towel dake kusa da filon ta rufe kanta.... Anwar meye haka? Ta fada da kyar .
Ya doka tsoki. Tashi muje hospital.
Ba sai naje ba na Sha magani..... Tashi muje hospital ya fada cikin daga murya..... Ta kalli Aisha ita Daman su kawai take kallo.
Cikin ya Kara katsawa ta runtse ido tare da dukewa.... Ya dagota da karfi ya kalli Aisha Ina hijab dinta?????.... Wayarsa tayi Kara... Ya dauka sadeeq ya?
Kana inane? Gani a bakin gidan ban ganka ba.... Okay Ina zuwa...ya kashe.
Tana son magana amma ta kasa saboda murdawar da cikin keyi ... Ya taimaka ma Aisha suka saka Mata hijab kawai sai ya sungumeta.......
Yi sauri ki fito...ya fada Yana kokarin fita da ita.
Sadeeq ya zaro ido Wai ciki ka shiga???? Seriously tayi penting ne????
Aisha ta fito da gudu rike da kofin oat.
Sadeeq ka same mu Sima hospital ya fada, ya kalli Mai napep muje sima.
Suna Zama ta janye jikinta daga nashi ta dora kanta bisa kafadar Aisha.

Bai bi ta kanta ba yace Aisha meye taci ne?
Bata ci komai ba Daman haka take fama dashi..... Ciwon cikin?
Eh, tana da wani magani da take Sha ne?
Eh, Amma dai baya lafawa da wuri.
Wane irin ciwon ciki ne Haka?
Tayi shiru kawai.
Kinji?
Ta ce hmmm, Daman duk wata sai tayi?
Bai gane ba ya kalleta duk wata Kuma?
Eh.
Mtseww...... Ya kalli Bilkisu kin taba zuwa asibiti an Miki test?
Tayi shiru kawai tana murkususu.
Ya Kara doka tsoki.
Ya dauki waya....hello yah good morning doctor please I have emergency patient are you....
Good. On my way...
Ya ajiye.
Ya kalleta sorry.
Aisha dai tayi zugum.
Bakin gate suka tarar da kijerar daukar marar lafiya.
Aisha ta Fara sumke dariya.
Suna saukowa yace hau Bilkisu...... Tayi karfin halin maka mishi harara sannan ta dafa Aisha suka wuce..... Ya biyota Baki lafiya amma Baki daina gardama ba ko?
Dashi aka shiga wurin doctor.
Ka ce ya fita , ta fada tana kallon doctor din cikin fushi..,.. yadanyi dariya to kaji yallabai an koreka.
Wallahi ba inda zanje ka Mata test kayi scanning..... Ya Fara Mata tambayoyi.
Ta yi shiru.. akayi Justin duniya tayi magana taki.
Dole Anwar ya fita. Yana fita sadeeq na isowa....Aisha na zaune tayi zugummm tana kallon ikon Allah.
Doctor menstrual pain ke damuna Amma bana son ya sani. Ina Shan wannan maganin amma baya mun idan akwai Wanda ya fishi pls help me...... Ya danyi murmushi I expect it.
Ya karbi maganin ta runtse ido tare da dafe cikin lokacin da ya katsa.....
Sorry ya fada tare da mikewa..... Ya dauko wata allura yace Amma fa zata Sanya ki barci sosai, sannan ya rubuta wani magani ya ce gaskiya babu Shi anan sai Kano ko katsina Yana da tsada kwarai.... Ba komai rubuta... Burummm ya banko kofa daidai ya Gama allurar tana murzawa. Ta dalla mishi harara.....
Doctor meye tace Yana damunta?
Yayi dariya it's normal an Mata allura ga magani nan na rubuta Yana da tsada da kudi sosai....... Ya karbe takardar Yana karanta sunan maganin.
Ya fiddo waya..... Hello musbah ga magani Nan Zan turo maka asiyo mun carton dinsa a Aiko Yanzu Yanzu ko ka tado wani ya kawo sannan kace a fada maka maganin menene da Kuma yanda ake shansa.
Kaje wurin nagari pharmacy kace ni na Aiko kaga hamisu a wurin.......

Ya Mika mishi hannu thank you doctor.
Tashi muje.... Idan kin hada Baki da doctor wannan maganin zaisa na San komai.
Idanunta suka Fara nauyi alamar allurar ya Fara aiki.
Allaurar zata sanyata barci sosai fa.....okay.
Ya ce Yana Shirin Kai hannu ya taba ta, ta mike da sauri tare da maka mishi harara...... Yayi dariya Kai yau Ina Shan harara ni Hamza.
Ta fito ya biyota ga oat din ki zauna Kisha Aisha Bata... Ka barshi Zan Sha a daki.. muje please.
Ya kalli Aisha allura akayi Mata Mai Sanya barci shine ke dibarta ga idanunta nan sun Fara canzawa da kunje kada ki yarda ta kwanta bata ci komai ba...... Ko na ajiyeta.... Ya banka mishi wani kallo. Wancen Mai napep din da na tsayar Kuma fa?
Ta kalleshi ka bi sadeeq ku tafi mu sai muje a napep din na gode.
Kamar zaiyi gardama yayi shiru....sai Kuma ya kada Kai okay.
Idan kin tashi barcin ki mun flashing please.
Ta ce toh.
Ya zaro dubu biyu ya Mika ma driver yace mayar dasu inda ka dauko mu.
Ya Dan leka Allah ya bada lafiya Zan kawo Miki maganin kinji ko?
Ta ce toh, tana ta faman lumshe ido..... Jinsa take har cikin ranta. Bata so ya tafi.....ashe shima hakan yakeji.......Sadeeq ya kalleshi abokin Bilkisu..... Ya Kai mishi duka. Shi Kuma ya tuntsure da dariya.....

Ta kalli Aisha kinji yayi waya maganin da aka rubuta a kawo carton dinsa daga Kano.....ta zaro ido carton?
Wallahi....
Bilkisu Anwar ya Fara bani tsoro...Nima Aisha. Anwar Yana bani tsoro. Da na motsa sai yace mun friend.... Ke ya mayar friend wannan abun nasa ya Fara wuce shari'a...Ni saboda ma duk na rikice can daki na bar wayar.
Aisha tayi dariya nima. Wai Kinga yanda ya wani fado kamar an jefo Shi????
Tayi tagumi tawa ta sameni Aisha......
Ta kyalkyace da dariya ai sai ma ya *FURTA* saboda tabbas Anwar gabbb yake da furta Miki Yana sonki alamomi dai sun gama bayyana..... Gabanta ya Fadi ta dafe kirji..... Na shiga uku.....ta galla Mata harara *Baki sonsa?*..........✍🏽 *Zainab wowo*💖

👉🏽💞mowa
👉🏽💕 Unex
👉🏽😡 Alaweez
[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
2⃣0⃣
*Gargadi* Bana son ana rubuta mun komai a page din dana tura. Naga 1⃣9⃣wat t rubuta *Anzo wurin* bana so. Duk wacce ta Kara taba mun page daga ranar *Wallahi wazai furta ya Kare*
Labarin Nan saboda soyayyar makarantar ne nake rubuta tashi na fada don ku nakeyi to a daure a karbi iya abinda aka gani.
Sannan masu cewa na Sanya sunan su a page ku sani cewa wallahi idan dambu yayi yawa bayajin Mai. Duk yanda kuke Sona wallahi nafiku. Akan KU nakan hana kaina abubuwa da

yawa don kada na Bata muku. Dan Allah a bani uzuri. Ina kaunar duk Wanda ke Sona ko wanene wallahi bana Raina masoya.💖💞💕😘😍🥰💗

Tsoron Corona yasa har yau na kasa lekawa RIGASA KADUNA🤪

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

👉🏽💞💕💕 *RUKAYYA BAKO DAN BATTA I love you so much, remember this always*🥰😍😘.

****************

*Federal University dutsinma*

........Ta rude ta kidime Ni kake Kora..... Ya bude mota da karfi ya fita ya zagayo ya bude kofar bayan....get out I said are you dumb?

Kwalla suka zubo Mata sharrrr...... Ta sauko a hankali. Suleiman na gefe yaga ta fito.

Ya koma gefe ya tsaya, tana fita ya maida kofar da karfi gammmm. Ta kalleshi da sauri, ya banka mata harara am I safe now??? Idanun sa sunyi jawur duk sun kawo ruwan masifa.

Ta kawar da Kai ta nufi wurin driver ya finciko ta da karfi kada ki shigar mun mota...... Zan dauki plate ne ta fada kwallah naci gaba da shatatowa.....ya ingijeta ya kwaso plates din watso kasa....ya kalleta Yana zare ido you can go now!!!!!!........ Anwar duk akan Suleiman....... Ya doka tsoki ya juya zai fada mota, wata zuciya ta debeta Bata San lokacin da ta fizgo rigarsa ba ya dawo da karfi...... Kai har ka iya kamun irin wannan wulakancin in kyaleka??........ Ya zaro ido. Suleiman dake kallon su shima fiddo nashi....... Ya daskare ya sankame tare da tsareta da jajayen idanun sa.....Wai me yasa yarinyar nan bata tsoro na.????
......... Kwallah kwance cikin idanun ta, ta turashi da karfi bayanta ya daki murfin mota tayi kansa kamar zata matseshi duk ta fita hayyacinta......... Na rokeka kazo Nan????
Ya yunkura zai dawo ta mayar dashi da karfi wasu zasu wuce suka Dan tsaya kamar zasu fahimci wani Abu, hakan yasa Shi kasa biye Mata kada su Tara jama'a........ Na ce kiranka nayi kazo??????
Matsa Bilkisu in wuce..... Ta galla mishi harara sannan ta juya kadan ta kalli inda ya watsar plates din ta ce ```dauko su day hanmunka``` ...... Ya kalleta da sauri..... Wallahi tallahi ka dauko su ka Miko mun da hannunka ko Kuma nida Kai har abada mun rabu daga Nan...... Gabansa ya Fadi... Ya Kara kallonta.

Ta matsa nesa dashi ta tsaya tare da rungume hannuwa..... Kaka kara Kaka...ya yi shiruuuu..... Ban tilasta maka ba, kana iya shiga mota ka tafi, wacce ka koreni cikinta kana ikirarin *motar ka*........ Ya runtse ido, taci gaba da cewa Amma ka sani na fita motarka salin alin wallahi Alan plates din nan Zan rabu dakai rabuwa ta har abada........ Ya Kara runtse ido tamau.

In ba rainin wayo ba, Kai har yau baka ganin kowa da mutunci kana iya cin mutuncin kowa baka shakkar......kawai taga ya dauko plates din ya Miko mata. Fuskar sa murtuk....... Ta karba ta juya...... Kizo ki dauki maganin...... Bana so *jikan karuna*..... Ka hada da maganin da motar ka cinye nafi karfin dukiyarka da wulakancin ka Anwar...... Ya fizgota da karfi, Ni kike gayawa magana????........ Ta fincike an fada maka ta nuna Shi da yatsa wallahi Ka Kuma taba ni Zan sharara maka Mari....... Ya zaro ido what?????

Ta kalleshi shekeke....kafi karfin hakan ne? To idan kana musu ka jaraba... mtsewww ta buga tsoki ta juya.....ya tari gabanta da sauri....

Wai ke da me kike takama ne? Ya fada da karfi..... Lokacin ne Suleiman ya karaso. ...... Anwar meke faruwa ne......  Ji kakeyi tasssssssss ya ramtse Shi da Mari..... Ya kidime ya gigice..... Bilkisu ta ja baya da sauri tare da daura hannu aka...... Yana dagowa ya daga hannu zai Rama ya Kara wanka mishi biyu double one after another.....sai jini ta hanci......... Bilkisu ta kwada ihu zata ruga ya janyota da karfi ta dawo kanta ya daki kirjinta........ Gashi na taba ki , Kuma na Mari wannan Dan iskan sai ki Rama mishi Kuma ki hukuntani da wani Marin Wanda Kika mun...... Ta zukunna kasa ta fashe da kuka .... Ya kalli Suleiman ko bar nan ko na halaka ka....... Suleiman Dan Allah tafi..... Dan girman Allah Suleiman tafi..... Sai nanatawa takeyi tana kuka, yasa habar rigarsa ya toshe hancin ya wuce kawai Yana huci,...  ya fizgi Wayarta ya Kira Aisha..... Anwar ne fito ina waje......

Cikin hanzari ta fito, ganin Bilkisu duke tana kuka yasa ta rikice wata kila ya Mata halin nasa..

Ya fiddo kwalin maganin ungo kije Mata dashi ciki, ko soke soken wuka mukayi hakan bazai shafi neman lafiyarta ba........ Bana so Ina ruwanka da lafiyata??? Aisha bar mishi tsiyarsa bana so, ta rushe da kuka........ Kin dai ga halin kawarki ko? Kiyi Mata fada........ Haihuwata tayi da zata mun fada?

Wai me ya faru Bilkisu??? Aisha ta bukata cikin damuwa....... Wai daga Suleiman ya kirani a waya fa, Ina abinda ya dameshi da wayata Ashe Yana son yace mun yazo ne ...... Uban me yazo yi?........ Kai me ya kawo ka? Ta daka mishi tsawa..... Ta kalli Aisha Kinga Marin da yayi mishi ya fasa mishi hanci........ Innalillahi yaushe? Aisha ta fada a rude. Yanzu Mana,
Ya buga tsoki, idan Baki ja mishi kunne yayi nesa da ke ba wallahi Zaki janyo mishi nasifa da bala'in....... Kai a wa? Ta Mike tare da rike kugu..... Ya kalli Aisha Kinga irin action dinta da mood ko? To a duk lokacin da wancen Dan iskan..... Ka daina zagin sa wallahi..... na ce mishi Dan iska ko Zaki Rama mishi?........ Don darajar Allah kuyi hakuri......... Bilkisu ta buga tsoki ta juya kawai ya fincikota da karfi........ Ta kuwa Kama hannunsa ta gantsara mishi cizo da karfi.....ya saketa da sauri Yana fadin Kai Kai Kai Kai, ta kwashi kasa ta watsa mishi a jiki sannan ta kwasa da gudu tayi ciki........ Tana shiga daki ta Sanya sakata ta ciki....... Ya biyota a guje, kafin ya karaso ta garkame........Aisha ta rude ta rikice gidan ya harmutse Jin irin hargagin da yakeyi akan ta bude..... Wallahi zan karya kofar nan ki bude kizo ki fada mun dalilin watsan kasa...... Ban budewa.......har daya yayi ma kofar ta fada ciki tayi tsalle ta Haye katifa ganin zata bigeta........ Aisha ta Fara rokonsa yayi hakuri ita Kuma ta makure ta Fara ihu tana kuka........ Ni Zaki watsa ma kasa saboda wancen Dan iskan........ Wallahi ba saboda Shi ba....... Ya

sungumeta a kafada yayo waje Aisha da sauran mutane suka biyo su....... Ya juya duk shegiyar data fito sai na karya ta. Aisha zo muje........ Ko wace tayi dakinta tana surutai......... Kafin kace kwabo magana har kunnen mufeeda.
Ya direta jikin mota ya kalli Aisha tambaye mun ita dalilin watsan kasa.......Dan Allah kayi hakuri Anwar.
Kika kawai Bilkisu keyi......
Ya kalleta ke kina da gadara da taurin Kai ko? Kina tunanin duk wannan abun ba shine Kika janyo wa fitina ba?...... Dan Allah kayi hakuri Anwar. Aisha ta Kara fada.
Aisha na fadawa Yarinyar Nan bana son yaron can me yasa bazata kyaleshi ba?.......Akan wane dalili Zan kyaleshi Kai meye naka aciki da zaka hanani mu'a mala da wani?.....saboda..... Sai Kuma yayi shiru.
Saboda me?
To baka Isa ba, Yanzu na Fara kula Suleiman...... Kinji ko Aysha? Kinji abinda take fada ko?
Dan Allah kayi hakuri Anwar zata daina kulashi........ Yaudarar ka zatayi, ba Wanda ya Isa ya rabani da Suleiman Kuma ka sani daga yau bani bakai, bana son abotar kaje ka nemi wata idan na Kara ganin ka anan ko kamun waya Kai ko tunani na kayi a zuciya ban yafe.......... Ya buge Mata Baki.
Ke kin Isa ki yanka mun doka?
Ta rike bakin tare da runtse ido...... Ya kalli Aisha kina Jin halin kawarki ko? Duk garin nan akwai yarinyar dake mun haka?
Ta girgiza Kai da sauri Babu kayi hakuri.....
Idan kin lura ta na nemana da rigima sosai......
Kayi zuciya ka kyaleni daga yau a fita harkar Bilkisu..... It's alright take care, Kawai ya fada mota yaja ya tafi .... Gabanta yayi mummunan faduwa, ta yi shiruuuuu kafin Ta figi hannun Aisha zo muje.
Suna zuwa daki ta fada katifa ta saki kuka.... Ai kinyi kuskure me yasa zakiyi mishi irin wannan wulakancin Bilkisu...... Ta dago fuska jage jage da hawaye.... Aisha na rasa gane inda Anwar ya dosa, masifar nan tashi ta isheni gara ya kyaleni na huta.... Wallahi bazaki huta ba. Ta Kara kallon ta da sauri, yes bazaki taba hutawa ba saboda kina matukar kaunarsa.... Bilkisu nasanki nasan wacece ke, gwargwado nasan waye Anwar shima wallahi tallahi matukar baku fito Kun fadawa junanku surrin da ke zukatanku ba tabbas zaku kashe kanku a banza...... Ni na taba ganin jarababbiyar soyayya irin taku?
Ko wane idan kishin Dan uwansa ya motsa sai ya Kare kansa?...... Ta kife Kai a filo ...ta Kara sakin kuka a hankali.......
Idan kin gama ki tashi kiyi parking, ga maganin nan na dauki kwaki goma .... Ta fice jikinta duk ya mutu tana mamakin irin wannan soyayya wacce ko a littafi Bata taba karanta irin ta ba.
Gaban sadeeq ya Fadi....... Anwar lafiya na ganka a firgice haka ko jikin....... Tashi ka shirya mu tafi Kano.
What?
Ya mishi wani kallo gaban Sadeeq ya Fadi ya tsorata Anwar lafiya?
Zaka je ko na tafi?
Ya kamo Shi ......ya fizge sadeeq Dan Allah ka kyaleni *I hate this world*........ Ya ci gaba da harhada Kaya...... Dole sadeeq ya Mike shima ya Fara hada jaka..... Amma wallahi bazaka tuka

mu cikin wannan mood din ba ... Bai rufe Baki ba ya wurga mishi keys din a kirji ya figi jakar sa yayi waje..... sadeeq ya bishi da gudu tare da rufe dakin....Sha biyu da Rabi na dare suka bar dutsinma yana kwance a sit ya Dora kafa daya a dash board ya kwantar da sit yayi filo da hannayen sa idanun sa rufe..... Kadan kadan sadeeq na lura dashi sai faman tsoki yakeyi.

Batayi tunanin abin zai dameta ba sai da ta koma gida, kwana daya , biyu...sati. Anwar bai nemeta ba.

Suleiman kuwa yayi Kiran duniya ta kasa dauka kamar tana son Jin haushin sa ganin shine jigon wannan fitina.

Gaba daya gidan an ga canjinta, bata walwala, kullum tana daki kwance.

Ranar da tayi sati biyu da dawowa mommy ta sameta daki, ta zauna bakin gado, Bilkisu mi ke damunki? Na lura tunda Kika dawo Baki da walwala, meke damunki? Saboda har dadyn ki ya Kai ga yin magana...... Ko maganin da Kika ce Anwar ya siya Miki ne kike ganin yayi yawa?....sai kawai taga kwallah na zubo Mata.... Hankalin momy ya tashi ko dai daukar magana Yar tata taje......subhanallah. tayi saurin kawar da tunanin. Ta janyota fada mun menene? Ta goge hawayen mommy bana Jin dadin abinda Anwar keyi mun...... Ta Bata labarin duk abinda ya faru..... Sai kawai taga mommy na dariya.

To Bilkisu Anwar ai kishi ne ke damunsa tunda baya son ki kula Suleiman din sai ki kyaleshi.... Ina wayar ki?

Ta Mika Mata kawai..... A'a Anwar din Zaki Kira kice yayi hakuri tunda ke kin damu bai Kira ba..... Tabbb wallahi bazan kirashi ba mommy..... To ya Zama dole ki fitar dashi a Ranki domin Shi da alama ya manta da ke kamar yanda Kika mishi gargadi...... Kirjinta ya buga da karfi kwallah suka Kara cika idonta ...mommy ta mike wannan shine sai ki zabi daya cikin biyu, Amma bazan dauki wannan dararewar ba da kikeyi cikin gidan Nan... Tana Gama fada ta fice tare da Jan kofa gammmm.

Tayi zugummm, dabara ta fado Mata kawai Bari ta Kira Sadeeq......

Anwar kuwa yafi Bilkisu shiga tashin hankali, ya koma kurman karfi da yaji, hankalin Hajiya yayi mummunan tashi tana zargin ASIRI ne ke son kamashi.

Ita kadai ke shiga dakin sa sai kuwa sadeeq, kullum sai ta lallasheshi yake cin abinci....

Abun har ya Fara affecting kasuwar sa, kowa shakkar kiransa yakeyi a waya saboda masifa da bala'i.

Tana zaune ta tsareshi ya shanye tea  din ta Sha mur alamar ba wasa kamar kullum, ya Sha mur, ya tsuke fuska rabonsa da dariya tun ranar da ya rabu da Bilkisu Yana cusa kwai a Baki jinsa yakeyi kamar madaci.

....... Sadeeq ne ya turo kofa Assalamu alaikum.

Hajiya yau kina ciki?

Eh sadeeq maraba, Wa'alaikumus Salam.

Kamar zatayi kuka ta kalli sadeeq na rasa ainahin meke damun Anwar, shin ko ta sanar dakai ......ya wurga mishi harara Yana horonsa da ido kamar kullum akan kada yace wani Abu...... Hajiya ina ga malaria ce, kin San fa dutsinma akwai sauro sosai Daman ya Saba duk hutu sai ya kwanta ..... Ba irin wannan kwanciyar ba. Yaro ya takure ya makure sammm Anwar ko murmushi ya daina yi...... Zai dawo normal hajia aci gaba da addu'a.

Ta Mike , kaima ai bakin ku daya, ko ma menene bazan yarda da wasa da abinci ba... Ta fita.

Ya kalleshi ...ya kamata ko don tsohuwar nan ka daina wannan abun, nasan wallahi duk wannan damuwar Bilkisu ce... Ta kirani dazun ta fada mun duk abinda ya faru hada kukanta, ta ce wallahi Babu abinda ke tsakanin ta da Suleiman, Anwar hakuri akeyi..... Please sadeeq ka kyaleni..... Bazan kyaleka ba tunda kaima baka kyale kanka ba .

Ta ce na baka hakuri....bazanyi ba tace na Kyaleta hakurin me zata bani?..... Har wannan maganar ta fada mun ta ce kuskure ne bacin Rai yasa ta Fadi hakan..... Karya takeyi. Tana son bani haushi ne don na Mari Suleiman...... Wannan zafin kishin naka bazai taba sany.... Kishin ubanwa zanyi? Ya Mike ....ya kamoshi da karfi ya mayar.... Dan Allah kayi hakuri Anwar tunda wallahi Koda mukayi ways kuka takeyi..... Kaine zata Kira taba hakuri ba ni ba? Tunda Kaine tayi wa laifi ko?

Ikon Allah.... Tana tsoron kada ku Kara wani fadan ko kaki dauka ....... Ni zaka zo ka tsara sadeeq???

Tsari??? Wallahi da gaske nake ita ce ta kirani....ya fiddo waya aljihu...duba ka gani ni na Kira ko ita? Minti nawa ka gani?

Sai kawai yayi murmushi ko kadan bai San yayi ba.....ya zaro ido are you smiling?????

Ya Kai mishi duka ya goce..... Munafuki ni na dade da sanin wannan cutar taka Bilkisu ce.... Dan Allah fada mun tayi maganar cikin damuwa?

Wallahi kuka takeyi lokacin da muna maganar alamar abun ya dameta...... Mtseww ita ce ke Sanya mu damuwa ai..... Iye? Sadeeq ya fada , ya banka mishi harara Yanzu dai kirata kace ta kirani da kanta ta bani hakuri..... Message ya shiga wayar Anwar din karammm..... Ya dauko da sauri jin alamar shigowar message din ta ne,

```I'm sorry very sorry please and I don't mean to hurt you```..... Sai kawai ya washe fuska.... Sadeeq Bilkisu ce....

Dan Allah Kira mun ita.... Suna Kira wayar a kashe. Abu kamar wasa kusan kwana uku duk lokacin da aka Kira a kashe..... Shi kansa ya nema Amma bai Samu ba.... Hajiya dai taga Anwar lokaci guda an warware har Yana fita tawon *Bike* da suke zuwa da marece Shi da yaran governor.

Ta warware amma duk ta Dan rame kadan..... Kullum tunanin Anwar.

Ta kasa bude wayar ta saboda tana Jin kunyar idan ya Kira me zata fada mishi bayan ita ce ta bayar da hakuri?

Ta Kama lahadi suna gida duka har daddy, tana sanye da Riga da skirt na atamfa super Holland Mai flower yellow dinkin ya bi jikinta, dogon hannu ne na *net* yellow duk atamfar yayyabe flowers din suke da stones masu sheki kamar diamond.

Kanta ba kallabi ta maida gashinta baya ta kulle jelar kwance bisa bayanta..... Motsin get suka jiyo. Daddy ya Mike da sauri ya daga labule....jibga jibgan motoci ne bakake suke shigowa.... Ya ce innalillahi.. waye zai bamu surprise visit Haka?.. aka Fara fitowa yaga securities ko wane da abin magana a kunnensa ya saki labule da sauri, ya kallesu inajin foreign affairs minister ne ..... Yayi ciki da sauri..

Suka tashi duk suka fada daki. Bilkisu ma ta shige nata.

Ya fito Yana gyara hula, falon kamshi kawai ke tashi na freshner ta ko Ina .... Ga A.C ta gauraye ko'ina.... Ring bell ya Fara kadawa a hankali... Da daddy da kansa ya bude..... Ya bude ido sosai cike da mamaki compound din gidan makil da securities suna tsaye ya Sha fararr gizna dinkin falmara ce yasha aiki kansa cikin kube murjin kanawa...... *Waye in ba Anwar
```

ba*....... Anwar??? Daddy ya fada ....sukayi saurin zubewa shida Sadeeq daddy Barka da yammaci...... Ku tashi .... ku tashi.... Ya kamo Anwar.... Ya riko hannun sa suka shigo ya kwadawa mommy Kira ta fito da sauri.... Tayi turus ganin Anwar tare da washe Baki *Anwar a gidan mu*?

Sai sumke Kai yakeyi.... Daddy ya zauna suka gaisa sosai ya kasa hada ido dashi sai sadeeq ne ke faman amsawa .

Tuni mommy tayi ciki tasa Rahina Mai aiki ta fara kawo musu abin Sha....

Daddy ya Mike ya haye sama.

Mommy ta shigo suka Kara gaisawa ta koma ciki.... ya kalli sadeeq Dan ubanka ka tamabaya kace Ina Bilkisu?????...... Ya zaro ido ya Kai mishi duka......

Tana kwance ta kunna t.v din ta tana kallon wani Korea series *Innocent man*

Mommy ta shigo, ke kullum idan anyi Baki sai ance kizo ki gaishesu??? Tayi zumbur Ina da niyya mommy ayi hakuri..... Ta galla Mata harara.... Tabbas kowa yasan surprise visit ya Bata don me zata fada Mata.... Gara ta fita idanunta su gane Mata.

Ta dauki dan mitsilin gyale ta Yana a fuska bai ko rufe rufe rabin gashinta dake kwance a baya ba..... Ta raba momyn ta wuce ..

Assalamu alai........ Ya dago da sauri sukayi tozali.... Sai kawai ta dafe kirji tayi baya da sauri kamar wacce taji tsoro , mommy na tsaye bakin kofar dakinta Bata fita ba.... Ta ruga ta makalkaleta..... Mommy da gaske Anwar ne?.........✍🏼

*Zainab wowo*💖

[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐

1️⃣9️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

👉🏽💞💕💕 *RUKAYYA DAN BATTA I love you so much, remember this always*🥰😍😘.

***************

*Federal University dutsinma*

........ Bani da wani feelings akan Anwar he always telling me we are just friends....just friends, so Ina tunanin all this is because he likes me as that shine kawai....... Kada ki yaudari zuciyar ki wallahi....... Kada ki rantse Anwar bashi da alkibla.

Idan Yana Sona let him say it idan Kuma bai *FURTA* ba I cannot waste my time and wait for unknown..... Anwar din ne unknown...yes to me he is.

Abinda na tabbatar wa kaina shine ko naji Ina sonsa bazan taba yarda ya gane ba bare har nace Zan fada mishi..nooo! Bana iya hakan.
Dai dai sunzo kofar gida, suka sauka Aisha ta biyota da sauri ganin ta yi saurin shigewa....... Amma saboda Allah bakya jin kin Fara son sa?
Tayi murmushi.
Um?
Aisha forget about this.... Dan Allah ki amsa ni. Ko kadan bakya jin kina sonsa?...
So!, So!.... Ta maimaita.
Suka bude daki ta fada bisa katifa..... To Wai ya zanji idan na Fara sonsa?
Yawan tunanin sa, son ganinsa ko Jin muryar sa, komeye zai yi zakiga baya Baki haushi.... Koda kin fusata zakiji azuciya Baki Jin haushinsa, kishin sa...... Tayi Yar dariya.... Please Aisha fita Kija mun daki barcin nan ya dameni.
Anya Bilkisu????
Anya meye?
To nidai Kisha oat din kada ki haddasa mun fitina anjima don Anwar sai ke wallahi.... Abeg go.!! Zan fita but please Kisha.... Zan Sha Yanzu.
..........ya dafa kafadar sadeeq, kaji menstrual pain ke damun Bilkisu.... Ka dubi girman Allah kada ka nuna Mata kasan haka zaka Bata kunya Anwar.
Ya tuntsure da dariya, to me yasa Bata boyewa Dr ba sai .....
Sai ubanwa? Shi ba Dr bane? Idan bata fada mishi rashin lafiyar ta ba zai San wane magani zai bata ne?.... Ikon Allah, sadeeq akan Bilkisu wata Rana kilan ka dakan ko?
Tabbas, saboda ka takura Mata da yawa fa...... Meye abin takura anan.
Na dai fada ma, wallahi kada ka nuna kasan me ke damunta zata ji babu dadi... Kai nafi so ta Saba da Hali na tun Yanz.... Maganar ta makale da alama yayi *Subul da baka*.
Hahahahahahahaha, finally..... Ya galla mishi harara finally what?
Nothing forget...ya fada Yana dariya.
*Sixtus* ya shigo kunji anyi closing school till further notice?????
Sadeeq ya kalleshi saboda me?
Corona virus...... Anwar yace hazbunallah are you serious?
Of course. Ya fada.
Anwar yayi saurin daukar waya ya Kira academic secretary.... Ya tabbatar mishi....
Ya kalleshi sadeeq is true.
Ya zaro ido Nawaoooo..... ya zanyi da yarinyar nan sadeeq??
Kamar ya?
Sai yayi shiru..... Ya kura mishi ido huh?
Mtsew ya buga tsoki ya fita waje.... Ya bishi da ido Yana murmushi, saboda ya gano inda zancen sa ya dosa.
Abinda ya tayar mishi da hankali ganin student nata parking ana buga ma wadanda Basu dawo ba akan su yi zamansu.....
Ya Kira number Bilkisu gashi tana ringing Amma Bata dauka ba, saboda barci ta sanyata silent mode da alama ta sami yin barci.
Aisha ta Kyaleta har kusan karfe shidda ta wuni zungur tana barci... Ko da ta tashi wata azababbiyar yunwa ce ta tashe ta, ga mamakin ta taga Yar cooler kusa da katifar, tana budawa

taga kuskus da miyar Dankalin turawa, tayi murmushi Allah sarki Aisha.
Sai da taci nayi nat! Sannan ta shiga wanka ..... Tana cikin saka riga Aisha ta shigo, kin tashi?
Ta fada tana murmushi, ta mayar mata da murmushin ta nuna Mata cooler da Baki tace Kinga alama can..... Sai duk sukayi dariya.
Yunwa ta tasheni, wallahi kin taimaka..... Ai kin shaa barci, Ni kuwa nasan haka na farka naga 23 missed calls..... Tabbb.
Kin kirasu ko?
Mommy kadai na Kira sauran sa nemeni idan ya damesuuu......wayar ta Fara kugi duk suka kalli juna.
Ta nufi wayar, ta Dan kalli Aisha *Anwar* ne.... Tayi Yar dariya Ina zuwa , ta juya tabar dakin....
Assalamu alaikum,
Kin tashi kenann....
Amsa sallama wajibi ne malam..... Wa'alaiki assalam. Sai me Kuma? Tayi Yar dariya, Ina wuni?
Ya kike ya jiki?
Alhamdulillah.
Cikin ya daina ciwo ko kina ji har Yanzu?
Bana ji da sauki sosai.
Zan kawo Miki maganin anjima kinji ko?
Ka bada akawo mun Mana ..... Saboda bakya son ganina?
Ba haka bane.
Haka ne Mana . Ba maganin kadai Zan kawo ba ai Ina son duba jikin ki ne...
Shikenan sai kazo.
Zaki iya dafan indomie din????
Innalillahi kaii Anwar fitina ne wallahi.... Nine fitina Bilkisu.????
Ta zaro ido kayi hakuri  wallahi maganar zuci ce ta fito....... Da kyau Ashe a fili kike nunan ba wani abu kina can kina zagina cikin Rai ko?
A'a wallahi....eh Mana. Gashi kin kirani da fitina....Dan Allah kayi hakuri.
Bazanyi ba.... Ya Fara fada kamar da gaske Yana son yaga how much she care about him ...
Kina da fuska biyu kenan Bilkisu? Watau a fuska kike nuna mun .....Anwar kayi hakuri....
Bazanyi ba nace.
Ba zakayi hakurin ba?
Gabansa ya Fadi ya tuna fadan su na baya..... Yayi saurin cewa zanyi amma ba Yanzu ba .
Sai yaushe?
Sai nazo anjima kin kalleni kin bani hakurin da gaske..... Tayi Yar dariya wannan na karya ne?
Da alama. Ya fada.
Shikenan sai kazo. Ya kake son indomie din?
Ki barshi kawai bana ci.
Dan Allah kayi hakuri..... Na ce ban hakura ba?
To ka fada mun yanda kake son indomie din kasan kowa da yanda yake son dahuwar indomie.....kiyi mun yarda ki ke dafawa idan zakici... Karfe nawa zaka zo?
Eight, ya fada Yana Yar dariya ko nayi latti?
Ta Dan harari wayar kamar Yana kallonta kawai tayi shiru..
Kinyi shiru kina ta Duran zagi a zuciya ko?..... Kaiii Anwar.

Eh Mana.
A'a wallahi.
To fadan da kikayi shiru me zuciyarki ta saka Miki?
Ta kyalkyace da dariya kaiii nikam na bani ..... Yayi murmushi.
Ke Kam kin bani zuciyar ta saka Miki?
Ta zaro ido... A'a.
To fadan me ta ayyano Miki.?
Cewa tayi eight din is okay..... Yayi Yar dariya are you sure???
Yes. Ta fada tana ci gaba da murmushi.
Shikenan sai nazo. Kin hada kayanki ko?
Sai anjima.
Ya zaro ido kinji labarin Coronan ne?
Eh, mommy ta fada mun da mukayi waya.
Yaushe Zaki tafi?
To gani dai.... Ban gane gaki dai ba.
Ka bari idan kazo anjima zamuyi magana.... Shikenan sai nazo.
Ashe yayi waya yace a kawo mishi mota da maganin. Ko da aka kawo sai driver ya juya gata haya yabar musu motar.
Katuwar mota kirar Jeep Amma Honda baka, Kai da kaga motar kasan lallai Mai ita *Don* ne.
Ta Sami Aisha daki, sai na jiki shiru.
Eh, wallahi Ina parking ne.
To Wai strike din ne ko Corona?
Duka fa, Anwar ya fada Miki?
Mommy, Ina tashi naga ta kira nabi Kiran,shine take fada mun, kema gobe Zaki wuce?
In shaa Allah, sai gida....Kare yasha taba. Duk suka bushe da dariya.
Ke sai jibi ko goben zaku wuce?...... Har na ma driver waya gobe in shaa Allah na fada mishi ana gama sallar asubah zamu bar garin nan six da izinin Allah..... Anwar din fa, ba dashi zaku tafi this Time ba????
Noooo, bama zai sani ba..... Gaskiya bazai ji dadi ba....kada Allah yasa yaji so what?
Ta kura Mata ido, wannan Jan ajin naki fa ya Fara yawa ki zauna idan zaren ya tsinke zakiyi wa kanki.
Tayi murmushi, sai dai ya tsinke Amma ko Zan rasa Anwar bazan taba binsa kamar rakumi da akala...... Yanzu me Zaki fada mishi? Ko kunyi maganar?
Bamuyi ba, sai anjima ya ce zaizo kawai Zan nuna mishi banyi deciding ba.... Bilkisu....
Aisha please mubar maganar Nan.
Dan Allah idan ya kawo Miki maganin ki dibar mun saboda Hafsa ( kanwarta ) ita ma the same problem with you.
In shaa Allah.....ohhh Wai carton, komai Shi sai yayi hauka..... Ba hauka bane kulawa ce.
Gasu mufeeda can time dinsa kawai suke so Amma sun kasa samu..... Haka ne .
Ai shu'umi ne wallahi. Nake ga kamar duk abun Nan Yana Axergurating ne don ya Sami sauki Yan mata.... Yanayi bil hakki da gaskiya.
Ko?
Allah kuwa.

Ta ce hmmm. Kawai.
Suleiman ya kirata, da sauri ta daga hello, Suleiman Ina wuni.
Bilkisu ya karfin jiki?
Na zo dazun har Kun fita da Anwar halan asibiti kuka je.
Eh wallahi. Jikin ma Alhamdulillah.
Mashaa Allah, sai Kika ji Kuma hutu ko?
Bari Kai dai.
Wallahi naji haushi da na Kara jinkirtawa Kinga da ban wahala a banza ba.
Ai kuwa. Ta fada.
Shikenan Allah ya say ya zamo alkhairi garemu duka ya kawo Mana karshen wannan fitina.
Amin ya Allah.
Sai nazo Allah ya Kara lafuya.....ta ce Ai.... Amma tuni ya latse Kiran Sam bai ji cewar zatayi wata magana ba.
Ta kalli Aisha naji Yana sai yazo kada yazo gobe na tafi ko in Kuma kiransa Kinga babu dadi. Kyaleshi goben sai ki Kira. Yanzu kada ya zargi wani abu kin San maza..... Eh Kuma fa. Ta fada.
Ta dafa mishi indomie da kifin gwangwani, ta Sanya tarugu da albasa Mai lawashi sai kuwa spices dinta.
Tayi masifar dadi sai kamshi ke tashi..... Kafin ta sauke ya kirata.
Ta dauka hello...
Ina waje. Yana fadin haka ya kashe.
Gabanta ya Fadi,jikinta ya Dan dauki rawa, ( Wai me yasa Yanzu ko waya sukeyi takejin wannan yanayin? ).
Doguwar Riga ce jikinta blue, tana da duwatsu yayyabe jikinta.
Ta dauko hijab maroon har kasa ta saka, ko kwalliya batayi ba turaren da ya siyo Mata ne ta fesa kawai ta juye indomie a plate ta rufe ta dauki robar ruwa da maltina ta fita.
Yana hangota da Kaya ya fito daga motar..... Gabanta ya Fadi. Anwar a irin motar uncle? ( Wani kanin mommy ne Mai masifar kudi ) wurin Shi suka Fara ganin motar Shi bama Nigeria yake zaune ba Soja ne a America.
....... Ya karbi plate din Yana Yar dariya, kawo na taimaka Miki.
Ya shiga motar ya zauna wurin Mai tuki ita Kuma tana tsaye ta rike murfin kofar tana son ya karbi ruwan da maltina.
Ya Dan kalleta zagayo Mana ki zauna....um um Nan ma ya Isa.
Ya Kara kafa Mata ido , sai Kuma yaki cewa komai ya Mika hannu ya karbi ruwan.
Zaman kujera yayi ya sako kafafunsa waje duka biyun Yan facing dinta. Ta Dan ja baya ,yayi kamar bai lura ba .
Riga round neck navy blue ya saka da jeans dark blue. Kansa yau ba hula, ya kwantar da gashin sa inda ya bada kusurwa kusurwa ( waves ).
Yayi kyau matuka.
Ya bude plate din sama, kamshi ya daki hancin sa ya Dan lumshe ido waww.... Daga ji zatayi dadi fa.
Tayi murmushi kawai.
Ina folk din ko hannu Zan saka????

Ta Dan bude idanu innalillahi...Bari na dauko na manta..... Ta juya da sauri.
Kinga dawo ga wani Nan ...
Ya fada .
Ta dawo ya gyara fuska alamar seriousness yace duba aljihun kujera a baya akwai spoons dauko mun ciki.
Ba gardama ta ce toh.... Ta bude ta shiga lalube takeyi sosai tun kafar ta na waje har ta shiga motar ciki tana tura hannu kawai taji kofa ta rufe wani Abu yayi Kara Nan da Nan ta gane locking yayi.
Ta dago Kai da sauri sai taga Yana ta cin indomie din a hankali..... Au dama da spoon dinka a aljihu kana son na shigo motar ne...... Kina baya Ina gaba hakan ai ba matsala bane unless Zaki takura na dawo bayan..... Karka dawo ta fada da sauri.
Motar ta dau sanyi da wani da dadden kamshi..... Kamshin ya Mata dadi Amma hankalin ta duk ba a kwance yake ba.
........ Amma indomie din nan tamun dadi kin ci?
Eh, ta fada da sauri.
Kice wallahi na ci.... Ba sai na rantse ba.
To idan ma bakici ba nidai na cinye tas!
Ta ce hmm.
Ya bude maltinar ya kafa Kai.... Yana shanyewa ya kalleta kina da fridge ne?
A'a.
Yanaji da sanyi ko siyo mun kikayi?
Ina ruwanka Kai dai kasha maltina.
Ya kyalkyace da dariya. Wallahi ke Bilkisun nan kin iya gwasale mutum..... Ta harareshi kawai.
Ya dafa kujerar say ta baya ya juyo sosai Yana kallonta..... Dan Allah in dawo Nan....a'a wallahi ta fada da sauri. Yayi murmushi shikenan.
Yanzu yaushe Zamu tafi gida?
Kai da wa?
Da ke!
Tayi murmushi, tare muka zo?
A'a Amma tare zamu koma.
Shikenan mu jira gobe muga abinda Hali ya bada ko?
Ya rungumi kujera okay as you wish...
Ya Miko Mata ballin magani ungo Kisha ga ragowar can a boot ance kullum daya zakisha har kwana hudu.
Sannan every month da kin Fara expecting Zaki Sha sau biyu a Rana safe da yamma har ki ganshi ...... Ta mishi banza.
Kin fahimta. Eh. Ta ce a kagare.
Ya sumke dariya ganin tana ta faman kasa da Kai.
.....Wayarta tayi Kara, Suleiman ne. Ta Dan zaro ido a hankali ta daga tare da kangawa a kunne yayi fit! Ya fizge. *Suleiman eco* yaga an Sanya.
Nan da Nan annurin fuskarsa ya bace ya sa handsfree hello kana magana da Anwar..... Kawai sai Suleiman din ya latse wayar...... Ya kalleta kutumar uba ni zaima hanging phone???
Ta mishi banza.

Ya daka Mata tsawa meke tsakanin ki da Dan iskan yaron nan?
Akan me zaka Kira Shi Dan iska???
Ya zaro ido.
What?
Ai kaji abinda nace. Kai ya Kira? Akan meye zaka dauki wayar da ba taka...... Ya wurga Mata wayar ta daki kirjin ta yace get out of my car.....
Ta dago da sauri ta kalleshi ... Ke kurma ce? I said get out ya Kara daka Mata tsawa......✍🏼✍🏼✍🏼✍🏼

Ayi hakuri da kadan yau ban zauna ba wlh
*Zainab wowo ce*💖

*ALAWIYYA NASIR MY FAVORITE THANK YOU SO MUCH TAWAJENA*🥰
[3/23, 8:00 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
2️⃣1️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

👉🏼💞💕💕 *RUKAYYA BAKO DAN BATTA I love you so much, remember this always*🥰😍😘.

**************
*ABUJA NIGERIA*

Ya kyalkyace da dariya, ya kalli sadeeq she was shocked..... Ai dole ta razana wannan babban surprise ne. Ya Kara dariya.
Yeah I like surprise

...... Da gaske Anwar ne mommy????
Tayi Yar dariya shina halan bai hwada Miki zai zo ba?
Bai hwada min ba mommy muje ki raka Ni..... Walla Baki da hankali ni Zan kaiki inda Anwar?
Ta Fara dire diren shagwaba.
Walla bani rakaki keji min ja'ira..... Ki kaisu can Fallon daddyn ki na baki zasu fi sakewa naga Anwar duk ya takura.... Mommy Dan Allah muje ki raka Ni.....
Ta kyalkyace da dariya yau naga ikon Allah....

To Wai ya ankayi yasan gidan mu?
Idan kinje Kya tambayeshi.
Ta tura ta waje daya ta fito da sauri..... Ta biyota da gudu mommy jirani....
Ta boye bayan ta, Koda yaga mommy ce ta fito yayi saurin yin kasa da Kai.... ta wuce abinta tana dariya.
Tayi tsaye tana Yar kyarma tana murmushi kanta kasa.
Sadeeq ya tsura Mata ido kinyi tsaye ki karaso Mana Bilkisu.
Tayi Yar dariya sannun ku da zuwa ya hanya.....
Sadeeq ya ce qalau.
Ta bi bayan kujeru kuzo muje tayi gaba kadan duk suka Mike..... Tana zuwa saitin kujerar sa ya yi charaf da hannun ta ya kalli sadeeq Dan ubanka shiga gaba.... Ya tuntsure da dariya, idan na shiga gaba in kaimu Ina?
Kwatanta mishi Bilkisu...... ta fizge hannun ta lokacin ne ta Sami damar kallonsa don ta bashi harara.....kyaleshi sadeeq muje..... Ya dawo da ita da sauri jeki sanyo hijab...... Ta kalleshi zaka Fara ko? Gidan namu ban tsira ba? Yasha mur jeki sanyo hijab wallahi kada mu sayar da Hali anan...... Dole ta juya tayi daki ya bita da kallo har ta shige ya hadiye wani tsinkakken miyau ya dawo Kan sadeeq ya Kai mishi uban duka Allah ya Isa Dan ubanka ka ga harammmm.....
Wata muguwar dariya sadeeq din ya saki .... Kayi a hankali fa...
Ashe duk dramar nan mommy na kitchen na hangen su..... Ta Kama dariya ita kadai....lallai Bilkisu tana da aiki.
Ta fito da doguwar hijab har kasa ta banka mishi harara muje..... Suka bi bayanta..
Ba sadeeq ba, Anwar kansa falon ya tafi da imanin sa, ya zauna bisa two sitter sadeeq Kuma ya zauna kujerar dake can karshe Shi kadai ya ma t.v kuriiiii ganin ana best film dinsa *mortal combat*
Ta zauna bisa three sitter tana facing sadeeq ta Kara gaishesu
Sadeeq ya kalleta Yana dariya sai Kika ganmu ko?
Tayi murmushi hmm,
Hakuri muka zo badawa..... Ke ki dawo Nan kin mun nisa... Ya fada Yana kallonta.
Tayi kamar Bata ji ba, sai kawai taga ya Mike tayi saurin kallonsa... Yana tasowa ya figo hannun ta Yana fadin ke wallahi wata bagidajiya kike wancen Dan iskan ba dashi zakiyi fira ba ni ne bakon...... Ta fizge hannunta... Akwai CCTV ta nuna mishi da hannu.... And then?
Ta zaro ido.... Kai Wai baka da tsoro?
Mtsew yaja guntun tsoki tare da figarta da karfi ya zaunar da ita kusa dashi, just sit down here.
Kaii Allah ya raba ka da rigima..... Allah ya rabaki da gardama kema.
Rahina ta shigo da tray cike da kayan marmari da lemuka masu sanyi ta Fara jerawa a dining table sannan ta fita tana kawo kuloli kala kala.....
Baza mu ci abinci ba fa saboda bamu sanar ba kada a takura ayi Mana.
Har an gama ai, idan baku ci ba mommy zataji babu dadi?
Me yasa Kika kashe wayar ki?
Tayi shiru tana murmushi.
Kinji?
Duk kin rame kinyi rashin lafiya ne?
Um, ta ce.

Ko dai tunani na ne?
Ta galla mishi harara , ya kyalkyace da dariya ni ma na rame ko?
Um, ta ce.
To ki tambayeni dalili Mana ...... Ta danyi murmushi kaiiiiiii Anwar.
Me yasa Kika koma da gudu bayan kin ganni?
Tayi Yar dariya....
Murna CE?
Ta Kara galla mishi harara.
Bacin wancen Dan iskan da Baki sako hijab din nan ba kayan sun Miki kyau kin San Haka?
Ta ce hmmm, kawai.
Gobe Zan dawo ni kadai kada ki Sanya hijab kinji ko?
Ta harareshi kammmm.
Yayi murmushi Dan Allah kisa irin gyalen dazun.... Bafa Zan saka ba dazun ma na manta ne..... Zan cireta idan Kika saka wallahi...... Anwar Nan fa gidan mu ne nidai ka rufa mun asiri.
Ni Yanzu ka janyo mun anjima dole in amsa tambayoyi wurin daddy?
Na mene?
Dalilin zuwan ka ko?
Kice fada mukayi gashi kin kashe wayarki nazo bayar da hakuri...... Nidai Dan Allah da baka zo ba saboda zai...... Ya tsareta da ido. Tayi shiru.
Uhum, Ina jinki saboda zai ce meye?
Nidai shikenan.
Ya kalli sadeeq jeka ci abinci fa, okay ya Mike ya nufi wurin
....ke Kuma kawon nawa anan inci.
Saboda me?
Saboda bana son kimun nisa Kuma bazan yarda gani ga ki ga sadeeq a wuri daya ba muna ci...... Wai Kai meke damunka....????
Yayi dariya kawai.
Suleiman ya kiraki?
Gabanta ya Fadi, wace amsa zata bashi kada Kuma ya Kara hasala saboda ta lura tabbas baya kaunar Shi.
Bari kawai na fada mishi gaskiya..... Ya yi ta Kira Amma ban dauka ba wallahi...au haba?
Allah kuwa.
Ko shine dalilin da yasa Kika kashe wayarki?
A'a ba Shi bane.
To nine?
Tayi shiru.
Saboda me Kika ki daukar wayarsa?
Anwar ka daina kawo maganar Suleiman tunda ita ke kawo Mana sabani..... Dole ki canza layi..... Ta zaro ido dole fa kace .
Yasha mur tabbatas and I mean it.
Ta Mike kawai tana hararar sa, ya Kai hannu zai kamata tayi baya da sauri tana fadin Zan kawo ma abinci ne.... Sadeeq ya banka mishi harara kaidai wallahi bakayi ba..... Yayi murmushi ka Gama kazo ka bar Falon nan ka isheni haka Nan .... Babu inda zaije. Ta fada tana zuba

mishi farfesun Koda da dankalin turawa....
Ki hanashi din ki janyo ma kanki Yanzu in ci ubansa anan har su daddy suji.... Gabanta ya Fadi tasan karamin aikin sa ne.
Ta kawo Masa ta Dan janyo stool ta ajiye ta koma ta dauko mishi juice exotic Mai sanyi na kwakwa da abarba.
Ke ce kikayi?
Ya kalleta lokacin da yayi lomar farko...... Mommy ce.
Yayi dadi amma gobe komeye za'ayi kiyi mun kinji ko?
Ta galla mishi harara kawaiyayi murmushi Ina dai Shan harara Ni Anwar.
In tambayeki???
Ya tsareta da ido.
Um,
Tsakanin ki da Allah kinji dadin zuwa na?
Tayi Yar dariya kawai..... Kinji?
Wai ya akayi kasan address din nan gidan?
Yayi murmushi sirri ne.
Ta Dan harareshi ka Sanya mun ido da yawa me yasa ka damu dani haka?
Saboda....... Yayi shiru Yana Yar dariya.
Ta tsareshi da ido, saboda me?
Saboda kawata ce ke my best friend.... Ta buga tsoki.... Ya kyalkyace da dariya. Yana ci gaba da Shan pepper soup din.
Sadeeq ya Mike Bilkisu bude mun kofar can naga exit ce ko?
Eh, amma ya zaka fita zaka biye maganar  sa ne?
Yayi murmushi a'a Zan dawo ne shidin banza ya hanani Zama anan?
Ya bisu da kallo kawai Yana Shan lemu.
Tana budewa ta hango iyayen motoci da katti sai gewaye gewaye sukeyi suna mazurai..... Ta dawo da sauri, Wai Kaine kazo da waccen bataliyar?
Ta tsaya gabansa tare da rike kugu, ya daga ido Yana murmushi tsiwar ce ta tashi?
Anwar waye baban ka?...... Ya fesar da lemun bakin sa saboda dariya. Ta tsuke fuska, ya fizgo hijab dinta tayo kansa zata fada yayi saurin mayar da ita gefensa ta zauna..... Innalillahi, Kai Wai wane irin mutum ne?
Idan za 'ayi tambaya Zama akeyi ba tsayuwa ba bakauya.... Nice bakauya ? Eh ya fada Yana hararar ta,
Ka amsani ........ Maganar ta makale ganin ana shigowa da jikkuna set/set..... Ta zaro ido ko yazo neman auren ta ne?????
Ta kalleshi da sauri meye ake shigowa dashi kamar wani lefe?????? Ya kyalkyace da dariya lefe Kuma an fada Miki na Isa Aure ne?
Ta daka mishi tsawa to na menene?
Calm down ya fada a hankali ganin tana neman tayar da hankali...... Na kawo Miki tsaraba.... Tsaraba ta mecece?
Anwar wanene baban ka a Kano? ....Kai Ina son in San waye Kai ayau... Dai dai sun gama ajiye jakunkunan set hudu ta daka musu tsawa ku mayar dasu mota bazamu karbi kayan Nan Haka ba fa.... Sadeeq zaiyi magana ya daga mishi hannu yace jeka kawai Zan Mata bayani......

Anwar ko hakan zai Zama batawar mu ta har abada...... Ki dubi girman Allah ki daina janyo mun tashin hankali ki jira na amsa Miki duk wata tambaya da Kika rasa amsar ta.
Zan amsa Miki wanene baba na a Kano....
Ta tsareshi da ido, ya yi Yar dariya.
Baba na ya rassu Ni maraya ne...... Jikinta yayi mugun sanyi.
Tayi saurin kallon sa kamar zatayi kuka...kayi hakuri Anwar ban San Haka ba.
Ta Fara magana a hankali Allah ya jikansa da rahama yasa mutuwa hutu ce, yayi murmushi cike da Jin dadi Amin ya Rabbi.
Sai kuma me?
Waye Kai? Ko Kuma wanene marikin ka?
Yayi Yar dariya nine *Hamza bushara*..... Ta dago Kai da sauri taja baya ta koma karshen kujera kamar wacce taga abin tsoro....
Ya Kara Yar dariya.... Bilkisu nine *Bushara* Wanda Kika ji ana fada a *Nigeria*.... Na shiga uku ta fada da karfi.... Ke kwantar da hanka... Ta Mike da sauri shima yayi saurin mikewa...... Idan Kika gudu Zan biki har gaban mommy wallahi.... Dan Allah me kake nema wurina Anwar?.... Na shiga uku. Ta Kara fada duk jikinta ya tsinke da rawa...... Zauna in Baki amsa ta Kara ja baya.... Ka kwashi kayan can kabar gidan nan tun kafin ma..... Ke Wai ya akayi ne ya daka Mata tsawa. ..... Ta daga hannuwa kayi hakuri na tuba *Bushara* ta Kara maimaitawa a hankali..... Ya buga tsoki ke bana son gidadanci zo Nan ya Mika hannu..ta ja baya .
Ya fiddo ido...ke me yasa kin cika kawo matsala? Yasha mur kina son in kamaki ko?
A'a, ta fada tana girgiza Kai, oya come and sit down let's sort out where the problem is...... Ta zauna a dosane..... Ya kyalkyace da dariya ji yanda Kika canza lokaci daya..... Kin taba ganina a TV?
Ta ce a'a.
Jarida fa?
Ban gani ba.
To Kuma.
Kika sani ko Ina zolayar ki ne?
Ta Dan kalleshi.
Yayi murmushi eh Mana .
To ko da wasan kakeyi?
Ya kyalkyace da dariya kawai.
Ta bishi da kallo.
Ke Ina Kika San *Bushara*?
Ta harareshi a Nigeria waye bai San wadannan sunayen guda biyu ba *Dan gote da Bushara*?
Ya Kara yin dariya..... Yayi saurin matsawa kusa da ita ya chafki hannuwanta.... Yawwa ya fada Yana murmushi....nine *Bushara* ki kwantar da hankalin ki nothing will happen sai alheri...... Kwallah suka shatato Mata ita kanta Bata San ko na menene ba...... Kuka again?
Ke bakya da wahalar kuka?
Bana son kayan can daddy zai tambayeni na menene Kuma zai mun tambayoyi akanka......Yanzu kukan na menen ciki? Kayan ko kuwa sanin da kikayi nidin waye?
Kai nidai gaskiya ka kyaleni.... In kyaleki? Kin Kara maimaita wannan kalmar Dana fi komai tsana ko?

Ta kalleshi Anwar me yasa ka mun waccen hidimar?
Ya saketa tare da watsa hannuwa kawai I feel to..... Ba yiwuwa ka fada mun me yasa kake wannan over acting din?
Na ce Miki kawai na siyo miki tsaraba ne bana son zuwa hannu biyu..... Ta Mike bazan karba ba ka mayar dasu gida idan ka Isa Aure ka hada wa matarka..... Ya Mike ta nemi kwasawa da gudu ya yi saurin rike hijab dinta.
Wallahi sai ka sakeni haka kawai daga muna course mate zaka jibgo irin wannan hidimar ka kawo mun..... Kawai ne Bilkisu?
Ya fada Yana matsawa kusa da ita.... Kawai ne wallahi, I don't value friends lemme tell you. Kina son ki kunyata ni ne?
Ta galla mishi harara Ni ma ai kunyata ni zakayi idan daddy ya tambayeni sai kawai ince abokai..... Kice *INA SON KI* ne.... Ta zaro ido jiri ya nemi daukar ta.........✍🏼
*Zainab wowo ce*

*Assalamu alaikum*
Masoyana Ina alfahari daku.

Nazo da wata tsaraba, hausawa na cewa kula da Kaya.......

1. Ina wacce ke fama da karancin ni'ima?
2. Wacce ke fama da budewa tana son jinta a matse da ni'ima sosai?
3. Ko kinsan yawan zubar da ruwa wani lokacin matsala ne? Wacece keson taji ta adai adai?
4. Wacece mijinta baya gamsar da ita?
5. Suwa ke fama da infection?
6. Akwai matan da har yau Basu San dadin Aure ba sam Basu Jin sha'awa ko kin San dalili?
7. Wacece keson ta gyara nonon ta da jikinta yayi luwai luwai?
8. Ina wadanda mijinsu baya gamsuwa dasu?
9. Wacece kullum sai tayi amfani da lubricant saboda karancin ni'ima?
10. Ina wadanda miji ke musu gani gani da hargagi kullum?

Akwai supplement masu kyau na dukkannin matsalolin aure daga zainab wowo, direct order ne muna turawa ko wane gari Amma Kano, Abuja da katsina zaku sameshi free delivery in shaa Allah. Masu bukata su tuntube Ni. Darajar annabi da alqur'ani serious buyer nake bukata Dan girman Allah na rokeku. Ga number ta 08089973394 in shaa Allah.
[3/23, 8:01 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
2️⃣2️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

👉🏽💞💕💕 *RUKAYYA BAKO DAN BATTA I love you so much, remember this always*🥰😍😘.

*Wannan page din na sadaukar dashi ga dukkan masoyan wazai furta*💞💗
Shi yasa yau na saki biyu don kuji dadi farincikin ku shine nawa wallahi.😭😭 Ina son ku😍😘🥰 kullum sai nayi kukan dadi.

**************

*ABUJA NIGERIA*

........ Ya tallabo bayanta ta dawo ta tsaya dai dai Amma ta kasa yarda su hada ido, *INA SON KI BILKISU* Yau na *FURTA* Abinda kike son ji..... Ta Kara kasa da Kai jikinta har lokacin bai daina kyarma ba....Wai mafarki takeyi ko kuwa da gaske ne?

Ya rungumota ta sunne Kai jikinsa.... Ya Kara Rada Mata... *ina son ki* tsikar jikinta ta tashi Yarrrr..... Duk wannan haukan da Kika ga inayi sonki nakeyi, Shi yasa na kasa boye kishina gareki...... Nasan kin fahimta Yanzu Kuma kin Sami amsar fadawa su daddy ko?

Ya dago fuskarta....ta koma da sauri.... Ya kyalkyace da dariya yau Kuma jikina ake son Hawa?

Kin wahalar damu da yawa, kina kawo rigima kullum because you want me to say it.... Ni nasan kina Sona I knew it...Kuma ko Baki furta ba nasan kina Sona wallahi....... Ki daga ni na tafi... Ya fada Yana dariya.

Kinga duk laifin ki ne, da kinsan zakiji kunya da hakuri kikayi muka tafi a Haka bakiji komai ba..... Ta zame a hankali ya mayar da ita da sauri, kafin ki gudu Dan Allah gobe kada ki Sanya mun hijab din nan kuma kiyi mun girki da kanki Zan zo around 10:00am kinji ko?

Ki ce b lefe na kawo ba, hasafi ne saboda Ina son ki.... Ta zame yayi saurin rike hannun ta ki jira na Baki kudin dinki Mana ..... Ka barshi nidai... Bakya so?

Ta daga Kai..... Da gaske bakya so?

Um, tace a hankali.

Yayi Yar dariya kudin ke Baki so ko Ni?

Kudin ta fada tana sim sim da Kai.

Yayi murmushi Ni kina Sona Kenan?

Ta yi alamar fizge hannunta.... Ya rike gamm. Kice inji Mana kina Sona?

Ta yi kasa da Kai ji takeyi kamar ta bude kasa ta shige ta huta.. ...ya Kara dariya sosai ohh ni Anwar Ashe akwai ranar da bakin nan zai mutu?

Ai Dana San wannan kalmar ce zata sa in Sami saukin tsiwa da tuni na Gaya Miki saboda na Dade Ina dakonta.......

Idan daddy ya Baki zabin auren mu kice kinfi so ayi kafin mu Gama school....... Lokacin ne ta banka mishi harara da sauri ta kawar da Kai.

Ya Kama dariya ya figi hannunta zo kiyi mun rakiya naga alamar nema kikeyi ki gudu ciki ko?

Ta biyoshi a hankali yasa hannu ya fiddo rafar kudi ya ajiye hannun kujera idan kin shigo ki

wuce dasu na dinki ne....na gode. Ta fada a hankali. Tayi murmushi ya ce my pleasure dear.
Ta Dan harareshi ya tuntsure da dariya shin na Riga na *FURTA* ai to boye boye name?.
Suka fito tayi saurin fizge hannunta ya Kama murmushi Yana fadin ke dai Yar kauye ce...... Allah yayi?
Sadeeq ya taresu.
Allah yayi sadeeq yau kwana ta saka ni sai da na *FURTA* Ina son ta...... Sadeeq ya you firgigi ya ce waoooh *Anzo wurin kenan*.... Duk suka bushe da dariya ita ko sai murmushi takeyi kasa kasa...... Munafuki ai duk Kaine tun farko kayi ta wahalar da ita... Shin ai nadai FURTA gobe Zan dawo *Zance* ya bangajeta da kafada ko Bilkisu???
Ta galla mishi harara suka kwashe da dariya.....
Kiyi mun tuwo goben.... Ya shiga mota tana tsaye har suka fice gate din....
Wai da gaske ka furta kana sonta?
Wallahi kuwa, sadeeq rigimar Bilkisu bana iya daukar ta, ta tsareni lallai sai tasan wanene Ni...... Saboda me zaka boye Mata Wai?
Ai na fada.... Amma fadar sai ta tsorata Kuma. Na rasa me take so, Kuma Wai ita ya zata fada a gida wace amsa zata bawa su daddy....na ce kice *Ina son ki* saura kadan tayi penting .....suka bushe da dariya...... Amma ka Mata gatsal! To ya zanyi da ita? Kaga yanda ta nemi ta firgice mun?
Banza finally ka furta dai.
Yayi dariya *Anwar ya furta* naji tsoro yarinyar Ina son ta saboda class wallahi.....gidan sa dake *Minister's hill* suka nufa.
Mommy..... Mommy ta Fara kwada Mata Kira tana Hawa sama.
Tana faman shirya jaka ta shigo dakin, mommy Anwar fa ya kawo Kaya da yawa ..... Wane irin Kaya?
Ina daddy?
Sunje sallah kasa.
Wane irin Kaya ne ya kawo.
Jikunkuna ne set hudu.... Ta kalleta da sauri jakunkuna? Na menene????
Ta sunkuyar da Kai ta sunga Mata kudi Kinga Wai su Kuma nayi dinki...... Duk Akan me?
Ta Kara kasa da Kai, ya ce tsaraba ce ya kawo mun.... Saboda???...... Ta Kara katseta da sauri.
Ya ce Yana Sona ne???
Muje naga kayan, bazaki ce mishi daddyn ki ya hana karbar kaya ba?
Wallahi duk abinda na kokari in sanar dashi bai yarda mommy.
Wohohoho ta fada tare da rabka salati...... Amma kin San daddyn ki zaiyi fada ko?
Mommy Anwar Shi ne *Hamza bushara*..... Mun sani. Ta ce a takaice ta zaro ido Kun sani mommy?
Yes, ta fada tare da wucewa tana fadin jekiyi sallah nasan fada ne yau duk sai mun Sha ni da ke.....
Ta falon ya shigo Yana ganin kayan ya kwala ma Bilkisu Kira.
Ta fito da gudu gudu.....

Wadannan kayan fa? Ta sunkuyar da Kai, Anwar ne ya kawo su daddy.

Na menene?
Ya ce tsaraba ce kada yazo hannu biyu....
Saboda me?
Tayi jimmmmm kafin ta ce *Wai Yana Sona ne* yanayin yanda ta Fadi maganar kamar Yar koyo mommy ta shigo ya kalleta Kinga Kaya?
Hada kudi....
Ya kalli Bilkisu ke kina sonsa?
Tayi shiruuuu kinji mamana kina son sa?
Tayi kasa da Kai kawai.... Yayi murmushi kina son sa kenan.
Ki mayar mishi da su kice bana karbar irin wannan kyautar idan har da gaske yakeyi ya turo iyayensa.... Ta dora hannu saman Kai.... Daddy bayar Dani zakayi haka da wuri ta kurma ihu tana kuka.
Ya yi Yar dariya, to tunda kin Sami Wanda kike so me ake jira..... Nidai kada a turo...ke bama son rashin wayo.
Turowar an fada Miki Yana nufin za'ayi Aure?
Hakan zai nuna idan da gaske yakeyi sai a ajiye magana.
Ta danyi shiru alamar ta gamsu.
Ya wuce Yana girgiza Kai Yana murmushi,
Mommy ta kalleta tana hararar ta, wannan koke koken ba komai zai janyo Miki ba sai raini wurin Miji. Komai ke sai ki bare Baki saboda kina ruwa ruwa.... Mtsew ta ja tsoki.
Wannan rawar Kan da Anwar keyi inba auren ba meye zai kamance ku?.... Mommy..
Yi min shiru, Ina ce Nan Kika diririce Kika firgice saboda yayi fushi da ke ko?
Ta zumburo Baki kaiii mommy....... Ke arrr kilibabba.
Ta wuce , ta Mike ta bita da gudu mommy yace zai zo gobe by 10... Sai kije ki fadawa su Rahina don su shirya mishi kin dai San ba Mai sauko Dani da safe ko?
Mommy cewa yayi ni Zan girka baya son nashi...... Sai kawai tayi dariya tace yaron nan hooo. To ya kyauta ma kansa sai kiyi asubanci saboda na sanki da shegiyar nawa da duminiya, Bilkisu za a Fara wa miji hidima..... Kai mommy ta bita tana shagwaba....
Ta kyalkyace da dariya. Ai munji dadin zuwan sa saboda kullum daddynki cikin waya yakeyi Yana jiyo labarin badakalar ku.....kamar ya mommy??
Tayi Yar dariya akwai wadanda kebin movement dinku kullum...... Ta zaro ido yasan Anwar na zuwa gurina mommy???
Tayi murmushi har ciwon cikin da kikayi ya je har cikin dakin ki,sannan ya balla Miki kofa.... Ta zare ido na shiga uku na... Ke dakata, tunda bai nuna Miki ba wallahi kada ki nuna kin sani Babu ruwana.... Cikinta yayi kulululu ta hadiye miyau kut!.
Mommy Dan Allah laifina ne? An fada mishi Nima bana son haka ko?
Ina Jin abinda yayi saving din ki kenan....
Ta saki ajiyar zuciya kaiii Anwar case ne.
Ko bude kayan basuyi ba yanda suka ajiye haka aka barsu a wurin.

*WASHE GARI*

Karfe bakwai tana kitchen, daddy ya fito zai je office ya leka... Bilkisu a bani abinda ya sauka

na jiyo kamshi ko Anwar din kawai keda shagalin?... Ya karasa maganar Yana murmushi.
Kaiii daddy ta fada cikin Jin kunya....
Har ciki ya shiga Rahina nata fere dankali, saratu na grating kwakwa, ya kallesu yau aiki ya karu ko?
Iyye hada kaza haka?
Ya bude oven.... Ta rufe fuska lallai yarinyar ashe catering school din bai tashi a banza ba...
Menene can?
Wipping cream daddy... Zakiyi cake ne?
Na Gama gashi can ma.... Ya sa hannu ya dauki daya ya Kai Baki..... Um um..ya naji wannan kamar ba irin Wanda ake Mana ba?...... Kai daddy ta Kara fada yayi dariya....
Mommy ta shigo ga break din can fa.... Zo kiga sonkai Bilkisu na hadawa Anwar gara ba irin ..... Kai daddy... Eh Mana.
Ta matso iyyeh lallai Shi yasa baji gida ya Fara daukar harami.... Ta bude tukunya.. hada Kan rago?......
Kai Kai Kai daukon kwano Shi zata zuba mun ja'ira..... Duk suka kama dariya.
Rayuwa irin ta gidan su Bilkisu tana da ban sha'awa......mommy ta kalli Rahina, yau taku ta sameku ko?.... Abinda na fada Yanzu kenan.... Daddy ku je falo Zan kawo muku nidai... Duk suka kwashe da dariya... Mommy tace komai Zaki debo Mana ko sai ankai wa Anwar din nazo na ce Zan Dauka..... Kaiii mommy Wai ya Zan ce baza ku ci ba ????
Suka fita suna dariya hannun daddy rike da cup cake Yana gutsira...
Ya kalli mommy in shaa Allah tarbiyyar da muka ba Bilkisu bazai taba Sanya muyi Dana sani ba.... In shaa Allah.
Ina ta fada akan catering school din nan Kika dage Kinga Yanzu amfanin yazo ko?
Ai na fada ma Kuma wallahi cewa yayi nata yakeso baya son na Yan aiki kaga Idan Bata iya ba zai aureta Yana sonta Amma can gaba matsalar dole ta taso.... Yaron Yana da rawar Kai akan Bilkisu hakan na bani tsoro, ya kasa danne feelings dinsa kin lura ko?
Hada yarinta ke damunsa..... Yes da giyar kudi.
Yama arzikin sa kankanta kawai hankali da natsuwa yaron ke bani sha'awa...da kunya Kuma....yes Yana da kunya of course.
Bilkisu ta shiryo musu komai a tray ta kawo Yana Shan Lipton da biscuit....daddy biscuit Kuma???
To wancen kwalayen biscuits idan bama ci ya zamuyi dashi na ce ku rabar Kun jibgesu.... Dasu mommy zata tafi sokoto ne na dibar Mana namu Yana store... Ohhh ban sani ba ... Ta ajiye ta koma.
Ya bita da ido, abinda ke tayar mun da hankali shine yanda yake son ringa nuna Mata komai da karfin tsiya..... Gaskiya fa.
Yanzu idan ya turo iyayen zuwa taushe zaka ce su kawo kayan baiko?
Eh, ki Bari zuwa dare zamu maganar kiji yanda na tsara lamarin.....
Karfe takwas ya fita office mommy Kuma ta Haye sama domin komawa barci.
Sauri sauri suka karasa aikin , goma saura kwata an shirya komai ta fada wanka.
Ta fiddo Kaya sunfi ashirin ta rasa wane zata saka?
Tabbas Bata son ta saka matsattsu tunda ya tilasta gyale zata saka.
Da kyar ta dauko wata doguwar riga bubu na boyel peach an mishi kwalliya da *Stones* blue.

Dinkin ya bude sosai, ta yi simple kwalliya ta shafa light pink na lipstick..... Rahina ta kwankwasa Mata kofa... Aunty kizo.

Inji waye? Ta fada tana gyara lagen gyalen... Uncle Anwar ne gashi can na bude mishi falo.... Ki ce Ina zuwa..

Ta Kara feffesa turaruka a jiki.... Ta juya ta Kara juyawa a madubi sai Kuma ta danji kunya tayi murmushi ta fita tana takawa dai dai cikin plat shoe light blue kalar gyalen.

Tana bude kofa sai kawai ta kwashe da dariya ganin sa bisa dining table Ya Fara cin abinci.... Na shiga uku Kai baka bakunta ne Wai??????

Ya kyalkyace da dariya inayi Mana gashi ni nake zubawa kaina? Idan bana bakunta ai zanje ciki na Kira ki zuban ..... Ta galla mishi harara Kai baka da aiki sai ci..... To ai yunwa ba kanwar ubana bace ko?

Ta kyalkyace da dariya ya akayi Kika San Ina son kan rago?

Ta ce hmm, ya lunkuma harshe a Baki Yana um...um...um please budan can menene?

...... Wai Kai baka ko irin Jan ajin Nan?

Ya kyalkyace da dariya kaiii Ni Zaki Sanya na kware wallahi.

Daukon lemu Mai sanyi ni bana Shan tea wannan sai ku Yan gayu..... Ta Kara hararar sa.... Ya kamata na Sanya wa hararar nan doka duk lokacin da kikayi ta ......

Ta Mike kawai ta Isa inda fridge ta bude wane kala Zan kawo maka?.... Peach daukon peach dinnan Amma fa roba biyu Ni daya bata Isa ta.... Ta Kara dariya ohh Allah gamu gareka....

Ya Miko Mata chips da egg Fara ci Nim zanci irinsa..... Kana da cikin Zane ne?

Yayi murmushi Amma kajin nan dasu Zan tafi fa don sai dare Zan dawo.... Zaka dawo Ina? Anan.... Ya fada Yana kallonta.. ke na dawo Abuja fa sai an koma school nida Kano......ta zaro ido duk kana me?

Ya nutsar da idonsa cikin nata yace duk Ina zuwa Ina ganin ki... Tayi kasa da Kai tana murmushi.....

Kill babba abinda kike son ji kenan ko?

Tun karfe nawa Kika tashi yau?

Ta Dan zumburo Baki ban koma barci ba tun asubah..... Nima haka ya fada Yana murmushi. Ta harareshi kana meye?

Ina kallon agogo na kagara 10 tayi kamar na Miki waya na ce na mayar dashi eight..... Ta yi Yar dariya yabi kuncinta da kallo..... Kinyi kyau sosai fa.

Ta ce hmmm.

Ni na yi kyau? Sabbin Kaya na dunka saboda zuwa Nan fa.... Ta kyalkyace da dariya Kai na bani yau to me nace?

Ya Dan Sha mur naga kamar Baki fahimci hakan ba.... mtsew ta ja guntun tsoki.

Yayi Yar dariya ya Mike Yana goge baki da tissue taso idan bazakiji ba muyi magana ba dadewa zanyi ba Zan barki kiyi barci sai na dawo da dare ko? Ya na maganar Yana tafiya tare da janyo hannunta..... Ohh Shi baya Jin komai ya Kai hannu ya tabani ni Bilkisu??.

Ya zaunar da ita sannan ya zauna kusa da ita.... Ya akayi Kika bar kayan can anan? Daddy yace ki mayar mun?

Ta daga Kai alamar eh,

Kin fada mishi in sonki?

Nan ma ta daga Kai?

Duk da haka bai karbi kyautar ba?
Ta ce eh,
Sunyi yawa?
Eh,
Yayi murmushi to Yanzu me yace?
Ta yi kasa da Kai yace ka turo iyayen ayi magana.... Ihu ya daka kawai sai ya Mike tsaye ya janyota ya Bata wani hot hug.
Ta zame ahankali ta zauna tana murmushi....... Dan Allah kizo na you hugging dinki...
Ta galla mishi harara ya zauna Yana dariya *Amma fa nazo da sa'a* .......kawai ta jiyo motar daddy alamar ya dawo.... Gama daddy Nan ya dawo.... Gooood ya fada tashi kije kice Ina son magana dashi.....
Ta zaro ido.... Meye zaka fada mishi?
Zan rokeshi yabar Miki kyautar nan bazan koma da ita ba.... Kai Anwar daddy fa baya son gardama.... Haba?
Allah.
Yayi murmushi jeki ce Ina magana...... Tashi kada ya shiga ciki please.... Ya mikar da ita...
Yana kokarin shiga ta fito daddy ka Kuma dawo? ..... Bilkisu kice ma Anwar securities din nan ya Basu damar Zama Mana tsayuwa ai babu dadi ko?...... Shine yace Wai zaiyi magana da Kai.... Ya kalleta da sauri Yanzu?
Eh, okay Zan biyo ta Nan Ina sauri ne nayi mantuwa.....
Police din da suka rako Shi suka bude mishi kofa ya shiga ta dayar kofar.
Ta dawo, yace na fito?
No. Zai biyo ta.... Ya banko kofa Anwar lafiya dai ko? Ana jirana office.... Da sauri ya sauka kujera ya zukunna.... Yayi saurin Mika mishi hannu taso inji menene???? Ya rike hannun sukayi hanyar fita.... Ya Kara kallonsa menene?
Ya kasa magana kunya duk ta kamashi.... Ya tsaya chak ya fuskance Shi...Anwar!
Ya Dan rusuna daddy Dan Allah abar Mata kayan bana son na koma dasu..... Ya kura mishi ido... Amma kasan sunyi yawa ko?
Ayi hakuri Zan kiyaye next time Amma now abar Mata don Allah.
Ya Kara kallonsa sosai sai Kuma yayi murmushi... Shikenan Amma bana so ka daina kaji ko?
Ya rusuna na gode Allah ya Kara lafiya da shekaru masu albarka...... Aminnnmm ya Rabbi.
Ta fada maka nace ka Aiko?
Ya Kara sunkuyar da Kai In shaa Allah zasu zo gobe... Yayi dariya
gobe yayi sauri zuwa asabar dai ko?
Ya noke Yana murmushi.... Shikenan sai na dawo ana jirana ......
Ya dawo Yana murmushi tana zaune.....ya karasa Yana fadin yace ki dauki kayan shikenan ko?
Ta kalleshi da sauri.
Yayi dariya rokonsa nayi, ya Kuma amince ... Ta ce hmmm.
Na ce mishi Zan turo gobe yace sai zuwa asabar....
Ta ce hmmm kawai... Yanzu Kinga Ina da hujjar cin uban Suleiman ko?
Ta zaro ido.... Dan Allah ka bar maganar sa, Zan fada mishi an Mana baiko...... Ban yafe ba Kika Kuma magana dashi ..... Ta zaro ido..lallai idan aka koma school akwai chakwakiya.

Ya Mike Zan tafi sai na dawo anjima kinji ko?
Ta ce toh itama ta mike, daukon kazar da wancen cake din dasu Zan tafi.
Ta sungumo mishi suka jera ya fizge gyalen tare da shafa gashin ta yaja.... Nayi sa'a fa domin Ina son yalo yalon gashi..... Rufen gashi ko na saki kayan Nan su zube... Da kin sake wasu wallahi.
Ya Kara shafa gashin Yana murmushi sannan ya mayar Mata da gyalen... Ta banka mishi harara... Kana da matsala wallahi hakan haramun ne... Astagfirullah na daina.
Ya fada Yana dariya...

Yana tafiya ta saki ajiyar zuciya tace kaiii Anwar case ne.
Ita da mommy suka bude jakunan.... Tsoro yasa suka mayar suka rufe..... Ta kalli Bilkisu yaron nan sai ya kusa haukata ki idan kukayi Aure...
Tayi jimmm... Kawai.
Tare da Sadeeq ya dawo..... Tana shigowa yace koma ki sako hijab........
Ikon Allah sadeeq ya fada tayi saurin juyawa.... Banza wallahi kwakwa ke kawo ka marar zuciya..... Naji kome zaka ce kai ne ka jawo ni dole na biyoka kuma na gama zaman zuruu...... Ya yi murmushi.
Abinda Zan Rama?? Kai kishin naka ma da bashi da aji..... Ya Kara kyalkyace wa da dariya, kishin har akwai Mai aji?
Ya mishi banza.....
Ta dawo rike da mango juice a cups..
.... Bilkisu kinji sadeeq Wai kishina baida aji kin yarda?
Ta ce hmm, kawai ya Miko Mata sim card ungo Ciro mun layinki.... Ta zaro ido...
Yasha mur yes dole ki canza layi ..... Dashi fa nake jin alert....wane bank ne?
Access bank. Ta fada cikin fushi.
A nan Kika bude account din ko sokoto?
Ta bishi da kallo.... Anan Abuja... Kawai ya dauki waya...hello , yes nine lafiya.
Zan turo ma wani account number please ayi blocking din sa zamu bude sabo amayar da komai can.... I don't know buh I'll ask her...
Ya kashe meye account number din???
Sadeeq kaga rigimar da Anwar ya kunno ko?
Ya danyi murmushi zamanki lafiya ki canza don tabbas kishin wannan zai janyo ma bank din matsala..... Tayi zugummm....
Ya figi wayar kawo na canza Miki..... Zan dauki no. Su Aisha.... Zan saka Miki duk no.s din kawayenki Mata Amma wallahi Kika yi saving maza sai......... Kana ganin Ina kula maza ne... Ta fada a hasale.... Ya dalla Mata harara su ai suna kulaki ko?
Ta Bata rai.... Sadeeq ya jiyo zaku Fara ko?
Hakuri zakiyi dashi fa halin sa ne ba yarda Kika iya... Ni bana son wannan zargin da yake mun... Na daina ya hakuri shikenan ko?
Tayi shiru. I'm sorry please. Shikenan ta fada tana hararar sa.
Yayi Yar dariya.....
Firar rigima rigima soyayya soyayya don ma sadeeq nasa Baki idan sun nemi rikicewa.....
Ya ce zai tafi Kano gobe zai dawo asabar Amma sai dare zai shigo bayan Baki sun tafi.

Ta masu rakiya ya hanata karasawa waje ya ce ta koma kawai....

Daddy ya buga ma kanen sa sokoto cewar yazo don su tarbi Baki, ya Kira yayan mommy da aminan sa biyu ministers.
An shirya gaggarumar tarba.
Misalin karfe Sha biyu suka karaso.
Abin mamaki ba kudi kawai suka kawo na neman Aure ba hada halawa da goro da biscuits.
Bayan an gama gaisawa aka ci abinci aka Kara gaggaisawa kowa ya gabatar da kansa, iyayen Anwar biyu ne daya kanen maman sa daya Kuma aminin mahaifinsa ne sai wasu dangin babansa daga kauye saboda baya son da yawa asan abinda yake ciki kamar yanda Hajiya ta gargadeshi. Daddy na gefe kanin sa ya Fara magana....
Alhamdulillah munji dadin kasancewa daku ayau ya Allah yasa wannan yaza alkhairi garemu Baki daya....
Mune da jin dadi hakika Hamza ya kawo mu gida na mutunci masu karamci Alalh yasa wannan yarinya tayi Hali irin na iyayenta....duk aka amsa da aminnn.
Ga Kaya mun kawo na neman Aure da kudi dubu dari biyu ya Allah yasa muga ranar da zamu taru haka da sunan dauruwar auren su, aka ce ammmmeeenn...... Alhamdulillah daddy ya katse Shi.
Duk aka kalleshi... Da sauri.
Kamar yanda na yanke shawara nida mahaifiyar yarinyar Nan da dangin mu, Ina ga a wannan haduwar mun Isa mu shaida Aure saboda haka na yanke shawarar wadannan kudin zamu karbe su matsayin sadaki goron Kuma aba kowa ya shaida Amma bisa ga sharadi..

Bana son yaran nan su San Haka har sai bayan sun kammala karatu tukun....
Masha Allah Masha Allah duk falon ya dauka nan da Nan aka Fara Shirin daurin

Aure kowa ya bada wakili..... Cikin mintuna da basufi ashirin ba aka ce faaaaatiiihaaaa.....😄✍🏽

*Zainab Dahiru wowo*💖💖😆
[3/23, 5:04 PM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
2️⃣3️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

👉🏽💞💕💕 *RUKAYYA BAKO DAN BATTA I love you so much, remember this always*🥰😍😘.

***************

*ABUJA NIGERIA*

...... Falon ya dauki surutai kowa sai fara'a yakeyi da murna.
Alhaji Hassan ya kalli daddy ya ce, ranka ya dade Ina neman afuwa amma Zan yi tambaya....
Cike da fara'a ya ce bisimillah Alhaji.... bisimillah kowa ma na jinka....
Akan daurin auren nan ne, a gaskiya kaina ya daure ban taba ganin irin wannan ba, mun zo neman Aure ne ba Sanya baiko ba, Jin magana ya kawo mu, amma kwatsam ka karbi Kaya da kudi a matsayin kayan Aure da sadaki dan Allah me yasa ka yanke wannan hukunci Kuma ka saka sharadin baka son yaran su sani....
Ya Kara fadada murmushi kafin ya Fara magana Yana kallon Alhaji Muhammad tambuwal, kaga maganar ka ta fito na wata kila su bukaci dogon bayani ko?
Duk sukayi Yar dariya ya maida kallonsa ga Alhaji Hassan ya na magana cikin natsuwa:
Abinda ke faruwa a gaskiya rawar Kan Anwar yayi yawa, tun asalin tura Bilkisu karatu dutsinma na kaita tare da masu tsaronta ba tare da ta sani ba, na baza securities sosai akan sanar Dani duk wani movement dinta.
Lokacin da suka Fara takun saka ita da Anwar na Sanya aka mun bincike akansa, Ashe babu Wanda ma yasan yaron shine *Bushara*, shaidar da ya samu ya sanya ban dauki mataki akansa ba saboda naji cewa yana da halin ko in kula, gadara, Yana Kuma da son addini.
Bayan mun Kai Mata ziyara na hadu dashi sai naga fuskar yaron kamar na Sansa, kwatsam kuwa taron da kamfaninsa yayi a Lagos nagan Shi a daily trust.
Boye boyen daya ringa yi ma Bilkisu yasa na bashi dama amma a gaskiya zafin sa yayi yawa daga baya muka gane kishi ne. Yana da rawar Kai musamman idan Yana tare da ita, ga kuruciya, ga giyar so da giyar kudi kunga komai zai iya faruwa, Shi yasa na yanke shawarar kawai mu daura masu Aure yanda komin ya Kai hannu ya taba ta Yanzu hankalin mu bazai tashi ba matar sa ce.
Dalilin da yasa bana so a fada masu shine, matukar ya ji matar sa ce Yanzu tabbas bazai barta anan gidan ba, kuma a gaskiya bamu shirya aurar da ita Yanzu ba abun yazo Mana kwatsam Babu yanda zamuyi...
Na biyu, wallahi sai ya Mata ciki Kota halin Kaka duk da ba haramun bane Amma ga al'ada irin tamu ta hausawa hakan zaifi dacewa idan ta tare a gidan sa kuma gashi wuri daya suke karatu..... Zahiri, inji Alhaji Hassan.
Yawwah, to Shi yasa na ce mu kyalesu har sai sun gama makaranta sannan tunda saura shekara daya..... Amma wani hanzari ba gudu ba Alhaji Muhammad ya fada...duk aka mayar da hankali wurinsa..
A sanar da yarinyar domin ta san cewa akwai hukuncin Aure akanta, kasan yaran Yanzu kuma tabbas Kun San cewa shaidanu Yanzu zasuyi ta kunno Kai.
A fada Mata sannan a ja Mata kunne a sanar da ita implication na fadawa Alhaji Hamzan ita abun zai ba ruwa...... Kuma fa. Kowa yafada Yana girgiza Kai.
Kenan idan mun fahimceku Anwar din kawai za'a boye mawa?
Haka ya kamata gaskiya daddy ya fada.
Masha Allah hakan yayi Amma dole mu sanar da Hajiya na tabbatar baza ta Bari ya sani ba zahiri..... Hakan Yana da kyau. Duk suka fada lokaci guda.

Nan aka kasa komai aka Basu nasu aka masu Sha Tara ta arziki suka tafi suna Murna......
Tafe suke suna al'ajabin dattakon wadannan mutane, abun ya matukar birgesu Alhaji Hassan yasha alwashin shima zai ma yarsa irin wannan gatan da tsare mutunci.
Tana kwance yau duk ta tashi tana Jin jikinta wani iri babu kwari, ga kasala ga yawan faduwar gaba, tayi lamoo wayar ta tayi Kara.
Tayi shiru don tasan shine kawai zuciyar ta a yau najin haushin sa kadan....ga naci ya dunga Kira ba arziki ta daga...
Hello ..ta fada a hankali.
Ke yunwa nakeji kiyi mun faten dankalin nan da kikayi mun last week.
Kamar ta kurma ihu Shi duniya baida wata damuwa sai ta abinci?
Kinji? Ya fada da karfi.
Naji..
Ya danyi kasa da murya Zan Sami gasassar kaza?
Lokacin ne ta danyi murmushi, ka lissafo kawai abinda za a maka Yanzu zaka Fara Zan Sami kaza?? Sai ka lissafo goma.
Ya kyalkyace da dariya sai meat pie da Dan yam balls Amma kada ki cika mun yaji irin wancen kinji ko?
Naji sai me?
Yayi murmushi sai kiyi kwalliya sosai kisa gyale Banda wannan Dan iskan zanzo don bama zai San fita ta ba.
Ta ce hmmm.
Ya naji kin yi la'asar ko an Fara fargaba ne?
Ta galla ma wayar harara fargabar meye?
Ya Kara dariya ya ce wallahi basan an mako mun harara.
Tayi murmushi hmm Kai dai ka sani.... Kema kin sani kilibabba Anwar na kalbinki amma kina wani sharewa irin ba sosai din nan ba..... Ta kyalkyace da dariya kaiii Anwar Allah ya shirya ka... Hubby zaki ce bagidajiya. Ke wallahi kina Abu kamar wata Yar kauyen kumus.... Tayi murmushi kawai.
Yayi kasa da murya kidan canza mun suna Mana sweetheart....... Kai wallahi Zan ajiye wayar Nan ...ya Kara kyalkyacewa da dariya yace ya hakuri nayi shiru.
Ta zumbure baki.
Yaushe Zamu fita yawo cikin gari?
Ana wannan Corona virus din zaka fita yawo?
Ke ban son unnecessary excuse.... Cutar ce unnecessary???
Ya ja guntun tsoki.... Ko *Amigo* muje please...... Anwar kana so asanya ni a labarai ko?
Yayi murmushi to muje ShopRite nasan kinfi son can.
Ki bari anjima Zan baki labarin abinda ya faru ranar da na ganki a ShopRite din na buya.... Ta zaro ido ka ganni?
Yayi dariya eh,
Fada mun Yanzu,
Ki Bari sai nazo,
Yanzu nake so .
Yayi murmushi. Kin tuna ranar da Kika tarar da securities a bakin kofa kikayi ta fada a Baki

wuri??
Ta zaro ido ba munyi waya lokacin ba, Ina kallon ki ai nine a wurin..... Innalillahi.
Ranar ne na biyoki har gida naga address dinki.... Na shiga uku.
Kin fita uku....ya fada Yana dariya.
Yau Zan baki labarai kala kala idan nazo kinji ko?
Tohm, ta fada a hankali.
Sai nazo ko?
Okay.
Ta latse.....
Daddy bai Sami damar shiga gida ba sai biyar saura.
Suna falon sama ita da mommy ya shigo... Ta Mike daddy oyoyo... Bilkisu meye kike dahuwa Kuma naji gidan duk ya hargitse da kamshi?
Mommy tayi karaf tana dariya.... Aikin Anwar ne.
Yayi murmushi da alama kin gaji uwaki wurin kula da miji ....... Maganar ta makale. Yayi saurin canza Babi da kallon mommy muje na ganki ya juya zuwa daki.
Suna shiga ta kalleshi har an daura?
Eh, Amma fa sun kawo shawara..
Ta me fa?
Ya zauna Baki gado, sun ce a sanar da Bilkisun Kuma I reason with them, kin ga yarinya ce karama kada ta je tana janyo ma kanta bala'i ba tare da tasan akwai sharadin Aure a kanta ba Kinga mu Allah zai Kama da laifin rashin sanar da ita tunda Bata sani ba..... Zata firgice gara ayi shiru.
Ba wani firgici kar ki nuna kin sani Ni Zan Mata magana da kaina.... Me zai hana ka mayar da ita nan gwagwalada ta karasa ..... Biyota zaiyi, wallahi Anwar bazai yarda ba.
Shikenan, Yanzu goben zamu tafi sokoton?
Eh, ke zakiyi gaba Zan biyoki bayan kwana biyu tare da Bilkisun.
Shikenan Allah ya tabbatar Mana da alkhairi......ammeeenn.
Bisa bike yazo yau, karar yasa ta fito da sauri ta leka ta taga daidai Yana cire helmet.
Kananan Kaya ne jikin sa, ya ajiye helmet din ya saka facing cap.... Mommy zo kiga Anwar yau a bike yazo.... Ta yi murmushi, daga race ya wuto nan din ko?
Race Kuma?
Eh, kin manta da marece idan mun fita muna haduwa dasu da yawa yaran ministers, president da su Anwar din?
Wai sune?, Hada Shi kenan?.... Gashi Kinga alama.!.
Zata Kara magana ta ce kije tun kafin ya nemeki ta Haye sama abinta.
Yana tsaye bakin kofar ta karaso, bazaka shigo daga ciki ba kayi tsaye?
Ta juya ciki ya biyo bayanta kin yi wa mommy magana Zan daukeki muje yawo?
Ta mishi banza har suka zauna bisa dining.
Kinji?
Ta ce a'a bazamu fita mu biyu ba..... Saboda kada na gudu dake?
Ta Dan kalleshi, Yanzu fa wannan maganar na iya haddasa matsala...kinji?
Kaci abincin Mana..... Ya janyo plate gabansa zanci amma kibani amsa.
Tayi shiru,

Ko na tamabayeta da kaina?
Ta kalleshi da sauri, yayi murmushi Allah kuwa.... Ya kamata kana da kawaici fa.... Akanki fa bani da Shi gara ma ki sani....
Zamu je?
Kaiii Wai Kai me yasa ka fiye naci?
Saboda na turo da maganar neman auren ki.
Ka bari sai Nan gaba....
Family na sunji dadin zuwa gidan nan fa, suna ta mun addu'a da murnar na dace da Mata in shaa Allah....
Ta ce hmm.
Yayi dariya Allah kuwa, an karamta su mood din su ya kasa boye hakan Amma sun dawo da wasu Kaya da goro Wai namu ne Haka akeyi?
Kai ni ban sani ba...... Ya kyalkyace da dariya ke wannan kunyar fa dole ki ajiye ta gefe kinji....
Ta galla mishi harara. Ya Kara yin dariya.....wannan hararar bansan lokacin da za a daina ta ba ko kuwa salon kallon love din naki ne Haka...... Sai kawai tayi murmushi tare da doka guntun tsoki....Kai dai ka sani....kema kin sani. Duk sukayi dariya.
Hajiya na son ganinki duk ta rikice na aika Mata da hotunan ki Wai Bata yarda ba zakuyi video call..... Ina ka Sami hotuna na?
A wayar ki na dauka lokacin Dana tafi da ita kin tuna????
Ta galla mishi harara tun lokacin abinda ke ranka kenan???
Ya kyalkyace da dariya meye ke Raina?
Tayi mishi banza.
Ya Dan gyara Zama ya lunkuma yamball baki kin San fa tun ranar da Kika raba kudin da hahilin nan ya baki class zuciyata ta bani na Sami matar Aure....ta Kara galla mishi harara.
Ya yi murmushi me yasa Wai ranar bakiyi gardama ba Kika bani kudin?
Ta ce hmm.
Anya ba tun tsiwar farko kin kamu da so na .....ta dauki robar ruwa ta Mike kawai ya taso bowl din yamball din a hannu da sauri Yana dariya zo ki daukon meat pie din idan kin gaji da table din..... Nima fa nafi son Zama kasa..... Ya zauna bisa carpet ya Mike kafa.
Ta dauko ita ma ta zauna dan nesa dashi kadan suna kallon juna.... Ya kalleta yace kamar irin Amarya da angon Nan ko?
Ta galla mishi harara. Yayi murmushi, Dan matso Nan kin mun nisa gaskiya... Ta Dan matsa kadan kada taja kuma ya kamota.
Ina son wannan rigar ina Kika siye ta?
Mommy ta siyo mun Dubai...okkay.
Me yasa bazakiyi mun kwalliya da wadanda na kawo Miki ba ko kina Jin kunya?
Tayi murmushi kawai.
Dan Allah ki saka,
Waye telan ki?
Mace ce,can cikin Area 8 ne shagon yake.
Ki debo kayan da Zaki Kai dinki gobe idan mun fita mu biya kinji ko?.....
Nifa bazan bika ba..
Ya kalleta dalili??

Tayi shiru.
Kina Jin nauyin tambayar mommy ko?
Tayi shiru.
Shikenan, Yanzu Zaki iya magana da Hajiya?
Ta danyi kasa da Kai tana murmushi nidai ka jira ba yau ba...
Ya kura Mata ido Anya ba sauri zanyi a daura Mana Aure ba?
Ta dago da karfi... Ya maida bayansa jikin kujera ya Dan kwanta.... Yes, saboda kunyarki tayi yawa gaskiya gara kawai na kawar da ita da wuri don Zaki ringa takurani.
Yar tsiwar ma an daina mun sai uwar harara .......Kai zaka karasa mun karatun?
Waya fada miki Aure na Hana karatu?
Ta harareshi Yanzu ma kana neman kisan Kai Ina ga da Aure Kuma???
Yayi murmushi ko Yanzu ma nikaf Zan siya Miki masu yawa ba shegen da zai Kuma ganin wannan beauty face din ba.... Ta zaro ido nikaf?????
Kwarai kuwa.
Ta zumburo Baki...
Ya danyi dariya ya tashi zaune ko kin fi son kullum ana tashin hankali????
Tayi shiru yaga kamar ranta ya baci.
Ya Kira sunanta a hankali..... Kinji haushi ko?
Ai wannan tsananin ke bana so, kana abu kamar Wanda bai yarda Dani ba kullum...
Yayi murmushi, wallahi na yarda dake.... To me yasa kake da takura?
Saboda *Ina son ki*
Ta kalleshi da sauri.. watau duk lokacin da yake cewa saboda ..yayi shiru abinda baya son fada kenan?
Kin gane ai Yanzu ko?
Ta Dan harareshi kawai. Ya kyalkyace da dariya yace *Bilkisu H. Bushara*........ Ta Kara galla mishi harara.
Sai goma da Rabi yabar gidan.
Tana shiga ta tarar da daddy falon Yana kallon News.
Ta wuce sum, sum, sum..... Zo nan Bilkisu.
Cikin Jin kunya ta karaso ta zauna kasa kusa da kafafun sa.
Anwar din ya tafi?
Eh,
Da alama zaiyi kula sosai ko?
Tayi shiru tana sunne Kai.
Sai dai Shi din ya fiye damuwa ko?
Ta Kara yin shiru tana murmushi.
Ya Aiko da iyayensa kamar yanda na umurta hakan ya nuna tabbas sonki yakeyi da gaskiya.
Amma kina ganin zaman ku makaranta Yanzu a Haka bazai takura ki ba yayi affecting karatun ki ba Bilkisu?
Nima Ina tunanin haka daddy, saboda Yana da rigima sosai..... Na sani.
Ko muyi wata shawara nida ke bazaki fadawa mommy ba?
Eh, daddy. Ta fada da sauri.
Kinga tashin hankalin baya shakkar kowa kada yaje wata Rana ba fata akeyi ba yayi aika

aika.....ko ?
Ta daga Kai.
Ko in sa iyayensa su dawo na daura Miki Aure dashi cikin sirri ba tare da ya sani ba?
Ta zaro ido cikin firgici zatayi magana yace jira kiji dabarata.......
Bazamu yarda ya sani ba, dalili kuwa shine irin damukar da yake Miki tabbas Yanzu zai Kara sake salo Kinga hakan akwai haramci Amma idan akwai Aure ko hannun ki ya taba ga Allah babu laifi iyaka kici gaba da nuna mishi Baki so har a Samu ku Gama... Kin gane ai ko?
Ta daga Kai.
Koda wasa kada ki fadawa kowa kinji ko?
Ta ce toh, Yanzu mubi wannan shawarar tayi ko?
Ta daga Kai yawwa,to ungo ya Mika Mata kudi...sadakin ki ne dazun kafin su tafi an riga an daura Miki...... Kudin suka Fadi sai kyarma kyaf,kyaf,kyaf..... Ya Bata labarin duk yanda akayi sannan yaci gaba da lallashinta har ta daina zubda hawaye.
Amatsayin sa na uba na gari ya fada Mata sharuddan Aure don ta kiyaye.........
Tana shiga daki ta fada Kan gado ta rushe da wani irin Kuka Mai tsima Rai.
Anwar kuwa na shawo kwana ya haska sadeeq can nesa bisa wani dakali da alama waya ce yakeyi.
Ko gida bai shiga ba masu gadi suka bude gate da sauri securities suka fito....
Ya sauka yace su shiga dashi ciki ya koma Yana sando a hankali ya nufi gurin da ya hasko sadeeq....
Zaune yake ya bada baya Yana waya.
Ya daga hannu zai bashi tsoro sai kawai yaji Yana cewa...... Wallahi tallahi baba an daura mishi Aure yau.. ya koma ya tsaya tare da rungume hannu.
.... Hajiya ke fada mun Amma basa son Anwar din ya sani..... Gabansa ya bada dammmmm.... Yaci gaba da cewa, wallahi kudin neman aure suka Kai shine mahaifin yarinyar kawai yace sun Isa shaida Aure aka daura... Wallahi kuwa.
Amin amin...
Eh, bana tunanin yarinyar ta sani gaskiya.
A yanda aka ce mahaifin yarinyar ne yace lallai sai an daura auren saboda rawar Kan Anwar yayi yawa..... Eh sai dai mun dawo din. Amma Dan Allah baba kada ka fada ma kowa babu Wanda yasan hakan.
Amin ya Rabbi.
Ya Mike ....juyowar da zaiyi suka hada ido da Anwar din cikin want irin yanayi ya razana ya firgita yayi baya da sauri ..........😄✍🏼

*MAMAN ABDALLAH* 💖💖💖

Assalamu alaikum. Ina Kara godiya ga masoya, Kuma Ina Kara bada hakuri Dan Allah masu kirana a waya a ringa mun chat saboda Kiran Yana hanani typing da wasu ayyuka. Duk wacce ta Aiko da sako Zan gani Zan kuma bada amsa ko amun voice idan bayanin nada tsawo Zan tura Mata hotunan magungunan da bayanan su.
Na gode Ina maku fatan alkhairi.👍🏼

Alawiyya🗣🗣🗣 Aiko da 24 yau an Sami daya as usual😄😄🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️ *Uwa Mai bada mama, I love you Mom ( Maryam adamu tikau maman amannas)*
[3/24, 2:11 PM] +234 813 598 0214: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
2️⃣4️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

👉🏽💞💕💕 *RUKAYYA BAKO DAN BATTA I love you so much, remember this always*🥰😍😘.

****************
*KADUNA RIGASA*

Wannan doka da tsari ya Kara taimaka wa zaman su sosai da sosai, gidan ya zauna qalau ba sauran tashin hankali idan Yana gari ko wace zata kama tsaginta har ya gama kwanakin sa ya koma sannan zasu ci gaba da ziyarar juna, Koda yaushe Ummi na sashen Amira musamman da ta Fara laulayi...........

***************
*ABUJA NIGERIA*

...... Juyowar da zaiyi suka hada ido da Anwar din cikin wani irin yanayi.....ya razana ya firgita, sannan yayi baya da sauri tare da fadin *You scared me*...... Meye naji kana fada?....idanun sa sun kada sunyi jawur kamar garwashin wuta..... Ya daka mishi tsawa nace meye naji kana fada??????
Look please understand...... Ya shako wuyan rigarsa Kai munafuki na ne ba Amini ba sadeeq?????
Ya girgiza Shi ya tura baya da karfi... Yayi taga taga zai Fadi.... *What the hell are you doing*..... Shima ya daka mishi tsawa.... Sai kawai ya dafe Kai ya duke wurin Yana fadin *Innalillahi wa'inna ilaihi raji'un*..... Hankalin sadeeq ya tashi ya kamo sa Anwar please.... Ya ingije Shi.. kyaleni sadeeq...kyaleni bana so... Zan maka bayani Anwar please calm down..ya Mike a hargitse ni za'a daura ma Aure ba tare da na sani ba??? Ya nuna kirjinsa Yana zaro mishi idanu.... Please.... Ya tura Shi baya I don't want to hear it..... Ya yi gida da gudu... Shima ya rufa mishi baya ya biyo shi....tare suka shiga daki Yana kokarin turo kofa ya rufe sadeeq din ya banka da karfi .... *Get out*.... Ya daka mishi tsawa... Ya maida kofar ya rufe , mutanen gida kowa ya fito yayi jugun , jigumm ......

Cikin bacin Rai sadeeq din ya Fara magana; Kana ganin laifi nane??
Ko kana tunanin Ina da laifi ko hannu aciki????....... Ya akayi ka sani ni ban sani ba???
Sadeeq wane laifi nayi da za a dauran Aure ba tare da na sani ba??
Ya bude fridge ya dauko ruwa Mai sanyi ya Mika mishi a cup ungo kasha let's talk peacefully please..... Bana Sha ka fada mun waye ya dauran Aure Kuma meye hujja???
Ita Bilkisun ta sani???? Ya Kara zaro mishi idanu...
Daddyn Bilkisu ya ce a daura.... Dalili????? Ya Kara tsareshi da ido....
Wallahi itama Bilkisun bata da masaniya, Kai waye ya fada ma???
Ban sani ba ya daka mishi tsawa..... Ya Mike tsaye bari kaji Anwar bana tsoron ka bana shakkar ka, ka saurara Zan fada ma abinda na sani akan wannan daurin auren idan kaga dama ka yarda idan Kuma ka ga dama ka Sanya a daureni sannan kaje ka dauki duk matakin da ka dauka...... Ya kura mishi ido, yau sadeeq ke mishi tsawa haka?
Lokacin da aka Kai kayan daddyn nasu ne yace a daura Aure saboda yanayin rawar kanka musamman yanda kake kakkama mishi 'ya.... Ko kasan cewa ya bada labarin duk bidirin da akeyi school???? Musamman Yana da wadanda suke bin yarsa suna monitoring?? Kasan gidan akwai CCTV wacce yake ganin duk zancen da kakeyi da Bilkisu???? Kaga laifin sa don ya kubutar daku daga halaka?
Muharramar ka ce da zaka na irin wadannan abubuwan?
To Alhaji Hassan ya sanar dani dalili kuwa saboda sun san nine shakikin ka ni kuma na shaida wa mahaifina akara samun shedu kasan duk duniya maganar nan bazata taba fita ba daga bakunan mu bacin da ka jiye ma kunnen ka.
...... Ya juya zai bar dakin cikin bacin Rai Anwar din ya riko hannun sa da da sauri, sadeeq din yace good cikin zuciya saboda yayi hargagin ne don ya nutsar dashi.
Ya dawo dashi a hankali duk jikin sa ya mutu ya ce zo zauna sadeeq.... Bazan zauna ba Ina ce ni munafukin ka ne ba Amini ba ..... Kayi hakuri I regret it.... Kayi hakuri.... Shima sadeeq din duk jikin sa yayi sanyi ya dawo ya zauna.
Sadeeq meye shawara?
Ya kalleshi kamar zaiyi kuka.... Kayi hakuri Anwar I know how you feel about this...... Forget about my feelings please what shall I do????
Shawara daya ce Anwar pretend as you don't know. Ka nuna Sam baka sani ba..... Zanyi haka saboda Zan tayar ma Bilkisu da hankali.... Ai anyi shawarar ita a sanar da ita saboda ta kiyaye sharuddan Aure...... Ya dafe Kai tare da runtse ido to ni me yasa basa so na sani?????? ...... Saboda rawar kanka. Sadeeq ya fada Kai tsaye..... Zan basu mamaki sadeeq.... Wallahi Zan nuna masu how true I love 'yarsu........ Alhamdulillah sadeeq ya fada tare da janyo Shi ya rungume Shi..... Anwar wannan ba karamin gata akayi maku ba wallahi hakan da akayi ya faranta zukatan dangin ka..... Ina ka taba ganin anyi Haka? Ka tabbatar gida kamar na su Bilkisu ba za su taba hakan don kwadayi ..... Mtseww please I don't suspect that.
Ya tashi zaune sadeeq an dauran Aure da Bilkisu?????
Ya kara runtse ido yayi baya ya kwanta bisa gado har lokacin bai bude ido ba.... Sadeeq Ina son Bilkisu, wallahi duk abinda nakeyi ina sane am just testing her , Ina jaraba ta ne sadeeq Kuma yarinyar taci jarabawa ta, tana Sona sosai I knew it amma kullum tana kokari ta danne don ta tsira da mutuncin ta Ina son Mata Mai Hali irin nata *she's exactly the wife am praying for*........ Ka Basu mamaki Anwar..... Ya bude ido ya dago da sauri..... *I will* wallahi zasu Sha mamaki

*trust me*
...... *How I wish ita ma su Kyaleta bazasu fada Mata ba?*
No, is better su fada Mata Anwar kasan Mata da wauta....... Yes ni Kuma ga kishi.... Duk sukayi dariya... Ya Mike tsaye ya buga wata Kara... Wuuuu *Mrs Bushara* wawwwwww!
Sadeeq ya bishi da dariya.
Ko su Hajiya baza su san na sani ba. Sadeeq Zan ba guys din nan mamaki..... Dan ubanka su daddyn ne guys.... Duk suka kwashe da dariya sadeeq yace *Yaro da kudi*...... Ya Kara sa da *Abokin tafiyar manya* suka tafa.
Ya zuki iska ya hurar *Honestly I can't believe we are now husband and wife*..... Kai zanje na kwanta I'm feeling sleepy. Sadeeq ya fada tare da mikewa..... Sadeeq Ina zamu je hado lefe? Ya banka mishi harara sai Corona tayi sauki Dan ubanka....... Ya kyalkyace da dariya, Shi Kuma ya fice yaja mishi kofa.
Ya fada bisa gado..... Wai ni nake da rawar Kai, zasu karyata hakan da kansu lallai Basu San waye *Bushara* ba.
Ya dauko waya lemme call her idan sun fada Mata nasan she's awake now, idan Kuma basu fada ba tayi barci....
Taci kuka har ta bani tayi lamoo bisa gado, wayar ta Fara Kara a hankali...... Kamar kada ta dauka sai Kuma ta tuna da nasihar daddy cewar Yanzu duk abinda tayi mishi na rashin Jin dadi Allah zaiyi fushi da ita.
Hello.... Ta fada cikin dusasshiyar muryar da Tasha kuka...... *What are you crying for?*....... Gabanta yayi mummunan faduwa Taya akayi yasan kuka tayi?
Um? Ya Kara fada.
Tayi shiru kwallan suka shatato Mata.
Bilkisu? Ya kirata a hankali.
Gabanta ya Kara faduwa tsoron ta daya Anwar ya San ita matar sa Yanzu tasan kawai *Ta mutu* Yanzu ma ya ta Kare dashi bare yasan matar sa ce....... Bazakiyi magana ba?
Ba komi, ta fada a hankali.
*Is that because you missed me?*
Ta buga tsoki..... Ya kyalkyace da dariya to kukan na meye daddy ya dake ki?
Tayi shiru,
Ki jirani karfe takwas da safe Zan zo inji dalilin.....
Ba sai ka zo ba....
Ta fada kamar zata Kara rushewa da kuka.
Saboda me?
Huh?,
Sai da safe Ina son nayi barci.... Karya kikeyi ba Zaki iya barci ba yau..... Gabanta ya fadi.
Bazan iya barci yau ba?
Eh,
Me yasa?
Saboda na tafi na barki.... Ta buga tsoki ya kyalkyace da dariya.
Kilibabba Allah ya kamaki Ashe kullum nabarki sai kinyi kuka ko?
Wallahi a'a .
To kukan meye kikeyi?

Ba komai.
Na Jin dadi kenan?
Eh. Ta fada cikin tsawa ya Kara dariya..... Ko dai ni nayi laifin?
Ta ce hmmm,
Ya lumshe ido, kiyi hakuri toh.
Tayi shiru....
Kinji?
Um,
Ba um Zaki ce ba toh ake cewa, ko inzo nan mu kwana....... Kamm, ta fada tare da latse wayar..... Ya Kama kyalkyatar dariya Yana mirgina bisa gado, dukkan su babu Wanda ya samu yayi barci, Shi Murna ita zullumi.

Yana gama sallar asubah barci Mai bauyi ya daukeshi, sai Sha biyu ya tashi,

Ita kuwa ta tashi idanu kumbure saboda kuka, karfe Sha daya mommy ta tafi airport, daddy Kuma ya na gida saboda hutun Corona virus.

Karfe biyu ya karaso, Rahina ta shigo Aunty ga Uncle Anwar....... Gabanta ya Fadi.

Daman tayi wanka ta Dan gyara fuskar ta har lokacin ana gane tayi kuka.

Yauma da kananan kaya, ya mayar da facing cap din gefe ya rufe idanun sa da bakin goggle.

Jiki ba kwari ta shigo ya kura Mata ido har ta zauna sai kawai ta bashi tausayi.
Ina kwana...... Wuni dai ko?
Yanzu Kika tashi barci ne?
Yana maganar a dake,
Tayi shiru.
Kin dafa mun abinci?
Ta girgiza Kai,
Saboda me?
Yanzu meye zanci toh?
Tayi shiru,
Ke me Kika ci?
Nan ma tayi shiru.
Jeki kawo mun abinda Zan karya..... Ta Mike sim sim....ya bita da kallo.
Ya zuki iska ya fesar tare da Dan zamewa ya kwantar da bayansa a kujera.
Wayoyi kawai yake amsawa har ta shigo da tray a hannu.....kawo nan bazan hau ba table ba....
Okay Zan Kira anjima kaci gaba da lissafi ka turon brake down...
Ya ajiye wayar Yana Mai saukowa bisa carpet.
Indomie da kwai ta kawo mishi da oat.

Ya hada oat din da kansa ya cika Madara yasa sugar kadan ya tura Mata bowl din wallahi tallahi sai kin shanye duka ni zanci indomie din....... Ya Sha mur,.
Zatayi magana ya harareta Zan hada Miki da indomie din Kuma itama nayi rantsuwa... Ai yamun yawa... Ba abinda ya dameni ko zakiyi amai sai kin shanye.

Yaci gaba da cin indomie din yanayi Yana satar kallonta, tana tsakura, tana tsakura har ta daga bowl din ta kafa Kai.... Da kyar ta shanye.

Ya mike zanje Kano anjima sai next week Zan dawo kinji ko?
Toh,

Ya kalleta kinyi zaune ba rakiya ko cikin ya cika da yawa?... Ya karasa maganar Yana dariya..... Ta banka mishi harara ta mike.
Yana tafiya ta koma daki, ashe hada yunwa ta hanata barci ko mintuna 3 batayi ba barcin yayi awon gaba da ita.
....... Kwana biyu ta warware, kullum basa yin waya sai cikin dare.
Hankalinta ya Fara kwanciya saboda sam da alama bai San an daura masu auren ba.
Hajiya ta kasa boye farin cikin ta Koda yaushe maganar ta Bilkisu.....
Ja'iri ashe mace kabi Shi yasa ka dage Kai anan zakayi karatu.... Ya yi dariya Wai waye ya fada miki mace nabi?
Coincidence ne ya hada mu, amma ni ba ita nabi ba.....yaki nuna ma kowa yasan wainar da ake toyawa.
Har suka je sokoto suka dawo bai nemeta a waya ba. Hakan ya Bata mamaki, ta Fara tunani ko daman rashin sanin inda alakar su ta dosa yasa yake yawan takura Mata Yanzu da ya tabbatar magana taje ga iyaye yasa ya Sami natsuwa?.
Har iyayen nata sai da suka fahimci hakan.
Shi kuwa yayi amfani da wannan Dan hutun ya Fara zirga zirgan nemar Mata transfer zuwa University of Abuja. Ko sadeeq bai fadawa ba yasa aka had a mishi transcript dinta cikin sati biyu ya kammala komai. Hatta kayan ta kafff yasa an balle dakin an kwashe sannan ya gyra kofar ya rufe.
Yana jira akoma ya Mata registration......
Ranar da aka koma, ya aika da komai washe gari yazo da takardun gidan su.
Tana ta shiryen komawa, bai Mata waya zai zo ba sai dai suka ganshi kwatsam, ta gama kulewa fushi sosai takeyi dashi saboda kusan sati daya kenan basuyi waya ba.
Yanayinta kawai ya kalla yasan fushi takeyi.
Yana zaune bisa hannun kujera alamar kamar sauri sauri yakeyi, ta Kara daure fuska..... Wai fushin na menene?
Ta mishi banza.
Yayi Yar dariya, kiyi hakuri abubuwa sun mun yawa ne, bana zaune..... Kuma shine baka da lokacin kirana???
Ya Dan yi murmushi to ke ba sai ki Kira ba?
Ko laifi ne Mata ta Kira mijinta..........dammmm gabanta ya Fadi ta kalleshi da sauri yayi murmushi yes tunda na Aiko gidan ku ai kin Zama matata ko wani ya Isa ya shigo Yanzu neman aurenki?
Ta Dan saki ajiyar zuciya, ya kusa sakin dariya..... Nayi missing dinki sosai Bilkisu, Ina ma ciki amma nasan komai na Dan lokaci ne daga ranar da aka mikon ke nasan komai ya Zama labari....... Gobe Zan koma school. Ta fada a hankali.
Keda waye Zaki koma?
Ban sani ba daddy yace na Fara sanar dakai tukun.
Da banzo yau Kuma fa?
Zan maka text.
Saboda me bakya son kirana?
Tayi shiru,
Ya kamata ki rage kunyar nan fa.

Tunda na Aiko gidan nan Bilkisu duk kin canza kinyi sukuku Anya kina Sona?
Ko baki son kiyi rayuwa Dani?
Baki magana?
Kina damuwa ne akan rabuwa dasu mommy??...... Sai kwallah suka zubo mata sharrrr...... Ya Salam ya tashi yaso gabanta , tunanin ta zai kamata kamar yanda ya Saba sai taga ya zauna gabanta ya harde kafa.......

Kinga ki kwantar da hankalinki wallahi Bilkisu bazakiyi dana sanin Aure na ba, bazan taba Bari ki tozarta ba.

Ke shaida ce, duk kudi na da commitment nawa bai hana na baki time din kanki ba, Ina son kula Shi yasa Nima nake kulawa dake, Ina son ki fiye da dukiya ta, wallahi tallahi ko Yanzu da Kika ga na Dan kaurace Miki I wanted to prove your parents how good I am, and how I truly loved you.

Kin San cewar nasan an daura Mana Aure?........ Ta Mike tsaye ta zaro ido, ya Kara Yar dariya yes I knew it and I promised my self I'll never touch you again, tunda an ce *Ina da rawar Kai* Ta Kara kallon sa da sauri, ya Kara dariya.

Ya Mika Mata takarda ga Shi gobe gobe Zaki je kiga registration officer na nan University of Abuja akwai abinda Zaki karasa, ta Kara zaro ido.

Me kake nufi?

Ya Dan Sha mur, Ina nufin na mayar da ke can anan Zaki gama.... Kai kuma fa?

Ni Zan karasa a dutsinma..... Wallahi ban yarda ba ta Mike tsaye.... Shima ya Mike, wannan shine umurnin da na Baki Kuma abinda na zartar a matsayina na mijinki....... Akan meye zakayi haka?

Saboda na nunawa kowa cewar ba sha'awar ki nake ba sonki nakeyi saboda Allah......Anwar.... Bilkisu kada Kija maganar nan, kada kuma ki sanar wa iyayen ki cewar nasan an daura Mana Aure kawai Ina son ke ki amince da *Ni Anwar son da nake Miki na Aure ne ba na sha'awa ba*............😄✍🏼

*Zainab wowo maman Abdallah*💖
Masu kirana waya kuyi hakuri ku aiko da sako ta whatsapp👏🏼👏🏼👏🏼
[3/24, 8:50 PM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐

25

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

👉🏼💞💕💕 *RUKAYYA BAKO DAN BATTA I love you so much, remember this always*🥰😍😘.

******************

*ABUJA NIGERIA*

.... Na rantse da Allah ban aminta ba, sai dai kaima ka dawo nan mu gama tare .... What do you take me for?

Bilkisu...... Da su mufeeda a school Zan Barka acan bana nan?.... Ya zaro ido...

Ta rike kugu billahil azim tare zamu koma FUDMA.... Abinda nake so ki fahimta..... I'll never understand you, amma ka mayar dani shashasha.... Wallahi bazan aminta ba,

Ya harde hannuwa a kirji ji yakeyi kamar ya kamota ya rungume....

Ta banka mishi harara, yanda kake da kishi nima haka nake dashi, dole ka zaba ko nan ko dutsinma Amma kafa ta kafarka....... Ya kyalkyace da dariya...

Ikon Allah Bilkisu ta dawo..... Ta banka mishi harara, Shi yasa ka daina kula ni ka kaurace mun?

Kana son proving meye?, Wannan ne prove? Ai prove shine gani ga ka ba Ina can kana can ba..... Naji maida wukar yanzu zauna ya kike so madam.....

Ta galla mishi harara kaje ka yo cancelling din komai mu koma FUDMA.... Ya maganar Sanya nikaf???? Wannan ce damuwar ka?

Zan saka...... Ya kura mata ido.... Sai Kuma kunya ta kamata ta sunkuyar da Kai..... Ya yi murmushi yace *Akwai chakwakiya*.......

Tayi shiru..... Watau kina son gani gaki ko?

Ni Zaki kure Bilkisu????

Kome zakace sai dai kace amma wallahi ba school din da zance ba tare da Kai ba, idan Kuma ka dage na rantse da Allah sai dai a warware..... Dal!.. ya buge bakin da yatsa... Mutu ka raba yarinya duk yanda kike so haka zanyi what next?

Ta zumbure baki shikenan....

Yayi murmushi yace *nawaoooo*

Har na siya Miki mota wallahi gata can awaje don bana son wani driver kawai da akwai masu binki a baya da tsaronki Koda yaushe..... Sai ka koma da abinka su Kuma ka canza masu aiki....

Ya tuntsure da dariya.... Anya Baki fini kishi ba????

Ta Dan harareshi cikin kunya.

Ya Kama dariya, Watau bazaki yarda gani ga mufeeda bakya Nan ba ko?

Ta rufe fuska nidai ya Isa,

Ya Kara dariya anya wannan semester din Babu damuwa????

Ba wata damuwa,

Ba Kya Jin tsoron anything can happen bayan nasan ke matata ce Bilkisu?

Ta harareshi ashe baza ka iya ba daddyn mamaki ba...... Yayi murmushi Zan iya Mana.

To Kuma.

Ya bi ta da kallo, ya zuki iska ya fesar tare da sakin ajiyar zuciya.

Gaskiya rigimar ki tafi tawa... Ta dan harareshi, but I'll try my best ya karasa maganar Yana murmushi.

Ta Dan sunkuyar da Kai, ya Mike Amma bazaki koma gobe ba sai next week ki fadawa daddy Zan Aiko a daukeki Zaki hau private jet na from Abuja direct to katsina zamu tare ki a can kinji ko?

Ta daga Kai kawai.

Yana Isa gida ya tarar da sadeeq a basket ball ground, ya chabe ball din .... Malam ya akayi ? Ya rike kugu,

Wai kasan nayi wa yarinyar nan transfer taki yarda?

Ka mayar da ita Ina?

Wallahi nan Abuja , ya danyi dariya, could you imagine kishi ke damunta??.... Sadeeq ya kyalkyace da dariya na fada ma miskilanci ke hana Bilkisu nuna maka so amma wallahi zaka Sha wahalar ta idan ta goge ...Amma fa ta birgeni.

Kai ta birge ko Ni sadeeq kasan dai akwai rigima ko?

Babba ma kuwa suka kyalkyace da dariya tare da tafawa.

Ya wurga mishi ball din suka Fara bugawa cikin nishadi.

Yanzu ya zakayi kenan?

Zan siyi gidan nan Wanda naga angama sabo na darawa ko nawane yayi Masa kudin bala'i Zan biya Mata,sai ta zauna ita da Aisha da Maryam Amma banda khausar don bana son yarinyar... Daddy zai yarda?

Dolen sa ma, Zan Sanya Mata masu gadi sosai Nima na siya Mana gida bayan gidan redio zamu bar hostel...... Sadeeq ya buga tsalle amma ka gama birgeni nawan suka tafa suna dariya...

Na Kira VC na fada mishi ayi meeting wallahi duk lecturer din da ya Kara Kira mun Mata Zan daure Shi..... Sadeeq ya zaro ido ai FUDMA sun gama shiga uku Yanzu...... Suleiman Kuma na mishi text na fada mishi na auri Bilkisu kallonta idan yayi ya gama Jin dadi har abada don zai Kare rayuwar sa a prison..... Anwar kada ka firgita makarantar can.... Yayi dariya kawai.

Da mota zamu koma yanzu?

Ya kyalkyace da dariya Kai mota ce dakuwar ka Wai?

To motoci ba mota ba, Zan fito musu a mutum sak!

Nawaoooo... Sadeeq ya fada.

Bilkisu kuwa, Miskilancin ta da zurfin ciki ya hana ta fada wa mommy abinda ya faru ba.

Haka suka taru sukayi Mata nasiha cikin hikima na duk darasin maganar bai wuce ta kiyaye tarayya da shi Kuma ta kula.

*******************

*Federal University dutsinma*

Aisha da Maryam abun ya daure musu Kai, gidan tsoro ma yake Basu, har basa son fita saboda kattin da gewaye da gidan, komai an saka gida abinda ke gida ga masu aikin abinci da gyaran gida.....

Da yake sun rigata komawa da kwana biyu shine yakai su ya masu bayanin anan zasu zauna tare da Bilkisu ranar duk da suka gayyato wata kawa ko namiji wallahi sai yayi maganin su.... Su Kam sunyi tsuru tsuru gashi har yau basuyi waya da Bilkisu ba.

Misalain karfe shidda na marece jirgin ya ajiyeta motoci hudu an musu layi Yana tsaye ya goya hannu a kirji ta Fara saukowa da zumbuleliyar hijab har kasa ya kura Mata ido tun kafin ta karaso ya bude Mata kofa....

Tana shiga ya shiga suka rufe kofa aka fizgesu sai dutsinma.....

Ya kalleta ba gaisuwa hajia?
Ta danyi murmushi,
Kin gaji ko?
Ta ce hmm kawai,
Ya makarantar?
Ta tambayeshi tana kallon fuskar Wayarta,
Lafiya Lau, Amma fa ban shiga ba har yau sai gobe nima Zan Fara zuwa lecture... Ta Dan kalleshi saboda me?
Ya Dan yamutsa fuska haka kawai.... Sai tayi dariya.
Dariyar me kikeyi?
Naga kana mun karairaya kamar mace... Ya kyalkyace da dariya Wai Ina son in birgeki.... Ta dalla mishi harara.... Ya Kara dariya.
Su Aisha sun kagara ki dawo...
Kai meye hadin ka da Aisha???.... Ya zaro ido ya watsa hannuwa ba komai fa....
Sai tayi murmushi,
Anya Bilkisu???, Ya leka fuskar ta.
Ta rufe tana Yar dariya.
Kin iya mota?
Um.
Good, to na ajiye Miki tana nan, zaku zauna keda su Maryam, nima nabar hostel muna bayan gidan redio nida sadeeq, idan daddy ya Miki magana kice ninayi Haka, akwai masu gadi da ma'aikata Amma fa ki sani idan zakiyi mun abinci kada kisa kowa naki nake so kin gane ko?
Ta mishi banza.
Ko bakiji ba?
Karatu nazo ko girki?
Komai ma kinzo yi, kin sani cewa akwai Aure na akanki ko?
Gabanta ya bada ras!
A bakin gate ya fita yabar su suka shiga gidan driver ya fito yabar Mata motar tare da Mika Mata key, ta zaro ido Wai wannan motar ce tawa?
Ya sunya eh Hajia, ta amsa kawai tayi ciki..... Su Aisha suka kwaso da gudu tana ganin su ta fasa ihu itama sukayi ciki suna Murna.........Suka tsareta da tambaya Wai ya Haka?
Ta fada masu ya tura iyayen sa neman Aure Bata sanar dasu akwai Aure akanta ba.
Mufeeda kuwa hauka kadai ke batayi ba da taji Anwar ya siya ma Bilkisu gida ba.
Zuwanta biyu Amma ko layin gidan Bata iya kaiwa saboda body guard, shima ta gano nashi gidan cikin Daren Nan ma securities ne gewaye unguwar.....

Ta dunga kunduma ashar tare da Shan alwashin gobe sai ta ji dalili.
Bakwai suke da lecture ta munafuki Richard, akayi sa'a Aisha ma nada 7am
Suka fito abin mamaki har an goge motar...
Ta kalli Aisha wallahi kunyar hawan motar Nan nakeji Aisha..... Meye na kunya?
Kuma ba ga nikaf kin saka ba?
Kai nasan yau na gama shiga uku makarantar Nan..... Ke muje ni ki ajiye ni kada na makara ta bude motar ta shiga ... Ko Zaki ja mu....??? .... Ni??? Ta daki kirji.

Anwar yau ya mayar dani kauyen mu kike so ko?
Ba yanda ta iya dole ta shiga tare da bata wuta suma suka tayar da mota suna jiran ta fita su bita ( securities biyu ),, ta fita gate din a hankali tana Hawa titi ta chilla da gudu saboda sun kusa makara. Suma suka rufa Mata baya.
Duk da safiya ce duk tsiraren mutanen da wuce sai sunbi motar da kallo.....
Kai Anwar karshe ne, shida sadeeq kasa suka tako, a bakin gate ta wuce su, ya kyalkyace da dariya Sadeeq yarinyar can gudu take da mota fa...
Dan ubanka mu ba ka hana mu dauko ba?
Ya Kara dariya suna ta sauri....
Ta tsaya Aisha ta sauka saboda ba hanyar su daya ba ita ciki zataje Aisha Kuma nan farko farko.
Tana zuwa kowa yayo ma motar chaaaaaa..... Chinayye ta gane ta da gudu ta makale tana fadin Bilkisu oyoyo.....
Ya akayi Kika ganeni?
Ta fada a hankali , haba ya bazan gane ki ba?
Wai kinyi Aure?
Inji waye?
Eh Mana ance you are married woman now....no, not yet. But am engaged... With Anwar??....
Shigowar sa yasa ta Kyaleta, ya rufe idanun sa da facing cap abin mamaki kawai ya wuce baya yaki Zama kusa da ita.
Suleiman ya shigo sai kawai ya chanza layi ya koma can baya saitin Anwar din.
Sai mazurai yakeyi cikin facing cap.
Mugun na shigowa sai cewa yayi test... Hankalin kowa ya tashi, ko ajikin Anwar,
Nan da Nan Bilkisu ta Fara kyarma.....
Question biyu ce, ba Wanda ya sani Anwar kadai ya amsa da kyar Bilkisu tayi attempting ta biyun sai kuwa su chinayye.
Yana fita ya taso da sauri... Kin amsa?
Ta zumburo Baki Ina na sani?
Bakiyi ba kenan?
To me Zan rubuta?
Ya buga tsoki this man .
Nan da nan Yan class suka Fara kallon kallo.
Shi kuwa Suleiman Richard na fita shima yabar ajin.
Ya zauna bisa table Yana kallonta, budo in Miki bayani ya saboda gaba... Ta Mika mishi book din, duk nikaf din ta ishe ta ba yarda zatayi ne.
Ya Fara Mata bayani a hankali ya lura sai mutsu mutsu takeyi yace Wai ya akayi?
Nikaf din nan ta isheni wallahi Dan Allah in cire?
Ya danyi dariya cire Mana .
Ta kalleshi da sauri da gaske ko gatse?
Sai kawai yasa hannu ya cire mata..... Dai dai shigowar mufeeda.... Ta tabbata wallahi, kutumar uba... Anwar da gaske An daura muku Aure da wannan banzar..... Ji kake tassssssssss! Fassss.....ratssssss duk illahirin hankalinta ya bace ta gigice ta kidime shima ya razana ainun ganin Bilkisu tsaye tana wanka Mata wadannan marukan.............na rantse da Allah Akan

*Anwar Zan iya kisa* don Haka ki kiyaye... Body guards suka gani cirko cirko nan da nan Yan ajin suka fara direwa ta taga saboda firgici.......✍🏼 Ayi hakuri da kadan.

*maman Abdallah*💖

*uwa Mai bada mama mom ( Maryam adamu tikau maman amannas) mom you are the best I love you so much Mom*

Wadanda ke cewa ba ni ke rubutawa ba a fada wa Mai rubutawa ta ci gaba da kokari Nima Zan dage wajen sharing.....😄✍🏼
[3/25, 12:48 PM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
2️⃣6️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

👉🏽💞💕💕 *RUKAYYA BAKO DAN BATTA I love you so much, remember this always*🥰😍😘.

**************

*Federal University dutsinma*

.......Ta shako wuyanta ta buga da table, gyalen ta ya fadi hular gashin da ke kanta itama tayo kasa, wani chukuikuyon kitso ya bayyana ba 'a ko ganin tsagar ga kegen can manne a wuya.....kaiii Bilkisu kina hauka...mAnwar ya fada a firgice..... Ta nuna Shi da hannu daya korar mun wadannan kattin ta kallesu tana zare ido.... *What the hell are you doing here*?????.... Wata Kara mufeeda ta saki ta dago ta da karfi goshinta ya Kara tsawo kamar wani bread da ake Kira danbisije na funtua...
Ya yunkura zai riketa ta Kara buga kanta a table....Zan nakasa ta Anwar wallahi...... Ya daga hannuwa sama okay ..okay... Ya kallesu kuje waje... Kofar class din da bakin tagogi students ne makil ...... Idanun ta sun kada sunyi jawur tana magana tana zare mishi ido...... Kai bazaka iya maganin ta ba ko? Zan ci ubanta yau saboda duk makarantar nan yarinyar nan ta tsone man ido..... Zan yi..wallahi zanyi maganin ta please kada ki janyo mun bala'i kada kiyi kisan Kai Bilkisu.... wannan cin fuskane ki barshi ta mayar da gyalenta please....Ta ingizata da karfi tayi baya ta fada cikin sit bayanta ya daki kujera da karfi ta saki wata Kara.... Yayi wurinta da gudu a firgice...... Tayi tsalle ta dira gabansa kana tabata Ina karairayata....... Chief security suka gani da wasu securities subhanallah meke faruwa anan.... Yana ganin Anwar yace ranka ya dade da kanka???

Dan Allah ku fita da mufeeda kuje da ita.... Magana yakeyi a harmutse duk ya rikice, Bilkisu kuwa ya dake ta Sha mur Kai baka taba cewa ita ce tayi wannan tashin hankalin ba....... Ya kalli security daya je da ita clinic.... Yallabai kuyi hakuri muje office... Ita ce tayi gaba...... Zuciyar ki tayi yawa Bilkisu wannan yarinyar ta wahala me yasa Zaki.... Ta dalla mishi harara , ka Sanya a daureni na daki sahibar ka kasa a kaini prison..... Ohh my God,
Da gudu sadeeq ya dawo cikin makaranta jin wannan mummunan labari,
Abin mamaki Bilkisu ta Sami shaidar lallai mufeeda ce ta Fara tsokanar ta..... Anwar ya shiga ya fita case ya mutu. Suka fito duk ta chukuikuye fuska... Sadeeq yarinyar kaga zata yi kisan Kai ko?
Bilkisu me...... Na rantse da Allah idan ka Kara mun maganar waccen Yar iskar Zan sameta har dakinta na Mata tsinannen duka Wai Anwar kasan Hali na kuwa?
Na sani a yau, na sani wallahi Dan Allah kada ki Kara kula ta zan kawo karshen matsalar..... Kada ma ka kawo zata ci ubanta.... Ya kalli sadeeq duk sukayi murmushi.
Kawo key din na dauko Miki motar sadeeq ku jira anan..... Ya wuce da sauri, sadeeq ya danyi dariya, duk kin hargitsa mun Anwar kin San Shi baya son tashin hankali..... Tunda takai fagen mufeeda ko? Ai Dole ya hargitse, wace irin masifa ce Suleiman ke bai gani ba?
Kasan Allah ka gaya mishi idan bai nesa da mufeeda ba sai na halaka ta...... Itama daga yau Dole ta shiga taitayinta kuma Zan fada mishi.
Ya iso, ganin baida niyyar fitowa yasa ta fada baya ta zauna Dole sadeeq ya shiga gaba.... Suna fita yayi hanyar gidan sa Yana fadin Bari ki Fara ajiye mu tukun ta mishi banza kawai.
Har ciki ya shiga da motar suna tsayawa ta fito ya dan koma gefe ta shiga wani mugun ribos da tayi sai da ta birge duk Wanda ke shiyyar.... Ya bita da murmushi kaiii sadeeq yarinyar can karshe ce..... Suka kyalkyace da dariya Ina so na ce ta dafan abinci amma duk na tsorata da ita.... Sadeeq ya kwashe da dariya Bilkisun kake tsoro????
.... wallahi tsoronta nake sadeeq, ya fada Yana dariya.
Kaga tsawar da ta daka mun Wai na ce su mustapha su fita???
Duk suka Kara kyalkyace da dariya.... sadeeq ya ce ko baba da babansa.
Mufeeda kuka kawai takeyi, ba dukan ya Mata zafi ba, irin yanda ta cire Mata hular gashi ta tozarta ta gaban jama'a..... Ta kasa daina kuka, kunya ta hanata fitowa daga clinic din ta tafi daki.
Hakuri kawai kawayenta ke bata, Asma'u ta ce Ina ga mufeeda ki shafawa kanki lafiya ki kyale Anwar... Wallahi ko Zan rasa rayuwata bazan hakura dashi ba..... Duk suka zaro ido.
Amina ta ce wallahi matar sa da gaske sunyi Aure mufeeda ki fita batun Anwar ki tsira da mutuncin ki nifa nake gane Miki Yanzu irin wannan cin mutuncin keda dadi?
Ta goge kwallan da suka zubo ko Zan kyale Anwar sai na Rama wulakancin da ta mun wallahi bata Sha lale ba..... Ai kuwa next ba ita ce zata nada Miki duka ba wadannan kattin da ke gadin ta..... Ku duk baku San abinda naji ba, wallahi Anwar fa shine *Hamza bushara* ...... Duk suka kwalalo idanu suna kallonta. Da gaske Asma'u?
Tayi murmushi wallahi kuwa, aini tuni na Fara sensing Anwar wani shege ne ko Kuma baban sa ne wani don gadarar gayen tayi yawa ko lecturers Kuna ganin shakkar sa sukeyi..... Mufeeda ta saki wani irin kuka irin shikenan ta shiga uku kawai..... Amina ta dafa kafadarta kiyi hakuri ba class din ki bane Anwar maganar gaskiya sai irin su Bilkisun saboda Kinga babanta wani me itama tsaye take.... Ba wani babanta wallahi ko Yar gidan malam shehu ce tunda Anwar na

sonta shikenan.....Kuma idan Kun tuna zuwanta ance sun Sha fada sosai da ita dashi tun farko ta nuna Bata tsoronsa, ke kuwa mufeeda ke ce Kika bayar da kanki yaushe Zaki ringa bin namiji Kuma guy kamar Anwar kema ai kinsan kin siya ma kanki buhun wulaknci.

Tana kokarin parking Aisha sauko daga napep ta shigo da gudu...... Wai kin daki mufeeda? Ta fada tana shessheka , ta fito motar, ta bi su mustapha ( body guard ) da harara tayi ciki tana fadin Aisha yarinyar nan Bata da tarbiyya Kuma duk laifin Anwar ne...Anwar Kuma? Shi meye nasa aciki?
Ta hayayyako Mata tafi karfinsa ne da bazai ce ta kyalesa ba? Me yasa sauran Yan matansa ke tsoronsa ita kadai ce zakakka????
Amma Yanzu kinji yanda ake Mata Allah ya Kara a school? Wallahi mufeeda ta shiga uku ko kunya ta isheta kinji labarin da ake yi kuwa?... Maryam ta kallesu ya akayi ne? Tana kwance falo suka shigo
Ta cire hijab ta fada bedroom dinta.... Aisha ta zauna...wallahi Bilkisu ta nakada ma mufeeda tsinannen duka har tana cire Mata hular gashi..ta karasa maganar tana kyalkyatar dariya.. Maryam ta tashi zaune bani in Sha.....
Hmm yarinyar nan ta debo ruwan dafa kanta Wai inba ita jakka ba waye zai shiga shirgin Anwar da Bilkisu soyayyar da kowa ji yake da kansa, soyayyar da sukeyi ma juna ta gadara wa ita ta shiga tsakani????
....ta danyi kasa da murya Wai kinsan an daura musu Aure Ashe?
Maryam ta zaro ido.... Tayi saurin Dora yatsa a lebe alamar tayi shiru....
Haba nidai wallahi nayi mamaki abun fa akwai alamar tambaya.... Kuma kin San waye Anwar? Ta zaro ido tana girgiza Kai alamar a'a.... *Hamza bushara*..... Ta kwalalo ido ta dafe kirji..kice wallahi.
Tayi Yar dariya wallahi kuwa ta budo Mata waya duba ki gani... A nuna Mata. Ta Kara zaro ido... Bilkisu ta sani?
Tayi dariya wallahi ta sani yarinyar can hmmm kibar ta kawai..... *Bushara* Maryam ta maimaita... Yanzu Bushara takeyi ma wannan iskancin Aisha..... Aisha ta kama dariya fitowarta yasa duk sukayi shiru....
Ta zauna bisa kujera Maryam kinyi break?
Eh, ta fada a darare....
Aisha tace naji ana Kiran wayar ki kuwa.... Ta janyo jakar sai kawai tayi tsoki ta wurgar.... Bazaki dauka ba?
Kyaleshi Anwar ne..... Maryam ta zaro ido..
Aisha tace me yasa bazaki dauka ba?
Me zance mishi?
Duk wannan hatsaniyar waye ya janyota?...... Meye laifin sa Bilkisu?
Ta Sha mur, Aisha har Yanzu Ina mamakin me yasa yarinyar nan ta kasa rabuwa dashi?
Kina ganin ba laifinsa bane??
Ba laifin sa bane..... Ta Mike tare da buga tsoki tayi kitchen......yunwa nakeji Maryam Ina masu aikin?
Maryam ta kalli Aisha itama ta kalleta Aisha ta kyalkyace da dariya Maryam kuwa kasa darawa tayi. Ta rike Baki *Bushara*..... Kut!
Ya kalli sadeeq nifa wannan fitinar yasa naso na mayar da ita Abuja kaga Yanzu da alama ni

ne nayi laifi.... Sadeeq yayi murmushi ai dole taji haushin ka mufeeda ta kasa kyaleka itama tana nuna bata tsoronka kaga kuwa Bilkisu Dole ta tuhumeka....
... sadeeq ya zanyi da yarinyar Nan? Wulakancin duniya wane ke ban Mata ba?.... Duk da Haka ya kamata kayi wani Abu da zata kyaleka... Kamar ya? Dukanta zanyi?
Zagi na gidan duniya na Mata amma Bata da zuciya domin Allah meye laifina?
Ka barta zuwa anjima kilan ta dauka..... Bilkisun? Tabbb, yarinyar nan wuyar lallashi gareta Yanzu kaga Ni ta janyo mun jidali shegiya.... Sadeeq ya kwashe da dariya....

Soyayyar ku na birgeni nawan.... Ya Kai mishi duka wane birgewa Dan ubanka ana ba juna wahala....Au Ashe Kai ma ka San Haka... Sadeeq ko zaka je ka bata hakuri ?
Eh, Amma Bari ayi sallah tukun.... Wai mu Dan ubanka baka kawo Mana masu girki ba?
... ....... Ba wani Mai girki da Zan kawo, Ni nafi son ta dafa mun.... To ka kirata a waya ko ka Mata text.... Bari dai ta huce.
Ya harareshi to ai kaga irin wannan ranar da aka kafsa fada mune Masha wuya ko?....
Ya Mike Bari na dafa indomie.... Please zanci.... Baka cinta Dan ubanka..ya wuce Yana banka mishi harara.
Sadeeq yasha tsayuwar Shi taki fitowa, inda Allah ya taimakeshi suna da lecture four....... Tana fitowa ta Kira mustapha.. kuyi wa Allah basai Kun bini ba Allah Yana tare Dani, bana bukatar tsaronku don kuwa bana wasa da addu'a...
Ya danyi murmushi toh Hajiya,....tana fita suka rufa Mata baya.....
Yana tsaye bakin kofa, ko kallonsa batayi ba ta wuce tana Zama shima ya zauna.... Ajin yayi tsit kowa ya maida hankalin sa wurin su don kuwa basa gajiya da dramar su. ....
Wai fushin na menene Bilkisu?
Ta harareshi kawai.
Yayi murmushi ke me yasa kin na son dauran laifi babu gaira?...... Au Ashe ma baka da laifi ko? Me yasa har yau mufeeda ta kasa kyaleka, saboda me baka son ta daina kulaka????
Ya daga hannuwa sama na rantse da Allah Ina so ta kyaleni Bilkisu baki ganin irin wulakancin da nake ma yarinyar can Amma taki zuwa???..... Kuma shine ke nuna tafi karfinka?
..... Zaiyi magana malamin ya shigo.....
Ya dauko wayarsa ya rubuta Mata text a WhatsApp...
```kiyi hakuri please```
Ya Dan zunguro ta galla mishi harara ya Mata nuni da baki cewar ta duba Wayarta......
Ta tura mishi da harara....
Ya rubuta ``` please sorry I don't want to see you pissed off```
Taki magana.
Ya Kara rubuta Mata..
```You snubbed your husband?``` tare da imoji na zare ido.
Ta Kara tura mishi harara
``` sai ya tura Mata kuka```
Ta Dan kalleshi ya langwabar da Kai ya rubuta... ``` wallahi Zan yi maganin ta please am sorry```
Ta danyi shiru sai ta rubuta mishi ``` it's okay```
Yayi saurin tura Mata ``` Oya smile na```
```

Ta Dan kalleshi ya sakar Mata murmushi... Sai kawai ta duke tana Yar dariya.

Malamin na fita ya hawo table ya zauna gabanta Yana Yar dariya *Mun shirya ko?*
Ta danyi murmushi.
Sai ki koyan abinda akayi tunda kin Hana ni naji komai... Ta harare Shi Nima halan naji?
Ya kyalkyace da dariya gaskiya wannan semester din akwai damuwa Anya Zaki Bari na ringa ganewa?
Ta Kara mishi harara...
Kun shirya ko? Ni an kyaleni cikin Rana daga Biko ya kalli Anwar Dan ubanka ka Kara Sanya ni cikin shirginku sai naci ubanka..... Tayi kasa da Kai tana murmushi Shi Kuma ya Kama dariya.
Suleiman yazo zai wuce Anwar yayi saurin rikoshi ranka ya dade idan ba hello ai akwai daga hannu ko?
Ya danyi murmushi ya Mika mishi hannu ya kalli Bilkisu, Hajia Allah yasa Allkhairi... Amin
Suleiman Dan Allah ara mana abinda akayi Yanzu idan ka rubuta..... Anwar yayi fit ya fizge littafin ni zaka ba Alhaji ba ita ba.
Yabar masu book din ya wuce Yana Yar dariya....
Anwar kenan, yau kuma Suleiman kakeyi wa magana????
Ya Dan Sosa Kai gayen Yana bani tausayi wallahi duk wulakancin da na mishi a masallaci idan muka fito wallahi sai ya bani hannu.... Ta ce hmmm.
Ya dan harareta ba hakan Yana nufin fa Zaki ringa kulashi ba fa..... Amma ai ma gaisa ko?
Eh, Amma idan kin saka nikaf, Wai yau me ya hana ki Sanya? Ya zaro ido......
Ta langabe Kai kamar zata mishi kuka Anwar Dan Allah ka saukaka mun da nikaf...... Wallahi sai kin saka ya dire Yana masifa...kammm idan Kika Kara fitowa babu nikaf wallahi sai kin koma Koda kuwa za ayi test ko exam..... Shikenan naji ta fada tana zumburo Baki.
Muje ki ajiyeni gida...
Wai Kai duk motocin da na gani gidanku fa.... Yayi murmushi kawai.
Ta haraeshi Wai Kai an fada ma har Yanzu ba'asan waye Kai ba?
Ya watsa hannuwa tare da daga kafada.... Ta danyi dariya tana son wannan move din....
Ungo kaja mu toh,
Yayi gaba abinsa bai ko kalleta ba.......
Ta bude suka shiga ta bata wuta.... Duk aka bisu da ido..... Ba karamin tafiya sukeyi da zukatan dalibai da malamai ba, ya kalleta Yana dariya waya koya Miki mota haka?
Ta mishi banza, ya kwantar da sit ya Dora kafa bisa dash board yayi filo da hannuwansa kinji kunya ta Hana mufeeda shigowa school?
Ta galla mishi harara sai kaje ka shigo da ita ai..... Ya runtse ido Yana dariya.
Taci gaba da hararar sa tana magana watau Kai hankalin ka na gunta kana bin kwaf kwaf....
Ke rufan asiri ya tashi da sauri wallahi da wasa nakeyi zolayace..... Hey nawaoooo....
Ta kawar da Kai kawai .
Ya canza maganar da cewa, me Zaki dafa mun yau?
Ta yi shiru.
Kinji?
Har abinci Zan maka?
Eh Mana, kiyi mun tuwo please kinzo da manshanu?

Ta ce um.
Amma anan zanzo inci kinji ko?
Ta kalleshi da sauri yayi Yar dariya ko ke Zaki kawon gidana na jiraki?......... Taci wani uban birki ji kake kuuuuuuu....😄✍🏼

*Zainab wowo mamar Abdallah*💖💖

*YOU ARE THE BEST AMONG BESTEST, ALAWIYYA NASIR*💞
[3/26, 9:53 AM] +234 703 965 3416: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
2️⃣7️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

👉🏼💞💕💕 *RUKAYYA BAKO DAN BATTA I love you so much, remember this always*🥰😍😘.

👉🏼💗💕 *Mz na nufin moza ( mother) watau ( Salamatu Dahiru ) wannan page din duka naki ne Allah ya bar mun me MZ ana mugun tare*🤝🏼 ```Aminatu na godiya kina qalbinta```

**************

*Federal University dutsinma*

Ya wuntsula ya Mike da sauri keeee kina hauka ne Zaki kifar damu, ki rufa mun asiri Ina son ganin Yan dagwai dagwai.... Ta galla mishi harara sauka munzo... Ya duba da sauri yaga an wangame get, zuwan keda wannan burkin ko kuwa kawon abincin?
Kinji?
Kazo kaci gidana..... Zaki zo ki daukeni?
In daukeka fa kace, Wai meye amfanin motocin can? Ta nuna da yatsa yayi murmushi kunyar hawan su nake Allah... Ta danyi dariya kunya?
Eh wallahi sai nake ga kamar kowa zai ringa kallona...

Sai Ni rasa kunya ka sa nake hawan Wagga?
Ya kyalkyace da dariya to ai ku Daman Mata da kyale kyale aka sanku duk neman da mukeyi suwa muke kaiwa kudin? Ko bakiji ance Mana *Bayin Mata muke?*
..... Nidai naji sauka ...kina korata?
A'a Ina dai son naje nayi tuwon ko?
Zaki zo ki daukon please?

Dan Allah Anwar kazo da kanka.... Ya bude motar fine... Zanzo bye take care ya shige .
Tayi Yar dariya kawai ta tafi.
Karfe takwas yazo shida sadeeq gidan falo biyu ne na farko da na can ciki, bai tsaya komai ba ya wuce ciki abinsa... Sadeeq Kuma ya zauna na farkon shida su Aisha.
Riga da skirt ne jikinta sun kamata, ta zumbula hijab ta wuce da abincin a tray.
Sai kace muna a gida, ji yanda ka dararrashe... Yayi murmushi kawai.
Ta zuba mishi komai ta mike.... Ina zakije?
Ke wace irin bagidajiya ce Yar kauye? Haka are serving Mai gida???
Ta galla mishi harara, ya ce, naji dai Amma zauna ki cire wannan hijab din..... Ta zaro ido to Bari na dauko kallabi ko gyale..... Ya ajiye chokali ya kalleta fuska daure.... Ina son ba daddy mamaki Amma da alama wannan gardamar taki zata janyo Miki.... Tayi saurin cire hijab din gashin ta ya warwaro bisa bayanta warrrrrr ya sauka....yabi gashin da kallon ya hadiye tuwo ba shiri Amma duk da Haka bai saki fuska ba....
Ta yi tsumu kunya ta baibayeta, musamman da ta lura Yana yawan kallon kirjinta. Kayan sun matseta duk ta takura.
Ba tare da ya kalleta ba ya ce ```Kinsan kina da kyau Bilkisu?```
Gabanta ya bada ras!
Jin tayi shiru yasa Shi kallon ta yace kinji??
Ta Kara yin shiru....wannan kalmar ta kinji idan ya fada tana Jin kamar ta gantsara mishi cizo.... Bazaki amsa ni ba?
Ya kafa Mata ido, ta danyi murmushi tana Kara sunne kanta sai murza hannu takeyi kamar Mai yin alwala....
Yayi murmushi,kina da kyau Bilkisu Ina son structure dinki ... Tsikar jikinta ta bada wani Yarrrr..... Ya ajiye chokali tuwon yamun dadi akwai Wanda zakiyi mun dumame da safe?
Um, ta ce a hankali.
Amma kamar generator dinku bashi da karfi ko? Naji AC din Bata tafiya da kyau ko kuwa fault din nata ne?
Huh?? Ya ce Yana kallonta...
Kila, ta fada ahankali... Wai kin takura ne?
A'a ta fada tana sunne Kai.
Bana son wannan ruwan daukon wasu marassa sanyi a can...ya nuna karamin fridge... Ta Mike ya bita da kallo, Koda ta juyo yayi saurin kawar da Kai kamar Yana latsa waya..... Ta mika mishi ya hada da hannun da ruwan ya fizgota , ta fada jikin sa zata kurma ihu ya toshe Mata Baki..... Kina ihu su sadeeq zasuce ga Bilkisu can ana harka...ya fada Yana Yar dariya.
Ta runtse ido jikinta ya Fara kyarma.... Dan Allah kayi hakuri..... Wayyo na shiga uku...
Wannan kunyar taki ke tunzurani kinki sakin jiki dani..... Dan Allah Zan saki sakeni ka gani.... Ya zagayo da hannayen sa ta gaba ya harde su daidai kirjinta ya soko kansa ta wuyanta Yana Mata Rada..... Ke nifa ba dutse bane ko katako.... Ta runtse ido wayyo na shiga uku Dan girman Allah ka sakeni.
Zan sakeki Amma wallahi Kika motsa kinji na rantse yau ba me kwatarki.... Naji Zan tsaya please na tuba.  .... Ya cire hannuwansa ... Ta saki ajiyar zuciya kanta kasa sai kyarma takeyi duk ta tsorata....
Kyarmar ta mecece ya riko hannunta..... Dan Allah kayi hakuri..ta fada kamar zatayi kuka.... Ya

Kara rungumota Dan Allah ki jira....Anwar kace zaka ba daddy mamaki fa.... Eh na sani. Ya fada kasa kasa .
Dan Allah ka sakeni.... Ke wallahi bazan iya ba, Dole na ringa taba ki don ki Saba kunyar Nan tayi yawa....ke Yanzu na say Miki ido kawai ba Dan romance ai Kya ce bani lafiya...... Wayyo ni Bilkisu na shiga uku...ta fada a hargitse .
Ya shafa gashinta.... Ina son gashinki .... Jikin ta ya bada tsammmmm....ta runtse ido.
Dan Allah kizo muje gidana ki kwana.... Sai kawai ta rushe da kuka.... Ke wasa nakeyi yi shiru.... Ya saketa Yana dariya... Jikinta sai kyarma yakeyi.... Ta goge hawayen ya bita da ido.... Haka kike da tsoro?
Ta hada Kai da guywa kawai....
Ya Mike shikenan tashi ki saka hijab muje ki rakani ...ya dauko hijab din a hannunsa.
Ta Mike .... Wallahi ko kiyi shiru ko na tafi da ke ... Tayi saurin goge kwallan, yayi murmushi matso na Sanya Miki hijab din... Ta matsa ya rungumota..... Dan Allah ki Dan ban minti biyu .... Ta sunne jikinsa ta Kara sakin kuka.... Ya buga tsoki... Kedai wallahi akwai ruwa ruwa...
Aure Dadi gareshi ki kwantar da hankalin ki mu.... Ta Kara sunne Kai ..ya kyalkyace da dariya to sakeni shikenan ba abinda zamuyi.
Ya saketa a hankali, Ya koma ya zauna bisa kujera ya zuki iska ya fesar tare da fadin ohhh my God.
Tayi tsaye har lokacin Bata daina kyarma ba ya fizgota ta fada jikinsa Yana fadin idan Baki saki jiki ba Allah yau sai dai mu kwana anan.... Ta sunne jikinsa, kokarin dagota yakeyi taki yarda.... Yayi dariya to ki daga ni na tashi ko?
Ta kasa dagowa.....wallahi Zan birkitar dake... Ta Mike da sauri ya riko hannunta tare da mikewa ya janyo bayanta ya kwanto samanta kansa bisa kafadar ta Yana magana cikin Rada Rada.... Bilkisu Ina Jin tsoro fa Anya Zan iya ba daddy mamaki wallahi duk kin rikitani.... Nidai Dan Allah kayi hakuri Anwar na tuba..... To ki jiyo in Baki kiss...... Ta zame ta zukunna tare da kankame jikinta tana fadin wayyo.... Ya Dan zukunna shima.... Wallahi kiss kawai zanyi please....nidai Dan Allah ka rufa man asiri....
Yayi Yar dariya okay naji tashi na tambayeki... Ta Mike da sauri ya matso ta matsa baya... Ya kalleta ya da matsawa?
Ta zumburo baki kayi tambayar inaji.... Ya nufota ta ringa baya baya... Bata Ankara ba taji ta daki bango ta kankame jikinta.... Ya tsaya gabanta ya harde hannuwa ya goya su a kirji tare da kura Mata ido duk sun kankance.....
An taba kissing dinki?
Jikinta ya bata tsammm..... Kinji? Ya fada.
Bazakiyi magana ba?
Wallahi ban taba ba..... Hada wallahi?
Wallahi tallahi ta fada kamar zatayi kuka...
Kina so kiji yanda akeyi?
A'a Dan Allah kayi hakuri.. .... Me yasa bakya so?
Tsikar jikinta ta Kara bada Yarrrr.....kinji?
Hakanan...
Ya sunkuyo daidai fuskarta tare da dafe bangon da hannu yace ki shirya anytime from now Zaki ji yanda akeyi.

Ya tallabota yasa Mata hijab ya figi hannunta suka fito....
Sadeeq shida Aisha kadai a Falon Maryam tayi ciki abinta..... Ta kalleshi idan ka Gama muna waje.....

Kanta a kasa ta kasa dagowa ta sanyata jikin mota ya matso kusa da ita sosai kamar zasu hada jiki ya Fara Mata magana a hankali.... Ina so ki sani ni ba katako bane,in shaa Allah bazan kasa ba daddy mamaki ba Amma da sharadin sai kin daina wannan kunyar kin sakemun jikinki..... Ta runtse ido ya sunkuya Yana lekenta..... Wannan kunyar taki wallahi tana Sanya mun sha'awar ki Bilkisu tabbas idan Baki saki jiki Dani ba to I have no choice but to sleep with you..... Ta juya ta kife Kai ga mota *na shiga uku ni Bilkisu*..... Ya juyo da ita, matsalar bani da kunya ko a gaban waye Zan iya taba ki don haka kina da aiki ja don duk ranar da na bukaci taba ki Kika Hana kamar yau to ki sani Zan...... Anwar please.... Ta fada tare da runtse ido. Ya kyalkyace da dariya... Sadeeq ne ya fito Shi kadai ba Aisha .... Ya kallesu to pigeon muje ko? ..... Sadeeq yarinyar nan ta fiye kunya fa tana takurani da yawa...

Tayi sukutiiiii, Sade yayi murmushi Bilkisu ya da kunyar miji Kuma?
Ya zagaya ya shige mota.....Yana fadin kasan baka Gama ba ka fiddoni..?
Ya kalleta sadeeq bai gaji ba ko mu koma?.... A'a kuje Dan Allah...ya Kyalkyace da dariya matsoraciya kizo mun da dumamen school gobe zanci a mota kinji ko?
Ta Dan saki ajiyar zuciya ta ce toh.
Ya langwabar da Kai Bilkisu bana son tafiya wallahi.... Ta ce ya Salam! Amma a zuci...

Zan say kawo Miki irin pad din kamfanina kiyi amfani da ita ance tana da kyau sosai idan Bata Miki ba Kinga Dole a canza sabuwa..

Ta mishi banza.
Yayi murmushi kinji?
Um, ta ce.
Ko Zaki bini..

Ta ingijeshi ta kwala. da gudu ya tuntsure da dariya ya fada mota...... Sadeeq anya Zan iya zuba ma yarinyar can ido?

Ka rufa Mata asiri Dan Allah... Ya fada Yana Yar dariya.
Amma fa tana da tarbiyya sosai could you imagine ta tsorata simply don na yi hugging dinta? .....wallahi Anwar Bilkisu na bani mamaki ta fita daban daga cikin Mata maganar gaskiya wannan lokacin kafin ka sami yarinya Mai kamun Kai irin ta Yana da wahala kasan abinda ke bani mamaki?
Ya girgiza Kai..

Yanda she's fully hijabite wallahi kaga fa tun zuwan ta school din nan Bata taba Sanya gyale ba Bata shigar banza ga addini sallah Bata wuce ta cikin jam'i naji ana rade radin ita za a ba Amira....
Ya danyi murmushi, wallahi har tausayi ta bani Yanzu duk jikinta ya tsinke da rawa sadeeq ta tsorata da nace zanyi kissing din ta wallahi hada kuka....
Ya kyalkyace da dariya ya ce baiwar Allah.
Sai ka lallaba ta ka Kara daurewa kada ka janyo ma kanka jangwam ta rikice maka Kuma......

Naga alama fa akwai rikici .
Kasan Aisha ta nuna tana da interest akaina?
Ya kalleshi haba???
Ya Dan Bata rai, no Bata mun ba, Ina son mace mai Jan aji nafi so na Sami mace wacce Ni ke binta tana ban wahala ba ita ce zata ringa zakewa ba..... Kamar Bilkisu kenan? Ya katseshi Yana dariya... Yayi murmushi Anya Zan Sami kamar ta at least ma ko wacce bata kaita ba.. da tana da kanwa ko Yar shekara biyar ce Allah da Zan jira..

Suka kyalkyace da dariya.

Ya zuki iska ya fesar.... Gaskiya Ina bukatar matata .....ka rufa mata asiri Anwar Dan Allah kaifa da kanka kace zaka bada mamaki...... Kai nifa ba katako bane ko?.
Eh,but at least ka duba yanayin idan ta Sami ciki fa?
Shine me? Ya harareshi, Ina nufin kaga na farko tun a laulayi idan Mai Shan wahala ce an Sami matsala musamman ga karatunta, kaga automatic spill over, na biyu bazata taba fita zargin mahaifan ta ba cewar ita ta sanar da Kai akwai Aure bayan an gargadeta da tayi shiru,na uku karatu da goyo Anwar is not easy akalla.... enough jor.... Ya daga mishi hannu... Amma Zan ringa Dan romancing dinta gaskiya ban iya daurewa..... Romance din zai ringa Sanya maka sha'awa akwai ranar da wallahi zaka kasa controlling kanka tunda kamar yanda ka fada din Kai ba katako bane...... Ya Allah !!! ya fada tare da maida Kai ya kwantar bisa sit, sadeeq meye dabara?
Ina ga mu rage ziyarar su gida , ka ringa tsareta school duk maganar da zakuyi nasan idan kana ganin jama'a bama zaka kawo komai a ranka ba..... Nawaoooo,!!! Ya fada tare da tashi zaune.. gaskiya nidai an kwareni ....
Sadeeq ya kyalkyace da dariya rawar kanka ta janyo maka....... Ya Kai mishi duka, naje nayi.
Yanzu dai ai daga wannan semester din saura daya ko?
Biyu dai....
Ya katseshi ...ya ja dogon tsoki kawai ya kwanta tare da runtse ido. Sadeeq ya bishi da kallo Yana murmushi......
Wai ya mufeeda ta hakura ko?
Ya yatsuna fuska, ance har yau ta kasa shigowa school saboda kunya..... Maganin ta kenan...
Ya tashi zaune Yana Yar dariya kasan ni duk wake bani dariya?
Ya ce sai ka fada.
Helen, tunda akayi case din nan Yanzu ko layin da nake zaune Bata bi kasan arna da shegen tsoro....... Suka kyalkyace da dariya.

Bilkisu ta zabga uban tagumi har lokacin jikin ta bai daina rawa ba, kirjinta kuwa sai dakan uku uku yakeyi, *Na shiga uku ni Bilkisu Wai kiss* .... Nikam dama na hakura da Abujan da Yanzu Ina can zamana qalau..
Ta runtse ido lokacin data tuna ya zagayo da hannayen sa bisa kirjinta ya kwanto jikin ta...... Tsikar jikinta tashi Yarrrr lallai akwai damuwa .... Ta bude ido su maza basa da kunya ko kadan....
Haka ta kwanta tana ta juye juye da ta tuno Shi da yanda ya ringa Mata sai ta kudundune jikinta

ta boye kanta cikin filo.....
Murjanatu cikin masu aikin gidan ta Kira da sauri ta ce maza ta dumama tuwon jiyan kafin ta fito wanka.....
Yau taga amfanin nikaf, saboda da Babu ita tasan bazata iya kallon Anwar ba.....
Tana shiga ajin anata raba test din da Richard munafuki yayi. Two over ten, three mutum biyu keda 5 su chinayye...... Itama two taci, Anwar ya saka tashi aljihu kawai lokacin da ya buda yaga yaci nine....
Ya kame Baki na shiga uku.... Mutumen nan wallahi mugu ne daman yafi so mu fadi.... Sadeeq na bayanta ya ce nawa Kika ci Bilkisu?
Ta mika mishi 2 ce shegen kaifa? Yayi murmushi three..... Anwar yayi fit ya fizge takardar ya na zagayo ya kalli root dake kusa da ita yace ban wuri.... Ta kwashi takardun ta ta koma sit din da ya taso.... Basai ka fizge ba two ce kai nasan nine kaci don ma baya bada cikon da tabbas ten zaka ci....... Inji waye ya fada Yana murmushi....ta zumburo Baki nidai fiddo naga Ni...... Ya Mika Mata Yana murmushi.... Kamar jira ake taje hannun Bilkisu aka Fara rokonta ta bada ayi snapping.... Ta Mika musu.
Mutumen can na daga mun hankali bana kaunar Dan iska.... Yayi dariya Kuma duk da Haka Baki taba faduwa course dinsa ba ko?
Ta harareshi Amma da yake akwai nikaf bai gani ba tace da hawan jini, da na ruwa ko?,ya kyalkyace da dariya, toh eh Mana,duk sai ya gama tayar Mana da hankali tukun Kuma *E* din nan dai ce ko *D* ..... Ina laifi ai yafi carry over ko?...... Zatayi magana malamin ya shigo..... Ya fiddo waya ya dan Mata magana a hankali..... Shiga WhatsApp...
```kinyi barci jiya?```

Ta maida mishi da ```me zai hana?```

```ni kuwa kasawa nayi saboda tunanin ki```
Ta kasa cewa komai

```kinji```
Ta ce ```Hmmm```

```smiles kin zo mun da tuwon?```

```yana mota```

```ina zamuje naci```?

```ina fa, anan waje ko?```

```Bana son waje is too open let's go to the field or new lecture rooms side I need quite place okay?```

Tayi shiru.

``` kinji ko?```

Ta maida hankali gun lecture.... Ya zunguro ta da hannu ....dole ta rubuta mishi

```naji```

Yayi murmushi.

``` sai Anja mun aji?```

```Ka bar mu muji lecture Anwar```

.....```ke ni ban wani ganewa ki Bari kawai zamuyi tutorial```

```Hmmm```
Malamin na lura dasu,
Yana gamawa ya ce tear a sheet of paper write your number only......

*Mun shiga uku ka ga abinda nake gudu ko?*
Ya sumke Yana Mata dariya.

Kina da black biro?.....
Banda Shi ta fada cikin tsiwa.
To kiyi sauri ki wanka ko na rubuta miki,?
Kawai kayi na kwafa idan Kuma ya tayar Dani shikenan.....
Yayi murmushi....
Ya Fara dictating questions based on what he discussed.
Ta Kara tsure Mata tana magana kasa kasa ... Wallahi kana ja mun wannan semester din.....
Yayi shiru Yana murmushi Yana rubutu.
Tana kokarin Jan layi ya turo Mata takarda har ya Gama Daman two questions ne. Ya ci gaba da rubuta nashi Yana layin karshe kawai malamin ya ce hands up...... Amma sai da ya karasa Kai Anwar karshe ne......ta galla mishi harara cewa zakayi kasan abinda ka taka, yayi dariya to meye acikin nan cubweb theory din ke da wahala?

Ta ce hmm, duk ya Gama birgeta, gunguni kawai ke tashi cikin ajin.
Yana zuwa layin ya karba ya dan harari Anwar din ya wuce ....
Yana fita sadeeq ya taso kaga mutumen Nan ko?
Yayi murmushi bana fada ma ba, gaskiya naji dadin bayanin jiya... Ta kalleshi da sauri au Daman kunyi wannan din?
Sadeeq ya ce wallahi jiya kamar wasa ya koyan Kinga da yau naci kaniya ta...... Ta ce hmmm kawai,
Anwar ya kalleta kema yau zamu Fara karatu kiyi hakuri..... Na fito karfe hudu kenan?
```

A'a ki Bari sai after Isha zanzo gidan....
Gabanta ya Fadi, na marecen nake ga zaifi ko kuwa?
No!, Bana son yawan fita inba lecture akeyi ba, kawai ki jira zanzo kinji ko?
Toh, ta ce a hankali.
Ya Mike muje....
Ka Kira sadeeq muje yaci..... Zan rage mishi ..
Anwar meye Haka? Wasa tare ci banban.... Ya danyi dariya yarinya kawai kice kina son wani kusa kada muje na cinyeki Ni kadai.... Laaaa ni ba Haka nake nufi ba..... Sadeeq!!! Ya kwala mishi Kira....
Ya karaso Yana murmushi ya akayi?
Tuwo aka kawon Wai bazan ci ni kadai ba sai tare da Kai... Yawwa Bilkisu Allah dai ya biya kin San kuwa yunwa nakeji wallahi.... Ya banka mishi harara Kuma Kai baka wuce tayi ko?
Ban wucewa kin ganshi Nan ko ruwan zafi bai iya dafawa .... Duk suka kwashe da dariya.
Ina zamuci tuwon?
Field... Anwar ya bashi amsa.
Okay kuyi gaba Zan biyo ku da mashin.
Ungo nidai kaja motar Dan Allah..... Ya wurga mata harara ya fada gaba ya zauna kawai.
Dole ta shiga ta ja motar a hankali.... Duk inda suka gitta sai an bisu da kallo.. ba karamin kashe zuciyoyi sukeyi ba a school din suna bada *Plus*
Sadeeq na gama ci yabar wurin yace zaije aski.
....me Zaki dafa mun da dare?
Abinda kake so, ta fada..... Ke daga nikaf din nan na ringa ganin idonki.... Ya karasa maganar Yana yakice Shi .... Ta yi kasa da Kai tana murmushi..... Ya shafa gefen fuskar ta Yana fadin ```lemme see this baby face``` ... Ta to dariya ta ce kaiiiiiii.....
Yes, ya fada Yana Kara kallonta,
Me Zaki dafan?
Abinda kake so, ta Kara maimaitawa.
Kiyi mun chips mana.
Toh, ta fada a hankali.
Babban fridge din nan Kinga akwai kaji da naman rago da kawuna ko?
Um, ta ce.
Idan kina bukatar kifi kiyi mun magana a kawo Miki Shi kinsan baya da dadin ajiya saboda karni ko?
Gaskiya fa.
Me yasa baki taba rokona wani Abu ba?
Ta kyalkyace da dariya kaiii Anwar... Yabi fuskar da kallo..... Yana murmushi.
```Bilkisu kin San cewa ke din ta daban ce kuwa?```
Na sani Mana... Ta fada tana murmushi.
Ya akayi kika sani.....
Tayi dariya saboda *Bushara na Sona*..... Ya kyalkyace da dariya for the first time kin kirani *Bushara* Dole na Miki kyauta yau Zan canza Miki motar Nan...... Dan Allah ka barta Ina sonta....... Karki damu ai ba rokona kikai ba, Ina son ki bar tarihi FUDMA a ringa kwatancen mu..
```

.. Yanzu ma anayi.
In tambayeki???
Ta ce um,
Yaushe Kika Fara Jin kina Sona?
Ta yi kasa da Kai tana dariya.....
Kunya kike ji?
Ta Kara murmusawa..... Okay rubuta mun ta WhatsApp..... Ka Bari Zan fada maka..... Yaushe?.
Tayi shiru tana murmushi.
Kunyar ki tayi yawa Bilkisu....
Muje ki ajiyeni gida .
Ta tayar da mota,
Har ciki ta shiga yau, ya ki fita ya tsareta da ido sai kuma ya ce affff.... Ki jirani Ina zuwa please ya shiga gidan da gudu.....
Ta bishi da kallo tare da sakin ajiyar zuciya a hankali....
Ya dawo dauke da Yar leda Mai kyau a hannunsa, ya leko ta taga, it might be Baki zo da English wears ba ko?
Kisa wannan anjima.... Ta zaro ido...
Ya Kara sunkuyawa ba abinda Zan Miki Allah kuwa kawai Ina son ganinki cikin su matsala daya za a Samu idan kika Fara wannan kunyar taki lallai Zaki janyo ma kanki na taba ki.... Ban Baki a boye ba, just wear it and feel free okay????
Ta daga Kai a hankali.... Yayi murmushi that's my babe...... Tayi baya da motar ta fita a hankali duk jikinta yayi sanyi duk da bata ga kalar kayan ba.....
Yabi motar Yana murmushi... Ya ce tsoron ta yayi yawa gaskiya. Ya zuki iska ya fesar ya wuce ciki.
Ta zabga uban tagumi daki ita kadai ta zuba ma kayan ido, doguwar riga ce Mai kame jiki da hannun vest, daga kasa akwai tsaga har kusan guywa maroon ce Dana da wani katon belt bisa kugu, da jefi jefin flowers jikin rigar red. Aisha ta taimaka Mata sukayi farfesun kaji, sannan suka soya chips din kaskon karshe ta shiga tayo wanka tabar Aisha ta karasa ta feshe jikin ta da turaruka masu kamshi ta gyara gashinta Amma ta mishi gammo ta nade tare da zumbula katuwar hijab.... Tana fitowa taci karo da Aisha bakin kofa zata shigo ....Wai duk meye kikeyi haka ga Anwar can yazo.... Gabanta ya bada ras!.... Shida sadeeq ne?
A'a Shi kadai ne gaskiya... Kin saka ma coconut juice din ice ?
Eh Yana fridge muje na Kama Miki.... Barshi baya son haka, ta katse ta.
Yana zaune kasa ya Mike kafa Yana ta latsa waya sanye da farin boyel Mai laushi kansa ba hula.
Ta ajiye plate din chips din da cooler farfesun ta ce ... Ina wuni?
Ya Dan dago sai Shan kamshi yakeyi ya ce ... Bilkisu ya kike?... Na Sanya ki aiki ko?
Ba komi, ta fada tare da mikewa... Ya bita da kallo duk kamshin turarenta ya kashe Masa jiki.
Ta dawo da sauran kayan ta zuzzuba mishi Yana satar kallonta da wutsiyar ido, da tazo dagowa sai ya basar.
Tana gamawa ya tura Mata Wanda ta zuba mishi ya janyo sauran da ke cooler gaban Shi ya ce wallahi sai kin cinye duka Koda zakiyi amai.... Ta dago Kai da sauri ,.. ya hade girar sama da kasa yasha mur ...

Dole ta dage ta Fara ci sai da tafi Rabi yaga da gaske turawa takeyi sannan ya ce mikon dankalin na Kara bai isheni ba.... Ta tura mishi da sauri ya cinye... Peppé soup din Nan yayi dadi fa.
Jeki Kai kayan kizo da books din da zamuyi ba dadewa zanyi ba.....
Ta mike da sauri ya bita da kallo sai kawai yayi dariya.... Tana dawowa ya Kara hade fuska.... Kina jira na ce ki cire hijab din????
A hankali tayi sama da ita.... Tsikar jikinsa ta bada Yarrrr, ya hadiye wani tsinkakken miyau sai kawai yayi kasa da Kai ya Fara budo littafin da ta Miko....
Tunda ya Fara bayani bai dago ba ..... Tun tana Jin kunya da tsoro har ta fahimci Sam ba ta ita yake ba gashi sai wani Shan mur yakeyi.....
Tana ganewa sama sama har sukayi course biyu.
Duk ta makure... Ya dago Kai kina ganewa kuwa?
Um, ta ce da sauri, saura kadan yayi dariya.
Yau barci nayi da Rana sosai...
Wai kin San cewa an gano nine Bushara school din Nan?
Ta danyi murmushi, nasan za a gane Kam...
Saboda me Kika ce haka?
To Anwar ko wadannan kattin da ke Bina da wadanda ke gidanka yaci asan Kai waye.... Ya danyi dariya inji waye kawai tsabar sa ido ne.
Naji class din mu za a yi jacket da shirt na graduation Ina ga ni Zan dauki dawainiya ko?
Ya dai kamata. Ta fada kanta kasa.
Yayi murmushi, Nima Ina son yiwa yaran Nan alheri me kike ga Zan raba musu?
Kudi, ta fada.
Kudi Kuma?
Eh, Mana kudi zaifi saboda kowa yasan meye damuwan sa Kuma kudi ke maganin komai ko kuwa?
Kuma fa, Shi yasa nake sonki wallahi saboda kina da hankali...kamar nawa Zan basu?
Yanda kayi niyya Kuma ai kafi kowa sanin iya karfin ka.
Ya kura Mata ido, ki fada mun Mana ai Yanzu shawara mukeyi nida ke ko?
Ka dai kiyasta Ni ban San nawa zance ba ko kayi shawara da sadeeq..... Da ke zanyi. Nawa kike ga ya Dace na raba masu?.
Tayi shiru... Ka Bari zanyi tunani toh.
Okay, sai na jiki tashi ki karon ruwan in Sha... Ta Mike ya bita da ido, kafin tazo kawai ya Mike kamar Mai neman wani abu,
Tana kokarin Miko mishi ya mameta ya kamo sai kawai taji ya hada bakin sa da nata, ta saki ruwan kasa..........✍🏼😄🙈

*Zainab wowo mamar Abdallah*💖

*Mz , mz, mz Ina nufin ( salamatu Dahiru ) Allah ya Kara zumunci mother kina Raina koda yaushe.*

*ALLAH YABARKI DA ALHAJI NURA NA'IMA AMADU SPEAKER YAN ADAWA BAKU IYAWA MUNE AMARYA KUMA UWARGIDA MUTU KA RABA IN SHAA ALLAH*💞💞💞

*Yauma page daya za'a samu Ina busy*
[3/28, 10:24 AM] +234 703 965 3416: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
2️⃣8️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano mam in huhan Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

👉🏽💞💕💕 *RUKAYYA BAKO DAN BATTA I love you so much, remember this always*🥰😍😘.

```Bazan taba mantawa da ke ba Maryam Aliyu Yar adu'a ( M. Ali ) uwar Noor my in-law kina Raina Koda yaushe```

👉🏽💕 *Mz ( salamatu Dahiru ) Ina Kara godiya Allah ya Kara dalili my mother*

*****************
*Federal University dutsinma*

....... Tun tana iya motsawa har jikinta ya mutu murus, duk illahirin kafafuwanta rawa sukeyi suna neman gagara daukarta, Jin tayi lakwas yasa Shi juyawa da ita ya zauna bisa kujera ita Kuma tana bisa kafafun sa..... Yayi iya gumin sa ya taba inda yake so, karkarwa jikinta kawai keyi duk ta firgita..... Ya saki ajiyar zuciya ya janye bakin sa a hankali..... Sai kawai ta tusa kanta cikin kirjinsa ta saki kuka... Yayi shiruuuu...
Zuciyar sa na mishi sake sake, shin ya biya bukatar sa ko ya ba dady mamaki?
Da ya motsa sai ta rikeshi gamm ta Kara sakin kuka.... A hankali yake fitar da numfashi.... Sai kawai ta bashi tausayi lallai ya Kara tabbatar wa kansa da Bilkisu yarinya ce karama.... Tunda har ta kasa supporting kiss kuma hakan ya bashi tabbacin this is her first kiss.....
Tayi Mai isarta, har lokacin jikin ta rawa yakeyi..... Da ya motsa sai ta Kara rikeshi.... Ya danyi dariya.. ``` To ki sakeni na tashi ko?```
Tayi shiru,

```Bilkisu```

Ya Kira sunan ta a hankali,

.... Ta Kara fashewa da kuka ``` Dan Allah kayi hakuri```
..... Ya Kara dariya naji sakeni Dan Allah ai ba Kya so ko?
Ta daga Kai cikin jikin sa...
Okay Zan tashi na tafi sakeni....
Ta Dan sakeshi.... Yana motsawa ta koma da sauri .... Ya kyalkyace da dariya da ya gane ba tsoro kadai ke addabar ta ba hada kunya..... Ni Kuma yau tawa ta sameni ni *Hamza*...... Bazaki sakeni ba? To gyara mu yi kwanciyar mu anan.... Ta sakeshi da sauri tare da soke kai cikin kujera..... Ya Kara dariya.... Ba rakiya kenan?
Tayi shiru..... Ya kawo hannu ya taba ta, saki kuka tare da kankame jiki..... Ya Kara dariya ya ce tohm na siyo ma kaina rigima da kudina..... Ya zukunna gaban ta, Shikenan daina kukan Zan tafi Amma Dan Allah ki dauki waya idan na Kira matukar bakya son na maimaita kinji ko?...... Saura kadan ta wawuro fuskarsa ta cije don takaicin kalmar ```kinji ko```.
Ya saki ajiyar zuciya ya mike sai da safe I will miss you honestly..... Ya fita da sauri.
Tafi mintuna ashirin a wurin kafin ta tashi zaune.... Ta Dora hannu a Kai *Na shiga uku ni Bilkisu idan Haka ne halin Anwar na gama banuwa* Shi baya da kunya?
Ashe abinda nake karantawa da abinda malaman islamiya ke fada gaskiya ne?
Ta Mike jiri ya kwasheta, ta koma ta zauna.... Ikon Allah, ta kalli hannuwanta sai kakkarwa sukeyi, tsikar jikinta tashi Yarrrr tana tuno abubuwan da suka faru... Namiji???? Shi har wata dariya yakeyi... Ta zumburo baki tare da zabga uban tagumi.
Yana shiga sadeeq yaji kamshin turarensa ya canja gashi cikin wani yanayi na nishadi .... Ya bishi da kallo kawai Shi Kuma ya fada toilet ya sakar ma kansa shawa.......
Duk su Aisha sun shige sun kwanta, ta shige dakin itama Kai tsaye kewayen ta fada......
Ta na rungume da qur'ani kiransa ya shigo..... Taji wani dammmmm a kirji.
Ta dauka Amma samm ta kasa magana....
Kinyi wanka?
Tambayar ta bata haushi ta mishi banza.... Kinji?
Um, ta ce a hankali.
Kin kwanta ne Yanzu?
Tayi shiru......
Ya ce kinji?
Ta ce um,
Yayi murmushi, Baki ya mutu ne?
Tayi shiru.......
Ya ce huh?
Da kyar ta ce hmmm.
Ya danyi dariya.
Thank you so much Bilkisu, wallahi naji dadi sosai Zaki Sami Lada Mai tarin yawa kin San Haka?
Tayi shiru...kanta sunkuye kamar Yana kallonta wayar ma kunya take Bata.
Ya Kara dariya Wai Baki magana?... Ko muyi video call........ Nidai a'a..... Ya tuntsure da dariya to kiyi magana inji, kiss kawai ya rikitaki haka Ina ga..... Zan kwanta Dan Allah..... Ta fada kamar

zatayi kuka ya kyalkyace da dariya..... Shikenan sleep tight sweetie.... Ta latse wayar da sauri kirjinta na bugawa ..... Ai shikenan Ni Kuma tawa ta sameni ta fada a hankali.

Ta Dade barci bai dauketa ba har kusan karfe uku da Rabi..... Shi yasa ta rasa lecture karfe bakwai don Bata tashi ba sai Tara saura.

....... Sadeeq ya kalleshi ya Bilkisu bata zo lecture ba?..... Ya danyi dariya kawai...

Ya bishi da kallon tuhuma.... Me ka Mata?.... Ya daga hannuwa yana dariya wallahi ban Mata komai ba kawai kiss ne ....... Ai nasan baka iya ba daddy mamaki Anwar Kuma yasan abinda ka je ya dawo Kan yarsa akanka yasa ya yanke wannan hukuncin...... Allah Ina iyawa.... Me yasa ka taba ta toh?

Ya galla mishi harara halan ni katako ne da Zan tsaya da Aure Ina kallon matata haka zikau ai ko Dan romance din a daga mun kafa ko?

.... Sanya ma Rai koshi ke kawo yunwa Anwar a haka, ahaka zaka je inda baka son zuwa Dan Allah Ina baka shawara ka tausaya ma yarinyar nan ka Bari akai maka ita...... Kuma duk ta tsorata jiya kaga yanda jikinta ke Bari?

Ai dole ta tsorata, bacin islamiya da sai ince anya tasan me ake ce ma Aure saboda yanayin yarinyar na bani mamaki...... Wallahi yarinya ce sadeeq nayi mamaki jiya ta kasa daukar kiss...... Mtseww ai ka yi sauri...

Shin Zan kiyaye ai dai na Dana.... Ya mishi gwalo... Ai Kuma ka Dano ma kanka ko? don na tabbatar Yanzu ka siyo rigima da kudin ka..... Wallahi
kuwa, ko agabanta na fada jiya..... Amma fa na kashe bakin rigima Zan Sami sauki saboda ta tsorata da Ni...... Ya ce hmm.

Yaki zuwa gidan ranar ta kashe wayar ta...

Ta ce ma su Aisha zatayi karatu ne daki Koda sun jita shiru.

Kwana daya , biyu har uku Bata shiga school ba. Taki kunna waya kuma.

Hankalin sa ya Fara tashi, ya Sami sadeeq ya fada mishi suna tare da Anas ya Dan kebe shi.

... Yarinyar nan fa taki kunna waya kaga kuma Bata zuwa class.. nasan za a rina Anwar ai ka Mata shigar kutse da ka bari da Yan dabaru da hikima sai ka shawo kanta amma Haka zikau ai Dole ta firgita..... Ya kamata ka fahimceni ya zaka biye Mata ka dauki taking side.... Ya fada a hasale... Na sani amma Ina kwatanta maka ne...... Naji nidai kaje ka lallasar mun ita don Allah Kuma in shaa Allah bazan Kuma ba tell her this please.

Shikenan....amma Zan Fara magana da ita ta waya tukun..... Kana da wani layin nata bayan Wanda ta rufe?

Through Aisha...... Okkkay.

Yayi sa'a kuwa suna tare zasu ci abinci...... Ungo sadeeq na magana ta Mika Mata wayar ......bayan sun gama gaisawa ya danyi kasa da murya Anwar din na tsaye sun Sanya handsfree..... Idan babu damuwa ki Dan ware muyi magana....

Batayi gardama ba .... Tana shiga daki ta zauna sai tace ...Ina ji.

Bilkisu nasan kina da hankali, nasan kina da ilimin addini, Ina so Dan Allah kiyi hakuri duk da abinda mijin ki yayi ba laifi bane wata kila hakan ya Sanya ki shiga wani Hali.... Sadeeq gaskiya Anwar na mun abinda bana so, da bakin sa ya ce zai ba daddy mamaki abinda ke tayar mun da hankali shine duk ranar da daddy yaji Ina Haka da Shi wallahi bazai taba yarda cewar ba ni na sanar dashi akwai Aure ba.

Ya kasa gane hakan..... Na sani Bilkisu, ya kalli Anwar kallon da ke nuna ```kaga abinda nake Gaya maka ko```...... Yaci gaba da cewa, kiyi hakuri ya mun alkawarin bazai Kuma ba..... Baya iyawa, na Fara planning kawai Zan koma gida ne sai ya mun transfer kamar yarda ya..... Ya fizge wayar.... Billahil azim bazan Kara ba kiyi hakuri Bilkisu.
Tayi shiru Jin shine ya karbi wayar.... Yaci gaba da magana.... Wallahi nayi hakan don ki saki jiki dani ba Wai..... Shikenan ya wuce.
Yayi murmushi, na gode Dan Allah kizo lecture two kinji ko?
Shikenan. Ta fada.
Thank you...... Ta ajiye wayar kawai ba tare da ta karasa ji ba.
Ya kalli sadeeq Yana dariya yace, ta kasa Yi mun fada .... Murmushi kawai yayi ya barshi wurin ya koma gun Anas.......
Gaban ya Fadi ganin dalleliyar mota ajiye kirar Toyoto 2019 Fara.
Ita da Maryam suka fita, kamshi kawai ke tashi a motar .... Me yasa baku fadan ya kawo motar ba?...... Sadeeq yace muyi shiru Kar mu fada.
Ta ce hmmm kawai.
....... An kafsa fadan ne ko?
Murmushi kawai tayi cikin nikaf Mai sauti..... Daga nesa ya hango motar ya saki ajiyar zuciya ya shiga class Yana jiran isowarta.
Har ta zauna bata lura dashi ba wurin taga tsaye sai bayan da tagan Shi tsaye kusa da ita..... Matsa na zauna. Ya fada a dake!
Ta matsa Yana Zama ta ce.... Ina wuni.
........ Keni ba lafiya ba. Ya hau masifa, idan na Miki laifi I prefer ki mun duk tsiwar da Kika iya da fada amma bazan iya daukar this type of your punishment ba...haba. kwana uku? You switched off your phone, you skipped class, I believe ko zuwa nayi Zaki gudu daki ki kulle Haka akeyi ma miji horo?.... Nidai shikenan.... Ta fada a hankali..... Ba shikenan ba, wallahi idan Kika Kuma kashe wayar ki idan na Miki laifi zakiji ni baibai.... Sai kawai ya bata dariya ta duke tanayi...... Au dariya ma na baki ya balle bottle din rigarsa na sama ji kasusuwa kamar ba hakki na nabi ba?
Shikenan nidai..... Kiban hakuri Dan wallahi kin sani cikin damuwa fa..... Kayi hakuri ta fada tana murmushi cikin nikaf.... Cire nikaf din ya fizgeshi..... Fuskar ta mishi wani fayau, ta Dan dake saboda bata son a gane tana blushing.......... I missed my baby wallahi. Ya fada..... Zai Kara magana malamin ya shigo....
Yana gamawa ya fita ya koma bisa table ya zauna gabanta..... Kunyar ki tayi yawa Bilkisu.
Zaka Fara ko?
To ki kalleni Mana Wai sumke sumken na menene?
Ta danyi murmushi,
........ Jiya sadeeq ya rabawa Yan class din nan twenty thousand each though sun gane kudin daga wurina yake fa..... Kunyi kokari Allah ya Kara arziki Mai albarka, rigunan fa?
Na bayar ayi a kamfanina da ke Paris zasu fi kyau daga can ko kuwa?..... Karaf suka hada ido ya sakar Mata murmushi, ta danyi dariya ta mike ..... Ina zakije?
Ba tafiya zamuyi ba?
No! Ki jira nayo sallah yau muna nan sai dare...... Nima zanje masallaci....ya Dan kalleta Yana Yar dariya me zakiyo masallaci? Kuma Yanzu nayi magana kice zakiji kunya.....Hajiya ki jirani anan Ina dawowa Zan sallami kattin can ko kuwa?......

Dama ai Kai ka damu dasu..... Eh dole su kula dake ...ke din ce bazaki gane ba ya fita Yana kwance agogo.....
Ta bishi da kallo ta zauna ... Watau yasan bani sallah. Kai Anwar case ne...... Hajiya ke bazaki je sallah ba?
Ta sakar Mata murmushi habawa Helen....ai duk kallon ku nakeyi Yan class din Nan Yanzu kowa sai shareni yakeyi kunyi dai dai wallahi ...... Ba Dole ba, kina son Anwar ya sa a kashe mutum ko?.... Kisa Kuma Helen.... Yes ko mace baya so ya zo gurin ki bakiga guards din da suke binki... Mtsew forget about guards zasu hana abota ne?
Hmmm, Bilkisu you won't understand.
Ehe Bilkisu... Tayi kasa da murya is it true you both got married????
Who told you?.... Abeg .
Tayi murmushi yes is true amma ba'ayi bikin ba kawai an daura Aure ne...... Jesus..ta fada da karfi.
Bilkisu ta kyalkyace da dariya.
You are lucky Bilkisu.... Anwar ya bada mamaki..... And he is that young Nigerian billonaire Bushara... Bilkisu ta Kara kyalkyacewa da dariya Helen Zaki kasheni, Bilkisu you are lucky ooo he gave us 20k and our shirts and jacket will come soon free for everyone....... Hango shi sukayi Yana magana da guards ta mike da sauri please tell him I'm your friend too we will keep talking any time Sha.....ta wuce da sauri tana waigen ko ya taho..... Bilkisu ta duke tana kyalkyatar dariya har ya karaso ...... Ke da waye haka?
....... Ta rike ciki Helen..
Yayi murmushi tana Miki hauka ko? Jiya naso kina class din nan kiga hauka ni Dole na fita nabar sadeeq da shirmen su...
Ya figo Jakarta yamcici nasan ba Kya rabo da Malaki.... Ya Ciro short bread biscuit da bounty.
Ka fiye neman magana ta fizge jakar.
Ya harareta pad kike gudun kada na gani Kuma na ganta dai.
Ta danyi dariya kaiiiiiii Allah ya shirya ka.... Tare da ke da zuri'ar mu baki daya...... Ki ce Amin...
Ta danyi murmushi na ce a zuci..... Ya sauko da hannun rigarsa da ya nade yana sanya links ....kin San jiya da daddare kamar Zan kurma ihu?
Ta dan kalleshi ta gefe... Yaci gaba da magana Yana murmushi.... Dana tuna kin kashe waya Kuma saboda ni sai naji kamar inta ihu ana jina a gari..... Ta danyi dariya .. kina yarda kike so ai.
Kayi hakuri ta fada tana murmushi.
...ai Dole in ma banyi ba nine masha wuya.
...... Anwar bana gane Alfa and bitas din ga na econometrics ... Ya danyi murmushi....Kuma basu da wuya fa.
Wannan drivation din ka ganshi.... Ya karbi littafin ya sauko kusa da ita ya Fara rubutu Kinga yanda yake......
A hankali a hankali yakeyi yanda zata gane.... Anwar marshene komai ya hada.
Duk inda ya shige Mata sai da yayi kokari yaga ta gane duk firar ta koma karatu hakan yasa ta saki jiki sosai shima kuma sai yaji dadi ganin ba wani sumke sumke ta saki jiki.
Ana Kiran magrib ya ce muje ki ajiyeni gida zanyi sallah masallacin unguwar mu. ... Shi yaja motar.

Tun daga ranar ya daina zuwa gidanta, abinci shike aikawa ana karbo mishi ko ta tafi dashi suci school, duk firar su a school sukeyi ya dake ya cije baya nuna zalamarsa fili.
Anayin hutu tare suka tafi Abuja Amma bai kwana ba ya koma Kano kwanan sa biyu yabar kasar......

🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐

2️⃣8️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano mam in huhan Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

👉🏽💞💕💕 *RUKAYYA BAKO DAN BATTA I love you so much, remember this always*🥰😍😘.

```Bazan taba mantawa da ke ba Maryam Aliyu Yar adu'a ( M. Ali ) uwar Noor my in-law kina Raina Koda yaushe```

👉🏽💕 *Mz ( salamatu Dahiru ) Ina Kara godiya Allah ya Kara dalili my mother*

*****************

*Federal University dutsinma*

....... Tun tana iya motsawa har jikinta ya mutu murus, duk illahirin kafafuwanta rawa sukeyi suna neman gagara daukarta, Jin tayi lakwas yasa Shi juyawa da ita ya zauna bisa kujera ita Kuma tana bisa kafafun sa..... Yayi iya gumin sa ya taba inda yake so, karkarwa jikinta kawai keyi duk ta firgita..... Ya saki ajiyar zuciya ya janye bakin sa a hankali..... Sai kawai ta tusa kanta cikin kirjinsa ta saki kuka... Yayi shiruuuu...
Zuciyar sa na mishi sake sake, shin ya biya bukatar sa ko ya ba dady mamaki?
Da ya motsa sai ta rikeshi gamm ta Kara sakin kuka.... A hankali yake fitar da numfashi.... Sai kawai ta bashi tausayi lallai ya Kara tabbatar wa kansa da Bilkisu yarinya ce karama.... Tunda har ta kasa supporting kiss kuma hakan ya bashi tabbacin this is her first kiss.....
Tayi Mai isarta, har lokacin jikin ta rawa yakeyi..... Da ya motsa sai ta Kara rikeshi.... Ya danyi dariya.. ``` To ki sakeni na tashi ko?```
Tayi shiru,

```Bilkisu```

Ya Kira sunan ta a hankali,

.... Ta Kara fashewa da kuka ``` Dan Allah kayi hakuri```

..... Ya Kara dariya naji sakeni Dan Allah ai ba Kya so ko?

Ta daga Kai cikin jikin sa...

Okay Zan tashi na tafi sakeni....

Ta Dan sakeshi.... Yana motsawa ta koma da sauri .... Ya kyalkyace da dariya da ya gane ba tsoro kadai ke addabar ta ba hada kunya..... Ni Kuma yau tawa ta sameni ni *Hamza*...... Bazaki sakeni ba? To gyara mu yi kwanciyar mu anan.... Ta sakeshi da sauri tare da soke kai cikin kujera..... Ya Kara dariya.... Ba rakiya kenan?

Tayi shiru..... Ya kawo hannu ya taba ta, saki kuka tare da kankame jiki..... Ya Kara dariya ya ce tohm na siyo ma kaina rigima da kudina..... Ya zukunna gaban ta, Shikenan daina kukan Zan tafi Amma Dan Allah ki dauki waya idan na Kira matukar bakya son na maimaita kinji ko?...... Saura kadan ta wawuro fuskarsa ta cije don takaicin kalmar ```kinji ko```.

Ya saki ajiyar zuciya ya mike sai da safe I will miss you honestly..... Ya fita da sauri.

Tafi mintuna ashirin a wurin kafin ta tashi zaune.... Ta Dora hannu a Kai *Na shiga uku ni Bilkisu idan Haka ne halin Anwar na gama banuwa* Shi baya da kunya?

Ashe abinda nake karantawa da abinda malaman islamiya ke fada gaskiya ne?

Ta Mike jiri ya kwasheta, ta koma ta zauna.... Ikon Allah, ta kalli hannuwanta sai kakkarwa sukeyi, tsikar jikinta tashi Yarrrr tana tuno abubuwan da suka faru... Namiji???? Shi har wata dariya yakeyi... Ta zumburo baki tare da zabga uban tagumi.

Yana shiga sadeeq yaji kamshin turarensa ya canja gashi cikin wani yanayi na nishadi .... Ya bishi da kallo kawai Shi Kuma ya fada toilet ya sakar ma kansa shawa.......

Duk su Aisha sun shige sun kwanta, ta shige dakin itama Kai tsaye kewayen ta fada......

Ta na rungume da qur'ani kiransa ya shigo..... Taji wani dammmmm a kirji.

Ta dauka Amma samm ta kasa magana....

Kinyi wanka?

Tambayar ta bata haushi ta mishi banza.... Kinji?

Um, ta ce a hankali.

Kin kwanta ne Yanzu?

Tayi shiru......

Ya ce kinji?

Ta ce um,

Yayi murmushi, Baki ya mutu ne?

Tayi shiru.......

Ya ce huh?

Da kyar ta ce hmmm.

Ya danyi dariya.

Thank you so much Bilkisu, wallahi naji dadi sosai Zaki Sami Lada Mai tarin yawa kin San Haka?

Tayi shiru...kanta sunkuye kamar Yana kallonta wayar ma kunya take Bata.

Ya Kara dariya Wai Baki magana?... Ko muyi video call........ Nidai a'a..... Ya tuntsure da dariya to kiyi magana inji, kiss kawai ya rikitaki haka Ina ga..... Zan kwanta Dan Allah..... Ta fada kamar zatayi kuka ya kyalkyace da dariya..... Shikenan sleep tight sweetie.... Ta latse wayar da sauri kirjinta na bugawa ..... Ai shikenan Ni Kuma tawa ta sameni ta fada a hankali.

Ta Dade barci bai dauketa ba har kusan karfe uku da Rabi..... Shi yasa ta rasa lecture karfe bakwai don Bata tashi ba sai Tara saura.
....... Sadeeq ya kalleshi ya Bilkisu bata zo lecture ba?..... Ya danyi dariya kawai...
Ya bishi da kallon tuhuma.... Me ka Mata?.... Ya daga hannuwa yana dariya wallahi ban Mata komai ba kawai kiss ne ....... Ai nasan baka iya ba daddy mamaki Anwar Kuma yasan abinda ka je ya dawo Kan yarsa akanka yasa ya yanke wannan hukuncin...... Allah Ina iyawa.... Me yasa ka taba ta toh?
Ya galla mishi harara halan ni katako ne da Zan tsaya da Aure Ina kallon matata haka zikau ai ko Dan romance din a daga mun kafa ko?
.... Sanya ma Rai koshi ke kawo yunwa Anwar a haka, ahaka zaka je inda baka son zuwa Dan Allah Ina baka shawara ka tausaya ma yarinyar nan ka Bari akai maka ita...... Kuma duk ta tsorata jiya kaga yanda jikinta ke Bari?
Ai dole ta tsorata, bacin islamiya da sai ince anya tasan me ake ce ma Aure saboda yanayin yarinyar na bani mamaki...... Wallahi yarinya ce sadeeq nayi mamaki jiya ta kasa daukar kiss...... Mtseww ai ka yi sauri...

Shin Zan kiyaye ai dai na Dana.... Ya mishi gwalo... Ai Kuma ka Dano ma kanka ko? don na tabbatar Yanzu ka siyo rigima da kudin ka..... Wallahi
kuwa, ko agabanta na fada jiya..... Amma fa na kashe bakin rigima Zan Sami sauki saboda ta tsorata da Ni...... Ya ce hmm.
Yaki zuwa gidan ranar ta kashe wayar ta...
Ta ce ma su Aisha zatayi karatu ne daki Koda sun jita shiru.
Kwana daya , biyu har uku Bata shiga school ba. Taki kunna waya kuma.
Hankalin sa ya Fara tashi, ya Sami sadeeq ya fada mishi suna tare da Anas ya Dan kebe shi.
... Yarinyar nan fa taki kunna waya kaga kuma Bata zuwa class.. nasan za a rina Anwar ai ka Mata shigar kutse da ka bari da Yan dabaru da hikima sai ka shawo kanta amma Haka zikau ai Dole ta firgita..... Ya kamata ka fahimceni ya zaka biye Mata ka dauki taking side.... Ya fada a hasale... Na sani amma Ina kwatanta maka ne...... Naji nidai kaje ka lallasar mun ita don Allah Kuma in shaa Allah bazan Kuma ba tell her this please.
Shikenan....amma Zan Fara magana da ita ta waya tukun..... Kana da wani layin nata bayan Wanda ta rufe?
Through Aisha...... Okkkay.
Yayi sa'a kuwa suna tare zasu ci abinci...... Ungo sadeeq na magana ta Mika Mata wayar ......bayan sun gama gaisawa ya danyi kasa da murya Anwar din na tsaye sun Sanya handsfree..... Idan babu damuwa ki Dan ware muyi magana....
Batayi gardama ba .... Tana shiga daki ta zauna sai tace ...Ina ji.
Bilkisu nasan kina da hankali, nasan kina da ilimin addini, Ina so Dan Allah kiyi hakuri duk da abinda mijin ki yayi ba laifi bane wata kila hakan ya Sanya ki shiga wani Hali.... Sadeeq gaskiya Anwar na mun abinda bana so, da bakin sa ya ce zai ba daddy mamaki abinda ke tayar mun da hankali shine duk ranar da daddy yaji Ina Haka da Shi wallahi bazai taba yarda cewar ba ni na sanar dashi akwai Aure ba.
Ya kasa gane hakan..... Na sani Bilkisu, ya kalli Anwar kallon da ke nuna ```kaga abinda nake Gaya maka ko```...... Yaci gaba da cewa, kiyi hakuri ya mun alkawarin bazai Kuma ba..... Baya

iyawa, na Fara planning kawai Zan koma gida ne sai ya mun transfer kamar yarda ya..... Ya fizge wayar.... Billahil azim bazan Kara ba kiyi hakuri Bilkisu.
Tayi shiru Jin shine ya karbi wayar.... Yaci gaba da magana.... Wallahi nayi hakan don ki saki jiki dani ba Wai..... Shikenan ya wuce.
Yayi murmushi, na gode Dan Allah kizo lecture two kinji ko?
Shikenan. Ta fada.
Thank you...... Ta ajiye wayar kawai ba tare da ta karasa ji ba.
Ya kalli sadeeq Yana dariya yace, ta kasa Yi mun fada .... Murmushi kawai yayi ya barshi wurin ya koma gun Anas.......
Gaban ya Fadi ganin dalleliyar mota ajiye kirar Toyoto 2019 Fara.
Ita da Maryam suka fita, kamshi kawai ke tashi a motar .... Me yasa baku fadan ya kawo motar ba?...... Sadeeq yace muyi shiru Kar mu fada.
Ta ce hmmm kawai.
....... An kafsa fadan ne ko?
Murmushi kawai tayi cikin nikaf Mai sauti..... Daga nesa ya hango motar ya saki ajiyar zuciya ya shiga class Yana jiran isowarta.
Har ta zauna bata lura dashi ba wurin taga tsaye sai bayan da tagan Shi tsaye kusa da ita..... Matsa na zauna. Ya fada a dake!
Ta matsa Yana Zama ta ce.... Ina wuni.
........ Keni ba lafiya ba. Ya hau masifa, idan na Miki laifi I prefer ki mun duk tsiwar da Kika iya da fada amma bazan iya daukar this type of your punishment ba...haba. kwana uku? You switched off your phone, you skipped class, I believe ko zuwa nayi Zaki gudu daki ki kulle Haka akeyi ma miji horo?.... Nidai shikenan.... Ta fada a hankali..... Ba shikenan ba, wallahi idan Kika Kuma kashe wayar ki idan na Miki laifi zakiji ni baibai.... Sai kawai ya bata dariya ta duke tanayi...... Au dariya ma na baki ya balle bottle din rigarsa na sama ji kasusuwa kamar ba hakki na nabi ba?
Shikenan nidai..... Kiban hakuri Dan wallahi kin sani cikin damuwa fa..... Kayi hakuri ta fada tana murmushi cikin nikaf.... Cire nikaf din ya fizgeshi..... Fuskar ta mishi wani fayau, ta Dan dake saboda bata son a gane tana blushing.......... I missed my baby wallahi. Ya fada..... Zai Kara magana malamin ya shigo....
Yana gamawa ya fita ya koma bisa table ya zauna gabanta..... Kunyar ki tayi yawa Bilkisu.
Zaka Fara ko?
To ki kalleni Mana Wai sumke sumken na menene?
Ta danyi murmushi,
........ Jiya sadeeq ya rabawa Yan class din nan twenty thousand each though sun gane kudin daga wurina yake fa..... Kunyi kokari Allah ya Kara arziki Mai albarka, rigunan fa?
Na bayar ayi a kamfanina da ke Paris zasu fi kyau daga can ko kuwa?..... Karaf suka hada ido ya sakar Mata murmushi, ta danyi dariya ta mike ..... Ina zakije?
Ba tafiya zamuyi ba?
No! Ki jira nayo sallah yau muna nan sai dare...... Nima zanje masallaci....ya Dan kalleta Yana Yar dariya me zakiyo masallaci? Kuma Yanzu nayi magana kice zakiji kunya.....Hajiya ki jirani anan Ina dawowa Zan sallami kattin can ko kuwa?......
Dama ai Kai ka damu dasu..... Eh dole su kula dake ...ke din ce bazaki gane ba ya fita Yana kwance agogo.....

Ta bishi da kallo ta zauna ... Watau yasan bani sallah. Kai Anwar case ne...... Hajiya ke bazaki je sallah ba?
Ta sakar Mata murmushi habawa Helen....ai duk kallon ku nakeyi Yan class din Nan Yanzu kowa sai shareni yakeyi kunyi dai dai wallahi ...... Ba Dole ba, kina son Anwar ya sa a kashe mutum ko?.... Kisa Kuma Helen.... Yes ko mace baya so ya zo gurin ki bakiga guards din da suke binki... Mtsew forget about guards zasu hana abota ne?
Hmmm, Bilkisu you won't understand.
Ehe Bilkisu... Tayi kasa da murya is it true you both got married????
Who told you?.... Abeg .
Tayi murmushi yes is true amma ba'ayi bikin ba kawai an daura Aure ne...... Jesus..ta fada da karfi.
Bilkisu ta kyalkyace da dariya.
You are lucky Bilkisu.... Anwar ya bada mamaki..... And he is that young Nigerian billonaire Bushara... Bilkisu ta Kara kyalkyacewa da dariya Helen Zaki kasheni, Bilkisu you are lucky ooo he gave us 20k and our shirts and jacket will come soon free for everyone....... Hango shi sukayi Yana magana da guards ta mike da sauri please tell him I'm your friend too we will keep talking any time Sha.....ta wuce da sauri tana waigen ko ya taho..... Bilkisu ta duke tana kyalkyatar dariya har ya karaso ...... Ke da waye haka?
....... Ta rike ciki Helen..
Yayi murmushi tana Miki hauka ko? Jiya naso kina class din nan kiga hauka ni Dole na fita nabar sadeeq da shirmen su...
Ya figo Jakarta yamcici nasan ba Kya rabo da Malaki.... Ya Ciro short bread biscuit da bounty.
Ka fiye neman magana ta fizge jakar.
Ya harareta pad kike gudun kada na gani Kuma na ganta dai.
Ta danyi dariya kaiiiiiii Allah ya shirya ka.... Tare da ke da zuri'ar mu baki daya...... Ki ce Amin... Ta danyi murmushi na ce a zuci..... Ya sauko da hannun rigarsa da ya nade yana sanya links ....kin San jiya da daddare kamar Zan kurma ihu?
Ta dan kalleshi ta gefe... Yaci gaba da magana Yana murmushi.... Dana tuna kin kashe waya Kuma saboda ni sai naji kamar inta ihu ana jina a gari..... Ta danyi dariya .. kina yarda kike so ai.
Kayi hakuri ta fada tana murmushi.
...ai Dole in ma banyi ba nine masha wuya.
...... Anwar bana gane Alfa and bitas din ga na econometrics ... Ya danyi murmushi....Kuma basu da wuya fa.
Wannan drivation din ka ganshi.... Ya karbi littafin ya sauko kusa da ita ya Fara rubutu Kinga yanda yake......
A hankali a hankali yakeyi yanda zata gane.... Anwar marshene komai ya hada.
Duk inda ya shige Mata sai da yayi kokari yaga ta gane duk firar ta koma karatu hakan yasa ta saki jiki sosai shima kuma sai yaji dadi ganin ba wani sumke sumke ta saki jiki.
Ana Kiran magrib ya ce muje ki ajiyeni gida zanyi sallah masallacin unguwar mu. ... Shi yaja motar.
Tun daga ranar ya daina zuwa gidanta, abinci shike aikawa ana karbo mishi ko ta tafi dashi suci school, duk firar su a school sukeyi ya dake ya cije baya nuna zalamarsa fili.

Anayin hutu tare suka tafi Abuja Amma bai kwana ba ya koma Kano kwanan sa biyu yabar kasar......Koda aka koma school bai samu ya dawo ba, topic din sa na project ta email suka ringa communication da supervisor din sa, Bilkisu itama da akayi accepting nata ya ce ta tura mishi Shi ya ringa yo wa Yana turo Mata, ita Kuma da sadeeq suna tura mishi lecture da akayi. Wuni sukeyi video call, ko meeting yakeyi wani lokacin sai ya latsota,

Duk CA din da akayi Shi sai da yazo exam aka mishi,satin sa daya akayi hutu suka tafi da yake course shidda ne...... Abun ya Kara rikicewa saboda hutun sati daya ne, gashi final semester ga daddy yasanya bikin su bayan sun Gama da sati.

Anwar baya zama Nigeria ko kadan, ya Kuma hana su dady fita ko Ina Wai kada ayiwa Bilkisu soyayyar komai.... Shirye shirye ya kankama, sadeeq ma baya zaune.... Koda suka koma makaranta ita kadai ce, lectures sun ragu, course hudu sukeyi kacal, project kuwa Shi ke turo Mata,

Wannan da wuri ya dawo exams saura sati uku, yazo da jackets din su day shirts ko wane da size dinsa, jacket din dark blue da ratsin harsh anyi tambarin fudma ( logo ), kowa da sunan sa bayan rigar, sai white shirt ta yin signing da wando dark blue.

A bayan rigarsa an rubuta *Bushara* Bilkisu Kuma *Mrs Bushara* ya siyo Mata Tommy skirt dark blue Mai wasu irin flowers rose dark blue a jiki kana iya taba ko wace flower ya hadu iyakar haduwa..... Bai Bata ba sai ranar last paper yace ta saka da gyale ya yafe ..... Ga takalmi hills tayi kyau matuka..... Yazo da ledoji na i.v din su ko wace Leda da ticket da gate pass na tafiya bikin.... A ka dauko kattin speakers suna gamawa aka Fara ihu da kidi..... Bilkisu na fitowa Yana tsaye ya ware hannu ta rugo da gudu ta fada aka dau ihu...... Sun birge kowa, ya bude Mata gaban rigarsa ta rubuta *Mrs Bushara* shima ya rubuta Mata *Anwar* a tata sannan ya duka aka yi ta mishi rubutu.... Ita kuwa Mata kawai yace su rubuta kada shegen da ya taba mishi Mata .... Akayi ta dariya...

Nan aka Fara watsin lemuka, ana hotuna..... Anwar na makale da Bilkisu ya Fara watsin dollars.... Makaranta ta rude aka Fara wawaso..... Kawai ya hango mufeeda can ana niyyar danneta wurin kwasar kudi ya zunguri Bilkisu ya nuna Mata Yana murmushi.....ta karbi sauran dake hannun sa ta karasa kawai sai dai mufeeda taga an sunno Mata dumshin kudi...ta dago da sauri tana ganin Bilkisu sai kawai ta riketa tare da sakin kuka...... Duk ta ji tausayin ta. Mufeeda daina kuka Mana... Ta Mika Mata kudin kawai ta juya....

Bata ga Anwar ba, sai ta hangoshi can shida Suleiman Yana sunna mishi wani abu da alama kudi ne baya son kowa ya gani.... Tayi murmushi Bata karasa inda yake ba...... Yana murmushi yayi godiya. Amma ban fadawa mutuniyar ka tare zamu tafi ba .... Au haba.

Allah kuwa. Na ce Mata kawai zamu tafi da wasu Abuja yau saboda Shirin biki sauran tunda akwai ticket sa taho..... Ai kunyi kokari Allah yasa albarka da zuri'a dayyiba..... Amin Suleiman. Sai ku shiga mota idan sun karaso bana son muyi dare kasan rigimar Bilkisu..... Duk sukayi dariya. Jaka ta na daki ta Kaya...... Kayiwa murtala magana ya tafin maka da ita kawai can akwai kayanku..... Ya wuce yabarshi gurin ya nufi inda Bilkisu take.

Motocin sa suka shigo a guje school din... Bushara 1, Bushara 2........ Bushara 10.

Nan wuri ya Kara rikicewa....... Shi da Bilkisu mota daya, sadeeq da Anas mota daya, Suleiman da Ahmad motar su guda......... Suka fice garin duk sun bar mutane da magana a Baki........ Abuja tayi dauka Kuma za a Fara Shirin biki........ though daurin Aure a sokoto za a dauro Shi Amma duk programs din Abuja za'ayi ............😄✍🏼

*ZAINAB WOWO MAMAN ABDALLAH*💖💖💖.

*ALLAHUMMA LAA SAHLAN ILLA MAA JA'ALTAHU SAHLAN WA'ANTA TAJ'ALUL HAXNA IZAAHHH SHI'ITA SAHLAN...."* MU ringa karantawa saboda wannan annoba

Ayi hakuri jiya nayi laifi ban turo ba. Nace ayi addu'a😀
[3/30, 8:37 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
2️⃣9️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

👉🏽💞💕💕 *RUKAYYA BAKO DAN BATTA I love you so much, remember this always*🥰😍😘.

******************
*ABUJA NIGERIA*
Suna Isa daddy ya ce maza Anwar yazo Yana son ganin sa.....
Su biyu a falo daddy bisa kujera Shi Yana zaune a kasa, yayi yayi ya hau kujera amma ya ce hakan yayi..... Ba karamin dadi yakeji ba irin Respect da kunyar Anwar din duk rawar kansa idan Yana gaban daddy bai iya ko kwakkwaran motsi..
... Abinda yasa na kiraka anan Ina son mu tattauna wasu maganganu, na farko akan kayan dakin bilkiyne, Anwar bisa ga Al'ada irin tamu ta hausawa kasan cewa duk diya da Kuma iyayenta suna son suga abinda suka saka ma yarta a gidan auren ta Amma Kai kace sammm baka da bukata, shine muka yi shawara zamu tura maka kudi a madadin kayan...
Na biyu, ta fada mun ka ce lefenta sai taje gidan ka, wannan tsari ya Mana dadi matuka....
Na karshe kuwa da zance shine, programs din da zakuyi tayi yawa ka mayar dashi party daya kwal! Kuyi Shi a jibi don in shaa Allah Ranar juma'a Zan dauketa da kaina in kaita daki bana son duk wadannan bidi'o'in.... Ya dago Kai da sauri ya kalli dadyn suna hada ido ya sunkuyar da sauri.... Yayi Yar dariya Kano zaka ajiyeta ko nan sannan ka hadani da mutum daya Wanda zai mun jagora don juma'ar bacin Kai da na fadawa mahaifiyar ta kadai tasan wannan tsarin nawa.
Ya Kara kasa da Kai yace toh.... A Kano zamu Fara Zama in shaa Allah.
.......madallah. Ina ga shikenan kana iya tafiya.
Ya Dan sosai keya Yana son magana Yana Jin nauyi...... Yaya akwai wata magana ne Anwar?

Ya danyi murmushi.... Ranar juma'a din da karfe nawa?....... Ka turon Wanda zai mun jagora gobe don in shaa Allah anan zanyi sallar juma'a bayan na dawo kaita....... Ya dankara kasa da Kai tare da zaro ido..

Ya rusuna Allah ya Kara girma mun gode....ya Mike.

Ya kalleshi account number zaka bayar kenan?

Ya danyi murmushi ya koma ya zukunna, ayi mun aikin gafara daddy bazan karbi kudi ba, amma idan ko hankali bazai Sami natsuwa Kan hakan ba, to a turawa Bilkisu tunda daman ko kayan akayi mallakin ta ne fatana a Sanya Mana albarka a ciki addu'ar kadai ce zata fi duk wani kayan masarufi ko kudin quality...... Daddy ya kura mishi ido Yana jinjina tunani da hankali irin na Anwar.

Yana tafiya suka Fara shirye shiryen hada party don cewar Anwar sai fa anyi.

Abokan sa na kasashen waje duk sun iso masu kudin Nigeria kuwa abokan huldar sa wurin kasuwa kawai ake jonewa Amma duk wani sha'ani na yarinta da 'ya'yan su Anwar keyi sune abokan.....Amma wannan bikin sun Alkawarin halartar partyn da za ayi a national conference Hall dake presidency a cikin Villa.

An kayata wurin mawaka duk sun hallara hada yaron nan matashi Dan katsina Mai tashe Yanzu watau *Aliyu nata ( Aure martaba )*

Iyaye da abokan arziki sun hallara wurin, dangi da duk wani Mai alaka da bikin kowa ya kure adaka.....

An tsantsara ma Amarya kwalliya suna saman bene za a shirya ta aka shigo da wata matsiyacitar *Gown* maroon color *Innalillahi* bana iya describing rigar saboda rigace akalla idan zuwa zakayi shago ka siyo zata haura millions, duwatsun jikin rigar kansu diamond ne, musamman aka mishi ita special da wasu laces da materials Wanda ya ware don party kawai Amma Yanzu daya zata saka.....

Kilibabbu magulmata wadanda ba a rasa irin su a kowane dangi Baki yayi gummm, saboda suna ta korafin duk kudin Bushara bikin sa ba lefe...... sunfi awa shida wasu abokansa a waje cikin motoci suna jiran fitowar Amarya bayan shiga da rigar saboda ganin rigar yasa dole aka canza pattern na kwalliyar.

Tunda ta Fara saukowa ake daukarta hoto, gidan ya rikice,Yan sanda da sojoji gewaye da ita sunki yarda ma a rabeta...... Su mommy da kawayenta na babban falo ana fama da ita Kan zuwa wannan party Amma tace sammm baza ta je ba.

Suna hango fitowar su ya fito mota dasauri...... Ya Sha farar shadda ta karshen karshe Yana isa duk aka dare kawai ya rungume ta.....wuri ya dauki ihu kanka yane cikin gyale sai da suka shiga mota ya daga Shi ya leka....... Ya tallabo fuskar...... tsarki ya tabbata ga mahaliccin Bilkisu..... Ya Kai bakin sa ga nata tayi saurin fadawa jikin sa ta na murmushi..... Ya danyi dariya.... Ke wallahi dadi na dake Yar garin mu ce, ya dagota ba da yawa zanyi ba please......ta Kara komawa jikinsa..... Ya kyalkyace da dariya kaiii Ni Kuma tawa ta sameni daga ni kada ki batan Kaya da Jan Baki toh, nasan karamin aikin ki ne...... Yayi juyin duniya taki yarda ta dago don tasan halin sa tunda yace zaiyi kissing dinta sai fa yayi.....

Ya Kama dariya ya rungume a sosai, ga son jiki ga Kuma tsoro sai a daga ni tunda ba'a son tukuici.

Yana shafa bayanta Yana magana a hankali wallahi nasan rigarnan dole ta Miki kyau. Tunda wasu suka ji labarinta an Fara damuna..... Ya dago ta da karfi Kuma sarkar nan ta hau kayan

ko?
Sosai, ta fada tana murmushi.... Wuf!  Yakai bakin sa ga nata sai kawai ta tafi jikin sit luuuuu tayi baya.......
Tsayuwar motar yasa Shi sakinta a hankali, tayi kasa da Kai ya danyi dariya na shanye Jan baki ya kura Mata ido ta sunne Kai kawai....... Ya shafi gefen fuskar ta Yana murmushi *shy girl*
Wuri ya dauku, Shi kansa bai taba tunanin ganin wasu mutanen ba Amma sun mishi surprise.
Rike yake da hannunta suna tafiya a hankali Kota Ina Yan daukar hoto ne, abokan su na bakin kofa suna jiran isowar su.
Kawayen Bilkisu sun Sha Anko na light pink lace da blue head sun hadu sun Gama haduwa abinda ga fresh and young graduates.
Daga ciki wani sound na kidi ya Fara tashi kawai Anwar yaga Yan matan nan sun Fara rawa iri daya Nan da Nan wuri ya dauki ihu da sowa...... Rawa sukeyi ta birgewa Anwar nata dariya ya tallabo kugun Bilkisu ya Dan duka ya Mata rada hada chorography kuka hada haka?
Tayi murmushi kawai. Rawar sukeyi sosai har suka raka su mazauni Anwar na Zama ya janyo Bilkisu ta fada bisa cinyarsa lokacin da take kokarin Zama wurin ya Kara rikicewa......
Yan matan suka ja layi tare da canza salon rawa hall din yayi tsit kidan kawai ke tashi an masu kuri da ido ba Wanda ke son ko kiftawa yayi kada ayi wani step din ba gani ba.......
Wani juyi da sukayi kawai sai ga maza sun shigo cikin rawar , sadeeq, Suleiman, Anas, mustapha da su Joseph...... Wayyo Allah wuri ya Kara rikicewa da ihu ganin mazan sun dauki sabuwar tsarin rawar da Yan matan keyi suna juyi iri daya......ai sai turawan nan da sauran abokai da mutanen arziki suka Mike ana barin dollars.
Anwar ya Kara kyalkyacewa da dariya ya Mata rada a kunne keda wa kuka tsara haka? It's seems like you people are surprising me ...... Ta danyi dariya tun a school suka fara practice...... Ke me yasa bakiyi ba?
Ta Kara dariya Kai ma ai baka rawa.
Inji waye? Yau Zan yi.
Tayi murmushi Nima zanyi anjima zamu sake wata..... Keda wa?
Nida su Helen....... Irin waccen?
Ta danyi dariya waccen tafi wannan kyau saboda mu shida kawai zamuyi ta.... Banda ni ko?
Ta Dan duke tana dariya ai baka yi rehearsal ba....... Ina menu na program din?
Ka fiye sauri gashi can ga Mc sai ma can wajen karshe zamuyi fa...... Can't wait. Ya fada Yana kallonta yana murmushi......
Amma Suleiman ya birgeni Kuma yaban mamaki duk ustazancin sa yau Yana rawa haka?
Ta Kara murmusawa ko a school anyi ta mamaki.......
Ana gama rawar aka Fara gabatarwa, kaiii wurin an tara basawan Nigeria wani ma sunan sa kawai kakeji, su Aisha ne kirjin biki  ko Zama sun kasayi.
Komai order akayi abinci ma musamman akwai masu bayarwa , basket ake ajiyewa mutum bisa table din sa komai a ciki. Duk abinda kake so akwai a basket din....
A ka umurci Ango da Amarya su fito fili..... Masu wakokin kowa nayo gaba gaba..... Anwar ya ce a Bata *Aliyu nata* ya rera musu *Aure martaba*......
Ai ana cewa rangwal..... Anwar ya Fara takawa Bilkisu da mutane aka Fara dariya..... Kafin kace kwabo fili ba masaka tsinke ana masu barin nairori ...... Ya samu ya gewaya ya kamo hannun Bilkisu ya Mata rada ```Ke maza sunyi yawa muje ki zauna``` sai kawai ta Kama

dariya.... Kishin Anwar yayi yawa ranar bikin nasu ma?.
Ya kaita har inda suke zaune sannan ya sauko ya dawo filin...... Nan da nan su sadeeq suka far mishi...... Ya Kama dariya suka Kama rawa.....
*Nata* har tsalle yakeyi duk ya rikice ganin irin barin dollars din da akeyi.
Bayan an gama ne aka Fara cin abinci.
Bilkisu taga ice cream a table din su.... Ta kalleshi yayi dariya kowa abinda yake so ake bashi, Suma can duk basket din da Kika gani ba abinda babu ke kuwa ni nace akawo ice cream don nasan Shi kikafi kauna ...... Ta danyi dariya.
Ya dauko katuwar robar ya bude ya Fara Bata a Baki ..... Kai Anwar karshene..
Bayan an gama ciye ciyen, aka ce Amarya da kawayenta zasuyi rawa...... Anwar ya washe baki yau zanga rawar ki...... Ta kalleshi ta danyi murmushi kawai ta sauka....
Ya kishingida bisa kujera ya Dora yatsa a Baki ya bita da kallo....
Ita ce gaba, Aisha da Na'ilatu nasir bayanta, sai Helen, maryam da chinyere a karshen layi duk sun canza Kaya sun kaso jeans dark blue da white t-shirt sai farin kambas da dark blue facing cap.......
A hankali kidan ya Fara tashi Bilkisun ta Fara wani moves suna kallonta kafin Suma su dauka ....... Wuri ya dau tafi da ihu ganin yanayin daukar rawar kanta..... Ga Na'ilatu daman da son rawa kawar Bilkisu ce ta cikin unguwa tun suna Yara. Mowa na son takawa amma Aure ya Mata katanga don tabbas da wurin ya Kara bada kala.
Unex kuwa ai ita akwai kamewa tana can da kawayenta suna kallon kowa dai dai.
Alawiyya kuwa bayan kujeru ta tsaya tana murza kattan duwawukanta ana Mata nata barin dalolin daga gefe.
Dariya kawai Anwar keyi , turawan nan kuwa duk sun rikice an Gama kashesu da salo.
Wani juyi da sukayi cikin wata rawa ta duke Anwar bai San ya sauko ba ya balle rafar kudi. .... Wuri ya dauki ihu...gani Bilkisun ta canza salon rawa sun mayar dashi tsakiya suna wani takun..... So sai mutane suka karasa gigicewa kawai ya canyota da karfi ya rungume aka dauki ihu aka taso ana barin kudi........
Biki yayi biki.... Partyn ya bada kala.......live aka ringa nuna program din a tashoshin television na gida da waje.....
Sai Sha biyun dare aka gama..... Sai da suka tabbatar kowa ya tafi sannan suka shiga mota . Ya janyo ta jikinsa, waye ya koya Miki rawa haka?
Ta danyi dariya..... Bude Baki kiyi mun magana ko Kuma na yakai hannun bayanta zai zuge Mata zip din Riga...... Ya hakuri jira inyi magana... Ya kyalkyace da dariya kaiii kin fiye tsoro.
Daddy jiya ya aika da motoci na abinci na ce kada ya siyi komai Amma yaki yarda, Ni Ina da kamfanin shinkafa meye za a kai mun?
Ni ke shigowa da Mai Ina da kamfunan man gyada Amma..... Duk da Haka ai al'ada ce..... Al'ada addini ce?
Ni yaban ke tsingirin gatarin ki na tafi abina..... Ta danyi dariya.
Ya Kara matsawa kusa da ita ..... Ina son salo irin na daddy Bilkisu a gaskiya ya iya dattako da daukar ma Kai mutunci.... Ta ce hmmm kawai tare da Dan muskutawa don taja baya.... Ya Kara matsawa ya janyo ta ya Fara lalube...... Ta ce innalillahi na shiga..... Ke! Kin shiga ukun ko? Ke Wai kin San shiga uku kuwa?
Ta soke kai... Ya Kai Baki wurin kunnen ta ya ce ```please in zuge zip?```.... Ta ja baya da

sauri..... Kayi meye?
Nidai don Allah ka rufan asiri. Ta fada kamar zata mishi kuka .
Ta Riga ta Kai karshe bakin kofa ....ya Kara matsowa Yana Yar dariya to Wai ke gobe ya zamuyi anya bazaki bani wahala ba?....... Ta kudundune Kai ta ce *Na bani* ya kyalkyace da dariya yace ikon Allah.... Motar ta tsaya. Ta say hannu zata bude ya kamota jira Mana saurin me kikeyi?
Anwar nidai Zan tafi gida Dan Allah..... Na Fara Baki tsoron ko?
Tayi shiru. Yayi dariya..... Ya tallabo fuskarta ke ko Yar karar Nan ki kawon gudummuwar tsumi Nasha ko?..... Ta zaro ido.
Ya kyalkyace da dariya, amma dai kin San nasan su waye sokotawa ko?..... Kai Ni ban Sha komai ba..... Ya Kai hannu zai kamota ta makale jikin kofa..... Karya kikeyi kinsha Mana Dan Allah an dafa Miki kaza?...... Na shiga uku ni Bilkisu.... Ya kyalkyace da dariya... Nidai Dan Allah ki dauri kici Kisha kinji ko?....... Naji sai da safe.... Ya janyo ta da karfi ta fada jikinsa yace .... Yawwa kin yarda kenan nasan Kuna ci.
Ohh yau ni tawa ta sameni ni Bilkisu.... Ya kyalkyace da dariya kina birgeni wallahi.
Ya Kai Baki a kuncinta Bari ko nan na Dan sumbata...... Ta runtse ido, ya Dan Kara tattabata yana fadin, ai nayi namijin kokari Bilkisu na ba da mamaki shekara daya ban komai ba .....Hana ai wallahi ko ban nema ba ya kamata gobe ki nemeni da kanki ko? ya saketa.... Da sauri tabar motar yabita da dariya.....
Gabanta sai faduwa yakeyi ita kawai tasan ta Gama mutuwa taje gidan sa.
Washe gari ko ita bata San inda zasuje da daddy ba don baya son fada Mata kada ta Tara mishi jama'a da kuka.
A airport ta kura mishi ido Amma yasha mur babu fuskar tambaya.
Koda ta shiga jirgi ta fahimci abinda ke Shirin faruwa sai kawai ta Fara kuka..... Ashe tun kwana biyu da suka wuce an kai duk Wanda zaiga gidanta ya gano.
Tsinken ragin ta ya Kai daki....... Gidan ba kowa sai Mai gadi kadai, Shi kansa Anwar din bai sanar da kowa ba .
Kuka take wiwi....gidan Yana daddy tsoro ya firgita ainun yasan waye Anwar Amma zahiri gidan ya tayar mishi da hankali Shi kansa ya tabbatar diyarsa ta Gama Dace duniya.
Ya Mata nasihohi masu shiga jiki ya janyo Mata ayoyi da hadisai, kannen ta duka biyun suna gefe suna Yan kwalla Yanzu gida ya koma sai su daddy kadai saboda su Daman London suke karatu basa Zama Nigeria sosai.
Da zasu tafi ta rike su, ta na wani irin kuka.
Haka suka lallabata suka barta kwance bisa gado ji takeyi kamar zata mutu.
Anwar kuwa karfe Sha biyu ya Gama sallamar duk wasu Baki. Banda Aisha da Maryam saboda su daga Kano zai Sanya akai su gida.
Ana saukowa masallaci suka wuce Kano din .
Gidan su makil da jama'a ana wani sabon bidirin.
Kano ta Kai ta kawo unguwar ta cika makil....... Isowarshi yasa garin da unguwar Kara rikicewa..... Yayi ma Aunty Salma waya da Hajiya rukayya Bako da su zo su dauki Amarya a tafi da ita can cikin dangi.....
Har lokacin Bata daina kuka ba, bayan ta shirya sun fito kawai ta hango su Aisha Nan ne zuciyar ta, ta Dan saki.

Bai yarda ko da wasa ta ganshi ba.... Acan aka kaita inda Hajiya... Nan fa ta ringa ganin gata da tarairaya......karfe hudu su Aisha suka tafi ba tare da ta sani ba, ya masu Sha Tara ta arziki Maryam duk ta gigice hada kukanta.
Karfe takwas aka shirya wata kwarya kwaryan dinner wacce har taso tafi ta Abuja danginsa sun yi namijin kokari.
Sai basarwa yakeyi, ita abun ma sai ya ringa Bata mamaki ganin bai waccen zakewar ko me yasa yake ma Yan Kano Isa da takama?.
Sha daya nayi yace a tashi haka dare yayi.
Suna fitowa ya shige mota da Amarya sukayi gida kawai......
Hannunsa da nashi rike maimakon taga sunyi bangarenta Wanda aka kaita dazun sai taga yayi nashi da ita.
Gabanta ya bada ras!
Suna shiga falon farko ya saki hannunta ya garkame kofa ya zare key ya kalleta muje sama ko?............✍🏼😄

Ayi hakuri da kadan jiya biki nayi na babban Abokina, aminina Kuma kanina sannan dan'uwana.
Ayi masu fatan Alkhairi please.
*ibrahim and naja'atu*

*Zainab wowo ce kawar rukayya Bako danbatta ( Allah ya raya Miki sauda da Salma ya Sanya masu albarka amin*💖
[3/31, 11:01 AM] +234 706 188 4461: 🤐 *WA ZAI FURTA?*🤐
3️⃣0️⃣

*Tukuici ne ga Aunty Rabi ( Hajia Rabi badawi Kano maman Ibrahim ), Allah ya Kara arziki ya shirya Miki zuri'a ya Kara Miki tsawon kwana. Amin.*

*KINA RAINA MAMAN WEEDAD*

*Domin ki...... beloved sister Khadija Dahiru wowo miji na gari I pray*

👉🏽💞💕💕 *MOM SAUDA AND SALMA I love you so much, remember this always*🥰😍😘.

*NA SADAUKAR DA LABARIN WA ZAI FURTA GA DUKKAN FANS DINA MASU SON LABARIN WADANDA KE GROUPS DA WADANDA BASA CIKI AMMA SUNA KARANTAWA*

******************
*KANO NIGERIA*
....... Ya dan yamutsa fuska ya rike hannunta suka Fara tafiya a hankali, yana Jin yanda hannun nata ke karkarwa tana kyarma.
..... Suna hawa step daya , biyu ya runtse ido ya saketa da sauri ya duka tare da dafe ciki .....Bilkisu cikina.

Ta zaro ido da sauri cikin tsoro saboda tun a party taga yanayin sa duk ya canza, ta Dan duka itama tana leken sa cikin ke ciwo?
Ya daga Mata Kai da kyar.... Innalillahi ta fada tare da kamoshi suka Mike...... Tafiya sukeyi da kyar da kyar, ya Dan kalleta Ina Jin yunwa ce Bilkisu rabona da abinci tun jiya da safe...... Subhanallah ta fada a hankali.
........... Katon daki ne yasha kayan alatu, makeken gado da wordrop ga wasu irin kujeru a gefe babu tarkace a dakin amma ya tsaru da kayan kece raini.
Ga mamakin ta an jera kayan ciye cite bisa kafet din.....ya tafi luuuuu ta Kara taro Shi tare da fadin *Na shiga uku* da karfi.
Suka Fadi rikichaaa bisa carpet din saboda Bata da karfi ko kadan...... Ya riketa gammm idanun sa rufe *Bilkisu cikina*.... ..Anwar ko dai a Kira sadeeq muje asibiti.... Kiban abincin sa naci Dan Allah ya nuna wurin da hannu.
Da sauri ta janyo dan table din da suke sama.... Ya Kara dafe ciki Fara bani something liquid please...... Ta dauko robar fresh milk Mai sanyi ta Mika mishi ya kafa Kai ya shanye, ta bude wani glass bowl sai ga dambun naman kaji ta Mika mishi ga dambu kaci....na koshi. Ta zaro ido Dan Allah kaci Anwar tunda har ka gano matsalar ka yunwa ce... Bazan ci ba ya fada da sauri..... Saboda me?
Saboda ke bakici ba .... Zanci kaci tukun...... Bazan ci ba sai kinci.
Zata Kara magana ya ce Miko madarar, ta Miko da sauri tunanin ta sai Kara ne, ya ce okay shanye duka sai ki ban naman.
Tayi shiruuuu, ya Dan kalleta mayar idan bakyaci duk mayar dasu...... A'a Zan sha ta kafa Kai..... Itama kusan abincin rabonta dashi tun jiyan.
Tana ajiyewa ya tura Mata naman ci sannan yasha mur Yana yamutsa fuska...... Tayi shiruuuu...... Kawai ya Mike da gudu yayi toilet ta jiyo Yana kakarin amai.... Hankalin ta ya tashi matuka lallai Anwar baya lafiya ta mike tsaye ta kura ma kofar ido...

Ya fito Yana layi ta karasa da sauri ta rikoshi sannu ko dai za a je hospital Anwar??...... Matsalata yunwa ce Dana ci shikenan kinsan ni bana wasa da abinci.... Na sani ta fada tana kamashi lokacin da zai zauna.... Ta tura mishi naman kaci Dan Allah ....... Wallahi bazan ci ba sai kinci ke meye Kika ci?
Meye acikin can?
Ya nuna cooler ta janyo da sauri ta bude..... Peppé soup ne okay zuban acan, ya nuna plate..ya dafe ciki tare da dukewa Yana matse ido.
Ta dauko duk ta gigice ta zuba tana gamawa har lokacin bai dago ba, ya ce maza shanye ki zuban nawa a ciki...
Ba yarda ta iya saboda tasan Anwar da kafiya, itama yunwar duk ta addabeta ba yanda ta iya ne, Dole ta dage sai gashi ta shanye tas!, Ta zuba mishi ta mika mishi, ya dan kalleta ya ce kafin na gama kici dambun nima Ina son cin sa.... Shima ta janyo ta Fara tsakura........ Haka haka sai ga Bilkisu tayi Nat! Hada uwar gyatsa.
Shi kuwa Wanda ta zuban ya turo ya ce bai iyaci ya kwanta Yana murkususu....... Ta karaso da sauru kamar zatayi kuka .....Anwar ko dai muje asibiti.... Karki damu da nayi barci shikenan.... Ya Dan gyara ya kwanta ruf da ciki ya juya kawai.
Ta zabga tagumi kawai sai Kuma ta Fara kwallah. Yana jinta tana ta sharbe..... A hankali taji

Yana saukar numfashi alamar yayi barci, ta Kura mishi ido.... A hankali barci ke neman daukarta itama, ta Fara gyangyandi....... Barawo Bata San ya sace ta ba .... Yana kwance yaji alamar hannunta.... Ya Dan juyo sai kawai yaga ta yi barci....... Ya danyi dariya ya tashi zaune...... Duk plan ne yayi don baisan ta Ina zai tarbo rigimarta ba.
Ya janye kayan ya koma gefe ya zuba ya cika cikin sa ya cire kayan say ya watso ruwa ... Yayi tsaye kanta Yana zullumin Allah yasa idan ya tabata kada ta tashi.
Sai da ya tabbatar ya gama komai ya kashe fitila sannan ya zukunna ya sungumeta a hankali a jiye bisa gado, ta saki ajiyar zuciya tare da gyara kwanciya barcin ya riga ya dauketa.....ya rage sanyin A.C saboda dakin yayi sanyi da yawa ya Kai hannu a hankali ya Fara cire mata jewelries dinta ..... Yaci gaba da zuge zip......... A firgice ta bude ido.....amma Ina is too late to cry... Zata kurma mishi ihu ya yi saurin rufe bakin da nasa..... Ta rasa inda zata sa kanta....ya riga ya cimmata.... Wasu zafafan hawaye kawai ke fita.............
Ya saki ajiyar zuciya a hankali ya Kara rungumeta a kirji ya lumshe ido ya kasa magana baya iya cewa komai..... Tayi tayi ta tureshi ta kasa ya riketa gammm. Ta Kara sakin kuka ta sunne Kai jikinsa, duk jikin ta yayi tsami....... Yaja blanket ya rufe su..... Ajiyar zuciya kawai takeyi Shi kuwa ya rasa abin yi duk ya gama kidimewa ya kasa kwakkwaran motsi..... Zuwa can yaji ta Fara sakin numfashi a hankali alamar tayi barci....ya Kara mannata jikinsa kirjinsa na harbawa a hankali..... Shikam cikin kunnensa aka Kira sallah..... Ya zame a hankali ya fada toilet.
Kasa zuwa masallaci yayi. Ya saka jallabiya Mai karamin hannu ya feffesa turaruka ya shiga wani daki ya fito da doguwar Riga, pant, bra da under skirt ya ajiye Mata bisa abun sallah..... ya koma gadon ya shige bargo ya Kara janyota jikinsa......
Barci Mai nauyi yayi awon gaba dashi.
Tafi mintuna goma da farkawa..... Tayi shiruuuu ta tabbatar da lallai barci yakeyi ta zame jikinta a hankali ta sauka gadon, tayi toilet da sauri.....  Tana shiga ta zukunna ta Kara sakin kuka.... Sai da tayi Mai isarta sannan ta fada cikin kwami.
Ba wani extra towel Dole Wanda yayi amfani dashi ta daura.
Ta leko a hankali har lokacin barci yakeyi ta sadado ta dauki kayan da ta hango ta koma da sauri....
A toilet din ta shirya, ta fito. Tana cikin yin sallah ya farka...... Lokacin da ta sallame taji motsinsa sai kawai ta koma tayi sujada Bata Kara dagowa ba.......  Ya kyalkyace da dariya ya taso.
Tana Jin Yana yowa inda take sai kawai ta Fara kuka......
Ya sungumeta yayi bisa gado Yana fadin ai na Sami Baki yanzu Zan bada hakuri wannan laifi Dana tabka....... Ta sunne Kai.
Ya dagota Bilkisu Allah yayi Miki albarka ya sa daddy da mommy aljannah firdausi... Hakika sun Baki tarbiyya Mai kyau a rayuwa.
Ya rungumeta kiyi hakuri wannan Shi ake Kira *Aure* Kuma wannan kadai zai tabbatar Miki da *how much I love you* kinji ko?
Ta yi shiru.....
Lafiyata Lau jiya Yar dabara nayi ki Samu kici abinci saboda na tabbatar bana iya kyaleki jiya Kam .....
Zo muje ya figi hannunta...... Tafiya sukeyi bayan gidan suka zagaya can...... Sai gasu sashen Hajiya.... Tayi saurin janye hannunta... Yayi dariya kunya kikeji?
Idan Kika ringa wannan sum sum din Zaki to nawa kanki asiri ace jiya..... Ta Kai mishi duka dai

dai hajiyar na fitowa.... Ya buga tsalle Yana dariya... Hajiya ta washe Baki...... Bilkisu mijin ake duka?
Ta kusa Suma don kunya ta zukunna da sauri ta ce *Ina kwana*
Ta yi Yar dariya lafiya Lau kuxo ga break din can......
Sai kusan azahar suka bar sashen ta dan sake kadan....
Suna shiga ya rikota zo ki gani..... Yabi da ita wani corridor suka shiga wani falo ya ce nan ma naki ne fa, ya bude bedroom din sai ga wasu irin set na gado royal masu kyau gefe jakun Kuna ne set talatin da shidda ya ce ga lefen ki Zaki gani Yanzu ko ba Yanzu ba?
Ta sunne Kai jikin sa kawai.... Ya danyi dariya *Bilkisu kunya*...............
Ya kamota ya zauna a kujera ita Kuma tana bisa cinyarsa.
Gaskiya kin saka ni farinciki Bilkisu naji dadi jiya har mutuwa nayi na dawo..... Bata San lokacin da ta kyalkyace da dariya ba .... Shima ya Kama dariyar ya ce Allah kinji nayi magana? Ai kasawa nayi.
... Next week zamu tafi Dubai a can zamu zauna Ina da gida a can, sadeeq zai ringa taking care na business din Nigeria tare da taimakon su Suleiman...... Ni Kuma Zan ci gaba da duba na sauran countries din nida su Alhaji murtala..... Kina son Zama Dubai?
Ta danyi murmushi ta ce um.Daga nan Zaki dauki Yan aiki ko kina son na can?
Duk yanda ka gani.... Yayi murmushi.
Zan baki appointment idan result ya fito kema kina amsar albashi kin San hausawa na cewa *Da namu gwamma da nawa* ya karasa maganar Yana dariya.... Kin San duk wakokin bikin Nan nafi son wakokin da *Aliyu nata* yayi Mana?
Ta danyi dariya gaskiya ya iya Waka, ya ce sosai ga babu zagi, ba habaici babu maganar banza yaron ya zo da basira Mai tsafta Shi yasa ake rububinsa..........
Ya Dan taba cikin ta Allah yasa jiya Yara sun shiga...... Ta soke Kai jikinsa..... Ya kyalkyace da dariya.............✍🏼

*KARSHE*

Allah ya bada zaman lafiya da zuri'a dayyiba.
Muna rokon Allah ya karemu daga cututtukan zamani.
Abinda muka karanta Allah yasa mu amfana da lesson din ciki na Shi mutunci Riga ne, ya kamata mu sani kunya na daya daga cikin abinda ke daga darajar mace a duk inda take. Kwadayi baya Kai mutum ko Ina sai tushen wulakanci da Kuma nadama.
Mai kudi da talaka duk bayin Allah ne, masu kuci da ke nuna Basu iya rayuwa tare da talakawa ku sani rayuwar dasu bazai rage ku da komai ba sai dai na ku Kara samun daukaka, mutuncin ku zai karu, zaku Sami lada a wurin Allah. Akwai fa'idoji da dama masu amfani akan Haka. ..... Abinda na hakake a labari shine Jan labari ba shine ba, matukar sakon da kake son isarwa zai je to a layi biyu ma ya wadatar...... Kadan Mai albarka yafi Mai yawa yuyuyu.
Rubuta batsa, maganganun banza da rashin kunya ga labari ba shine ke kawo wa mutane kwarjini ga labari ba. Ma'anar labarin , tsabtar sa da Kuma kyautata rubutu saboda Allah. Duk abinda muka rubuta zamuyi depending din sa a wurin Allah. Ya Allah kada ka kamamu da laifin da mukayi bisa ga tunanin munyi da kyakkyawar niyya. Allah ka yafe Mana ka shirya Mana zuri'a.

Qalubale ga itaye, ku daina tura yaran ku makaranta ba tare da binciken abinda sukeyi ba, ku ringa Kai masu ziyarar bazata Kuna saka ido ga yaranku musamman mata, mazan ma abin kula ne Yanzu.

Yan Mata ku sani bin namiji ka nuna kana sonshi bance haramun bane Amma ku sani kunya ma cikon Imani ce, duk abinda musulunci yazo dashi muna daukarshi da muhimmanci .

Allah ya sada mu da alkhairi.

Wanda labarin bai mawa ba sai yayi hakuri.

Sai mun hadu a wani sabon labarin bayan sallah idan Allah ya kaimu.

*Zainab wowo*💖

*MAMAN AL'AMYN, AMINATU AND ABDALLAH*